

Esquire
LBV makeovers
NI DA ABOKIN
BABA NA

# NI DA ABOKIN BABA NA

A nutse nayi sallama dakin Daddy na, dakin a shimfide yake da tattausan carpet sakar hannu kirar kasar India, ruwan hanta ne kamar yadda jeren kayan dakin suke.A hankali na zauna a kusa dashi ina kallon yadda yake sarrafa laptop dake hannunshi cikin kwarewa, ganin bashi da niyar dawo da hankalinshi gare ni, dama dai nasan halin baba in dai yana aiki baya maida hankalinshi ga kowa har ni er gaban goshin shi kuwa har sai ya gama. Remote na dauka na canza channel daga sports zuwa Zee World. Na ma manta ranar suna shirin da nake nacin kallo, Love Look Like What You Made Me Do.Dan Murmushi nayi nace woah, ni na ma manta da shirin nan. Daddy ya dan yi glancing din wajen da nake zaune ya kafin ya maida hankalinshi ga laptop dinshi. A takaice har aka gama shirin suka fara tallace-tallace Daddy bai gama abinda yake yi ba. Ba a jima ba naji na fara hamma, remote na dauka na mayar mishi da tashar da yake kallo na mike, daidai lokacin daya rufe laptop din

nashi ya kalle ni cike da kulawa. "Uwata, ya aka yi ne?" sunan mahaifiyar shi gare ni shi yasa yake kirana da Uwata, su Mommy kam Ummi suke ce min. Baki na turo cikin dan jin haushi nace "ni barci nake ji..... Sai da safe!" er dariya yayi ya kamo hannuna ya rike ya janyo ni na koma kusa dashi na zauna ina kara tura baki na. Kumatu na ya dan ja, "ohhh m soooo sorry princess, na tsaida ki koh? Akwai muhimman bayanai dana tura ne yanzun shi yasa, ayi hakuri. Gobe zamu je mu sha ice cream ni da princess dina, are we good now?" kaina na kawar daga kallonshi, yasa hannu ya juyo da fuskata zuwa gare shi, "hey, m trying to pay for what I did, aren't we good yet?" bansan lokacin dana yi er dariya ba ganin yadda yayi da fuskarshi, Ina son babana fiye da tunaninku saboda yana sona sosai, kaunar da yake min ko mahaifiyar data haife ni bata nuna min kwatankwacinta. Ban sani ba ko don hakan yana da nasaba da cewa ni Kadai ce diyar su??. Kai na girgiza ina dan murmushi, "naji na hakura, but we will also go for shopping, agree??" ya gyada kai, yes. Tashi tsaye nayi

nace to sai da safe Daddy. Murmushi yayi, ki tashi lafiya Uwata.

A main parlour naci karo da Mummy, da alamun turaka zata tafi ganin yadda taci kwalliya, ba wai ta fuska ba, ta jiki sai tashin kamshi take. Murmushi nayi naje na rungumeta, "Mommy sai da safe!" bayana ta dan shafa, "OK, sweet dreams baby" ta sake ni ni na wuce dakina ita kuma ta tsaya tana kashe wutar falon.

Ina shiga dakina wuta na kunna na shiga zare kayan jikina daya bayan daya, towel na zara na daura a jikina na fada toilet din dake manne a dakina. Cikin bathtub na shiga na zauna bayan na tara ruwa mai dumi, ban jima a ciki ba na fito. A cikin toilet nayi shafe shafen da zanyi, na fito. Kayan barci na saka marasa nauyi, kayan dana bari a tsakar daki na tsince na watsa cikin kwandon da nake tara kayan datti don nasan idan na bari Mommy ta gani gobe sai raina ya baci. Mommy mace ce mai tsabta da bata jurar kazanta ko ta anini. Kan katoton gadona nayi tsalle na haye kamar wata karamar yarinya,

wayana na cire daga jikin socket na kunna data, social media na shiga na fara chat da friends dina. Ban samu barci ya dauke ni ba sai wajen karfe goma sha biyu na dare. Ban jima da fara barci ba na naji numfashi ya fara min wahalar shaka, rigar jikina na fara adjusting daga jikina, ji nake kamar ita ta shake min wuya na kasa numfashi. Daga karshe tashi nayi gabadaya na cire rigar na jefar kasan gado na koma na kwanta. Dama don dole nake saka riga idan zan kwanta saboda fadan Mommy, ban cika kwanciya da riga a jikina ba saboda a yawancin lokuta na kan ji kamar rigar na shake ni ne, ban sani ba hakan sabo ne ko kuwa hali ne ko cuta? Ban sani ba, n I don't give a damn akan lallai sai na sani.

☆☆☆☆☆

Kiran sallar asubahi a cikin kunnena da yake masallacin unguwar mu a jikin gidanmu yake. Na saki gurnani a hankali saboda barcin daya cika min ido, da kyar na samu na iya bude idanuna suna komawa suna rufewa, na dauki kusan mintuna biyar kafin na iya tashi zaune,

gashin kaina daya tattare ya barbaje min a fuska na tattara na maida shi baya, a hankali iska ya shiga kada sassan jikina hakan ya ankarar dani yanayin da nake ciki na babu riga, da sauri na dira daga kan gadon na dauki rigata na saka. Daidai lokacin Mommy ta leko, ganina a tsaye yasa ta maida kofar ta rufe ba tare da ta min magana ba. Sighing na danyi softly cike da jindadin bata kama ni ba. Bandaki na fada direct na dauro alwala, nazo nayi sallah na zauna Ina lazumi har sai da gari ya danyi haske, tashi nayi na fita daga dakina. Sai dana je na gaida Daddy sannan na shiga kicin inda na samu Mommy da Mama Sauda wadda take taya ta en aikace-aikace suna ta kokarin hada break fast, a nutse na gaida su sannan nima naje na kama musu.

Muna gamawa na koma daki nayi wanka na fito, na bata lokacina sosai wajen fente fuskata da nau'in kayan kwalliya Kala-kala kamar wadda zata je biki. Sai dana gamsu da kwalliyar fuskata sannan na tashi na bude wardrobe dina wadda take shake da kaya kamar na mutane biyar ko fi. A hankali nake kare musu kallo har

idanuna ya sauka akan wata atamfa cote d'voire ruwan coffee wadda aka mata zane da peach da yellow a jiki, dinkin riga da siket ne. Siket din pencil ne sai rigar doguwa don ta kusa kai kin gwiwa, ita kuma dinkin ya kama ni cif daga kirjina, daga uku ne ya saki sosai yayi baza. Ina gama saka kayan nayi simple daurin dan kwali, na dauko gyale mai dan fadi peach color da er karamar jakar vincci na rataya na fita bayan na dauki wayar hannuna da takalmi coffee color mai dan tudu. Akan dinning na samu Mommy da daddy har sun fara karyawa, duka kallona suka yi ganin yadda naci kwalliya cike da alamun tambaya. Kujera naja na zauna a kusa da daddy ina kallonsu, "School zan shiga in amso IT letter na daddy"daddy ya gyada kai yaci gaba da cin kosan shi yana korawa da kunun gyada mai gardi, nima kunun gyadar na tsiyaya a cup na bude nadarar peak na kara a ciki na fara sha. A nutse muka gama cin abincin, na tashi na dauki jakata tare da yafa gyalena Ina kallonsu, "Mom, Dad, zan wuce sai na dawo" mom tace Allah ya kiyaye, daddy yace "ko dai in sa driver ya kaiki tunda ba jimawa zaki yi ba?" kai na girgiza, noo daddy,

zan bi bus kawai. Ya gyada kai, "kudi pa?" nan ma kai na girgiza, "I've enough money wit me daddy" nan ma kai ya gyada, "OK, take care baby" Murmushi nayi na juya na fita cike da jindadin yadda iyayena suke kulawa dani, ta kowane fanni ni kam sai dai in godewa Allah daya bani iyaye kamar su.

Bus na hau directly har kofar gate dinKadPoly inda anan nake karatun Diploma na akan Science Lab Tech. Kasancewar an tafi hutu makarantar babu mutane sai tsilli-tsillin wadanda basu tafi hutu ba kawai, a hankali nake takawa har cikin ofishin IT coordinator namu na karbi IT letter na na fita. Hostel din mata na wuce daga can dakin kawata Ramla don nasan bata tafi hutu ba, ila kuwa, Ina sallama cikin dakinsu muka ci karo da juna. Cike da doki muka rungumi juna muna juyi a tsakar dakin kafin daga karshe muka dire a Kan gadonta muna dariya. Kallona tayi tun daga sama har kasa har sama, ta gyada kai tana er dariya, "inye diyar daddynta! Wannan fresh haka kamar wadda aka wanke da inji?" duka na kai mata a cinya Ina dariya, "ke ba baki da mutunci Ramla, duk uban kashin wannan dana tara a

wuya zaki ce wai nayi fresh?" sai da muka gama shakiyancinmu na abokai sannan na kalleta, "ke ni ba wannan ba, ya zancen inda zamu je muyi IT ne don ban karbi letter na da wuri ba ban sani ba cikin wajajen da suka bamu ko zan samu?" Ta girgiza kai, "duk an cika a wajen pa gaskiya babu, nima tun last week na kai nawa suka ce wae an cika" fuskata ta dan yamutse, "lallai! Ya zanyi kenan?" kafada ta daga, "oho! Bake wae dadi gida ba kinje kin zauna kina hutu ba? Gashi next week zamu fara. Ni a Kano zanyi nawa" na kalleta "Kano? A Ina??""cikin BUK, kin san Aunty Habi tana aiki da Lab dinsu, shine tace in je can inyi kawai. Har an kai letter sunyi accepting. Abinda ya shigo dani makarantar kenan na kawo accepting letter din" shiru nayi ina jijjiga kai, "Ramla ko dai nima can zanje inyi nawa IT din kawai? Nasan mawuyaci ne in samu waje anan" ta kalleni, "wa kike dashi a Kano?" nace oho! Daddy yana da mutane da dama acan, nasan ba za a rasa ba. Idan can dinne sai in dinga zuwa weekend gida..... Zan tambayi daddy inji dai tukun. Yaushe zaki tafi Kanon?""ranar assabar kila" ta bani amsa. Na gyada kai kawai. Kayanta na

tayata hadawa, tare muka fito da ita na janyo mata trolley ita kuma tana jan karamar jaka. Muna tafe muna hira da ita har bakin gate, anan muka ci karo dashi, My Crush!. Wata irin farinciki da murna suka rufe ni, Ya Allah ji nayi kamar in daka tsalle. Ta gaban mu ya wuce without glancing at us, duk yadda naso in daure kasawa nayi, ban san lokacin dana kira shi ba. "Muneer!!" cikin wata iriyar murya mai kama da whisper, duk da haka sai daya dakata da tafiyar da yake yi ya juyo ya kalleni, Kai na sadda kasa ina jin wasu irin abubuwa na min yawo a jiki. Cikin siririyar muryar shi da zan iya cewa ita tafi daukar hankalina game dashi yace, "ohh Ummie, ya kike?" Murmushi na saki a hankali kaina a kasa, nace "lafiya qalau, ya karatu?""Lau..." ya amsa, "....bari in wuce sai anjima..... By the way, I like ur dressing" bin shi nayi da kallo yana tafiya a nutse ina wani irin murmushi kamar kumatuna zasu hade da kunnuwana. Sai dana daina ganin kurar shi sannan na maida Kallona ga Ramlah wadda ta coge a gefe tana jifana da harara, murmushi kawai nayi tare da daga mata kafada naja trolley din nayi gaba. Tsaki taja ta biyo bayana, "wallah

Tallahi Babe kina bashi haushi a rayuwa akan Muneer dinnan, kin rabe wa namiji yana yazga ki. Yanzu kaf fadin KadPoly waye bai san cewa kina crushing din wannan player din ba, abun haushi ma da alamun baya yi dake!" fuska na hade sosai. Abinda ke hada ni da ita kenan, kushe Muneer. Bata damu da yadda na hade fuska ba taci gaba, "haba babe, ki daina bayar damu mana. There r so many guys out there ciki da wajen makarantar nan dake karakaina akan ki, don Allah ki kyale wancan yaron. Ba son ki yake yi ba!" a fusace na kalleta, "yeah right! Ai dama ban ce miki yana so na ba koh? Hakan bai dame ni ba, inda rai da rabo, zan ci gaba da bibiyarshi kuma har sai ya so ni Ramlah! Idan hakan yana bata miki rai ki kauda idanun ki daga gare mu, dats all" Kallona ta tsaya tana yi kawai, ba wai yau muka saba irin wannan musun ba in dai akan Muneer ne, Kai ta girgiza a hankali tare da furta Allah ya ganar dake! Cikin gatse na amsa da Ameeen. Muka ci gaba da tafiya har bakin gate ba tare da kowa ya sake cewa komi ba, dama zuciya ce ta kowa a wuya, magana kadan sai ta tunzura mu. Muna fita bakin gate kowa yayi nashi bangaren, ita

ta hau motar Abuja ni kuma na dau drop din tricycle har Unguwar Rimi.

Lokacin dana isa gida karfe sha biyu na rana bata karasa ba, kayan jikina na cire na saka na shan iska marasa nauyi na tafi kicin. Tare da Mommy muka hada abincin rana, ta shiryawa daddy nashi a cikin wani katon Basket mai kyau har da wani kayata shi da roses. Wannan Al'adar tunda na tashi naga Mommy tana yin ta, Indai daddy yana gari to abincin shi daga gida ake kai mishi, ba zan boye ba, abin yana burge ni, ina da niyar yin wannan Al'adar idan nayi aure. Direba ta ba ya kai mishi ofishin kula da harkar shigi da ficin jirage ta jahar Kaduna inda anan ne yake aiki a matsayin President na wajen. Ni kam sallah nayi sannan na fito dinning din, tuwon semovita ne muka yi da miyar danyen kubewa wadda ta sha busasshen kifi da tantakwashi da man shanu sai tashin kamshi take yi, sai zobo mai sanyi Shina anyi decorating dinshi da fruits. Muna hira da Mommy jefi jefi muna cin abincin na gaya mata yadda muka yi da Ramlah game da IT dina, shiru tayi tana

Kallona kafin tace "zaki iya kuwa Ummi?" er dariya nayi, "haba Mom! It's not like ban taba zaman Kanon nan bane. I will b fine, after all anan zan dinga yin weekend dina ai" kai ta gyada, "sai ki jira daddyn ki ya dawo".

Koda na fadawa daddy abinda ake ciki ya dan nuna damuwarshi akan gida da zan bari, yace "Uwata tafiya zaki yi ki barmu mu biyu ne a cikin gidan nan kamar mayu?" ni kaina kuma sai a lokacin naji jikina ya fara sanyi, a sanyaye nace to daddy ko dai zan bari ne sai shekara mai zuwa sai inje? dariya suka saki shi da Mommy, daddy yace "oh ma silly princess! M not that wicked da zan hana ki karatun ki, bari in kira Dr. Ibrahim abokina ne, lecturing yake yi a BUK sai muji yadda za ayi" muna zaune ya kira shi suka gama magana suka yi sallama, "wai yace zaki samu sai dai a
microbiology lab din su" Murmushi nayi, "daddy kasan fa dama nace maka idan na gama wannan program din zan nemi microbiology a ABU" yace faduwa tazo daidai da zama kenan? Na gyada kaina Ina Murmushi. Yace

gobe zan tura mishi letter din sai a kai, Allah sarki princess dina zan yi kewar ki!.

Da dare kuwa kamar yadda daddy ya min alkawari muka fita, chicken republic muka je ya sai min gashin kaji muka tsaya a freeze center ya sai mana ice cream da tarkacen snacks muka koma gida. Tare muka zauna muka ci komi, sauran kayan mommy ta je ta adana su. Mun danyi hira dasu kadan har zuwa karfe tara da rabi, kafin na musu sallama na wuce dakina. Kayan barci nasa na kwanta a rub da ciki idanuna a rufe, daddy gaskiya ya fada. Tun yanzu nake ji kewar su tana dabaibaye ni, anya zan iya kuwa???!

Tun da muka gama hada breakfast na koma na kwanta barci, ban tashi ba sai wajen karfe goma na safe. Brush nayi na fita falo na karya, daddy ya fita wajen aiki. Dama dai Mommy full house wife ce, babu aikin da take yi. Shi yasa nace muku rayuwar auren iyayena tana matukar burge ni, Mommy tayi karatu har matakin masters akan Pharmacy amma daddy ya hanata aiki, duk wasu bukatu

nata kuma ya dauke su ba kamar sauran mazajen yanzu ba da idan matarsu tayi karatu taki yin aiki sai labari yazo ya sha banban saboda ba zasu raba hidimomin gida tare ba. Wanka na shiga nayi, na fito na shirya cikin doguwar riga ta wani material grey mai dan nauyi, dinkin ya kamani tsam ya bi jikina, sai daga kasa ne ya baje sosai. Saboda yanayin kirar jikina dama ba wai kiba gare ni ba, er siririya ce ni amma fa Akwai kira, daga sama har kasa kam sai dai in gode Allah. Kalar fatar jikina baki ne, duk da ba wai can ba, zaku iya cewa chocolate color dai. Gyale na dauka na dora shi akan kafada ta na fita. Dakin mommy nayi knocking na shiga, tana zaune a gefen gado da dan littafin hisnul Muslim a hannunta. Kallona tayi na zauna a gefenta, a dan shagwabe nace "mommy dan Allah inje gidan Anty Uwani?" anty Uwani kanwar mommy ce, yaranta hudu duka maza, mun saba dasu sosai saboda zumuncin iyayenmu. Lokaci zuwa Lokaci na kan je can har in musu weekend. Mommy tace "kinga baki tambayi daddy dinki ba Ummie, babu ruwana pa!" kara shagwabe fuska nayi nayi nace "mommy da wuri pa zan dawo Allah" Kallona

tayi na lokaci kafin ta gyada kai, "shikenan,but kar ki kai yamma fa!" cikin murna na gyada mata kai. Cike da doki na tashi, har na fita na sake komawa, purse dinta na bude na zari dubu biyar na fita da sauri ina dariya, kallo kawai ta bini dashi. A Unguwar Rimi suke zaune, sai dana tsaya na sai dangin fruits a bakin hanya sannan na karasa gidan. A can na wuni sur, sai gab da magrib sannan ta sa direba da danta na biyu AbdulJalal wanda yake kusan sa'ana ne suka rako ni gida. Daddy har ya dawo, Allah ya taimake ni ban sha fada ba saboda Daddy baya son yawo ko kadan. Bayan sallar isha'i ina zaune ina kallon film din Kaabil daga cikin laptop dina Ramla ta kira ni, murmushi nayi da naga sunanta a jikin wayata, wato har ta gama fushin kenan?? Da er dariya ta na daga kiran, "Lauratu ya ne?" haka nake kiranta idan naso tsokana. Ina jin dan siririn tsakin data saki, "ke pa u r a prof a ruining mood din mutum wallahi, meye wani Laure kamar wata Goggo a kauyen kayau?" dariya na sheke da ita cikin tura haushi, hakan ya kara tunzura ta kuwa. Sai da na gama tsokanarta sannan na tsaya ina sauraronta, hakuri ta bani game da abinda ya faru ranar,

nima hakurin na bata tunda dukanmu we are at fault. Daga nan hira muka hau yi da ita, mun share fiye da awa daya muna hira har sai dana gaji don ni dama can ba gwanar hira bace musamman ma hirar waya, sallama muka yi kowa ya ajiye wayarsa.

Da dare muna falon daddy mu duka muna en hirarraki, aka kira daddy a waya. En maganganu suka yi kafin ya ajiye wayar yana kallona, "Uwata kinji an karbi letter dinki pa!" ban san dalili ba, gabana ya fadi ras! Rasa abin cewa nayi kawai na tsaya ina kallonshi, yaci gaba, "ranar Sunday zaki tafi mun gama magana da Ibrahim din. Sai ki fara shiri koh?" jikina naji yayi sanyi sosai, kafin kace me! Hawaye sun fara min yawo a kumatuna, cike da damuwa daddy yake kallona, "Uwata lafiya?" kai na gyada mishi a hankali, "I just started missing u ne daddy!" Dariya ya saki yayin da mommy tayi murmushi, hannu na ya rike a tausashe, "ohh my loving princess.... We gonna miss u!" group hug muka hada kamar zamu yi kuka.

Shirye-shiryen zuwa Kano na fara yi, hada tarkace, sallama da dangi da en abubuwa. Komi cikin sanyin jiki nake yin sa, wannan shine karo na farko da zanyi tafiya ta fiye da watanni uku. Daddy dinmu dan asalin garin Malumfashi ne ta Katsina, danginshi duk a Katsina suke zaune don haka mu kan je can idan mun samu hutu in musu kwanaki zuwa sati. Amma Ina jin wannan tafiyar ta banbanta, zuwa zanyi fa in zauna da mutanen da ban sani ba na tsayin watanni hudu zuwa biyar, a garin da ban sani ba duk da cewa mun yi zaman Kano na shekaru biyu, amma that was then, I think tun ina primary 5 ne??? Haka dai naci gaba da Shirye-shiryena har zuwa ranar Sunday. Sai wajen karfe biyar na yamma muka bar Kaduna, daddy ne ke jan motar, mommy na gefen shi ni kuma ina gidan baya. Tafiyar tayi min wani irin sauri, sai naga kamar muna tafiya ne akan iska ba kan kwalta ba. Cikin dan lokaci kankani mun isa Kano, unguwar Tal'udu muka wuce tunda anan gidan yake. Naji daddy yana ba Mommy labari game da abokin nashi, yace lecturing yake yi amma ba a staff quarters yake zaune ba, yace dan asalin garin Kano ne kuma

yanzu haka yana neman kujerar dan Majalisa ne. Yaran shi uku da matar shi daya..., ni dai tunda naji yace yana harkokin siyasa na maida hankalina kan wayata, dan siyasa? Allah ya gani basu cika burge ni ba, ban son siyasa.

Kugi na karshe da motar tayi a cikin garejin gidan ne, tun daga cikin mota nake karewa gidan kallo. Ba wai yanke hukunci kai tsaye ba, yanayin gidan tafiy kafin ace mallakin just a lecturer (sorry lecturers, m not underestimating ur payment or something). Gida ne hawa daya, parking lots din gidan cike yake da manyan motoci ba na wasa ba, ga bikes da kekuna ina ji na yaran shine. Daga nan kana iya hango wani dan karamin garden a can gefen gidan, har wani dan karamin wajen wasanni na gani.

A hankali muka fito daga cikin motar, already wani da nafi kyautata zaton mai gadi ne ya fara kwasar kayana yana shiga cikin gidan dasu. Shi yayi mana jagora zuwa wani babban falo daya min kama da fadar uwargidan sarkin Kano, ya sha jere na wasu narka narkan leather seats kala biyu, farare da browns, ko wane jeren kaya

yana da nashi dinning table, Plasma TV wadda zaka yi zaton zata cinye bangon falon saboda girmanta. Kafafunmu suka nutse cikin wani tattausan rug carpet kamar auduga, nayi iya bakin kokari na wajen ganin cewa ban hangame baki nayi kauyanci ba, maganar gaskiya ban taba shiga tsarraren falo irin wannan ba duk da cewa ba laifi nayi shige-shige a parlours da gidaje na manyan mutane, wannan kam looks extraordinary sosai. Kujera muka samu muka zaun 3 seats, ina tsakiyar su daddy, er aikin gidan ta fito daga kitchen ta gaida su daddy kafin ta shige wata kofa a cewarta zata kira madam. Ina jin lokacin da daddy yake gayawa Mommy ai Ibrahim din baya nan, yaje wani seminar. Ni dai ba baki, I was very nervous a lokacin. Mintuna kamar goma sai gata ta fito, Ya Allahu!! Meye wannan a gabana? Naji zuciyata tana tambaya lokacin da nayi tozali da matar. Don fari fa Akwai fari kamar Baturiya, kyawu ma Akwai shi Masha Allah, wata irin kiba marar fasali ne da ita. Lokacin data zauna akan kujera suna gaisawa dasu daddy sai naga ta shirge a waje guda kamar kayan wanki. Da kyar na iya saisaita kaina na dan

zame daga kan kujerar na gaisheta, da er fara'ar ta ta amsa har da ambatar sunana, "Safeenah ko?" na gyada mata kai a hankali. Ta maida kanta gasu daddy suna er hira, idanuna suka ci gaba da wandering a cikin falon bana ma jin me suke fada. Aka kira magrib daddy ya fita sallah, ni da Mommy kuma muka yi a cikin falo don bamu samu albarkacin samun gayyata zuwa dakin matar gidan ba, kuma ba a nuna min inda zan zauna ba, karewa kayana ma suna nan baje a tsakiyar falon. 'yar aikin gidan muka tambaya ta nuna mana bayi dake nan cikin falon muka shiga muka dauro alwala, motar daddy naje na dauko prayer mat muka shimfida anan muka yi sallah abinmu.

Daddy yana dawowa daga sallah yace mommy ta tashi su tafi, nan fa idanuna ya raina fata da naga Mommy ta yiwa er aikin gidan magana akan taje ta gayawa matar gidan zasu tafi, idanuna suka yi raurau kafin kace me na fara hawaye shabe-shabe. Ba a dauki mintuna biyar ba sai gata ta fito tana taku da kyar, ban sani ba na takama ne ko kuwa dalilin kibar ta ne? Sallama suka yi dasu ta

koma daki abunta. Hannuna mommy ta kama na musu rakiya har bakin motar su, zuwa lokacin kam kuka nake har da shessheka, suka saka ni a tsakiya suna lallashina har na samu kukan ya lafa. Ina nan tsaye suka shige mota suka ja suka tafi bayan na sha nasihohi daga gare su. Na bi bayan motar nasu da kallo har suka bar gidan aka maida gate aka rufe, na maida kallona ga dankareren gidan da zan rayu a ciki zuciyata cike da tarin damuwa iri-iri, daga can kasan zuciyata ina jin wata irin nadama na dabaibaye ni, Me ya kaini???? A hankali wasu siraran hawaye suka biyo kan Kumatu na.....!

Sai dana kwashe lokaci mai tsawo a cikin farfajiyar gidan a tsaye kafin na samu kwarin gwiwar jan kafafuna da kyar na koma falon. Ina shiga na ci karo da er aikin gidan wadda saboda tsabar wata irin shiga mara fasali da tayi yasa na kasa gane ko wace irin yare ce, cewa tayi in zo muje ta nuna min dakin da zan kwanta inji madam dinta, babu musu na dauki jakar hannuna na janyo daya daga cikin jakunkunan dana taho dasu nabi bayanta bayan

itama ta dauko wasu. Abinda na kula duka dakunan gidan a falon kasa suke, ni tunda nazo ban ga kowa ya hau saman ba. Wani dan madaidaicin daki cikin jerin dakunan dake cikin falon ta bude muka shiga ciki. Dakin yana da fadi ba laifi, Akwai toilet a ciki ga wani medium size gado ruwan golden, mirror da closet sai er karamar sofa da study table. A tsakiyar dakin an malala wani tattausan circle carpet baki, sauran dakin kuwa malale yake da wasu en ubansun marbles fari da gold, well, ba laifi ya burge ni sai dai yadda aka tsara dakin ne sam bai min ba. A raina nace sai na canza shi. Ina ta karewa dakin kallo har ta gama shigo min da kaya na duka, ta tambayeni idan Akwai abinda nake bukata? Kai kawai na girgiza mata tare da mata godiya, ta min sai da safe ta wuce abinta. Jakar hannuna na jefa akan gado na samu gefen gadon na zauna Ina kara karewa dakin kallo, tashi nayi na leka toilet, Shima babu laifi ya hadu, na dawo na bude closet din babu komi a ciki sai er guntuwar kura data yi, tsumma na lalubo na goge ta tas na lalubo turaren kaya a cikin kayana na watsa a gefen closet din kafin na fara shirya kayana a ciki, sai dana cika ta tsil da

kaya wasu ma da kyar suka shiga, na makare kan mirror na da tarkacen kayan shafa dana kwalliya da nau'in perfumes kamar a wani dan karamin super store. Sallar isha'i nayi na hada da shafa'i da wutiri, ina gamawa naji wayana tana kara, ringing din dana sakawa daddy ne. Da sauri na tashi na daga kiran, gaisawa muka yi ya fada mun sun isa gida lafiya, mun danyi hira kadan yaba mommy wayar itama muka dan yi hira, sai data kara min da en nasihu akan wadanda ta min sannan muka yi sallama na ajiye wayar. Ruwa na watsa a jikina na nemi kayan barci marasa nauyi na saka na kwanta, amma kwata-kwata barci yace bai san idanuna ba, tunanika iri-iri suka dinga min yawo a kwakwalwa, daga karshe waya ta na dauko na fada duniyar gizo.

Washegari kamar yadda na saba da asubahi na tashi nayi sallah, shiru Ina kan abin sallah a zaune ina debating akan in fita in taya matar gidan aiki ko kuwa in zauna a daki? Daga karshe dai kawai na tashi na fada wanka, usual ways din harkokin rayuwata na bi, kwalliya data kwashe ni kyawawan mintuna talatin, minti ashirin

na fiddo kayan sawa da shiryawa, zuwa lokacin dana tsaya a gaban dogon yaro ina sake duba kaina, karfe bakwai da mintuna ashirin. Cike da tunanin yadda zan karasa cikin makarantar BUK na fito falo, babu kowaa cikin falon amma na jiyo motsi a can wata kofa dake gefen dakin matar gidan. A hankali na karasa tare da lekawa, hangame baki nayi kamar zai rabe biyu. Wani dankareren kicin dana gani wanda zan iya cewa ya lunka dakina sau biyu, kayan electronics na kicin babu kalan wanda babu. A gaban gas cooker na hangi er aikin gidan tana soya plaintain, karasawa wajenta nayi muka gaisa cikin girmamawa, na tambayeta matar gidan tace min wai bata tashi daga barci ba, Kai na gyada cike da mamaki. Wace matar aure ce ke kai karfe takwas na safe saura tana barci?? Tambayarta nayi yadda zan isa wajen IT dina, tace ai Direban da zai kaini yana waje yana jirana, tun dazu yayi magana. Juyawa nayi na fita, daga kicin din tace min breakfast fa? Nace mata zanyi acan. A farfajiyar gidan na hangi direban, a mutunce na gaida shi ya bude min gidan baya na shiga yaja motar muka wuce. Mintuna talatin mun shiga cikin BUK, har gaban

microbiology lab muka je yayi parking, tare dashi muka shiga lab din ya samu lab attendants suka yi maganganun da zasu yi, ya tafi ya barni bayan ya fada mun lokacin da zai dawo ya dauke ni. Ina zama sai ga Ramla sun shigo ita da Antin ta, nan muka rungume juna cike da murna, itama Anty Halima tafiya tayi ta barmu anan. Da yake ranar farkonmu ce a wurin babu wasu ayyuka da muka yi, wajen karfe goma sha daya muka fito ni da ita zuwa Cafeteria din dake cikin department din. Tafiya muke yi a hankali, tsarin makarantar ya burgeni kwarai, er hira muke yi da ita game da wajen har muka shiga cikin cafeteria din, babu students sosai zama kawai muka yi muka yi order din abinda zamu ci.

Muna gama cin abincin lab muka koma, lab attendants din were very friendly don haka cikin dan kankanin lokaci muka saba dasu. Wadanda suke yin aikin project dinsu sun kawo ayyuka, nan ne fa muka tashi muka fara aiki. Sai wajen karfe biyu muka tashi, wani dan karamin garden muka zauna muna ta hirarmu ni da ita ina jiran Direba yazo tunda ita sai ta jira Anti Halima ta gama

ayyukanta, sai wajen karfe biyu da rabi sannan Bala Direba ya iso. Ina hango motar na gane ta saboda a cikinta muka zo. Da sauri nawa Ramla sallama na tashi nayi wajen da yayi parking, a mutunce na gaida shi na bude bayan motar na shiga.

Wata kyakkyawar yarinya cikin kayan makaranta dogon wando navy blue da shirt fara ta dago kyawawan idanunta tana kallona, ban san lokacin dana sakar mata murmushi ba saboda tsananin burge ni din da tayi, a gaban motar kuma maza biyu ne suma cikin shigar kayan makaranta irin na yarinyar, duk suka juyo suna kallona. Zama nayi sosai a gefenta ina ta watsa musu Murmushi yayin da direba yaja motar, yarinyar da nake tunanin shekarunta zasu kai bakwai zuwa takwas tace min ke ce bakuwar da daddy yace zata zo mana gida? Na gyada kai ina kallonta, nice beauty, ya sunanki? Murmushi tayi, sunana Hafsah amma daddy yana ce min pretty Hafsey, su yaya Abdallah kuma suna ce min Hafsatu... Ta karasa tana pouting cike da shagwaba. Er dariya nayi tare da jan kumatunta, "kai amma Yaya

Abdallah bai kyauta ba! Hafsatu ai sunan tsofi ne" ta gyada kai tana turo baki tare da kallon wanda yake kama da shine babban yayansu, "ai kullum sai na gaya mishi amma sai yace wae ai nima tsohuwar ce" na kalli yaron Ina Murmushi, "Yaya Abdallah baka kyauta ba gaskiya, tana yarinyarta ka dinga ce mata tsohuwa?" yaron yayi dariya, "sunan maman Daddy gareta pa, don Allah ba tsohuwar kenan ba?" daya yaron na gefenta ya kwashe da dariya, "tsohuwa ce mana, baka ga har ta fara furfura Akanta ba?" Hafsat ta kai mishi duka a kafadar shi, ya kauce yana mata dariya. Tsokanarta suka ci gaba dayi suna dariya har sai data fara kwalla sannan na tsaida su, "here, enough with the teasing, a kyale pretty haka nan ko?" ta gyada kai tana min murmushi, kanta na shafa ina jinta har cikin raina. Yarinyar tana da wani irin kyau duk da suma sauran yaran suna dashi amma ai kun san kyan mace ya banbanta dana namiji, ina mamakin inda ta gado shi a raina nace kila sai dai wajen mahaifinsu don babu mai kama da mahaifiyar su, dama dama dai Qaseem mai bin Abdallah, naga suna dan yanayi da Anti Mubeenah. Kafin

kace me mun saba da yaran, dama ni bani da wahalan sabo suma naga hakan a tattare dasu. Muna isowa gida na dauki school bag din Hafsat ita kuma ta rike lunch box dinta, hannunta cikin nawa muka shiga falo ina taya ta miming din wakar twinkle little star. A daya daga cikin kujerun falon, Anti Mubeenah ce zaune ya harde tana duba jarida, yaran suka zube a gabanta suna bata labarin makaranta, sai dana bari suka gama hayaniyar su sannan na duka na gaida ta. Fuskarta dauke da dan murmushi ta amsa tare da ce min Akwai abinci a kicin, godiya na mata tare da cewa sai nayi sallah, dakina na wuce nayi sallah, na janyo wayata na kira mom don nasan daddy yana office ni kuma ban cika son kiranshi a wajen aiki ba, mun jima muna hira da ita kafin muka yi sallama, ana kiran sallar asr nayi na janyo system dina na kunna kallo tunda babu abinda zanyi, da a gida ne kila na shiga kicin ina taya mommy na girkin dare.

Ina zaune anan ina kallo Hafsat ta shigo cikin kayan makarantar islamiya, na daga Kaina na kalleta ina dan murmushi, "pretty Hafsat an dawo ne?" ta zauna a

gefena tana turo baki, "malam ya bamu aiki a makaranta kuma ban iya ba, gashi Abbu da yake koya min karatun baya nan" zama nayi sosai akan gadona nace bani littafin in gani, ta bude jakar ta ta miko min na duba, Tawheed ne, tambayoyi akan imani. Murmushi nayi na kalleta nace "yanzu dai je ki kiyi sallahr magriba tunda an kira, bayan isha'i sai ki dawo mu yi" da murnarta ta tashi ta tafi, har ta kai bakin kofa ta dawo da gudu ta rungume ni, "Aunty thank u" dariya nayi na bita da kallo har ta bar dakin, kai na girgiza na tashi na fada bandaki.

Bayan sallar isha'i ina kan sallaya a zaune Qaseem yayi sallama ya shigo dakin, yace Aunty Nafeesah wae Mami tace kizo mu ci abinci, ba musu na tashi nabi bayanshi don dama yunwa nake ji. A kan dinning na samesu su duka suna cin abinci, gefen Hafsat naja kujera na zauna. Ganin kowa serving din kanshi yake yi yasa na dauki plate na bude flask din abincin, tuwo ne kaman na semovita miyar danyen kubewa, tunda naga miyar tsululu kamar ba danyen kubewa ba nasan cewa tuwon

sai a hankali, Illa kuwa ina kai loma daya bakina da kyar na hadiye, tuwon gashi nan latab kamar danyen gari alamun bai gama dahuwa ba, miyar sai dan banzan yaji kamar da taruhu kadai aka yi ta, babu taste ko na anini sai shegen karnin kifi. Da kyar na iya hadiye lomar farko, ban yi kuskuren kai wata bakina ba don na tabbata idan na kuskure ta sake shiga bakina sai na amayar da dan guntun abincin daya rage a cikina. Su kansu na ga tsakura kawai suke yi, kallonsu kawai nake yi cike da mamaki. Ta ya za ayi mutane su rayu da irin wannan abincin a duniya? Koda yake yau ne karo na farko dana ci abincin gidan, ban sani ba ko kila rana ce ta bacewa mai girkin kawai, da wannan tunanin na gyada kaina na tashi daga kan table din bayan na wa Anty Mubeenah sai da safe. Dakina na koma naje nayi brush na wanke bakin da mouth wash, cikina wani irin hautsinawa yake yi saboda yunwa, jikar dana fita da ita dazu na bude, wata irin ajiyar zuciya na sake ganin Pack din cookies din New Yorkers, na manta dashi ma ni shaf dazu muka saye shi a cikin makaranta. Zama nayi akan gado na bude shi na fara ci, wayata na hannuna ina chatting, Hafsat ta shigo

dakin. Tare da ita muka cinye cookies din, daga nan na koya mata aikin da aka basu, kallon film dina da nake kallo muka ci gaba dayi sai wajen karfe goma da rabi ta min sai da safe, na shafa kanta nace ki tashi lafiya pretty., kar ki manta pa kiyi addu'ar kwanciya barci kinji? Ta gyada kai, "thank u Aunty, sai da safe" na dan hade fuskata, "ohh pretty, sau nawa zan gaya miki bana son Aunty dinnan? Call me Yaya Nafee, bai fi dadi ba?" ta girgiza kai cikin tsokana, "babu dadi gaskiya" kofar dakin na nuna mata "oya, bi can sai da safe" ba musu ta tashi ta fita tana er dariya kasa-kasa. Tana fita na janyo wayata ina kallon screen din, a cikin messages nake ina shawara da zuciya ta akan abinda nake shirin aikatawa, daga karshe dai nayi typing, "you sleep?" na turawa Muneer, tsawon mintuna sha biyar babu amsa, na sake tura "seems like you are, good night!" na kashe wayar na dorata akan bedside table na kashe wuta tare da yin addu'ar kwanciya barci na kwanta.

Nayi tunanin idan na tashi zan ga reply daga Muneer ko kuma missed call dinshi, sai dai har na gama shirina tsab

babu shi babu alamun shi. Sai zuwa lokacin ne na fahimci imma dai yana sane yaki min reply jiya ko kuma yayi barci wulakanci ne ya hana ya biyo sahuna da safe, kwafa nayi ina jijjiga kai.

Ranar ma dai abincin safen sai godiyar Allah, plaintain ne aka soya da shayi da soyayyen kwai, tsakani na da Allah nasan ba zan iya cin abincin nan ba, haka nan dai na dan tsakura har zuwa lokacin da Bala yazo muka dunguma gaba daya har su Hafsat muka fita. A mota daya muka tafi dasu, sai da muka biya ta makarantar su muka ajiye su sannan muka wuce. Da rana koda muka dawo bamu samu Anti Mubeenah a gidan ba, har dare bata dawo ba sai bayan isha'i likis sannan. A zaman sati dayan da nayi a gidan zan iya cewa zama ne na takura, if not for Hafsat dasu Abdul I didn't think I would've survived. ita dai matar gidan yadda na kula da ita, bata cika jan mutane a jikinta ba, ni dai tunda nazo gidan ban ga bare ya leko ba, makota ne, abokai ko dangi. Tsakanina da ita gaisawa ne kawai, idan mun hadu a dinning mu danyi hira sama-sama, ga yawo, idan ta

saka Kafa ta fita daga gidan tun safe sai dare take dawowa duk da Hindatu mai aikinsu naji tace tana da saloon da take kula dashi. GA er aikinsu kuwa ban ma san me zan ce ba, ni ban ga dalilin da zai sa in dauko er aiki ba kuma ba zata min gamsasshen aiki ba in kyaleta duk da cewa ni har ga Allah I dont have any plan na daukar er aiki Ina nayi aure, ga Hindatu dai kam abin babu bayani, ita ba ga girki ba, ita ba ga gyare-gyare ba. Aikin data iya daya; ta sha kona sanwa idan ta dora ta fara kallo.

A takaice dai kafin zagayowar ranar juma'a sai da naji Kano ta fita daga raina, ni ban saba irin rayuwar kadaici dinnan ba. Ranar juma'ar kuwa Ina dawowa daga wajen IT dama dan karamin kit dina a Shirye yake tsab, Anty ta fita yawon data saba sai sako na bari a wajen Hindatu nace tace mata na tafi weekend gida, dama Daddy ya turo wanda zai dauke ni, a farfajiyar gidan ma na dawo na tarar dashi yana jirana don haka babu bata lokaci muka wuce Kaduna. Sai wajen karfe biyar da rabi muka isa gida saboda yanayin go slow da muka samu a hanya

kafin mu fita daga cikin Kano, da ihu na da komi na shiga gidan, kit dinma sai driver ne ya shigo min dashi. Mommy tana kicin tana girki ita kadai, na rungumota ta baya ina tsallen murna, juyowa tayi tana kallona cikin murmushi, "oh ni wannan yarinya tawa ban san yaushe zata girma ba" na buga kafa cike da shagwaba nace "mommy!!" dariya tayi ta rungumo ni jikinta cikin nuna kewa. Dakina na shiga an share min shi tass sai tashin kamshi yake yi, na cire kayan jikina na fita zuwa kicin na kamawa Mommy girkin, muna yi muna hira, yawancinta tambaya ce akan wajen da nake zaune, babu matsala dai ko? Kina cin abinci? Tambayoyi dai iri-iri. Muna nan Daddy ya dawo, har cikin kicin din ya shigo ya daga ni sama Cak yana juyi dani, dariya na saki na rirrike shi har ya dire ni kasa. Sannu da zuwa na mishi ya amsa yana shafa kaina, na amsa brief case din hannunshi na raka shi har dakin shi kafin na fito na barshi ya shirya.

Bayan isha'i muna falo zaune akan babbar tabarmar cin abinci, hira nake musu, duk abinda nake yi a Kano babu

wanda ban tsallake ba, su kuma suna sauraro cikin nuna rashin gajiyawa na dariya su yi, na mamaki kuma su jinjina kai. Ranar kam sai wajen karfe sha daya muka yi barci muna ta hirar yaushe gamo. Kwana na biyu a gida na koma Kano cike da kewar iyayena, ji nake kamar inyi zama na acan.

Hindatu kadai na samu a gidan, tace yaran dama a gidan kakannin su suke yin weekend, ita kuma Anty Mubeenah tace wajen bikin kanwarta mawuyaci ne ma idan ba kwana zata yi a can ba, na jinjina kai tare da kwaso tsarabar fruits dana musu a hanya na shirya su a cikin fridge. Wajen karfe takwas na dare ina zaune gidan shiru babu motsin kowa, nasan da su Hafsat suna nan da yanzu suna dakin ko dai muna hira ko kallo ko kuma ina koya musu assignment. Horn din mota naji a bakin gate kafin naji karar bude gate, a raina nace Anty Mubeenah ta dawo kenan. Hasken motar ya ratso ta cikin windown dakina zuwa cikin labulaye na da yake window din dakin a kusa da garejin gidan take. Minti kamar biyar na bata na tashi na fita da niyar inje in mata sannu da zuwa.

Tsaye a jikin fridge hannunshi dauke da gorar ruwan Sanah yana sha directly daga cikin gorar, hannunshi daya rataye da suit dinshi yana kuma rike da brief case. Dogo ne ba can ba, idan da ba don na sanshi a hoto ba to da zan iya rantsewa da Allah ince bashi bane, saboda ko a cikin hoton ban hangi yarintar dana gani a tattare dashi ba a lokacin, da nace yarinta ba wai ina nufin yaro bane, aah Ina nufin wanda bai kai girman daddy na ba; Abban su Hafsat ne. Wata irin gigicewa naji nayi, haka kawai naji kafafuna sun yi wani irin sanyi wanda ban iya daurewa ba sai dana dangana gwiwoyina da marble din dake malale a tsakiyar falon, ban sani ba tsabar kwarjinin da yayi min ne yasa gabana ya tsananta faduwa ko kuwa wani abu daban?? Cikin rawar murya nace "sannnnnu da..... Zuwa...... Abbbbuh!!".........

Wasu kyawawan idanu farare tas suka dago suka kalleni, ban sani ba ko tsananin hasken da falon yayi ne ta dalilin hasken chandeliers din falon ko kuwa idanunshi ne a haka? Brown eyelids suna ta wani sparkling da sheki, haka kawai na tsinci kaina da faduwar gaba. Ya sauke

robar ruwan daga bakinshi ya jefa ta cikin waste bin tare da cewa,"lafiya qalau Nafeesah! Kin zo bana gari koh? Hope komi lafiya?" na gyada kaina da kyar, wani irin nauyin mutumin naji ya dabaibaye ni. Ya gyada kai, "OK!" ya wuce dakin Anty Mubeenah abin shi. Kafa na na masifar rawa na tashi na fada daki, hannuna dafe da kirjina kamar wadda take kokarin tsayar da racing din da zuciya

na take yi wanda ya wuce misali. Idanu na zare sosai ina kallon reflection dina a jikin mirror, I couldn't believe wai a haka na fita gaban Abbu. Kafar wando na daya a gwiwa, gashin kaina wani yayi baya, wani ya zubo a kafaduna, wani kuma ya tattare a gaban goshina saboda hular dana saka., idan ka ganni dai a lokacin babu bata lokaci zaka danganta ni da psychiatric patient dinnan irin stage one ma, kunya ta rufe ni sosai kamar in nutse a kasa haka naji. Tsalle nayi na dira akan gado na fara birgima, sai da nayi kaca-kaca da gadon sannan na saurara ina maida numfashi...

Karfe bakwai da mintuna biyar na safe na fito daga dakina a shirye na tsab, babu kowa a cikin falon. Kan dinning an shirya kuloli manya masu kyau, kila saboda dawowar maigidan ne aka fiddo sabbin kuloli don ban taba ganin irin su a gidan ba. Na bude kulolin, farfesun kan sa ne sai kamshin er daddawa da tafarnuwa yake yi, sai masa fara tas itama tana ta tururi a cikin wata kula, kunun gyada har da kosai. Kujera naja na zauna na zuba farfesun na fara ci kunnena har motsi yake yi, duk yadda aka yi abincin ba daga cikin gidan yake ba, idan ma daga gidan yake to ba Harira er aikin su bace ta dafa. A raina nace kila Anty Mubeenah ce ta dafa, Amma koda wasa ban ji kamshi yana tashi ba jiya ai. Na dai ture tunanin komi na ci gaba da dura abinci abu na, ina nan zaune na kusa gamawa Anti Mubeenah ta fito daga dakinta sanye da wando da riga na barci, ni kaina ina mace sai da shigar ta bani haushi. Gabadaya kirar ta marar fasali ta fita, tumbinta da zai sa kayi tunanin cikin en biyu ne ya fito yayi nashe-nashe a gaban ta, gashin kanta yayi buzu-buzu dan ma wai tana da yalwar gashi babu laifi, fuskarta sai naso take yi bana tunanin tunda

ta tashi da safe ta wanke ta. Nayi kokarin kauda takaicin ta daya taso min na gaishe ta, ta amsa a kaikaice tana wani basarwa irin yadda take amsa min ta bude kofar dake fuskantar dakinta ta shiga, ina tunanin nan ne dakin maigidan don ban taba ganin ta shiga ciki ba tunda nazo gidan. Ni dai na gama cin abinci na na wuce abina. A farfajiyar gidan Malam Bala yana jira na, cike da girmamawa na gaida shi na bude bayan motar da kaina na shiga saboda na hana shi ya dinga bude min. Y'all ja motar muka tafi har cikin makaranta, ranar an kai wasu sabbin en IT lab din daga Leather Research Zaria don haka bamu samu cunkushewar ayyuka ba. Cikin dan lokaci muka saba dasu. Ranar tun karfe daya da rabi muka tashi, bayan mun fito daga lab din Zainab da Ikram suka mana sallama suka wuce gida, ni da Ramlah muka zauna a dan karamin garden din da muke zama muna tattaunawa akan saurayinta da yake so ya tura gidansu ita kuma tana ki wai bata so tayi aure yanzu ni kuma ina nuna mata rashin dacewar hakan, muna nan na hangi motar gida tana tunkaro mu duk da ba wadda aka saba kawo ni bace amma nasan duk motocin dake

gidan, wannan shine karo na farko ma da aka zo daukar mu da motar, Anty Mubeenah naga tana jan motar. Na tashi muka yi sallama da Ramlah na tunkari motar, sai da nace tazo mu sauke ta tunda gidan su a hanyar mu yake amma tace zata jira Anti Haleemah don haka na kyaleta. Tun daga nesa Hafsatu ta fito daga cikin mota a guje tana min oyoyo, na tare ta da dan guduna muka fara juyi a wajen kamar wata yarinya, sai da muka gaji sannan na ja hannunta muka tunkari motar. Sai dana jira ta shiga sannan nima na shiga, na daga baki da niyar gaida Malam Bala kamar yadda na saba, "Malam Bala barka da war hak.....!" naji maganar ta kakare min sakamakon wanda na gani a gaban motar yana kokarin tada ta, da saurin na sadda kaina kasa tare da cewa "Abbu ina yini?" ya amsa idanunshi na kan titi. Ji nayi kamar wadda aka jefa ni cikin kankara, na kasa maida hirar dasu Qaseem suke min kamar yadda muka saba idan muka taho sai dai in gyada kai ko in bisu da uhm da ehh har muka isa gida. Cikin sauri na bude murfin motar na fita har ina hadawa da tuntube, ban tsaya a ko ina ba sai cikin dakina. Na zauna a gefen gado ina ajiye

numfashi da kyar da kyar, ni kam me ke damuna ne haka? Ni dai nasan bani da wahalar sabo da mutane, amma me yasa a gaban mutumin nan nake ji na kamar wata haliita daban? Me yasa na kasa sakewa dashi? Me yasa nake jin kwarjinin mutumin har cikin tsakiyar kaina? Wata zuciyar tace min saboda ban jima da sanin shi bane, after all babban mutum ne kuma idan zan iya tunawa tun daga kan abokan daddy na har zuwa en uwanshi ni dai bude ido nayi na gansu tare, wannan kuwa daga sama kawai na san dashi, hakan da nake ji rashin sanayya ne kawai, idan na saba dashi komi zai daidaita. Da wannan tunanin naji na samu hope, na maida bayana na kwantar akan gadon tare da lumshe idanuna, a hankali barci ya sure ni, nasan biyan bashi ne tunda jiya ban samu nayi barcin kirki ba.

Sai wajen karfe biyar da rabi na yamma na tashi daga barcin, toilet na shiga nayi wanka na fito na kimtsa jikina cikin wasu simple Pakistan riga da wando marasa nauyi, turare kadai na fesa a jikina da yake bana yin Sallah sai na koma kan gado na fara sana'ar chatting da kallace-

kallacen film. Babu wanda ya leko dakina sai bayan isha'i Hafsat ta leko wai inje mu yi dinner, ina jin yunwa amma jin muryar Abbu a falon yasa nace mata a koshe nake, tayi tayi dani naki fita dole ta juya ta tafi tana gunaguni. Can kuma sai gata ta dawo dakin, "wai Abbu yace mai kika ci?" nace ban ci komi ba, Tun lunch ne amma ciki na a cike yake. Ta juya ta tafi, mintuna biyu ta sake dawowa, "Abbu yace ki fito ki ci abinci ko ran ki ya baci!" nayi shagaraaaa da baki ina kallonta cikin rashin abin cewa, ganin bani da niyar tashi yasa ta juya tana fadin "bari inje in gaya mishi kin ce ba zaki zo ba" da sauri na tsayar da ita tare da tashi tsaye na lalubi hijabi dogo har kasa na saka, Hafsatu ta saka ni a gaba kamar wadda zata gudu har gaban dinning table din Inda suke zazzaune bayan ta gama mitar wai gidan wa zan je dana saka hijabi, ban tanka mata ba, fargabar yadda zan zauna a teburi daya da Abbu ta cika min ciki, tsakani na da Allah ina jin kunyar shi. Naja kujera daya na zauna a hankali kamar wadda tayi laifi, daga Qaseem sai Abdul a wajen sai shi Abbu din Anty Mubeenah bata nan ban sani ba ko bata gidan ne? Tun kafin in gaida Abba ya

tare ni, "wasa da cin abinci ko Nafeesah??" na sadda kaina a kunyace nace "Abbu na koshi ne" ya girgiza kai, "that's not an excuse, dokar nan gidan ba a skipping meals uku ko da wasa, idan ma mutum bai jin yunwa sai ya tsakura, idan kuma ya ki dura muke mishi koh?" ya kalli su Qaseem kamar yana tambayar su, yaron ya gyada kai yana er dariya wadda ta fito mishi da goyen hakoran shi, ni kaina I couldn't help it sai da nayi er dariya jin abinda yace, yace oya ci abinci. Babu musu na dauki spoon na jefa cikin jollop shinkafa da aka yi an kawata ta da nama, kifi, coleslaw da wainar kwai. Kamar dazu da safe abincin yayi dadi sosai kamar kunnen mutum zai tsinke, ga zobo mai sanyi a gefe ya sha kayan kamshi an yanka kankara, apple, cucumber da wasu nau'i'kan fruits dana kasa tantance ko menene. A nutse muke cin abincin, su Hafsat suna hirarsu da Abbu jefi-jefi su kan Sako ni a ciki ina amsawa da uhm ko a'ah, tun dai ina nodding har na dan sake na fara maida musu amsa sosai, Abbu yake tambayana game da karatu na ina bashi amsa a nutse. Muka gama cin abincin na kwashe kayan duka na kai kicin, sauran abincin da drink

din na saka su a freezer su kuma kayan na wanke su tass. Falon na koma na zauna don Hafsat tayi kini-kini ta hana ni tafiya dakina dole na zauna a cikin su, su Abdullahi game suke yi a laptop din Abbu ita kuma Hafsatu na canza channels, bayan dogon lalube muka tsaya a mbc 3 suna hasko Despicable Me part 1. Muna cikin kallon muna kwasar dariya ni da Hafsat, gabadaya mun hade falon da hayaniya. Abbu ya fito daga dakin da yake fuskantar dakin Anti Mubeenah sanye da bakar jallabiya a jikinshi, take nayi tsit kamar bani ce nake ihun dariya ba. Ya zauna a kujera tare da daukar Hafsat ya dora ta akan cinyar shi tare da kallona, "are u a kindergarten kike kallon cartoon da girman ki??" kafin inyi magana Hafsat tayi caraf tace "Abbu tana dasu da yawa a cikin system dinta, har dasu na Disney princesses da fairy tales da......." ta fara jero mishi sunayen films kala kala ni wasu ma ban rike su ba, Abbu sauraren ta kawai yake yi yana gyada kai amma fa idanunshi suna kaina, hakan yasa naji gabadaya kamar wadda aka zare mata duk wani kuzarinta. Sai data gama lissafin sannan ya magantu, "wato dama saboda fina-

finai kika sa aka sai miki laptop ba don karatu ba koh?" nayi saurin girgiza kaina, "a'ah Abbu! Ina yin karatu fa. Akwai text books a ciki da yawa da videos dinsu kuma Akwai docs da dama duk a ciki, da gaske ina yin karatu" ya kalli Hafsat, wai?? Ta gyada kai da sauri ehh Abbu, watarana ma tana koya min, kuma har Assignment take koya mana ni dasu Yaya Abdullahi. Ya daga gira daya, "Ohh really? A wani mataki kike a Islamiya?" kaina a kasa nace "nayi saukar Al-Qur'ani mai girma, na gama harda watanni biyar da suka wuce, na sauke littafin Umdatul-Ahkam, Riyadussaaliheen, Tafseerul-Jalalaini da Tafseerul-Ibn-Khatheer, da littafai da dama. Na fara Annissa'u war-rijaalu fil jannah amma ban gama ba har yanzu" yace "Mashaa Allah! I am impressed gaskiya" na sadda kaina kasa ina murmushi zuciyata cike da kaunar iyaye na da suka tsaye min na samu karatu mai inganci, tun ina primary six na sauke Al'Qur'ani mai girma, ban fara harda ba sai dana sake yin wata saukar sannan na fara tare da wasu manyan littafai na addini nasan ko a haka na tsaya Alhamdulillahi bani da matsala amma ban tsaya din ba, har yanzu ina cigaba da karatu na duk da

cewa har gida Malamin yake zuwa yana koya min. Ganin ban yi magana ba yasa ya cigaba, "da alamu nima zan kawo nawa littafan ki dinga koya min don cikin wadanda kika ambata Akwai wadanda har yau ban gama su ba, zaki koya min?" mamaki ya matukar Kama ni, duk cikin saukin kan mutumin ne haka ko kuwa wani abu daban? Dana rasa abin cewa sai kawai nayi murmushi na maida kallona ga TV ba wai don ina fahimtar abinda ake yi ba anymore, sai don in janye yawan tambayoyin Abbu wanda nasan da kyar ne in samu amsoshin su. Ina ji yana tambayar Hafsat karatun ta tana gaya mishi abinda suka yi a Islamiya ranar, ta karanto mishi Hadisi da Qur'an ya saurara tare da gyara mata Inda ta kuskure.

Karfe tara da rabi suka gama film din da muke kallo, Abbu ya umarce mu da muje mu kwanta saboda makaranta. Sai da safe muka mishi kowa ya wuce dakin shi, anan muka bar shi yana danne-dannen laptop. Ina shiga daki su Mommy na kira don gabadaya ranar bamu yi waya dasu ba, muka gaisa dasu mun jima muna

hirarraki kafin na musu sai da safe muka kashe wayar. Bayi na shiga na kimtsa jikina nazo na kwanta.

Washegari abincin mu marar taste da armashi ya dawo, Ashe wanda muka dinga ci daga gidan su Abbu aka kawo shi. Ni dai na tsakuri iya wanda zan iya ci na tashi, suma yaran haka nan dai suka tsattsakura muka tashi muka tafi makaranta.Ranar juma'a kamar satin daya wuce, ina dawowa naci karo da direba yana jira na, sallama nawa Anty da Hareera na tafi Kaduna wajen Mommy da Daddy na.

•••••••••••

Kimanin wata na daya da zuwa Kano, na riga nayi adopting da garin da yanayin gidan da nake zaune. Abbu bai cika zama a gida ba, it's hardly yayi sati daya cur a gida, yawanci zuwa seminar ko kuma harkokin shi na kasashen turawa, na Ji Malam Bala ne ranar nan yace

wai suna shiryeshiryen bude wani kamfanin kirar kayan sawa ne a China shi da abokan shi. Anti Mubeenah ma dai bata cika zama a gidan ba, yawanci ko tana gidan ma bata cika zama a falo ba shi yasa har zuwa lokacin bamu wani shaku da ita ba, tsakani na da ita gaisuwa ne kawai. Abin yana matukar daure min kai, ban taba ganin wani daga cikin dangin Abbu ba a gidan, amma nata da abokanta suna yawan zuwa har yini suna yi, daya daga cikin nasihun da Mommy ta min lokacin da zamu taho Kano shine kada in kuskura in shiga harkar da babu ruwa na, banda shisshigi da sa ido a rayuwar mutane, don haka na kauda kaina daga rayuwar su, koma meye ke faruwa dai rayuwar su ce ba tawa ba.

Wannan satin ina gida ban je Kaduna ba saboda su Daddy sun tafi Malumfashi wajen bikin dan gidan Yayan Daddy din, ina zaune a daki ranar assabar da safe Hafsat ta shigo dakin, a shirye take tsaf cikin riga da siket na atamfa da dankwalin atamfar a saman kanta bata daura ba. Na kalleta da mamaki nace Hafsy ina makaranta ne yau baki je ba? Tace "hutu muke yi ai" na kalli kwalliyar

da tayi nace "ina zaki je?" ta langwabar da kai, "Yaya Nafee ke da na gaya miki yau sunan Anti Raliya kanwar Daddy?" na dan dafa kaina, "na manta ne wallahi, har zaku wuce kenan?" ta gyada kai, "mu duka fa zamu tafi, idan kina so ki zo muje" cike da jin dadi na kalleta don dama gabadaya na takura da zaman hakanan da nake yi tun safe, nace "really? Can I??" tace why not? Bari in jira ki shirya. Dama ban dade da fitowa daga wanka ba, a gaggauce na shirya,

na saka wata doguwar rigar material sky blue dinkin buba ne ta min tsaf a jikina, ban yi wata kwalliya ta azo a gani ba na shafa turare kawai na dauki gyale na yafa. Na kalli Hafsy nace "mu je?" dankwalin hannunta ta miko min tana turo baki yadda ta saba idan tana jin rigima, "dan Allah ki daura min irin yadda kika yi dinnan ranar nan?" ba musu na amsa na nada mata shi kamar gwaggwaro, ta kuwa yi kyau sosai wayata na dauka muka fara hotuna har sai da muka Ji karan horn sannan muka fita da sauri. Su duka suna cikin motar Abbu picnic yana zaune a seat din direba Anti Mubeenah a gefenshi su Abdullahi kuma a baya, ban san ko yaushe Abbu ya

dawo daga tafiyar da yayi ba don tun ranar Laraba baya nan babu mamaki jiya da dare zai dawo.
Gabadayan su suka bimu da kallo ni da Hafsy har muka shiga motar, a nutse na gaida Abbu. Thank goodness na daina jin wannan faduwar gaba da rikicewar idan ina kusa dashi, yaja motar a hankali muka bar farfajiyar gidan muka cilla kan titi. Muna baya ina nunawa su Abdullahi hotunan da muka yi ni dai Hafsy su Abbu kuma suna hirarsu shi da Anti Mubeenah kadan kadan Abbu ya kan juyo ya kallemu ko yaja Hafsy da hira har muka isa Gwamna Road inda anan ne ake sunan, ko shiga gidan Abbu bai yi ba yana ajiye mu ya juya tare da cewa bayan Magriba zai zo ya dauke mu.

Muna shiga gidan sunan su Hafsat suka yi nasu wurin ko dakin mai jego basu karasa ba. Ni da Anty Mubeenah muka karasa har uwar dakan mai jegon lokacin babu mutane ma sosai, aka dan yi en gaishe-gaishe Anty ta hakimce a gefen gadon ta janyo wayar hannunta ta fara danne-danne da kiraye-kirayen waya. Gabadaya naji na takura don bansan kowa a wajen ba gashi su Hafsat sun

bace a cikin gidan kwata-kwata, wata farar mata ta shigo itama kana ganinta Kasan er uwarsu Abbu ce don ga kama nan kamar an tsaga kara, da dan saurinta ta shigo tana mitar ina su Ni'ima suka shiga ne sun barta da aiki ita kadai? Ta kalli sauran matan dake dakin tace ku taso muje mu gama aikin samosa din can don Allah kafin rana tayi mana, duk suka mimmike yayin da Anty Mubeenah ta kara hakimcewa akan gado, ni kam ganin zan takura na tashi na bi bayan wadanda suka tashi. A can BQ suke yin aikin, na shiga na kama musu muka fara aikin suyar Samosa, Anti Amina kamar yadda naji ana kiranta ta Kalle ni tana murmushi tace "kece wadda take IT a gidan Ibrahim ko?" na gyada kaina, tace ai last week na sha labarin ki wajen Hafsat har sai da kunnuwana suka gaji. Nayi er dariya nace Ai Hafsat Akwai surutu, ta gyada kai. Kafin mu gama aikin mun saba da Anti Amina sosai, su Ni'ima suka dawo dauke da plastic robobi wadanda za a zuba soye-soyen da za ayi a ciki, kusan dukan su sa'annina ne Sa'adiya ce ta girme mu sosai don ta bamu kusan shekara uku zuwa hudu, dukansu suna jami'ar Bayero ita Ni'ima a level two tana

mass comm yayin da Sa'adiya take shekararta ta biyan karshe a BS.Kafin kace me mun saba dasu kamar wanda muka yi watanni da sanin juna, muna gama suyar samosa din muka fara shirya abubuwan a cikin robobi muna sawa a cikin Leda, abinci dama odar shi aka yo. Sai gab da la'asar muka koma cikin gidan, Anti Mubeenah bata nan wai ta tafi gidan wata er uwar su dake aure anan cikin unguwar, ina jin kananun maganganu na tashi game da halayen Anti Mubeenah din kun san taron mata ba a raba shi da kananun maganganu balle harka ta hado ku da dangin miji dama sai a hankali, ni dai nayi kunnen uwar shege dasu naki maida hankalina kansu don ba harkar shiga ta bace. Wanka muka sake yi Ni'ima ta bani wasu riga da siket na Swiss lace na saka saboda nawa na lalata su da abun fulawa sun yi fari tas. Bikin suna yaci gaba da gudana lafiya qalau, ina daga cikin masu kai da kawo na entertaining din baki, kawo abinci, dauke kaya, daukar gifts din maijego da wasu abubuwan. Duk Inda na motsa da sannun Anti Ameenah nake motsawa, naga alamu na shiga ran matar sosai. Anti Ameenah itace babbar Yayar

su Abbu kuma babbar diya a wajen Alhaji Mad'udu Galadanchi, su shida ne wajen iyayensu kamar yadda Sa'adiya take bani labari, Anti Ameenah ce babba sai Abbu, sai Anti Rahina, Aminu Yayan Sa'adiya yana Bangladesh yana karatu sai Sa'adiya da Ni'ima auta. Family din sun burge ni sosai a gaskiya, na kula da hadin kansu kwarai da gaske abin ya burge ni ba kadan ba, ina son ganin yan uwa wadanda suke kula da zumuncin su sosai.

Bamu muka samu kanmu ba sai bayan isha'i, mutane duk an tattafi sai baki na nesa da dangin maijegon na kusa, muna wani daki dake kusa dana maijegon inda anan muke bidirin mu, hira muke dasu Ni'ima lokacin da Hafsat ta leko dakin tace in fito Abbu yazo zamu tafi, na dan hade fuska jin an katse min hira mai dadi da muke yi amma haka nan na tashi saboda bani da yadda zanyi na fito su Ni'ima suka biyo bayana, dakin Anti Rahina na shiga da niyar mata sallama. Abbu na zaune a cikin falonta kusa da Anti Ameenah yayinda maijegon take zaune a kujera daya rungume da babynta da alamun

hirar en u want aka ce ake yi na durkusa na gaida Abbu tare da yiwa su Anti Ameenah sallama, Abbu ya mike nabi bayanshi. Su duka har maijegon suka fito mana rakiya, su Qaseem na jikin motar Abbu din suna jiran mu, duka muka shiga cikin motar. Su Ni'ima suka leko suna kara min sallama dama mun yi exchange din number waya dasu, Anti Ameenah ta miko min wata Leda mai dan girma tana kara min godiya tare da jaddada min in fa nemi maganin ciwon jiki in sha ina amsa mata da toh, Mai jegon MA ta leko tana min Allah huta gajiya da godiya sosai. Abbu kam baki a sake yake kallon en uwan nashi cike da mamaki, wannan shine karo na farko da suka fito wai da sunan mishi rakiya, sai daga baya ya kula ashe ma ba shi aka yiwa rakiyar ba, kulawar daya kamata ace matar shi ce suke wa sun kare da ba wata can, abinda yakamata ace matar shi ce tayi suke mata wannan yabawar wata can ce ta samu romon. Koda yake bai ga laifin su ba, Mubeenah ita tayi wasa da garinta har yayi ruwa, shi kanshi yaji haushin abinda tayi yau a wajen sunan nan, ance tunda taje ta gaida mai jegon bata kara yiwa kowa magana ba ko Anti Ameenah

bata gaida ba, daga baya ma suka ce wai ta ajiye musu dubu goma ta tafi tun kafin ayi Azuhur abinda ya bata ran Anti Ameenah kenan, ya girgiza kai cike da takaicinta, duk iya kokarin shi na ganin Mubeenah ta ra6u da dangin shi don su saba abin yaci tura.Shi har bai san me zai mata ba kuma.

Sai da muka gama sallamar mu sannan suka koma gefe suka tsaya suna kallonmu tare da daga mana hannu har Abbu yaja mota muka tafi. Tunda muka fara tafiya babu wanda yayi magana, su Hafsy tuni tayi barci akan cinya ta. Muna isa gida na ciccibe ta muka wuce Abdullahi ya dauko min ledar da Anti Ameenah ta bani, dakin Hafsy na fara wucewa na kwantar da ita. Closet dinta na bude na ciro mata kayan barci na dawo na cire mata na jikinta na saka mata wadannan, addu'ar kwanciya barci na tofa mata tare da sauka daga kan gadon a hankali gudun kar in tashe ta daga barci, ina juyawa naci karo da Abbu a bakin kofa a jingine yana kallon mu. Na sadda kaina kasa na je zan wuce ta gefenshi, packet din magani ya miko min, nasa hannu na amsa ina kallon shi cikin

alamun tambaya, yace maganin ciwon jiki ne Anti Ameenah tace in baki, ki sha kafin ki kwanta. Na gyada mishi kaina, "sai da safe koh?" ya fada yana kaucewa daga bakin kofar dakin, na bi ta gefenshi na wuce ya bini da kallo. Ina shiga dakina kayan barci kawai na saka na afa maganin a baki, sai dana bata mintuna kusan goma yadda maganin zai yi settling a jikina sannan na kwanta, babu dadewa barci ya kwashe ni, ni kaina nasan cewa a matukar gajiye nake saboda ba karamin aiki muka sha a gidan sunan nan ba.

Sai karfe goma na safe na tashi, nayi mika mai tsawo ina jin ga6o6ina kamar an bubbuge min su, kai tsaye toilet na fada nayi wanka da ruwa mai dumi, nayi brush kafin na fito. Wandon jeans na saka wanda bai kama jikina ba da shirt, na daure kitson kaina a cikin tafkeken hair band na dora hula a kaina. Falo na fito saboda wata mahaukaciyar yunwa da take nanikata, babu kowa a cikin falon haka babu hayaniyar yara nasan suna makaranta. Anti Mubeenah na hakimce a kan kujera a falon da takardu a gabanta tana buga lissafi, na durkusa

a gefenta ina gaidata. Hankalinta yana kan takardun ta amsa min, baki na dan tabe na mike, har ga Allah halayen matar basa burge ni, wata na daya a cikin gidanta amma wani idan ya ga yadda take yazga ni sai yayi zaton bakuwar jiya ce a wajenta. Kan dinning table na wuce kaina tsaye sai dai kwalam!Babu komi, cike da mamaki na tsaya ina kallon wajen a raina ina tambayar ko lafiya? A iya sani na ni dai a gidan nan ko an gama cin abinci ba a dauke kayan sai idan za a sake shirya wani meal din. Daga bayana naji Antin tana cewa "Yau bamu yi girki ba, Harira bata nan taje garinsu wajen biki. Yara ma sai oats na dama musu, kije kicin kema ki dama anjima kadan zan bada a yo take away" na jinjina kaina cike da mamaki, oats? Yaushe rabona da in sha Abinnan? Kicin din na wuce, kulolin da aka yi amfani dasu ba a wanke ba suna cikin sink har sun fara wari, nayi iya dube dube na a kicin din ban samu abu mai sauki da zan saka a bakina ba don bazan iya dama oats Inci ba, kawai ledar da Anti Ameenah ta bani jiya ta fado min a rai da sauri na koma daki na janyo ledar na bude, tarkacen su doughnuts, cake, cincin dasu biscuits ne a

ciki har da naman suna, falo na koma na bude fridge na dauko lemun exotic na dawo nayi daidai a tsakiyar daki na fara ci, sai da naji nayi nak sannan na tattare sauran na ajiye a gefen gado. Waya na dauko na bude, missed calls na gani bila adadin nasu Ni'ima dana Daddy sai wata bakuwar number da ban sani ba, su Ni'ima na fara kira suka min ban gajiya sannan na kira bakuwar number nan ashe Anti Ameenah ce, itama dai ban gajiyar ta min har sai data saka ni jin kunya yadda take ta yaba min tana sa min albarka, muna yin sallama da ita na kira Daddy, nan muka kwashe lokaci mai tsaye ina bashi labarin abubuwan da suka faru cikin week din, bayan mun yi sallama kan gado na koma na kwanta ina sake-sake, ban san iya lokacin dana dauka ina tunanika ba sai dai na bude ido naga karfe sha biyu tayi, a raina nace su Hafsat karfe biyu suke dawowa daga makaranta, and I can't stop imagining ya suke manejin oats a cikinsu fiye da awowi biyar. Cimak na tashi na fita falo, Anti ta gama lissafin nata tana zaune ne kawai tana kallon tashar CBN, na zauna a gefenta nace "Anti me za a girka ne na rana naga su Hafsat sun kusa dawowa?"

dagowa tayi tana kallona cikin wani kallo dana kasa gane ma'anar shi, ta yamutse baki kafin tace "ke har kin iya girki ne dama?" nace sosai ma, ina taya mommy idan tana yi. A raina kuwa cewa nake "a yadda nake jina akan girki Allah na tuba ai gani nake zan iya karawa ko da wani irin chef ne!" saboda ba yabon kai ba, dishes dai tun daga kan na hausa, na Yoruba da abinda ya danganci na mai jajayen kunne na kware a yin su don mommy na gwana ce in dai akan girki ne. Sai daga kare min kallo kafin tace ki dafa shinkafa da miya to, zaki iya kuwa? Na danyi murmushi kawai, da alamu gani take girki wani katoton aiki ne bata san a wajena kamar shakar ruwa ne, nace "zan iya Anti" tace to shikenan, je ki fara" babu musu na tashi na fada kicin din ina tattare hannun riga ta.

Tsaye nayi a tsakiyar kitchen din ina tunanin ta Inda zan fara, sai dana danyi sighing kafin na tunkari freezer na bude, kayan vegetables da nama ne da dangin kifi a shirye kala-kala a ciki saboda tsabar ajiya duk da cewa a cikin freezer suke amma sun fara sauya kama

musamman vegetables din. Kashe freezer din nayi yadda zan samu in ciro kaya ta sauqi, na shiga store nan ma kayan abinci ne dankare kamar a super market babu nau'in da babu daga na gida har na waje. Maimakon shinkafa da miya sai nayi fried rice wadda na wadata ta da dangin veggies, na yanka hanta kanana a ciki. Na dauko fresh sardines na wanke na yanyanka shi na soya wanda zan yi decorating din shinkafar dashi. Ina tsaye ina slicing din albasa wadda zanyi onion sauce da ita, ban ji shigowar mutum kicin din ba sai magana naji a baya na, "what are you doing here?" na juya a firgice na kalli wajen da sautin maganar ya fito. Abbu ne tsaye a kofar kicin din ya rungume hannuwa a kirjin shi yana kallona, naji na diririce da kyar na iya cewa "ammmm.... Girki?!" na fada kamar ina tambayar shi, ya shaki numfashi yana lumshe idanu, yace "woah! What a delicious smell!! meye kike dafawa haka ya cika mana hanci da kamshi?" dan murmushi na saki kadan, "fried rice ne" yace I hope kin kusa saukewa? I can't wait to taste it. Na gyada kai nan ma, nan da en mintuna zan sauke. Ya juya zai bar kicin din, "OK! I'll go and take a

shower then sai in dawo" ya karasa fita daga kicin din yana uttering "thank Goodness!" a kasan zuciyar shi, dama dawowa yayi yayi wanka ya fita ya samo musu abincin da zasu ci sai kuma yana shigowa yaji wani mahaukaciyar kamshin abinci yana fitowa daga kicin wanda ya taso mishi da yunwar shi ta kwana da kwanaki da yake dannewa da lemuka, yana shiga kicin din yaci karo da "beautiful sight' a cewar shi, tana yanka albasa a cutting board cikin kwarewa kamar irin chief cook dinnan a 5 stars hotel, da kyar ya iya suppressing din urge din daya taso mishi na aikata wani abu da yasan will never ever be appropriate, wanda yasan mawuyaci ne idan bai zubar mishi da kimar shi ba a idon yarinyar na har Abadan. Sai kawai ya buge da jingina da bango.

Ina gama yin sauce din na juye shi cikin wani kwanon tangaran, itama fried rice din sauke ta nayi don ta gama, ta min yadda nake so kuwa, wara-wara, yellow shar sai tashin kamshi take yi, na fito da babban food flask na zuba ta a ciki. Oranges na dauko manya da apple da water melon, na bare lemun na saka a juicer ta markada

min shi na tace ruwan, na yanka kankanar itama na cire yayan tas, na yanka ta kanana a cikin lemun tare da tuffa, na kawo syrup sugar na zuba a ciki na watsa kankara na fara ciccibar kayan zuwa dinning table. Ina gama shiryawa su Hafsy suka fado falon a guje da alamun gajiya a tare dasu, lokacin dana tare su sai na dinga jina kamar wata Mummy dinnan mai jiran 'ya'yanta su dawo daga makaranta, nayi kokari na kauda weird tunanin daya lullube min zuciya na karbi jakar hannun Hafsy na kai mata daki, ai ko kayan makaranta basu cire ba kowa yayi settling akan kujera na fara serving dinsu kafin na zauna a gefen Hafsy nima na fara ci. Zo kaji santi kuwa, Qaseem har da cewa wai shekarata nawa a makarantar koyon girki? Dariya kawai nake musu acan kasan zuciyana kuwa jin kaina nake a sama, me yafi yabo dadi a duniya?? Abbu ya fito daga dakinshi sanye da wandon jeans da shirt na shan iska, Shima kan dinning din yazo ya zauna. Na mike na fara serving din shi abincin yayin da yake gaisawa da iyalan shi, na zuba mishi komi na ajiye a gaban shi na koma mazaunina na zauna muka ci gaba da cin abincin mu.

Wajen cin abincin ya koma shiru, Abbu bai yi magana ba sai kai kawai da yake girgizawa, rashin magana ma yabawa ce. Sai da kowa ya cinye abincin plate din shi duka, suna gamawa kowa ya wuce dakinshi saboda ranar ba zasu koma makaranta ba. Na fara tattare plates din da muka yi amfani dasu na kai kicin, Abbu yana zaune a har a lokacin yana cin dura abinci a cikinshi cikin alamun rashin saurarawa, na fahimci matsananciyar yunwa a tattare dashi. Na kai hannu da niyar dauke jug din juice din da nayi, cikin rashin sa'a shima ya kai nashi hannun don haka nayi saurin janye nawa hannun amma duk da haka sai da hannunshi ya dan gogi hannuna, Ya Allah!! Wani irin current naji ya taba ni kamar na taba budaddiyar wayar wuta. Naja baya da sauri ina shivering, shi kam hannunshi ya kurawa idanuyana kallo kamar wani bakon abu kafin ya dago idanunshi yana kallona mai cike da ma'anoni wadanda na kasa pathorming abinda suke nufi. A hankali ya maida kanshi ga plate dinshi ya cigaba da cin abincin amma fa cikin rashin kuzari, ganin haka yasa sumi-sumi na wuce dakina kafafuna na shaking. Ina bada baya ya maida

kanshi ya jinginar da kujera yana ajiyar numfashi da sauri-sauri, what the hell did he just felt??! Yake tambayar kanshi embarrassingly.

Ina shiga dakina na zube a bakin kofa rawar da jikina yake yi ta karu, Innalillahi!! Kadai naji bakina yana furtawa da karfi, da kyar na iya daidaita natsuwa ta.Wannan wani irin abu ne haka? It's not as if ban taba gogar hannun namiji bane, God Forgive me amma ni har hugging dinsu nayi amma ban taba jin rabi rabin abinda naji ba yau da Abbu ya taba ni, ban taba jin hakan a tattare da ko wane namiji ba sai shi, ko me yasa hakan?? Ban zurfafa tunani na ba na mike na fara gyara daki na ba wai don yayi wani abu ba sai don bani da aikin yi kawai. Har bayan la'asar ina gyara, dana gama wayata na dauka na shiga dakin Hafsy, tana zaune a kasan carpet tana kokarin warware kitson kanta, na zauna a gefen gado ina kallonta, "ya ne pretty?" as usual sai data yi poutingkafin ta kalleni da dara-daran idanunta, "na manta ban fadawa daddy a kaini saloon ba har ya fita,

kuma idan Anty Kate taga kaina a haka gobe sai ta dake ni!" na shafo kitson kaina nima ina kallonta, yakamata ma in tsefe shi don ya fara tsufa. Nace "to taho in taya ki" ta waro hakora, "yauwa, kin iya kitso ai koh?" na girgiza mata kai, ta 6ata fuska, nace "noo, kar ki damu, zamu san dabarar da zaa yiwa kan yadda Anti Kate ba zata taba min ke ba koh?" ta gyada kai tare da zuwa ta zauna a kusa dani. Haka kuwa aka yi, muna gama tsifar ta dauko kayan kitso dasu ribbons na fara gyara mata kai, kalba na mata manya wadanda na kayata da ribbons din da dutsunan kitso kuma ga mamaki na yayi kyau sosai, ita kanta data kalli kanta a madubi tsalle-tsalle ta hau yi. Ni kam dariya na mata na tashi na fada kicin don yamma tayi sosai, sakwara nayi da miyar ganye, na wadata miyar da nama da busasshen kifi, na hada fruit salad na kai komi kan dinning na ajiye. Da wuri na tattaro kan yaran muka ci abincin mu kowa ya koma daki ya kwanta duk a dabara ta na kaucewa haduwa da Abbu, sai Allah ya taimake ni har na koma daki bai dawo gidan ba. Sai da na gama shirin kwanciya barci sannan

na jiyo tashin muryar su shi da Anti a falo da alamun tare suka dawo gidan.

Washegari tun da safe na fada kicin, potato chips nayi da egg sauce sai ruwan shayi wanda yasha kayan kamshi, na soyawa su Qaseem doya da kwai wanda zasu tafi makaranta dashi na zuba musu a lunch boxes dinsu, yin komi nake yi cike da kuzari da walwalata. Aikin daya jima yana burge ni kenan, kullum naje gidan Aunty Uwani ina ganin tana hadawa yaranta abincin tafiya makaranta irin haka, abin yana burge ni ba kadan ba, at last yau gashi dai nima na hadawa nawa. A gurguje na shirya na fito saboda lokaci daya fara wucewa, yanzu ma mu hudu kadai muka karya don daga Abbu din har ita Aunty din babu wanda ya fito, muka gama karin mu muka wuce makaranta.

Gabadaya kwanakin girkin gida da kula da gidan ya koma hannuna yayin da ita uwar gida mai gayya mai aiki kullum sai dai tayi rashe-rashe sai dai a dafa ta zauna

taci ta tashi ta kara gaba abun ta babu godi bare na gode, dama dama ma Abbu. Yana nuna jin dadin shi kwarai game da hakan, ina kuma shan godiya a wajen shi sosai wanda ina ga hakan ne yasa nake dagewa tun karfi na ina musu dadadan girki wadanda zasu sa zuciyar shi a farin ciki yayi ta mun addu'ar daya saba, halin Aunty kam tun ina damuwa dashi har na daina. Matar is really complicated, gane halinta da Inda ta saka gaba abu ne mai wahala kam, to mai wahala mana. Ban ka kula da cin abincin miji, baka san shan miji ba, Baka san gyara muhallin mijinka ba, ba ido na saka musu ba, amma nasan bata kwanan dakin miji, ko ina suke ko a gaban wa suke she is always making it obvious that bata damu da mijinta, rayuwar Aunty Mubeenah fa tana bukatar gyara sosai da sosai. Allah Allah nake juma'a tazo in wuce Kaduna, va wai don na gaji da hidimar da nake yi dasu ba in fact, kwanaki biyar zuwa shidan da nayi ina yiwa Abbu da iyalan shi girki has been the best and happiest moment na rayuwata, sun kara min kusanci da iyalan, sun kara min so da qaunar su kamar yadda suka kara musu sona da qaunata. Kawai dai nayi

kewan su Mommy da Daddy ne don haka ranar juma'a da wuri na dawo na hada kayan da nasan zan bukata, Abbu baya gari yayi tafiya ranar Thursday. Direba yana zuwa na fito tare da kulle gidan don babu kowa, Hajiya Aunty Mubeenah an tafi neman kudi bayan babu abinda ta nema ta rasa a gidan auren ta.

"Paradise is a home of Honor, Dignity, Rest, Satisfaction, Beauty, Joy and Peace., May Allah make it to be your permanent Home Ameeeen, Jumma'at Kareem!!"
Abinda na karanta kenan daga wayana bayan na shiga dakina, Kimanin awowi biyu da dawowa na kenan. Na duba kasan message din inda nake zaton zan ga sunan wanda ya turo text din saboda babu suna a jiki sai number kawai. 'Galadanchi!' shine sunan dana gani. Crap! Abbu ne!! Zuciyata ta hau fadi ina jin tana wani tsalle-tsalle, wayar na zurawa idanu ina lalubo abinda zan tunana amma komi ya tafi blank, na lalubo su da kyar na shiga jefawa kaina su kamar ni ce Abbu din, "Friday message kuma? Why would he?" zuciya ta tace stupid! Kuma ba zai miki message ba kike nufi ko me?

You know this is a normal thing tsakanin mutane yanzu, ke da Daddy da sauran uncles dinki ba kuna exchanging irin wannan messages din a tsakanin ku ba?? Na gyada kai a hankali kamar wawiya, sai a lokacin kuma na gano shirmen da nayi, God! I can be silly sometimes, saboda Allah addu'a ya min mai dadi amma ban amsa mishi ba na hau tuhumar dalilin da yasa ya turo min sakon. Da kwarin gwiwa ta na tura mishi amsa, 'Ameen Abbu, and same to you. How's your presentation? Allah ya dawo daku lafiya Ameen!'. Shiru har aka dauki lokaci babu reply, na daga kafada ta, watakila I've gone too far ne, meye nawa na wani tambayar yadda harkokin shi suke tafiya kamar wata shakikiyar shi? Na tabe baki na tashi daga kan kujerar dana zauna don wai da zama nayi ina jiran amsar shi kamar wata sakara. Kayan jikina na shiga cirewa ina jifa dasu cikin laundry bin, na daura towel a jikina nazo fada bathroom.

☆☆☆☆☆☆☆☆

Idanunshi kur akan wayar yana kallo cikin wani irin yanayi, kalmomi ne da rabon daya jisu daga bakin matar auren shi har ya manta su, anya ma ya taba jin su kuwa? Ta yaya ma aka yi tasan cewa presentation yaje? He can't recall telling her, wani sashe na zuciyar shi yace ba mamaki wajen su Pretty taji don ya kula tana son yarinyar sosai, yana mamakin yadda idan suna hira da Hafsy take maida kanta kamar yarinyar har ka kasa tantance yaro da babba a cikinsu. Ya lumshe idanu a hankali...... Bai san cewa ya zurfafa a tunani ba sai daya ji muryar Chairman dinsu ta microphone, "Dr. Galadanchi?? Anything from you??" yayi firgigit ya dawo daga duniyar imagination daya tafi, "yeah of course Mr. Collins..." ya jefa wayar shi a aljihu ya dauki wasu takardu ya tafi kan step fara bayani a nutse....

●●●●●●●●●●

Wannan weekend din ziyara nayi, naje gidan Anti Uwani na musu yini a can, daga nan ni da AbdulJalal muka shiga gari sai bayan isha'i ya sauke ni a gida bayan mun

tsaya a Mcbae mun sayi tarkacen chocolates da ice cream. Washegari lahdi sai wajen karfe biyar na bar gida cike da kewar Mom da Dad, amma fa can kasan zuciyana wani farin ciki da doki ne dankare a cikinta, dokin in koma inci gaba da yiwa Abbu dadadan girki na yana ci yana yaba min har da santi. Sai dai koda na isa sai na tarar Hareera ta dawo daga biki, Abbu kuma baya gari, gwiwa na yayi sanyi sosai, jiki a sanyaye na shige daki na.

Washegari a tsaitsaye muka ci abinci muka wuce makaranta, ranar mun sha ayyuka a lab kamar me! A matukar gajiye muka zauna akan dakalin da muka saba zama ni da Ramlah cikin dan garden din da muke hutawa, na kalle ta ina dan murmushi, "ke jiya fa muka hadu da Muneer" bata nuna alamun abun ya dadata da kasa ba kamar yadda nayi zato, tayi fuskar shanu tace a ina? Nace "McBae, mun shiga siyayya ni da AbdulJalal. God! Baki ga yanda gayen nan ya kara kyau ba, yayi fari yayi kiba sosai, I think he misses me so much, kin kuwa ga irin fara'ar daya dinga min? Rabona da in....." tayi saurin katse ni, "ai fa kin kika fara bada labarin Muneer

kamar wata radio mai jini ba kya ko son kiyi shiru, to sai ki tashi an zo daukar ki" na kalli inda suka saba tsayawa idan suka zo, gabana ya fadi sosai, Abbu ne yazo daukar mu! Ganin Qaseem ya fito yana tunkarar wajen da nake yasa na mike ina lalubar jakata nawa Ramlah sallama. A hankali kuma a sanyaye na bude bayan motar na shiga, "Abbu ina yini?" na furta cikin sisiriyar murya ta, ya amsa "lafiya qalau Nafeesah, ya kika baro Kaduna?" na amsa da lafiya lau. Yaja motar muka tafi babu mai furta uffan. Hafsat ce ta ciro drawing book dinta daga cikin school bag dinta tana nuna min Assignment din dana taya ta jiya akan zanen gidaje da motoci, tace "Kuma Uncle Jamilu yace ni na cinye 20 over 20 duk cikin class din" na shafa kanta ina murmushi, "Ohh that's very good princess, am proud of you" tayi dariya tana kwantowa a jikina na rungume ta. Muna isa gida sallah muka yi, na bude fridge na ciro fura da nono dana kawo daga gida, musamman Mommy ta bada aka yi, na zauna na dama ta da dan kaurinta na saka kankara da dan sugar, cups na dauko na zuzzubawa su Abdullahi. Muna zaune a falo muna sha kafin lokacin zuwa Islamiyar su

yayi. Abbu ya fito daga daki hannunshi dauke da jakar laptop dinshi, dan karamin coffee table din dake gefen mu ya janyo ya dora laptop din nashi akai, kasa kasa yake kallon mu har ya zauna. Ya kalli kofin dake hannuna yace meye wannan kuke sha haka babu tayi? A kunyace nace fura ce! Idanunshi suka dan ware cikin mamaki, "wow, daga ina muka samu fura?" Hafsat tayi caraf tace "daga gidansu tazo da ita jiya!" ya jima sosai idanunshi suna kaina ban san ko tunanin me yake yi ba, ya kauda kanshi ya maida shi ga laptop dinshi, "tunda ba a mana tayi ba ni zan yiwa kaina, a bani idan da akwai" da sauri na tashi naje na dama mishi na kawo na ajiye mai a gefenshi. Su Hafsy suna wucewa makaranta na koma dakina na zauna ina kallo.

Tara da rabi ta nuna lokacin dana kalli agogo, nayi mika ina hamma ina jin kasusuwan jikina na amsawa saboda gajiya, ban kai ga kwanciyar da nayi niyar yi ba na jiyo kamar muryar Abbu a
falo yana kwala min kira. Na saurara sosai har zuwa lokacin dana sake jin wani kiran kafin na warci hijabi na

zura na fita, yana kan dinning a zaune yana kokarin rufe daya daga cikin food flasks din da aka ajiye akai, ya kalleni fuskar shi dauke da wani irin expression dana rasa ko wani iri ne; na jin haushi ne, embarrassment ne ko fusata? Shi dai ya bar wa kanshi sani. Na dan duka a gefenshi nace Abbu gani a sanyaye. Sai da yayi gyaran murya sannan yace "Please samo min noodles ko simple abu da zan ci, am quite hungry" na danyi jim kamar ba zan tashi basuna da er aiki, yana da matar shi, ba za a ga laifi na ba idan na tashi na fada kicin na dafa mishi abinci? Koda yake ban ga laifin shi ba, abincin da Hareera tayi yau yadda kasan faten shinkafa saboda yadda shinkafar ta cafke, ita kanta Anty Mubeenah sai data mata fada yau dai har da ce mata idan ba zata gyara ba to lallai tana gab da barin gidan don ita ta gaji haka nan.... Abbu ya dan sake gyara murya ya kalle ni, "well??" nayi saurin dawowa cikin hankali na, "umh.... Dama zan ce ne noodles din kadai ta isa?" ya gyada kai, da sauri na tashi na wuce kicin cikin hardewar kafafu, zuciyana na gaya min cewa idanunshi shi a kaina suke. Tukunya na dora akan gas na hada duk abubuwan da

nake bukata, ruwan yana tafasa na zuba indomie a ciki na kara da sardines, na dora ruwa a cikin kettle na zuba danyar citta da kanumfari er garlic don naga alamun kamar mura tana dan damun shi. Ina sauke indomie din na soya kwai na dora a sama, na juye shayin a cikin flask na dora duka kayan akan tray mai fadi na fita. Yanzu ya dawo tsakiyar falon ya zauna hannunshi rike da waya yana karatun labarai, na ajiye su a gefenshi na tura indomie din gaban shi da fork a ciki, na dauki kofi na tsiyaya shayin na mika mishi, shayin ya fara kaiwa bakin shi, ya dan yamutse fuska yana kallon shayin jin kamshin tafarnuwa na tashi, da sauri nace "umh... Naga kamar kana mura ne shine....." na kasa karasawa saboda kalmomin sun kare min kuma sai ya girgiza kai kawai ya fara kurbar shayin a hankali. Naje na dauko mishi ruwa da lemu irin wanda naga yana sha masu rangwamen sanyi a cikin fridge na kai na ajiye a gefenshi, "Abbu kana bukatar wani abu kuma?" ya girgiza kanshi, "babu Nafeesah, nagode. Sai da safe koh?" na tashi da sauri na bace a wajen. Duk zaman da nayi jina na dinga yi kamar akan kaya, zuciyana wani

irin duka take kamar zata tsaga kirjina ta fito, ban san me yasa Abbu yake da wani irin effect a kaina na saka ni cikin rashin natsuwa ba.

Washegari ba laifi anyi abinci mai sense don mun zauna mun ci sosai, Abbu ya kalle ni yana ajiye spoon din hannunshi, "Nafeesah ko zaki iya dora min shayi irin na jiya?" a hankali na saci kallon Inda Anty take zaune, abincin ta take ci Hankalinta kwance kamar bata san Allah yayi ruwan tsirar mu a wajen ba. Na dan jijjiga kai na tashi, cikin mintunan da basu gaza bakwai ba na gama na juye a cikin flask, na hada da cup na fito falon. A gaban shi na ajiye su, ya kalle ni yana furta thanks! Kafin ya kalli su Hafsy, "oya a tashi a tafi koh? Malam Bala yazo" duk suka mike kowa yana daukar school bag din shi, muka musu sallama muka tafi.

Muna zaune da Ramlah a lab muna hira na kalleta, "babe ya za ayi ne? Ina bukatar wankin kai da kitso fa kaina yayi datti wallahi" tace ba damuwa, idan mun tashi sai mu biya ta saloon din Anty Haleemah, nima ranar

Saturday naje aka wanke min" nace "to shikenan". Muna tashi kuwa Allah yasa su Malam Bala sun zo kenan, nace su wuce gida kawai ni Akwai inda zani. Muka je saloon aka wanke min kaina aka min kitso, da yake ba laifi Masha Allah ina da gashi sosai, Mommy irin bakaken fulanin nan ne, na gado zubi da kira irin tasu da kuma yalwar gashi,kalar fatar jikina kuma ta daddy ce, haka dangin shi suke wankan tarwada duk da cewa Akwai farare, kyawawan dara-daran idanu farare tas da bakaken eyelids, dogon dan siririn hanci kamar an zana da biro, dan karamin zagayayyen baki da jerarrun hakora kanana kuma farare tas da er siririyar wushirya a tsakiyar su. Muna gamawa da saloon gidan Anty Haleemah muka wuce, gidan flat ne dan madaidaici mai kyau dakalin ganshi kaga gidan mutum daya. Mijinta navy ne don haka bai cika zama a gidan ba, tare suke zaune da kanwar mijinta Khaleesat, mun dan saba da ita saboda a cikin BUK take karatu, tana yawan zuwa wajen Anti Haleemah din. Danta daya Mahmoud, nan muka wuni a gidan sai bayan Magriba ta hada ni da direba ya maida ni gida, kafin mu isa tuni an kira sallar

isha'i. A bakin gate ya ajiye ni, na gaida maigadin gidan na wuce ciki. A hankali na tura kofar falon na shiga baki na dauke sallama, babu kowa a cikin falon. Na maida kofar na rufe na fara tafiya zuwa dakina, kamar daga sama naji maganar, "Where the heck have you been???". A gigice na juya, Abbu ne zaune akan kujera yana kallona kamar a fusace? Cikina ya bada sautin kululu.... It seems like m in trouble.

Ya Allah! Cheerful Abbu din dana sani ya tafi, wannan Abbu din ban taba ganin shi ba, a fusace yake sosai kamar wanda zai tashi daga zaunen da yake ya hau ni da bugu, gabadaya jikina ya dauki rawa hawaye suka ciko idanuna, bana son fada ko kadan a rayuwata. Cikin rawar murya irin ta wanda yake so ya fashe da kuka nace, "Naje saloon ne shine na biya gidan su kawata Ramlah" ya galla min harara, "da ixinin wa??" nace "umh, ai na fadawa su Malam Bala da suka zo dauka na dazu", yayi shiru kawai yana kallona. Malam Bala ya fada mishi tun dazun, that means he have no right to be angry at her, but still, he's just pissed up. Dan siririn

tsaki yaja ganin har na fara shesshekar kuka, ya shafa tattausar sumar kanshi da a koda yaushe a gyare take tana sheki, "it's okay....Bani ruwa a fridge" da sauri naje na dauko na kawo mishi, yasa hannu ya amsa fuskar shi har lokacin a murtuke, ganin nayi tsaye naki in tafi yasa ya juyo yana kallona, "what?" he sounds so pissed up at me, da sauri na hau share kwallar data fara xubo min again nace "Abbu don Allah kayi hakuri, wallahi ba zan kara ba don Allah" ya lumshe idanunshi a hankali, "it's okay Nafeesah, banji dadin abinda kika yi ba, a gidanku kina kai har Magriba a waje?" nayi saurin girgiza kai, "to me yasa a gida na? Saboda kin raina ni ne ko kuma don kin baro gidanku kina tunanin zaki yi duk abinda kike so anan ba tare da an miki fada ba?" nan ma kai na girgiza a hankali nace "tun dazu muka taho, gidan Akwai dan nisa ne daga yau" yace "bana tolerating abubuwan nan Nafeesah kin gane? Daga yau kada ki sake wuce bayan Magriba a waje...... No! Duk inda zaki fita you must tell me first indai kina cikin garin Kano, understand?" nayi saurin jijjiga kaina, yace "you can go now!" kamar wadda take akan kaya, da sauri na wuce dakina. Sallah

na fara yi kafin na kira mommy muka gaisa, labarin abinda ya faru na shiga bata, budar bakinta cewa tayi "ai yayi min daidai wallahi, wato har kin fara yawo barkatai ko?" sai lokacin naga wautata dana fada mata, na batan fuska kamar ina gabanta tare da turo baki, "mommy! Saloon fa naje saboda Allah daga can na wuce gidan su Ramlah, Ramlah ce fa kawata ke kanki kin shaida sau nawa take zuwa gidan mu ta kwana?" tace "but still baby, bai kamata ki tafi ba tare da kin fada mishi ba, kin san dole ranshi ya baci dama" na shiga diddira kafata a kasa ina gunaguni, "ni dana sani dama ban fada miki ba tunda ba zaki goyi bayana ba" ta sassauta muryar ta, "Ohh Nafeesah baki fahimta koh? Ba goyon bayan shi nayi ba, it's just the fact. Ke yanzu amanar muce a hannunsu, kina ganin ya dace ya barki ki dinga fita kina dawowa duk lokacin da kika ga dama a garin da yake bakon ki iye? Ko kina ganin girmamawa ce ki kama hanya ki fita ba tare da kin sanar dashi ba? Wani Malam Bala is not an excuse tunda ba a karkashin kulawar shi kike ba kin gane?" na gyada kaina a hankali she's right. Muryar daddy na jiyo ta cikin wayar,

"Habibty ke da waye kuke waya kika kyale ni ni kadai a falo?" da sauri na shiga mata magiya akan Kar ta fada mishi hirar da muke don nasan kadan daga cikin aikin Mommy ne, ta ba daddy din muka gaisa. Hira muka shiga yi yawanci ta wajen aikin shi ce, mun jima sosai kafin muka yi sallama dasu. Kayan barci na na zura na bi lafiyar gado ko abinci ban nema ba.

Ina kan sallaya ina lazumi bayan nayi sallar asubahi, ban cika komawa barci ba a irin wadannan lokutan, kofar dakin naji ana kwankwasawa, na tashi naje na bude, Harira ce. Muka gaisa da ita a mutunce tace "dan Allah Nafeesah ko zaki taimake ni da girkin yau? Bana jin dadi ne" nayi fuskar tausayi nace "Eyyah sorry pa! Meye za a dafa?" tace "ki dafa duk abinda kika ga ya dace nace "to shikenan" tace nagode ta wuce dakinta. Daki na koma na dauko karamar hijabi data tsaya a kuguna na saka na fita zuwa kicin, yam delight nayi, kafin dahu sai na dauko fresh kifi a cikin fridge na fara shirin yin farfesun kifi.

Da gudu na karasa wajen shi na riko hannunshi dake rike da brief case, tambayoyi nake watsa mishi ba kakkautawa, "Abbu lafiya? Abbu mai ya samu kafar ka? Abbu accident kayi a kan hanya?!....." ya zauna akan kujera yana maida numfashi, "it's just a minor targade, an gyara min. Kar ki damu" jin hanyaniya su Hafsy duk suka fito daga dakunan su, ganin halin da yake ciki tuni Hafsy ta fara kuka, sai da Abbu ya jata jikinshi ya rarrashe ta sannan tayi shiru. Ya kallemu duk munyi carko-carko a gabanshi muna muzurai, bai san sanda ya saki dan murmushi ba. "nace muku lafiya ta lau guys, oya Nafeesah dauko min abinci anan zan ci" jiki ba kuzari na koma na zubo mishi iya wanda zai iya ci na dora akan karamin coffee table na kai mishi, na koma kicin na dauko ruwa shima na ajiye mishi. Mu kuma muka koma kan dinning table muna cin abincin amma fa hankulan mu suna kanshi, muna cikin ci Anty Mubeenah ta fito daga dakinta, hankalina yana kanta har ta tsaya kusa da Abbu kamar suna yin magana ne, ta kalli kafar shi da yake nuna mata ta yi magana kafin ta nufo kan dinning din. Duk muka gaishe ta kafin muka

koma wa cin abincin mu. Muna gamawa na tattara komi na kai kicin na wanke kayan tas na dawo falo, Abbu baya falon, na zauna ni dasu Abdullahi muka danyi kallo kafin na musu sallama na tafi dakina. Shirin kwanciya barci nayi na janyo wayana na shiga chats da friends dina ta whatsapp, dp din Muneer naga ya dora hoton wata kyakkyawar yarinya matashiya da alamun ta dan girme ni, naji wani abu ya soke ni a makogaro, kasa daurewa nayi na tura mishi tambayar "who is she?" mintuna biyu kyawawa kafin reply ya shigo, "a sister" nayi ajiyar numfashi lokacin dana ji wani sukuni yana ratsa ni, "Ohh! Ashe sistern ka ce.... Ya kake?" muka danyi chatting sama sama kafin ya min sai da safe wai barci yake ji, ni kuwa har da tura mishi hearts da clouds. Yana sauka nima na kashe wayana don dama saboda shi na tsaya.

Washegari ta kama daya ga watan mayu, public holiday ne don haka muna gida. Sai wajen karfe goma na fito daga dakina, nayi break fast na koma daki nayi wanka

na sake fitowa falon. Su Qaseem suna zaune yanzu suna game, na zauna a tsakiyar su muka fara bugawa. Muna nan zaune muka ci karan intercom, Abdullahi yaje ya bude, sai gasu sun shigo shi da Aunty Ameenah. Da sauri na mike tsaye ina mata sannu da zuwa har ta zauna akan kujera, na shiga kicin na dauko mata lemu da ruwa na kawo mata, gaishe ta nayi ta amsa da fara'ar ta na koma gefe ina kallonta, wannan shine karo na farko da naga wani dan uwan Abbu a gidan tunda nazo. Qaseem ta tura yaje ya gayawa Abbu tazo, tare suke fito dashi, har yanzu yana dingisa kafar shi.

Na bishi da kallo cike da tausayi har ya zauna, na gaida shi tare da mishi ya jiki ya amsa. Aunty Ameenah tace "tare muka zo da Abban Ikhlas, zai shigo ya duba maka kafar" na kai dubana ga kafar tashi, sai da cikina ya kada ganin yadda kafar ta kumbura suntum! Ya yamutsa fuska "kema na fada miki ba wani abu bane ba, targade ne an gyara min shi kuma, kumburin saboda targaden ya dade a jikina ne shi yasa" ta Harare shi, "ai ba cewa nayi kayi lecturing dina ba koh?" ta daga wayarta ta kira wata lamba, ba a jima ba wani kamilallen mutum da zai

yi sa'an daddy na ya shigo falon, ya ba Abbu hannu suka gaisa. Kafar tashi ya kalla yana girgiza kai, "Anya haka zamu yi da kai kuwa Farfesa?" Abbu ya rausayar da kai kamar wani karamin yaro, "AbbanIkhlas kawai neman rigima ne irin na matar nan taka, sai dana fada mata targade ne amma taki yarda" ya kara kallon wajen, "anya targade anan wajen kuwa? Bari dai mu duba mu gani" ya fiddo kayan aiki, wata er karamar naura ya fiddo ya jona da wani abu, ya kara abun a kafar Abbu sai ga komi na kafar dake kasan fatar shi ya fito a jikin na'urar, amma babu abinda muka fahimta tunda ba profession dinmu bane, ya gama dube-dubenshi ya daga ido ya kalli matar shi, "tsagewar kashi ce!!" ta zaro idanu yayin dana dafe kirji, yace yanzu bari in kira mai gyara yazo tukun. Muna nan zaune jugum-jugum har mai gyaran yazo, har kuma zuwa lokacin bamu ga ko giccin Anty Mubeenah a cikin falon ba. Wani dan tsamurmurin farin dattijo ya shigo falon, maigadi wanda ya rako shi ya duba jikin uban gidan shi kafin ya juya ya fita. Mai gyaran ya fiddo kayan aiki ya fara, yana taba kafar Abbu na saki kara saidsai da duk suka juyo suka kalleni, jikina

rawa yake, tsigar jikina tana tashi, Ji nake kamar nice naji ciwon. Abbu yace mu tashi mu koma daki amma fir naki, ganin mun ki tashi yasa ya kyale mu. Tunda aka fara gyaran kuka nake har da jan shessheka, ganin ina kuka sai Hafsy itama ta fara, nan da nan falon ya karade da kukan mu ni da ita, Anty Ameenah dariya ma ta hana ta lallashe mu. Mai gyaran ya gama gyaran da zai yi yawanci fara maida tarkacen kayan gyaran cikin jaka yana dan murmushi, "da alamun amaryar ce koh?" ya tambaya yana kallon Abbu, kusan a lokaci guda shi da Aunty Ameenah suka ce "ehhh?? Aah!!" ya bisu da kallon mamaki kafin ya murmusa yace to Allah ya kara sauki. Ya dauki jakarshi ya saba a kafada ya mike, mijin Anty Ameenah ta rufa mishi baya. Abbu ya kalleni a sanyaye, "bani ruwa Nafeesah!" da sauri na mike har ina hardewa, na dauko ruwan na kawo mishi na koma kusa da Hafsy na zauna.

Mijin Anty Ameenah yana dawowa falon ya mana sallama ya tafi, Anty Ameenah ta dan taka mishi kafin ta dawo suka hau hira da Abbu. Mu kam muna zaune

muna kallon news don in Abbu yana falo bamu cika kallon tashoshi barkatai ba, motsi kadai zai yi in Allah ya yarda da sannu na yake motsawa, bana ji a rayuwata na taba jin irin wannan feeling na 'protecting' da 'caring' ga kowane Bil'adama irin Abbu ba. Aka kira sallar Azuhur, Anty Ameenah ta umarce mu da mu tashi muje mu yi sallah, duk muka mike, mazan har Abbu suka fita zuwa masallaci ni kuma na tashi zan wuce dakina, Hafsy tana kan kujera tana barci, har na kai tsakiyar falon sai na juya na kalleta, "Anty ko zaki shigo kiyi sallah a daki na?" ta kalleni tana dan murmushi, "Eyyah, hutu nake yi Nafeesah, je ki abinki" a dan kunyace da jin kalamanta na juya. Ina gama sallah na koma falon, ina zama suma su Abbu suka shigo, muka bi Abbu da sannu ni da Anty Ameenah har ya zauna akan kujerar daya tashi. 'yar aikin gidan ta fito da niyar dora abincin rana, bata san abinda yake faruwa a gidan ba, ita dai taga bakuwa ta gaishe ta sannan ta wuce kicin abinta. Muna nan zaune sai ga Anty Rahina ta shigo goye da danta a baya, na tashi da sauri ina mata sannu da zuwa, hannu na mika

a bayanta ta sauko min da babyn, na rungume shi tsam a jikina, Ya Allahu!!
Ina son yara kamar me!
Anty Rahina ta zauna a gefen Abbu, sannu take jera mishi kamar bakinta zai tsinke na kula suna matukar ji da kanin nan nasu, fuska cike da damuwa take kallonshi, "me ya faru Ibrahim? Garin Yaya??" yayi shiru kawai yana kallonta, to me zai ce??

Flashback
Yana tsaye a bakin titi a kokarinshi nason yayi crossing ya shiga wani babban shopping mall a garin Lagos kafin su taho ya tuno da ita, haka kawai ya tsinci kanshi da son yi mata tsaraba ko don shima ya faranta ranta yadda itama take faranta mishi ta hanyar yi mishi dadadan girkegirke masu kara lafiya. Don haka ne ya ciro wayar shi ya tura mata da text.
"......yes, In shaa Allah. A dawo lafiya Allah ya kiyaye hanya....". Reply din data dawo mishi dashi kenan, yayi murmushi sosai, har kullum kulawar yarinyar zuwa gare

shi tana matukar burge shi ba kadan, tunanin amsar da zai tura mata yake yi lokacin da aka ba wadanda suke kasa hannu su wuce, taku daya biyu yayi, bai tantance mai ke faruwa ba sai jin shi yayi kwance a kasa rike da kafar shi ta dama, ashe yabi ta wrong way ne, daidai lokacin an ba ababen hawa dake wajen hannu, ba tare da su duka sun kula ba wani mai mashin yabi ta kan kafar shi ya wuce.....!

Yaja numfashi a hankali bayan ya gama tunano abinda ya faru, kallonta yayi yana dan murmushi,
"kawai ikon Allah da tsautsayi" ta girgiza kai, "to Allah ya kara kiyayewa" duk muka amsa da Ameeeen. Maigadi yayi sallama ya shigo dauke da manyan kuloli, Malam Bala ya biyo bayan shi rike da wasu, Anty Rahina ta umarce su dasu kai kan dinning su ajiye, suka ajiye suka juya. Ta kalli Abbu, "na dafo maka abinci daga gida, kana jin yunwa ne?" ya gyada kai, ta mike "bari in zubo maka toh" da sauri na mike ina kara rungume Baby Jameel a hannuna, "Anty bari in zubo mishi" tayi

murmushi tace to shikenan. Ta koma ta zauna ni kuma na wuce kicin. Harira nata kokarin hada miya, nace "kiyi abincin kadan fa, Anty Rahina ta kawo abinci" tace to shikenan. Na kwashe plates da spoon da zasu isa na koma falo, na zubawa Abbu abincin na kai mishi kafin na koma na zubowa su Anty Ameenah, ni da yara kuma muka hau dinning. Anty Mubeenah ta fito daga dakinta, na kalli agogo. No wonder! Lokacin cin abinci yayi ai! Ganin su Anty Ameenah a falon sai data danyi turus! Kafin ta karasa, ta zauna akan kujerar dake kusa data Anty Ameenah tana dan murmushin yake, wai "su Yaya Ameenah ne? Ai ban san kuna gidan ba, ina daki ina ta barci" Anty Ameenah ta danyi murmushi, "Allah sarki! Muma mun zo duba mai jiki ne ai" tayi shiru kanta a kasa, Anty Rahina kam bata tanka ba Hankalinta na ga shayar da dan jariri. Ta gama kame-kame dai ta tashi tazo ta zuba abinci ta fara ci, Kai kawai nake girgizawa, rayuwar Auren bayin Allahn nan tana da matukar daure kai.Ita ta fara tashi daga kan dinning din, sai dai wannan karon maimakon ta koma dakinta, kan daya daga cikin kujerun falon ta koma ta zauna. Muma muna gama cin

abincin na kwashi kayan da muka bata na kai kicin na sake dawowa falon, Baby Jameel kamar yadda nake kiranshi tunda suka shigo na amsa daga hannun maman shi, yaron ya bude idanunshi farare tas Mashaa Allah dasu yana ta walainiya dasu a tsakiyar falon, Ji nake kamar in lashe shi saboda yadda yake burge ni. Na fara jujjuya shi ina jan kumatun shi ina mishi en wasanni kafin na fara manna mishi kisses a kumatu, Abbu ya maida kanshi jikin kujera ya kwantar idanunshi a lumshe; "What he'll pay to become that baby!!".

Da gudu na karasa wajen shi na riko hannunshi dake rike da brief case, tambayoyi nake watsa mishi ba kakkautawa, "Abbu lafiya? Abbu mai ya samu kafar ka? Abbu accident kayi a kan hanya?!....." ya zauna akan kujera yana maida numfashi, "it's just a minor targade, an gyara min. Kar ki damu" jin hanyaniya su Hafsy duk suka fito daga dakunan su, ganin halin da yake ciki tuni Hafsy ta fara kuka, sai da Abbu ya jata jikinshi ya rarrashe ta sannan tayi shiru. Ya kallemu duk munyi carko-carko a gabanshi muna muzurai, bai san sanda ya

saki dan murmushi ba. "nace muku lafiya ta lau guys, oya Nafeesah dauko min abinci anan zan ci" jiki ba kuzari na koma na zubo mishi iya wanda zai iya ci na dora akan karamin coffee table na kai mishi, na koma kicin na dauko ruwa shima na ajiye mishi. Mu kuma muka koma kan dinning table muna cin abincin amma fa hankulan mu suna kanshi, muna cikin ci Anty Mubeenah ta fito daga dakinta, hankalina yana kanta har ta tsaya kusa da Abbu kamar suna yin magana ne, ta kalli kafar shi da yake nuna mata ta yi magana kafin ta nufo kan dinning din. Duk muka gaishe ta kafin muka koma wa cin abincin mu. Muna gamawa na tattara komi na kai kicin na wanke kayan tas na dawo falo, Abbu baya falon, na zauna ni dasu Abdullahi muka danyi kallo kafin na musu sallama na tafi dakina. Shirin kwanciya barci nayi na janyo wayana na shiga chats da friends dina ta whatsapp, dp din Muneer naga ya dora hoton wata kyakkyawar yarinya matashiya da alamun ta dan girme ni, naji wani abu ya soke ni a makogaro, kasa daurewa nayi na tura mishi tambayar "who is she?" mintuna biyu kyawawa kafin reply ya shigo, "a sister" nayi ajiyar

numfashi lokacin dana ji wani sukuni yana ratsa ni, "Ohh! Ashe sistern ka ce.... Ya kake?" muka danyi chatting sama sama kafin ya min sai da safe wai barci yake ji, ni kuwa har da tura mishi hearts da clouds. Yana sauka nima na kashe wayana don dama saboda shi na tsaya.

Washegari ta kama daya ga watan mayu, public holiday ne don haka muna gida. Sai wajen karfe goma na fito daga dakina, nayi break fast na koma daki nayi wanka na sake fitowa falon. Su Qaseem suna zaune yanzu suna game, na zauna a tsakiyar su muka fara bugawa. Muna nan zaune muka ci karan intercom, Abdullahi yaje ya bude, sai gasu sun shigo shi da Aunty Ameenah. Da sauri na mike tsaye ina mata sannu da zuwa har ta zauna akan kujera, na shiga kicin na dauko mata lemu da ruwa na kawo mata, gaishe ta nayi ta amsa da fara'ar ta na koma gefe ina kallonta, wannan shine karo na farko da naga wani dan uwan Abbu a gidan tunda nazo.

Qaseem ta tura yaje ya gayawa Abbu tazo, tare suke fito dashi, har yanzu yana dingisa kafar shi.
Na bishi da kallo cike da tausayi har ya zauna, na gaida shi tare da mishi ya jiki ya amsa. Aunty
Ameenah tace "tare muka zo da Abban Ikhlas, zai shigo ya duba maka kafar" na kai dubana ga kafar tashi, sai da cikina ya kada ganin yadda kafar ta kumbura suntum! Ya yamutsa fuska "kema na fada miki ba wani abu bane ba, targade ne an gyara min shi kuma, kumburin saboda targaden ya dade a jikina ne shi yasa" ta Harare shi, "ai ba cewa nayi kayi lecturing dina ba koh?" ta daga wayarta ta kira wata lamba, ba a jima ba wani kamilallen mutum da zai yi sa'an daddy na ya shigo falon, ya ba Abbu hannu suka gaisa. Kafar tashi ya kalla yana girgiza kai, "Anya haka zamu yi da kai kuwa Farfesa?" Abbu ya rausayar da kai kamar wani karamin yaro, "AbbanIkhlas kawai neman rigima ne irin na matar nan taka, sai dana fada mata targade ne amma taki yarda" ya kara kallon wajen, "anya targade anan wajen kuwa? Bari dai mu duba mu gani" ya fiddo kayan aiki, wata er karamar naura ya fiddo ya jona da wani abu, ya kara abun a kafar

Abbu sai ga komi na kafar dake kasan fatar shi ya fito a jikin na'urar, amma babu abinda muka fahimta tunda ba profession dinmu bane, ya gama dube-dubenshi ya daga ido ya kalli matar shi, "tsagewar kashi ce!!" ta zaro idanu yayin dana dafe kirji, yace yanzu bari in kira mai gyara yazo tukun. Muna nan zaune jugum-jugum har mai gyaran yazo, har kuma zuwa lokacin bamu ga ko giccin Anty Mubeenah a cikin falon ba. Wani dan tsamurmurin farin dattijo ya shigo falon, maigadi wanda ya rako shi ya duba jikin uban gidan shi kafin ya juya ya fita. Mai gyaran ya fiddo kayan aiki ya fara, yana taba kafar Abbu na saki kara saidsai da duk suka juyo suka kalleni, jikina rawa yake, tsigar jikina tana tashi, Ji nake kamar nice naji ciwon. Abbu yace mu tashi mu koma daki amma fir naki, ganin mun ki tashi yasa ya kyale mu. Tunda aka fara gyaran kuka nake har da jan shessheka, ganin ina kuka sai Hafsy itama ta fara, nan da nan falon ya karade da kukan mu ni da ita, Anty Ameenah dariya ma ta hana ta lallashe mu. Mai gyaran ya gama gyaran da zai yi yawanci fara maida tarkacen kayan gyaran cikin jaka yana dan murmushi, "da alamun amaryar ce koh?" ya

tambaya yana kallon Abbu, kusan a lokaci guda shi da Aunty Ameenah suka ce "ehhh?? Aah!!" ya bisu da kallon mamaki kafin ya murmusa yace to Allah ya kara sauki. Ya dauki jakarshi ya saba a kafada ya mike, mijin Anty Ameenah ta rufa mishi baya. Abbu ya kalleni a sanyaye, "bani ruwa Nafeesah!" da sauri na mike har ina hardewa, na dauko ruwan na kawo mishi na koma kusa da Hafsy na zauna.

Mijin Anty Ameenah yana dawowa falon ya mana sallama ya tafi, Anty Ameenah ta dan taka mishi kafin ta dawo suka hau hira da Abbu. Mu kam muna zaune muna kallon news don in Abbu yana falo bamu cika kallon tashoshi barkatai ba, motsi kadai zai yi in Allah ya yarda da sannu na yake motsawa, bana ji a rayuwata na taba jin irin wannan feeling na 'protecting' da 'caring' ga kowane Bil'adama irin Abbu ba. Aka kira sallar Azuhur, Anty Ameenah ta umarce mu da mu tashi muje mu yi sallah, duk muka mike, mazan har Abbu suka fita zuwa masallaci ni kuma na tashi zan wuce dakina, Hafsy tana kan kujera tana barci, har na kai tsakiyar falon sai na

juya na kalleta, "Anty ko zaki shigo kiyi sallah a daki na?" ta kalleni tana dan murmushi, "Eyyah, hutu nake yi Nafeesah, je ki abinki" a dan kunyace da jin kalamanta na juya. Ina gama sallah na koma falon, ina zama suma su Abbu suka shigo, muka bi Abbu da sannu ni da Anty Ameenah har ya zauna akan kujerar daya tashi. 'yar aikin gidan ta fito da niyar dora abincin rana, bata san abinda yake faruwa a gidan ba, ita dai taga bakuwa ta gaishe ta sannan ta wuce kicin abinta. Muna nan zaune sai ga Anty Rahina ta shigo goye da danta a baya, na tashi da sauri ina mata sannu da zuwa, hannu na mika a bayanta ta sauko min da babyn, na rungume shi tsam a jikina, Ya Allahu!! Ina son yara kamar me!

Anty Rahina ta zauna a gefen Abbu, sannu take jera mishi kamar bakinta zai tsinke na kula suna matukar ji da kanin nan nasu, fuska cike da damuwa take kallonshi, "me ya faru Ibrahim? Garin Yaya??" yayi shiru kawai yana kallonta, to me zai ce??

Flashback

Yana tsaye a bakin titi a kokarinshi nason yayi crossing ya shiga wani babban shopping mall a garin Lagos kafin su taho ya tuno da ita, haka kawai ya tsinci kanshi da son yi mata tsaraba ko don shima ya faranta ranta yadda itama take faranta mishi ta hanyar yi mishi dadadan girkegirke masu kara lafiya. Don haka ne ya ciro wayar shi ya tura mata da text.
"......yes, In shaa Allah. A dawo lafiya Allah ya kiyaye hanya....". Reply din data dawo mishi dashi kenan, yayi murmushi sosai, har kullum kulawar yarinyar zuwa gare shi tana matukar burge shi ba kadan, tunanin amsar da zai tura mata yake yi lokacin da aka ba wadanda suke kasa hannu su wuce, taku daya biyu yayi, bai tantance mai ke faruwa ba sai jin shi yayi kwance a kasa rike da kafar shi ta dama, ashe yabi ta wrong way ne, daidai lokacin an ba ababen hawa dake wajen hannu, ba tare da su duka sun kula ba wani mai mashin yabi ta kan kafar shi ya wuce.....!

Yaja numfashi a hankali bayan ya gama tunano abinda ya faru, kallonta yayi yana dan murmushi,
"kawai ikon Allah da tsautsayi" ta girgiza kai, "to Allah ya kara kiyayewa" duk muka amsa da Ameeeen. Maigadi yayi sallama ya shigo dauke da manyan kuloli, Malam Bala ya biyo bayan shi rike da wasu, Anty Rahina ta umarce su dasu kai kan dinning su ajiye, suka ajiye suka juya. Ta kalli Abbu, "na dafo maka abinci daga gida, kana jin yunwa ne?" ya gyada kai, ta mike "bari in zubo maka toh" da sauri na mike ina kara rungume Baby Jameel a hannuna, "Anty bari in zubo mishi" tayi murmushi tace to shikenan. Ta koma ta zauna ni kuma na wuce kicin. Harira nata kokarin hada miya, nace "kiyi abincin kadan fa, Anty Rahina ta kawo abinci" tace to shikenan. Na kwashe plates da spoon da zasu isa na koma falo, na zubawa Abbu abincin na kai mishi kafin na koma na zubowa su Anty Ameenah, ni da yara kuma muka hau dinning. Anty Mubeenah ta fito daga dakinta, na kalli agogo. No wonder! Lokacin cin abinci yayi ai! Ganin su Anty Ameenah a falon sai data danyi turus! Kafin ta karasa, ta zauna akan kujerar dake kusa data

Anty Ameenah tana dan murmushin yake, wai "su Yaya Ameenah ne? Ai ban san kuna gidan ba, ina daki ina ta barci" Anty Ameenah ta danyi murmushi, "Allah sarki! Muma mun zo duba mai jiki ne ai" tayi shiru kanta a kasa, Anty Rahina kam bata tanka ba Hankalinta na ga shayar da dan jariri. Ta gama kame-kame dai ta tashi tazo ta zuba abinci ta fara ci, Kai kawai nake girgizawa, rayuwar Auren bayin Allahn nan tana da matukar daure kai.Ita ta fara tashi daga kan dinning din, sai dai wannan karon maimakon ta koma dakinta, kan daya daga cikin kujerun falon ta koma ta zauna. Muma muna gama cin abincin na kwashi kayan da muka bata na kai kicin na sake dawowa falon, Baby Jameel kamar yadda nake kiranshi tunda suka shigo na amsa daga hannun maman shi, yaron ya bude idanunshi farare tas Mashaa Allah dasu yana ta walainiya dasu a tsakiyar falon, Ji nake kamar in lashe shi saboda yadda yake burge ni. Na fara jujjuya shi ina jan kumatun shi ina mishi en wasanni kafin na fara manna mishi kisses a kumatu, Abbu ya maida kanshi jikin kujera ya kwantar idanunshi a lumshe; "What he'll pay to become that baby!!".

'In a nation where the Poor face hardships, suffering and fears, only the riches and the one's that has power lives in peace, thrives and prospers....... Assalamu Alaikum Wa Rahmatullah Ya Ibaadullaheessaaliheen!!!......'

Sai gab da Magriba su Anty Ameenah suka mana sallama zasu tafi, na leka dakin Anty Mubeenah wadda tunda aka kira sallar la'asar ta tashi da niyar zuwa tayi sallah bata dawo ba, na gaya mata zasu tafi ta leko suka yi sallama ta koma dakinta. Ni dasu Hafsy har Abbu mai kafa sai da muka taka musu har gaban motar da Anty Rahina tazo da ita. Anty Ameenah ta kalleni na goya baby Jameel a bayana yana ta shakar barci abin shi, tayi murmushi cike da tsokana tace "to Hajiya Nafee a bamu baby din koh?" na fara kokarin sauke yaron daga bayana, "Allah Anty ji nake kamar ku bar min shi!" su duka suka kwashe da dariya, Anty Raliya tace "kina son yara ne har haka?" nayi dan murmushi, "sosai ma! Amma mommy taki ta haifo mana wasu" na karasa ina

pouting kamar inyi kuka dana tuno diramar da muke sha da ita idan ina mata maganar me yasa bata kara haihuwa daga kaina ba? Sai tace ai Allah ne bai kawo ba, ranar nan ma dana takura mata da tambaya zagi ta dankara min tace in cewa daddy na ya karo aure mana sai a Haifa min yaran, na tuna lokacin kuka na fashe dashi saboda zagin data min, shi kuwa daddy dariya ya dinga mana. Daga ranar ban kara mata korafi ba, sai dai in yiwa daddy. Su Anty Ameenah kam dariya suke min, sun fahimci tsantsan yarinta da sokancin da aka san Yaya irinmu nayi a tare dani. Anty Ameenah tace "Kar ki damu, in shaa Allah kema zaki haifi naki, kinga kin huta kenan koh?" na gyada kaina ina murmushi, "daddy ma haka yace ranar nan!" suka kara sakin dariya kafin suka shiga motar, na mikawa Anty Ameenah babyn tare da maida murfin motar na rufe mata tare da daga musu hannu, suka ja motar suka tafi. Na dan saci kallon Abbu kallona yake sosai with astonishment in his eyes, murmushi yake yi kamar kunnen shi zai zage, na samu kaina da tambayar dalilin sudden change dinshi curiously. Na kama hannun Hafsy muka koma cikin gida

ya biyomu a baya. Muna gama dinner na musu sai da safe na koma dakina, sosai nake jina a gajiye ga wani barci daya rufe min idanu.

Kwana uku muna jinyar Abbu ni da yaran shi, ba laifi ya warke duk da cewa bai fara fita ba, kuma har zuwa lokacin Tafiyar shi bata koma irin ta normal people ba. Cikin wannan lokacin mun ga jama'ah ba kadan ba, ko wace rana sai mun ga bakin fuska cikin masu zuwa duba shi gaskiya Abbu yana da jama'ah sosai. Saurayin Ni'ima zai kawo mata ziyara ranar alhamis, ranar a lab muka wuni tare dasu suna jira mu tashi su wuce gidan su dani, na gaya musu Abbu ya hana ni yawo amma ina! Suka ce they wouldn't take no for an answer, dole suka saka ni kiran shi. Na fita daga cikin lab din bayan na danna mishi kira, bugawa daya biyu ya dauka ana uku, a sanyaye na gaida shi tare da tambayar jikinshi ya amsa da lafiya, nayi shiru ina kamo bakin zaren daga inda zan mishi maganar har sai daya tambaye ni ya? Sannan na gaya mishi kamar wadda take tsoron tayi maganar,

shiru ya biyo baya kafin ajiyar numfashi mai nauyi, "amma kada ki wuce karfe bakwai baki dawo ba" da sauri nace "in shaa Allahu Abbu" daga nan muka yi sallama. Ranar tun kafin lokacin tashin mu yayi muka tafi. Unguwar Galadanchi muka nufa, ashe mahaifin su shi yake rike da sarautar Galadanchi ta garin Kano, babban gida ne wanda ginin shi na asalin gidajen sarauta ne, sashen Hajiya Fati muka fara shiga ita ce mace ta biyu a gidan, mace mai karimci ta tarbe mu da faraarta, na kula su Ni'ima kamar babbar Yaya suka dauketa don a sashenta ma suka ce zasu saukar da Bashir din. Cike da girmamawa na gaidata ta amsa da fara'ar ta tare da sawa aka kawo mana ruwa, mun dan jima a sashen nata kafin muka mata sallama muka wuce sashen Hajiya Siyama mahaifiyar su Abbu. Sashen nata in ka shiga baka taba cewa dakin er dattijuwa ka shiga duk da cewa shima sashen Hajiya Fati babu laifi. Babban falo ne wanda yasha saitin royal kujeru ruwan zuma, muka zube a kan wani tattausan carpet muna gaishe ta tana zaune akan sallaya tana lazumi, kana ganin kamilalliyar fuskarta zaka san cewa ka kalli fuskar

ma'abociyar addini, babu abinda Abbu ya baro nata sai dogon siririn hancinshi, ita nata yana da dan fadi, sai data gama lazuminta kafin ta amsa mana cike da kulawa. Daga nan su Ni'ima suka jani muka je dakin su muka yi sallah, kayan jikina na canza muka shiga kicin muka fara shirya kayan abinci kala kala. Na bata shawarar mu yi snacks wanda zamu basu a matsayin tsaraba idan zasu tafi gobe, don haka muka yi doughnuts wanda muka yi icing dinshi muka watsa shredded cheese da chocolate akai. Karfe biyar suka karaso shi da abokin shi, mun riga mun kai komi sashen Hajiya Fati, mun shirya koina sai kamshi kawai dake tashi a wajen. Ita uwar gida ta musu rakiya zuwa inda aka tanadar musu mu kuma muka tsaya karasa gyara kicin din, sai da muka gama gyaran jikinmu sannan muka je muka gaisa dasu. Bashir din nata kamar yanda take fada dan kyakkyawa dashi ga barkwanci, abokin nashi ne ma bai mun ba ko kadan, sai wani shisshige min yake yi yana jana da hira duk ya takura min don haka na mike nace musu zan wuce gida, duk suka kalleni da mamaki ni kuwa Na Kauda kaina gefe don ma kar

suga fuskar hana ni tafiya. Sa'adiya ta taso ta kama hannuna muka fita, abokin Bashir da naji yana kira da Fahad ya taso ya biyo mu, ganin babu fuska yasa ya juya. Na saki tsaki kasa kasa, Sa'adiya tayi dariya tace da alamun gayen bai miki ba, kai kawai na girgiza mata muka wuce sashen Hajiya Siyama. Tana kan daya daga cikin kujerun falon tana kallon tashar Saudi, ta kalle mu cike da mamaki, "lafiya dai ko?" Sa'adiya tace "wai gida tace zata wuce!" tace Haba ai kin tsaya kici abinci koh?" nace "Hajiya Abbu...." tayi saurin katse ni, "kyale shi kawai, ba zaki tafi ba sai kinci abinci fa" bani da zabi dole na wuce dakin su Ni'ima don bazan iya komawa wajen su nataccen abokin Bashir ba kuma bazan iya zama kusa da Hajiyar ba.

Sai wajen karfe bakwai da rabi sannan muka fito ni da direban da xai maida ni gida, bayan naci tuwon tsakin masara da miyar kalkashi wadda taji yajin daddawa, tantakwashi da man shanu ga kunun aya mai sanyi da Gardi a gefe. Tare dasu Ni'ima muka ci abincin bayan Tafiyar su Bashir, ta bude tarkacen kayan tsarabar daya

kawo mata ta ciro min kayan shafa, turare ne da kayan makulashe naki amsa, sai da suka yi kamar zasu yi fushi sannan na saka hannu na dauko turaren 'splendid' tsohon turarena ne tun a secondary school, daga baya ya bata na gaji da nema na komawa kamfanin lily cool, Sa'adiya ta kara min da tarkacen sweets muka fita falo. Kicin na shiga na dauko doughnuts din dana debar wa su Hafsy, Hajiya na falon a zaune na durkusa a kusa da ita na mata sallama, ta min godiya sosai har sai dana ji kamar in nutse a kasa. Ta mikawa Ni'ima wata karamar silver grey din jaka tace ta bani, na mata godiya sosai kafin muka tashi, sai da muka je ta sashen Hajiya Fati na mata sallama kafin muka fita waje inda direba yake jira na, na shiga motar muka kara yin sallama dasu kafin muka tafi. Nayi shiru a bayan mota ina tunanin abinda zan fadawa Abbu, a raina addua nake ina karawa akan kada Allah yasa yayi fushi dani, naki jinin fushin Abbu kamar yadda na tsani bacin ranshi. Har cikin gida direba ya shiga dani, na fito daga motar ina mishi godiya tare da sai da safe, iska ake yi sosai kamar ta dauki mutum tayi yawo dashi, idanuna a rufe saboda kasar da iskar

guguwa ta watsa min na shiga falon bakina dauke da addu'ar da ake yi idan guguwa ta tashi, kamar hadin baki ina shiga aka dauke wuta. Na bude idanuna da kyar ina murza su, kafin inyi adjusting da dan guntun hasken falon wanda ya ratso ta cikin shara-sharan labulayen dakin daga farfajiyar gidan wanda lantarkin solar ta samo dashi, naji kafana tayi stepping akan wani abu mai tsananin sul6i, kafin in tantance meye naji ni na fara tafiya sululuuuu.....!! A tsakiyar dakin, na kwala ihu sosai ina salati tare da laluben abinda zan kama in rike tunanin farko daya fado min a cikin raina shine hango ni da nayi na kai da bakina, kyawawan kananun hakora na guda biyu na gaba malale a cikin jinin dake fita daga bakina....... Karo na kaiwa wasu hard muscled chest wadanda ko a cikin duniyar mafarkina ban taba hangoni a kansu ba, sai ga gangar jikina a jikinsu yau kamar a mafarki, dogayen tausasan hannuwa suka zagaye bayana, daya a kuguna daya a gadon bayana, jikina yake dauki rawa kamar wadda ta rungumi kankara cikin hunturun sanyi yayin da naji wasu dogayen zara-zaran yatsu suna suna tapping din gadon bayana a hankali.,

ban san lokacin dana saki ledojin hannuna, purse dina da wayata akan tiles din dake cikin falon ba.....!!.

Hankalina gabadaya ya dauke daga jikina, babu abinda nake fahimta sai tattausan kamshin dake fita daga jikin Abbu, bugawar da zuciyar shi take yi da dan sauri-sauri, dumin dake fita daga jikinshi....... Ya dago fuskata daga jikinshi yana kallona kamar hadin baki, aka dawo da wuta lokacin. Na samu kaina starring at his brown oily eyes da suke wani irin sheki kamar zaiba, "Nafee, are you ok??" cikin daukewar tunani na daga baki nace "umh???" ba tare dana yi kokarin dauke idanuna daga kanshi ba, ya dan jijjiga kafadata, "hey!" kamar wadda aka daddaba daga barci, nayi firgigit ina kallon cikin falon, Ya Allahu! What the heck just happened?? Da sauri na durkusa na tattara kayana da suka zube nayi hanyar dakina a sukwane, da sauri ya riko tsintsiyar hannuna, nayi cik ina sauraren abinda zai ce ba tare dana juya na kalleshi ba, "lafiyar ki kuwa Nafeesah?" da sauri na gyada kaina, "lafiya lau, kayi hakuri dan Allah" ina jin sautin murmushin daya saki, ya sakar min hannu

dama abinda nake jira kenan don haka na bazama dakina a sukwane. Kofar dakin na maida na rufe tare da murza key, nayi wuri-wuri a tsakiyar dakin kamar wadda take neman wajen buya kafin na zube a kasan dakin akan gwiwa na, zuciyana wani irin gudu take yi, na rasa abinda yake min dadi a lokacin. Ban san iya lokacin dana dauka a wajen ina zaune ba, tare da taimakon Innalillahi.... Dana dinga ja na dan samu sukuni a cikin raina, tashi nayi na fara bandaki na watsa ruwa mai sanyi a jikina duk da sanyin da ake yi sakamakon iskan da aka gama yi. Na fito daure da tawul a jikina na tsaya a gaban mirror, lotion na shafa na saka rigar barci wadda ta tsaya min a gwiwa, duk abinnan da nake yi idanun Abbu suna cikin memory na, na rasa abinda zan yi da zai dauke min tunaninshi daga cikin raina, chatting! Zuciyata ta tuna min, da sauri na tafi inda nayi jifa da kayan hannuna tare da wayar na dauko ta, ina daga ta na dan saki kara ganin yadda screen dinta ya tsattsage, na ciza tattausan lebena na kasa ina ji kamar in dora hannu aka in saki ihu saboda yadda nake son wayata dinnan, bana so ko datti ya hau kanta. Ganin chatting

din ma bai mun abinda nake so ba yasa na janyo system dina na kunna na fara kallon Baywatch, ajiyar zuciya na dan saki ganin hankalina ya dauke zuwa ga film din.

Sai Washegari na ba su Hafsy doughnut din dana kawo musu, tare dasu ma muka cinye shi a cikin mota. Yau Daddy da kanshi yazo daukata, yazo duba jikin Abbu ne. Sai da aka yi sallar la'asar muka wuce Kaduna, bakin daddy bai yi shiru ba a hanya yana ta bani labarin kirki da mutunci irin na Abbu, bai san cewa yanzu bana cikin mood din sauraren labarin Abbu bane, ko sunan Abbu aka ambata sai naji faduwar gaba, shi yasa yau nayi duk kokarin da zanyi wajen ganin na kaucewa haduwa dashi, nayi, sai dai dole sai da na ganshi lokacin da muke mishi sallama ni da daddy. Kaina na jinginar da jikin seats din da nake kai na lumshe idanuna kamar mai barci, hakan yasa daddy ya kama bakinshi ya bame har muka isa Kaduna.

Da dare Ni'ima ta kira ni, bayan mun gaisa take fada min wai Fahad dinnan ne abokin Bashir ya dame ta akan ta bashi number na, na tabe baki nace "kada kiyi kuskure bashi Ni'ima" tace me yasa? Nace ban gane ba? Waye a cikin ku bai san cewa Akwai wanda nake dating ba? Taja tsaki, dallah dating ko crushing?? Waye bai san cewa crushing din Muneer kike yi shi baya son ki ba?? Na dan dakata kadan kafin inyi magana, "Ramlah mai bakin Aku!! Ita ta fada muku koh?" daga can tace that doesn't matter ko kadan ai, ni ai zan bashi number! Nace cikin gatse, "ki bashi din toh, zaki gani ne" na katse wayar tare da jifa da ita akan gado. Muneer!! Na maimaita sunan, it's kinda strange. Rana bata taba fita ta koma ga ubangijinta ba ba tare dana tunana bawan Allahn nan a cikin raina ba, amma har ga Allah yau dai, yau gabadaya na manta da existing dinshi a duniya, Anya lafiya ta lau kuwa??! Tashi nayi na koma falo wajen su daddy muka sha hirar mu, sai dana fara hamma sannan na musu sallama na wuce dakina.

Da safe na ba daddy waya na nace a canza min screen din, Koda ya tambaye ni dalilin tsagewar ta cewa nayi faduwa tayi, to me zan ce mishi? Kafin azuhur sai gashi da sabuwar Samsung edge plus, nayi tsalle, nayi ihu na rungume shi, wayar da nake masifar so kenan sai dai bana so in takurawa iyayena da zancen wayar da nasan kudin abincin wani na shekara daya ne, shi yasa nayi shiru, sai gashi yau Allah ya bani ba tare dana roka ba. Daddy kam yasha addu'a ranar kamar bakina zai tsinke, haka nake ni kam, idan aka min kyauta sai in wuni ina wa mutum godiya. Mommy na cewa ta bada ayi fura don na kula Abbu yana so sosai, duk ranar dana kai fura ranar ita ce abincin shi har ta kare. Washegari na doshi hanyar Kano cike da tsaraba don sai da muka shiga shago na saiwa Hafsy dasu Qaseem sannan muka wuce, cike kuma da wani longing, longing to see someone wanda na ma rasa a wane matsayi zan ajiye shi cikin raina., abokin Babana ko kuwa Abokin Rayuwata??!

Aunty Mubeenah da wata kanwarta Shakirah kadai na taras a gidan, ina ga Abbu ya fita zagaya unguwa kamar yadda yake yi lokaci zuwa lokaci da er sandar taimaka tafiya, na durkusa na gaida su, Anty Shakirah ta mun sannu da zuwa har tana tsokanata da ina tsarabar ta tunda Allah yasa tana nan nazo. Matar tana da kirki, duk tafi sauran en uwan Anty Mubeenah da suke zuwa gidan, wasu idan suka zo ko kallon mutane basa yi balle su amsa gaisuwar su, wasu kuwa kallon mutane suke yi kamar kiyashi shi yasa nima bana kula da kurar data debe su. Dariya na dinga yi tana tsokanata, na ciro chocolate din kit-kat babba na bata nace ta kaiwa yara, na ciro wani hadadden turaren wuta na asalin en maiduguri na ba Anty Mubeenah inji Mommy na, ta amsa babu yabo babu fallasa, babu godiya ba komi kamar wadda ta bani ajiya, naji haushin abun ba kadan ba, na mike daga zaunen da nake na dauki jakar hannuna na wuce dakina. Kayayyakina na ciro na shirya komi a inda ya dace, na ciro fura da nonon da aka wa Abbu na Kai fridge na ajiye, daga kicin ina jiyo hirar dasu Anty Shakirah suke yi saboda a falo na biyu suke wanda yafi

kusa da kicin din, Anty Shakirah ce take tambayar Anty Mubeenah mai yasa bata son turaren? Tace to mai zanyi dashi? Idan baki so ki bani ai ban rasa wanda zan ba bane, da sauri naji tace ina so wallahi, turaren ne yana da tsada naga gashi yana da wahalar samu shi yasa! Nayi kwafa ina girgiza kaina, wato kyauta ma tayi da turaren wutar da babu yadda ban yi da mommy akan ta bani in kaiwa Anty Haleemah ba mommyn taki ita ala dole sai ita, to ga abinda ya faru nan ai!. Dakina na koma cike da takaici ban jima da shiga ba naji hayaniyar su Hafsy a falo, da sauri na fita. Suna gani na suka kwashi ihun murna duk suka rugo, kowannen su so yake ya rungume ni, ni kam dariya kawai nake ina ihun su sake ni daga cakumar da suka kin kar su kayar dani amma ina! Sai da suka gaji dan kansu sannan suka sake ni, Abbu yana bayansu ya jingina bayan shi da kujera yana kallonmu cikin murmushi, da sauri na zube a kasa ina gaida shi, can kasan zuciya ta wani irin farin ciki yake mintsini na. Yaran naja muka tafi dakina tun kafin inyi abinda zan zo ina dana sani don wani sashen na zuciyata wai rada min inje in rungume shi yake yi. A daki na baza

musu tsarabar dana kai musu, nan muka baje muka ci wasu a gun wasu kuma suka diba suka tafi daki lokacin da aka kira Magriba, ni da Hafsy kuma muka yi tamu a daki.

Muna gama dinner na mike da niyar inje in kwanta, Abbu ya kalleni yace "Nafeesah Akwai fura ne?" na gyada kaina a hankali, wata irin kasala ta rufar min saboda yadda ya kira sunana, yace dama min pls. Na wuce kicin na dama mishi furar, nasa ayaba lokacin da nake damawa dana gama kuma na watsa kankara a ciki na dauki bowl din dana juye furar a cikin na koma falo, yana sec parlour a kishingide akan kujera da alamu waya yake amsawa, cikin harshen turanci yake wayar. Na ajiye a gabanshi na fara kokarin zubawa a cikin cup ina satar kallonshi, wayar yake amsawa cike da wata irin yangayana yi yana wani lumshe ido, accent din turancin shi ko kadan bai yi kama dana bahaushe ba, idan kana ji sai kayi zaton ko rainon kasar Ingila ne, to waya sani? Naji ance a LA ya kammala digiri dinshi na farko. Na danyi murmushi ina girgiza kai, sau tari ina mamakin

yadda Abbu yake da yanga kamar wata mace, zaka iya mistaking kace yanga ce kam idan baka zauna dashi ba don a zahirin gaskiya haka yake naturally. Ya ajiye wayar hannunshi akan kujerar yana zama sosai, "what's funny?" da sauri na girgiza kaina "ba komi?" na mika mishi cup din, ya kura min idanu kamar yana so ya karanci abinda ya saka ni murmushin da kanshi, nayi kasa da kaina, ina jin sighing din daya saki kafin ya amshi cup din, da sauri nayi niyar tashi ya tsayar dani ta hanyar tambayana ya Daddy na? Nan fa na zauna na fara zuba mishi labari har na wayar da daddy na ya canza min, ya daga girarshi yana dan murmushi, "inye! Her daddy's girl!!" na sadda kaina kasa ina murmushi in ma zan iya cewa kila har da blushing, ya jefo min tambayar data kada min ciki, "garin yaya har screen din wayarki ya fashe?" na yi wuki-wuki da idanu kamar wadda aka kama tayi karya, ya sake tambayana, kafin in lalubo abinda zan ce wayar shi tayi kara, yana dauka na lallaba na mike da sauri sai dakina. Ina shiga na ajiye numfashi da karfi, Allah ya cece ni yau. Kayan barci na saka, na dauko log book dina na bude na dan dudduba

kafin na janyo system dina na cigaba da kallon Pinocchio dana fara yi. Wajen karfe tara da rabi naji wayana tayi kara, na daga ganin bakuwar number yasa na daga da sallamata, daga can wata familiar murya ta amsa sallamar tare da karawa da "gorgeous!" cike da mamaki nace "waye?" sai dana kusa dakin zagi lokacin da naji yace "Fahad ne, abokin Bashir Saurayin Ni'ima" na hade fuska kamar yana gani na, jin nayi shiru yasa yace "gorgeous, baki gane ni bane?" a raina nayi exclamin kalmar 'wai gorgeous!' cike da jin haushi nace na gane ka mana, and please suna na Nafeesah ne ba wani abu wai gorgeous ba ka gane!" ya saki wata dariya data kara kular dani, "Haba gorgeous! To me kin cancanci abinda yafi wannan sunan ma. Kawai ki bani dama in nuna miki how precious you are to me, wallahi tun ranar dana saka ki a idanuna naji cewa na samu macen dana dade ina nema a rayuwata, tun daga ranar na baki wani matsayi mai girma a cikin raina, Gorgeous, wallahi u've become a very special part of my being, you are my happiness, you've got everything I need from my wife you are classy, beautiful, hafiza.....!!" blah-blah-blah ya shiga

jero labarai har na gaji da saurare, ganin yaki dasa aya yasa na tsaida shi, "please Malam! Ita wadda ta baka number dina bata yi maka bayanin ina da Mijin aure bane?" ya kara sakin dariya, "ta dai fada min cewa kina da wanda kike so and unfortunately though to my relief baya sonki in return, baby just leave him, bai san ciwonki ba. I promise you zan so ki fiye da yadda yake sonki, na miki alkawarin mantar dake cewa kin so gayen can baby, just give me a chance kinji?" ni kam ina baki? Zuciyata cike da takaicin tonon sililin da Ni'ima ta min. Da kyar na saisaita kaina daga ihun da nake ji a cikin kaina na son in sossoka mishi zagi na dai yi kokari nayi calming din kaina, after all ai ba laifin shi bane, zamu gauraya da mai laifin. Duk da haka ban iya tsaida tsakin daya fito min ba, nace "Malam I don't need your love or whatever trash you are talking about ka gane? Don Allah Kar ka sake kira na!" na kashe wayar da sauri. Ni'ima na kira, cikin sa'a ta dauka a ringing din farko, ko sallama ban bari tayi ba na fara zazzaga mata ruwan masifa, daga farko hakuri ta fara bani, daga kuma sai ta fara tsokanata wai akan ta ma taimake ni? Nace taimakon ki

din banza? Nace miki ina so ne? Tace baki fada ba, zuciyar ki ta fada min. Ganin ta maida abun wasa na kashe wayar ina kara maimaita mata ta kira Fahad ne koma uban waye sunan shi ta gaya mishi kada ya sake kiran wayata don duk ranar daya kuma sai naci Mutuncin shi, ita kuma ta jirayi haduwar mu gobe!! Tace "Allah ya kaimu" cike da izgilanci, na kashe wayar ina kwafa. Ajiyar zuciya nake saukewa cike da takaici kamar zan hadiyi zuciyata in mutu. Karan wayata naji, da sauri na wawuri wayar ina tunanin kalar zagin da zan narka, ganin sunan Mommy ne yasa na dan saki fuskata kafin na dauka, gaisawa muka yi ta tambaye ni na sauka lafiya? Na amsa mata da lafiya lau. Mun danyi hira da ita kafin muka yi sallama, na dora wayar akan bedside drawer ni kuma na kwanta bayan nayi dimming din wutar dakin.

HADITH

Abdullah bin `Amr bin Al-`as (May Allah be pleased with them) reported: A man asked the Messenger of Allah (PBUH): "Which act in Islam is the best?'' He

(PBUH) replied, "To give food, and to greet everyone, whether you know or you do not.'' [Al-Bukhari and Muslim].

Washegari kam su Ramlah sun ga tsiya a lab, Tunda muka zo na samu gefe daya na zauna fuskana a cune, ban mata magana ba balle sauran en lab din, su Ni'ima ma Suka zo naki kallon inda suke, ina ji suna tambayar Ramlah meke damuna ne tace itama tunda taxo a haka ta same ni. Har muka tashi a ranar ban kalli inda suke ba, sunyi maganar sunyi tsokanar duk a banza. Muna fita na fara kokarin wuce su, Ramlah tayi saurin tare ni tana harara ta, "wai ke dallah malama meye kike wani yazga mutane tun dazu?" nima na harareta, nace "ban sani ba dallah bani hanya!" Ni'ima ta matso tace "in dai akan zancen Fahad ne don Allah kiyi hakuri, wallahi dana san Abun zai bata miki rai da ban bashi number din ba, kiyi hakuri sis kinji?" na ajiye numfashi tare da kallonta, "ni fa ba bashi number din da kika yi bane ya bani haushi sai zuwa da kika yi kina yada sirrina a wajen stranger. Saboda Allah meye na zuwa kina gaya mishi wai ina

crushing din wani?" tayi fuskar tausayi "Nima nasan ban kyauta ba, da gaske ban san lokacin dana gaya mishi ba wallahi, hira ce tayi hira ni kuma na saki baki ina bashi labari, amma don Allah kiyi hakuri" nace shikenan ya wuce, ta rungume ni tana er dariya, thanks sissy. Na harari Ramlah nace "ke kuma ba zaki bani hakurin bane?" ta zaro ido waje, "ni kuma me nayi?" nace waye ya gayawa su Ni'ima cewa ina crushing Muneer idan ba ke ba?" ta ta6e baki, "dadin ta ma ba karya nayi ba" nayi murmushin yake, zan ga ranar da Ramlah zata yi abu like a good girl in dai akan zancen Muneer ne, she's always playing bad, making it obvious that bata son gayen ko kadan, to amma ya zan yi? A gani na Allah ne ya dora min son Muneer bani na dorawa kaina ba.

Da haka dai muka shirya muka hau hira har Malam Bala yaxo muka tafi har su Ni'ima din zasu je su ga jikin Abbu. A can muka Tarar dasu Anty Rahina suma sun zo, nan muka wuni dasu muna ta hira har Yamma tayi kafin Suka tafi. Tun daga ranar kuwa ban sake ganin kiran wayar Fahad a waya na ba.

Satin Abbu uku yana jinyar kafar shi kafin ya warke ya fara fita harkokin shi. Naje gida weekend muka je Malumfashi, Malam Inuwa kanin baban su Daddy ya rasu, kakanni na na ainihi sun jima da rasuwa ban yi wayo na ganni dasu ba, shi yasa su Hafsy suke burge ni ba kadan ba, suna da kakanni ta kowanne fanni abin su. Wato naji dadin zuwa Malumfashi wannan karon ba kadan ba, cousins dina duk sun dawo daga makaranta wasu hutu suka zo wasu kuwa sun zo wajen gaisuwa ne, nan muka hadu muka yi ta yawace-yawace da ziyara har ban so lahadi tayi ba, haka dai muka yi sallama da dangina muka wuce gida. Muna isowa na wuce Kano Saboda yamma tayi don haka a gajiye likis na isa gida, babu abinda na iya tsinanawa, ina gama sallah na bi lafiyar gado sai da gari ya waye.

Mun je lab Ramlah take bani labarin wata er ajinmu a Kasu zata yi aure wannan week din, er Kano ce, ta tambaye ni zan je nace ai dole ne, Sahiba mutuniyar mu ce ta sosai. Tun a ranar na kira daddy na fada mishi ba zan samu zuwa weekend wannan satin ba saboda bikin

abokiyar karatun mu yace shi kenan Allah ya kaimu wani satin. Nayi shiru ban kashe wayar ba, tuni ya fahimci abinda nake nufi, "kudin anko koh?" naji ya tambaye ni, na saki murmushi mai sauti, wato Daddy ya karance ni kamar bayan hannunshi, yace "I will wire you the money in the next few minutes" nace "to Daddy nagode, Allah ya bar min kai!" yayi dariya tare da cewa "uwata kenan". A ranar muka shiga kasuwa muka sayo ashoben bikin, muka biya ta wajen telan Ramlah muka ajiye dinkin. Ranar juma'ah muka je saloon aka mana wankin kai da kitso, ni har kunshin hannu aka min, dama gani da son lalle kamar me. Ya kuwa yi min kyau sosai, sai da Ramlah taga na hannuna wai take cewa data sani da an mata itama, na kuwa dinga mata dariya. Daga nan muka yi shatar taxi muka wuce gida, sai da muka ajiye ta kafin muka wuce. Ina shiga falon naci karo da buhunan Irish, plantain ne, kayan marmari dasu doya, tunda na gani nasan cewa Abbu ya dawo daga tafiyar da yayi zuwa Ibadan taron Doctors na fadin Nigeria, Allah ya taimaki rayuwata na mishi text na gaya mishi zamu biya ta saloon daga lab, yau da na shiga uku na ai. Na

taimakawa Harira muka kai kayan kicin muka ajiye su a inda ya dace kafin na wuce dakina nayi sallah. Ina xaune Hafsy ta leko dakin tace in fita mu ci abinci, bana ma jin yunwa amma haka nan dai na fita don nasan bani da wani excuse din badawa. Na dauki gyale mai fadi na dora akan doguwar rigar jikina. Bana yarda in fita daga dakina ba tare da mayafi ba matukar nasan Abbu yana gari sai dai by mistake. Suna kan dinning table a zaune, Abbu na fara hangowa. Sanye yake da shirt din KC brown da bakin Jeans, ya kara wani irin kyau na musamman a kwanaki shida din da nayi ban gan shi ba. Na tafi da dokina na durkusa na gaida shi, shima cike da fara'ah ya amsa min, na gaida Anty Mubeenah kafin naja kujera na zauna muka fara cin abinci. Da muka gama Abbu ya fita, Anty ta wuce daki mu kuwa muka zauna a falo muna kallo har wajen karfe goma da rabi, har lokacin Abbu bai dawo ba. Na kashe kayan kallon kowannen mu ya nufi dakin shi ya kwanta.

'Turn to Allaaah he's never far away......

'Put your trust in him, raise your hands and pray..... Ohhh Ya Allah! Guide my steps don't let me go astray..... You're the only One Who can show me the way..... Show me the way........ Show me the way..........'
In Shaa Allah by Maheer Zayn

Da kyar na samu na sauka daga kan gadona ganin na gaji da juye-juye barci yaki zuwa misalin karfe tara kenan na washegarin ranar Assabar. Na fito daga dakina sanye da wandon Sports da rigar shi cotton ruwan madara, na dora hular beanie akaina wadda na nannade gashin kaina na saka a ciki. Wandering na fara yi a cikin falon hannuwana saye cikin aljihun wandon. Na tsaya a kasan staircase din dake falon, tunda nake a gidan ban taba Hawa saman ba, jifa-jifa dai na kan ga ko dai Abbu ya hau ko kuma yara sun sauko kuma ban taba tambayar me suke yi a wajen ba. Out of curiosity na fara takawa ina hawa saman, Tun kafin in karasa na saki baki galala ina kallo. Gym zan kira shi ko kuwa amusement park?? Kayan wasan yara kala-kala da different types of exercising machines ne birjik a wajen, wasu na san su

saboda nima ina zuwa gym duk weekends lokacin da ina gida. Na fara zagaye wajen cike da mamaki, as in Abbu will never cease to amaze beings. Kan Dip station na hau na fara kokarin dagawa amma ko motsi, da alamun yafi karfina ne don haka na sauka. Daga bayana naji ance "hey! What are you doing here??" da sauri na juya, yana tsaye a jikin wata kofa sanye da sportys ya rataya dan karamin tawul a wuyanshi, na sadda kaina kasa cikin rashin abin cewa. Ya fara takowa a nutse har yazo gab dani, ya jingina da station machine din, jin yayi shiru nasan sauraren amsar da zan bashi ne yake yi, nace "umh! Dama kawai ina zagaye ne sai kuma naga na shigo nan" yace "this is your first time here I believe?" na gyada kaina. Yace I see. Are you interested in exercising?? Da sauri na dago ina kallon shi, "sosai ma Abbu! A gida ma ina zuwa gym duk sat...." wani irin kallo yake wata min babu shiri na kama bakina na bame, na sadda kaina kasa ina jin kafafuna suna dan shaking. Kokarin fita ya fara yi yana cewa "sai ki dan motsa jikinki ko? Ni zan sauka kasa..... By the way, I like your lalle!" nayi murmushi ina kara kallon hannuna, ni kaina nasan

lallen yayi kyau sosai. Yana fita na fara wasa da karafa, sai wajen karfe goma da rabi na sauko falo, break nayi na koma dakina, sai lokacin naji gajiya da barci sun tarar min na kwanta. Kiran wayar Ramlah ne ya tashe ni daga barcin da nake yi, tace gata nan ta shigo layin mu daga amsar dinki in fito waje, na tashi da sauri na dora hijabi akan kayana na fita. Abbu da maigadi da wani makocin Abbu din suna kofar gida akan dan benci suna hira, na gaidasu. Ina tsayawa sai gata cikin napep, ta fito ta biya mai napep din, ta gaida su Abbu kafin muka shige cikin gida. Muna shiga ta fara jefo mun tambaya a rikice, "ke waccan giant gaye din waye? Anan gidan yake zaune?" cikin alamun tambaya nace wa kenan? Tace "wani farin gaye haka da jallabiya baka a jikin shi??" dariya na kwashe da ita nace "wai dama baki san Abbu ba duk abinnan da ake yi?" tayi turus! Da gaske wancan ne Abbu? Na gyada mata kai, "Ya Allah! He's cool babe, dan dai yana da mata wallahi....!" duka na kai mata ina dariya, "da bashi da mata fa sai kiyi me maras M? Kina da mijin aure a hannu dai shegiya" ta turo baki. A dakina muka zube, ta fiddo kayan sun yi kyau sosai, "sai dai

rigar tayi show me da yawa" na fada cikin korafi ina kara juya rigar, ta harare ni, "to sheikha. Ina cewa gyale zaki saka?" na turo baki kafin na daga kafada sama.

Wajen karfe hudu muka isa wajen shagalin bikin. Tuni an fara shagalin, yawancin en makarantar mu sun je abin an jima ba a hadu ba nan muka hadu aka yi ta hirar yaushe gamo ana hotuna. Ana gama sallar ishai'i aka fara daukar mu zuwa wajen dinner. Mun sake wata kwalliyar cikin doguwar rigar gown ta ankon zuwa dinner, purple ce sai rose head maroon color da heel shima maroon sai er karamar jaka maroon. Mun sha kyau abinmu kamar ka sace. Mun fito muna kokarin shiga mota zuwa wajen dinner nace karo da Bilyamin abokin Muneer, da mamaki ya min magana na juyo ina kallon shi, nima mamakin ne ya kama ni kafin muka gaisa dashi yake gaya min angon abokin shine. Ya Kalle ni tun daga sama har kasa yace "amma kinyi kyau sosai Nafee" nayi murmushi sosai har da fari, I'm a sucker for compliments. Yace "naga kina yawo ke kadai, Zan iya rokon alfarmar ki zama date dina for today?" nace "y

not?" na kira Ramlah tazo muka shige mota abin mu muka wuce. Muna tafe muna ta hira har wajen dinner, wajen ya tsaru sai sautin kida ke tashi muka samu waje muka zauna, amarya da ango ana kan high table. An fara shagali kawayen couple din suka fita fili muka dan taka rawa da liki muka koma wajenmu muka zauna, ana ta shagali har ban san lokaci ya tafi ba sai dana ji karan shigowar message a wayana ta hanyar vibrating, na daga karfe goma da rabi gabana yayi mummunan bugawa, na duba message din daga Abbu ne, "Where are you now?" na mike da sauri jikina yana rawa, su duka suka juyo suka kalleni, Ramlah tace meye? Cikin rikicewa nace "Abbu..... Gida. Gida zan tafi yanxu" tace haba! Ki jira a tashi mana dan Allah kinda fa sauran mutane suna nan" nace "noo Ramlah. Abbu just texted me, nasan ma sai na sha fada yau wallahi" ta kalle ni sosai, "to sai me? Ina ce ba Daddy bane? Nasan ko daddy ne ba zai miki fadan kinyi dare a wajen dinar biki ba" na girgiza kai, "baki san Abbu bane Ramlah..... Bilyamin don Allah ko zaka taimaka ka mika ni gida? Babu nisa daga nan" na maida maganar ga Bilyamin don

nasan idan nace zan tsaya fahimtar da Ramlah zamu iya kwana a wajen bata fahimta ba, ya mike yana lalubar makulli a cikin aljihun wandon shi, ya ciro key din ya Kalle ni, "muje koh?" na wa Ramlah da wasu daga cikin mates dinmu dake kusa da inda muke muka tafi. A cikin mota Bilyamin yana ta ja na da hira amma sam hankalina baya wajen ko kadan, da kwatance yayi parking a kofar gate. Na bude murfin motor na fita shima ya fita, na zagaya ta gefen shi nace "to Bilyamin ka gaida gida, thanks for the ride" yace "Kar ki damu.... Me za a cewa mutumin ne?" na danyi murmushi nace "kyale mutumin nan naka, kwana biyu shiru amma bai neme ni ba" yayi dariya yace to sai da safe. Sai dana shiga cikin gidan kafin ya tashi motar shi ya tafi. Bakina dauke da addu'ah da komi na shiga falon, babu kowa a ciki, da sauri na shige dakina na rufe, na tuge dankwalin kaina na zauna a gefen gado ina ajiyar xuciya cikin samun relief. Wayata ta dauki kara, ganin Sunan Abbu a jiki sai dana yi kamar Kar in dauka, na dai daure na daga na kara a kunnena tun kafin inyi magana muryar shi ta doki dodon kunnena, a fusace yake maganar, "wato

Nafeesah kin raina ni koh? Karfe nawa na kafa miki dokar dawowa gida idan kin fita?" jikina yayi sanyi, naji dama ban je wajen dina din ba da ran Abbu bai baci Saboda ni ba, nace "Abbu don Allah kayi hakuri, wallahi dinner din ne ba a fara da wuri ba" yace "sai kuma aka ce dole ne sai kin je wajen dinner din koda zaki kai karfe sha biyu ne a waje koh?" na girgiza kai kamar yana gabana, yayi shiru. Har ina murna ya gama fadan shi sai kuma naji yace "waye ya kawo ki yanzun?" nace "Bilyaminu ne, dan makarantar mu ne" yace "dan makarantar ku? Kawai Saboda yana dan makarantar ku zaki kwashi kafa ki shiga motar shi babu tsoron komi a matsayin ki na diya mace?" nayi saurin cewa "ai abokin....." sai kuma nayi shiru, harshe na yayi min nauyi sosai na kasa fadar kalmar. Shiru ya biyo baya, bai yi magana ba ni kuma na kasa karasa abinda nayi niyar fada, "it's okay!" naji yace daga can a hankali kamar ba shine wanda yake daga murya yanxu ba, "goodnight!" ya kashe wayar. Na bi wayar da kallo cikin sanyin jiki, da kyar na iya sauka daga kan gadon na cire kayan jikina nasa na bacci na kwanta.

♡Jeedderh♡

Wajen karfe uku na dare na farka, kishi ya dame ni sosai ji nake kamar numfashina zai dauke dole na farka daga daddadan barcin da nake yi, gidan dama duniyar gabadaya tayi shiru kamar babu mai numfashi babu ko karar fan saboda an dauke wuta. Fitilar wayana na kunna na lalubi goran ruwa dana saba shiga daki da ita a kullum Saboda na sanni da bukatar shan ruwa sometimes sai dai babu, da alamun na manta ban shiga da ita ba ranar. A hankali na bude kofar dakina na fito, na fara tip toeing zuwa kicin kamar wadda zata je yin sata. Daidai kafar dakin Anty Mubeenah na jiyo kamar alamun sautin tashin maganganu, ban san dalilin daya saka ni kara kasa kunne ba, muryar Abbu ce take tashi kamar cikin fushi, "For goodness sake

Mubeenah! How long has it been?? Kin san yaushe rabona dake? Kina ma kirga yawan kwanakin kuwa? Me yasa ne?! Me yasa ne ba zaki yi treating dina kamar yadda kowanne namiji yake samun kulawa daga matar auren shi ba? Na tambaye ki time without numbered

Mubeenah, idan ma wani laifi na miki don't you think it's high time da zamu manta da komi mu rungumi rayuwar yayanmu hakanan ba?" tsaki naji taja, "kace duk abinda zaka ce Ibrahim! Ba damuwata bace, yaya da kake magana a kansu inaga ai bai kamata ka sako su ba, kai kace I just need to have birth to them, you will take care of them, meye hadina dasu then??" shiru na tsawon mintuna biyu ya wuce yayin dana kara kasa kunne, a sanyaye naji muryar Abbu wannan lokacin, "hakkina fa kuma Mubeenah?""ni fa kaga ka dame ni ka hana ni barci na haba! Saboda tsabar fitina da jaraba a kyale mutum yayi barci ma cikin kwanciyar hankali ma ba za ayi ba?" amsar Anty kenan. Cikin daga murya yace "am fed up with ur cruel habits Mubeenah, dole ki gyara halinki idan kuma ba haka ba....!" katse shi tayi ta hanyar sakin dariya, ".... Idan ba haka ba zaka kara aure? Go ahead then, ko a da can ma hakan bai dame ni ba Ibrahim balle yanzun ka gane? Allah yasa matan duniyar nan zaka auro, I wouldn't give a damn! Now can u get out please? Ina so inyi barci!!" ina jiyo hucin daya dinga fitarwa a fusace kamar zuciyar shi zata fito waje,

cikin wani irin threatening murya yace "zan shayar dake ruwan mamaki kuwa Mubeenah" cikin muryar ko-in-kula, I bet she was shrugging her shoulder up ma lokacin kila tace "m looking forward to it" daga nan naji ana kokarin fitowa daga dakin nata, a sukwane na fada bayan labule tare da saka yatsa na danne saitin wajen dake samar da hasken flashlight a wayata. Yana fitowa ya maida kafar dakin da karfi ya rufe ji kake 6ammmmm!!! Ina jin lokacin daya bude kofar dakinshi ya shiga, sai dana bashi kyawawan mintuna goma kafin na fito daga maboyata na fada daki ruwan da ban sha ba kenan na koma kan gado na kwanta xuciyata fal cike da tausayin ma'auratan. Me ke damun Rayuwar Auren su ne haka??

Am sorry for the late update, jiya through out a kwance na yini ban jin dadin jikina ne sam. Yau din ma ta maza ce nayi shi yasa wallahi. Just kara hakuri dani pa!

Juyi kawai nake yi na kasa barcin, na rasa abinda yake min dadi a cikin raina. In normal sense nasan cewa da

ace wani ne ya min ihu da daga muryan da Abbu ya min yau sai naji bacin rai saboda ni fa na tsani kawai mutum ya dinga nuna he has control over me alhalin baya da, abunda nasan cewa koh a gida nake Daddy ba zai min kwatankwacin fada da tuhumar da Abbu ya min ba, yes! Daddy zai min fada amma ta cikin lumana da nasiha ba irin na Abbu ba. Amma me yasa? Me yasa ko kadan ban ji cewa Abbu bai kyauta ba a cikin raina?? Na juya daya gefen ina kallon wani frame, hoton mu ne ni da Hafsy, ni na dauke mu ya min kyau sosai shi yasa na kai aka wanke min shi. I was extremely confused a lokacin, kwata-kwata na ma rasa a wani matsayi na ajiye Abbu balle in yanke hukunci. I never, even in my dreams wai inyi mafarkin ajiye shi a cikin jerin abokan Baba na, to amma idan ba Abokin Baba na bane shi ba to waye?? Da wadannan tunanukan barci ya dauke ni cike da wadansu irin mafarkai marasa kan gado. Ranar har so nayi in makara sallarAsubahi, sai wajen karfe shida da rabi nayi sallah, ina gamawa na koma na sake kwanciya. Yatsun kafata naji ana ja, cikin barci na janye kafafuna na maida su cikin blanket tare da kara kankame pillow.

Tafiyar tsutsa naji ana min a wuyana, da sauri na bude idanuna tare da hantsilawa kasan gado har ina dan buge kaina, na dago da sauri, yanayin fuskana ya canza daga harara zuwa na mamaki. Da mamaki nake kallon su, Ni'ima ne da Sa'adiya. Zaune suke a gefen gadon suna kallona, nayi tsalle a kansu muna shewa, sai da muka gama na zauna a gefen su nace "me kuke yi ne anan yammata?" ni'ima tace ziyara muka kawo, ko it's not allowed? Nace "ni na isa in ce? Amma da safe haka?" idanuna ya sauka akan agogo, karfe goma da rabi. Sa'adiya tayi murmushi tace "Abinci fa muka kawo wa babban Yaya." na Kalle su "Abbu?" Ni'ima tace "to da wa?? Funkasu ne da mijin taushe mai dadi wallahi, tashi kixo ki ci kafin ya huce" na sauka daga kan gadon ina cewa "yanxu kuwa" toilet na shiga nayi brush, na fito na bude wardrobe na janyo bakar BF jacket ta cotton na dora akan vest din dake jikina, na nannade kitson da aka min na daure da ribbon na saka hular beanie muka fita falon, dama nasan yara suna makaranta don haka ban yi mamaki da naga falon babu kowa ba, sai da muka shiga second falo ne na ga Any Mubeenah zaune akan

kujera, muka gaida ta ni da su Ni'ima da alamun suma sai lokacin suka gaisa, ta amsa kamar ko da yaushe, babu yabo babu fallasa. Lamarin Anty Mubeenah sam ya daina bani mamaki, shi yasa bana ganin laifin dangin mijinta akan duk abinda zasu ce a kanta, tunda koma meye ai ita ta jawowa kanta. Ace kannen mijin auren ki wai kina amsa musu gaisuwa kamar wasu baki ko irin dangin nan na nesa? Kai ko dangin nesa ne ai ya cancanci ace ka dan nuna sanayya. Na saci kallon su Ni'ima da alamun su abun bai dada su da kasa bama. Muka nufi kan dinning muka zauna, har su na zuba mana funkasun muka fara ci muna er hira. Abbu ya shigo sanye da wata farar riga da farin wando, ya gyara sumar kan shi sai wani irin sheki take yi, da sauri su Ni'ima suka taryo shi suna babban bros! Da fara'ar shi ya tare su ya jingina kowaccen su da jikinshi yana kallonsu, "wato ku dai idan ba aiko ku aka yi ba ba a ganin ku sai a gida ko?" Sa'adiya tace "bros ai kasan halin Baba, baya bari muna yawo fa" yace "ba wani nan dadin baki, ai naji ance har weekend kuke zuwa gidan su Ameenah, wannan ba yawo bane ba kenan?" Ni'ima tace "kar ka

damu bros, yau yini ma zamu yi anan" yace ban yarda ba, kwana zaku yi. Ni kam idanuna yana kansu, fadar irin burge ni din da suka yi bata baki da lokaci ne, ban san sun zauna ba sai dana ji muryar Ni'ima a saitin kunnena, "me kike kallo?" nayi firgigit na kalleta, "umh?? Babu komi" ta jefa min wani irin kallo alamun bata yarda dinnan ba, nayi saurin maida hankalina ga Abbu na gaida shi, fuska a cune ya amsa duk sai naji ba dadi, ba haka yake amsa min gaisuwa ta ba. Ji nayi abincin ma ya fita daga raina, na fara tsakura ina turawa a bakina ba don ina jin dadin abincin ba. Su Ni'ima kam hirar su suke yi da Abbu suna dariya. Sa'adiya ta dan tabo ni, na kalleta a sanyaye, cike da kulawa tace "you okay?" na gyada mata kai kawai, Abbu ya kalleni na dan lokaci kafin ya maida kallon shi ga Ni'ima. Anty Mubeenah tazo tayi joining dinmu itama, lokaci zuwa lokaci Abbu yana saka ta cikin hirar da suke yi da kannen shi amma bata cika maida hankali ba duk da nima suna sako ni amma sai dai kawai in danyi murmushi ko inyi nodding a haka dai muka gama cin abincin. Hirar su suka cigaba da yi, na tashi na hada kan kayan da muka 6ata

na kai kicin. Kasa komawa inda suke nayi kawai sai na shige daki, Su Mommy na kira na hada mana video call, daddy ma yana gida don haka hirar mu muka sha sosai, na basu labarin bikin da muka je har hotuna da videos din da muka yi na tura musu. Ban yi kuskuren fada musu har dare nayi a wajen bikin ba wanda dalilin haka yasa Abbu ya mun fada kuma har yanxu yake fushi dani saboda nasan kuskurene hakan, kamar nayi kirari ne na dabawa kaina wuta. Su Ni'ima suka shigo dakin na wa su Daddy sallama, nan muka bude sabon shafin hira dasu.

Kamar yadda suka ce, yini sur suka mana a gidan. Da rana Abbu yace kar mu yi abinci, oda aka mana daga Chicken Delicacy peppered chicken da spaghetti lasagna sai yoghurt mai sanyi, muka ci muka yi nak tare dasu Hafsy. Bayan mun gama cin abincin na ja su kicin muka yi baking din cupcakes, babu kayan icing don haka bamu yi icing din shi ba. Da yamma likis Abbu yace su fito ya maida su gida, na rataya gyale a kafada ta muka fita tare dasu zan musu rakiya, cikin motar Abbu picnic su

Qaseem ne a ciki sun hakimce Hafsy tana gaba su kuma suna baya Abbun yana jingine da motar yana amsa waya cikin hadadden turancin shi hannunshi daya saye cikin aljihun wandon shi, su Sa'adiya suka shige mota ni kuma na tsaya daga waje muna er hira har ya gama wayar ya shiga motar ya tayar, na ja baya kadan ina daga musu hannu, ya zuro kanshi ta cikin motar yace "yah? Baki zuwa ne ke?" na kalli su Ni'ima kafin na kara kallon shi, "can I?" ya tabe baki, "that is idan kina son zuwa fa" na bude motar nima na shiga ya ja motar. Hira muke dasu Ni'ima amma jifa-jifa idanuna su kan sauka akan Abbu dake tuki hankali kwance, wata dagawa da nayi idanuna suka sauka cikin kyawawan sparkling eyes din shi masu cike da kwarjini ta cikin madubin gaban motar, kamar wadda aka zarewa kuzari haka naji jikina yayi sanyi, gashi na kasa janye idanuna daga nashi sai shine ya janye nashin. Nayi ajiyar zuciya a hankali tare da sauke kaina kasa, ina kallon su Ni'ima suna kus-kus suna en da-re-re-ku a raina nayi fatan Allah yasa ba jirgina suka harbo ba. A gidan muka yi sallar magriba da ishai'i muka ci dambun couscous sannan muka musu sallama muka

tafi. Dawowar tamu shiru, su Hafsy kadai su ke shan hirar su
ni kam ina kan wayata ina buga game din piano tiles saboda bana son satar kallon Abbu da idanuna suke yi har ga Allah. Muna shiga falo ban tsaya a falo ba nayi hanyar dakina, Abbu ya tsaida ni ta hanyar kiran sunana, na juya a hankali. Cewa yayi "Plss dafa mun shayi mana" nace toh. Kayan hannuna kawai na ajiye a dakin na shiga kicin na dafa shayin da kayan kamshi a ciki, na matsa dan lemun tsami na zuba a cikin butar shayi na dora akan tray tare da kofi na kinkima na kai mishi. Yana zaune ya sa system dinshi a gaba da tulin takardu a gefen shi da alamu aiki zai yi, na ajiye akan coffee table dake gefenshi na durkusa a gaban shi, ya dago a hankali ya kalleni, "lafiya Nafeesah?" na sadda kaina kasa nace "Abbu don Allah kayi hakuri da abunda ya faru jiya, in shaa Allahu ba zan kara ba. Don Allah ka daina fushi dani!" shiru yayi yana kallona kafin ya nisa, "ba fushi nayi ba Nafeesah. Kawai ban ji dadi bane yadda kika biyo namijin da baki sani ba cikin dare, what if God Forbid, something bad happens to you Nafeesah? Bayan

wannan kin duba shigar dake jikin ki kuwa? Haba Nafeesah!! Ke da nake ganinki da hankalinki da komi, how could you walk in front of many people with that dressing? And you were smiling and laughing in front of that guy, me yasa??" na sake yin kasa da kaina, ina mamakin ta yadda aka yi har Abbu ya ga irin shigar da nayi da kuma hirar da muka yi da Bilyamin, sai dai yanxu is not the right time to think about that, fata na daya kawai shine Abbu ya daina fushi dani. Last 20 to 23 hours has been like a hell to me, sukuni da walwala sun kaurace min saboda fushin mutumin nan daya; Abbu. Ji nake idan na kai gobe ba tare da na ga murmushin shi a gare ni ba zuciyata zata iya bugawa. Kaina na kara yin kasa dashi nace "kayi hakuri Abbu, ba zan kara ba" yace "dadi na dake Nafeesah kina da saurin admitting mistakes naki ki kuma yi repenting immediately, Allah yasa ki dore a haka" nayi kasa da kaina zuciyata ta fara washewa, da alamun ya huce. Yace "tashi ki je ki kwanta, ki daina damun kanki kuma ba fushi nake yi dake ba kin ji?" na dago a hankali na kalle shi kamar mai son karanta gaskiyar abinda yake fada, ya sakar min

murmushin shi reassuringly. Naji wani irin sanyi ya mamaye min zuciyata, nima murmushin na sakar mishi sosai cike da farin ciki nace "Abbu nagode sosai, Goodnight!" na mike cike da kuzari da kwarin jiki na tafi, ya bini da kallo yana murmushi sai dana shiga daki sannan yayi ajiyar numfashi ya dauki shayin dana hada mishi ya fara kurba a hankali yana gyada kai cike da nuna gamsuwa. Ni kam ina shiga daki har sai dana yi dan tsalle cike da murna, na shiga bayi nayi brush na fito ina en wake wakena cike da farin ciki nayi shirin kwanciya barci, tsalle nayi na fada kan gadona, na mirgina daya gefen inda wayata take na bude, sai dana yi chatting na shiga accounts dina na twitter ne, instagram, facebook duk nayi posting ina cikin muudu mai dadi kafin na kashe wayar, na kashe wuta, na balle ma6allan gaban rigata na gaba guda uku naja bargo har wuyana, nayi addu'ar kwanciya barci na shafa na rufe idanuna, ba dadewa barci mai dadi ya yi awon gaba dani.

"I heard that You are leaving the lab at the end of this week koh?" cewar Mrs Smith Head of Lab dinmu. Na gyada kaina nace "yes ma'am" tace "bayan kin gama Program din me zaki yi? Zaki wuce da HND ne?" nace "I'm not very sure ma, I'm thinking of filling D E form" tace "ina fata a nan BUK ne?" na girgiza kaina da sauri, "no ma'am, ABU Zaria ne" ta kalleni tana murmushi, "why?" na sadda kaina kasa kawai, me zan ce? Nace "maa nafi son Zaria ne sabida mun fi kusa dasu, bana son yin nesa da gida" ....ina so nayi nesa da Abbu da Iyalan sa Saboda ina jin tsoron abinda zan janyowa kaina, naso in kara da gaya mata haka sai dai nayi shiru. Ta gyada kai, tayi signing din takardar dana bata ta miko min nasa hannu biyu na amsa, tace "am wishing you all the best Nafeesah" nace "thanks ma'am" na fita.

Mun gama ayyukan mu na ranar muna zaune a cikin lab din muna hira ni da Ramlah, su Khaleesat tuni suka gama nasu IT din sati biyu da suka wuce. Nayi scrolling down ta cikin facebook account dina, anan na ci karo da status din da Muneer yayi mintuna biyar da suka wuce, "Soon.....!" na dan rausayar da kaina cike da alamun

tambaya, me yake nufi? Na danna button din like. Ramlah ta kalle ni tana tabe baki, "ni har na rasa abinda zan fada miki game da Muneer wallahi. Ki kyale gayen nan haka nan kin ki kiji, yanxu har ta account din shi kike bi kina stalking din shi?" na yamutsa fuska, "stalking kuma Ramlah sai kace wata mara aikin yi? Kawai ina chatting ne na ci karo da status dinshi nayi liking, shine nayi stalking saboda Allah?" tace "ni dake da marar aikin yi duk daya nake ganin ku wallahi, wani mara aikin yi din ma ya fiki Nafeesah. Kin makalewa namiji daya kamar wata wadda bata da masoya, da girman ki da class din ki da komi. Allah ban taba ganin mutum marar fahimta ba irin ki ban sani ba ko duk sangarta ce ko kuwa? Amma......""For Heaven's sake Ramlah!!" na katse ta a fusace har ina hadawa da buga hannuna akan bench, "this is my life kin gane? You have no right da zaki zauna kina lecturing dina akan abinda yake feeling dina ne kina ji? Baki son Muneer fine!! Ni da nake son shi sai ki bar ni inyi ta son nashi please!!" cike da mamaki ta kalleni, ta daga baki zata yi magana nayi saurin tashi na bar mata wajen. Yinin ranar haka

nan muka karasa shi cikin kuncin rai su kan su en lab dinmu sun fahimci akwai abinda ke faruwa damu don basu saba ganin mu a haka ba, we are always cheerfulkoda yaushe muna tare muna hirar mu mai burgewa muna tsokanar juna amma ranar kowa tashi yake yi a cikin lab din, ina kallon Ramlah sosai ranta ya baci don har sai data share hawaye, jikina yayi sanyi sosai, ni kaina nasan Ramlah bata cancanci abinda na fada mata dazu ba, Raina ne ya 6aci sosai, so many annoying thoughts were running through my mind a lokacin, zan iya cewa Ramlah Sara ne tayi akan ga6a na sauke fushi da takaicin wasu a kanta. Karfe biyu tana cika na suri jakar hannuna na musu sallama na fita, a bakin kofar na tsaya, bayan kamar minti goma Ramlah ta fito. Da sauri na tari gabanta, "am sorry babe, I shouldn't have said what I said earlier.... M sorry, really" ta kauce daga gabana, "me zan ce miki Nafeesah? Ban cancanci in miki magana bama balle inyi intruding din personal life dinki ba, m sorry!" nasan cewa magana ce ta gaya min, naji kunya ta kama ni a lokacin, A taron mu da Ramlah I must have hurt her feelings da

maganganun dana fada mata, bata cancance su ba ko kadan. Da sauri na kara tarar gabanta tare da riko hannunta, "look Ramlah! Wallahi I really didn't meant what I said da gaske nake, ni kaina abun yana damuna Ramlah. I'm trying, ina kokarin ganin cewa nayi yaki da son Muneer a cikin raina amma na kasa. No matter how hard I try, na kasa shi yasa nake jin haushin kaina nima, ina jin takaicin abun nima Ramlah har na fiki sai dai ya zan yi? Zuciya ta taki aminta da hakan ban san ya zanyi ba Ramlah...." zuciyata ta karye na kasa cigaba da maganar, idanuna suka yi jawur, lebena na ciza ina kokarin tsayar da hawayen dake kokarin xubo min. Ramlah ta dafa hannuna fuskarta cike da damuwa, "m sorry too Nafee. Bana jin dadin abinda yake yi miki ne ko kadan, it's hurting me. I love you babe, duk abinda zai bata ranki ina kin shi har cikin raina, na ga alamun baki son kyale shi bayan nasan cewa yana bata miki rai, I didn't know, ki yafe min" rungumeta nayi ina tapping bayanta, "I love you too Ramlah, m sorry too. I shouted at you" ta rungume ni itama, mun dan jima kafin muka saki juna, ta kalleni fuskarta da wani expression dana

kasa ganewa, ta sake cewa "m sorry Nafeesah" nace "what for again? Idan maganar Muneer ce ta wuce don Allah mu daina yin ta haka nan" ta gyada kai. Muka samu waje muka zauna muna er hirar mu har Malam Bala yazo na mata sallama na tafi tana daga min hannu, taron mu da Ramlah kenan.

'Some nights I can hear you., Screaming on the phone over something that he did....., And I wonder what can I do to make you throw him out so you can let me in.....!' A song by Shayne Ward Titled 'Melt the Snow'. I hope you will enjoy listening to it.

Juyi yake yi akan gado, barci yake ji sosai amma ko kadan barcin yaki zuwa. Gadon da yake Kai ya mishi fadi, gado ne wanda a kalla zai iya kwashe mutane biyar ba tare da wani ya takura wani ba amma kullum ta Allah shi kadai yake murzar shi, yana Juyi a kanshi, yana jin shi kamar wani mara galihu. Disappointedly ya sauka daga kan gadon, kan sofa yaje ya kwanta, yafi jin dadin kwanciya anan duk da cewa kafafun shi suna kan

hannun kujerar ne saboda tsawon shi. Wani modem daya shigo dashi ya tuna ya baro shi a parlour, wasu muhimman bayanai ne a ciki ba shiri ya tashi ya fita, babu kowa a Cikin falon, wutar falon ya kashe yayi amfani da wayar hannunshi ya dauko Modem din. Kan three seats ya koma ya kwanta a parlour na daya, Family picture dinsu ya kurawa ido yana kallo. Ya gaji haka nan, Ya gaji da jiran canzawar halin Mubeenah, Ya gaji da kasancewa kamar wani marar aure alhalin yana da mata kuma yana da right din karo guda uku kwarara, yana bukatar rayuwar aure irin ta kowane normal mutane, rayuwa mai cike da soyayya da girmamawa ba irin rayuwar auren gidanshi ba, rayuwar auren da ba zaka taba ganin murmushi ko kafar matar auren ka a dakin ka ba sai idan tana bukatar either kudi ko bukatar namiji ta motsa mata, kai kuma naka bukatun ko oho! Yana ganin lokaci yayi da zai maida komi inda yake, maganar gaskiya yana bukatar mace ya kuma gaji da bin kan Mubeenah tana yankwana shi kamar wani mara galihu, Allah ya gani yayi iyaka Kokari da hakurin da zai yi. Yana nan kwance Cikin zazzafan tunani zai iya cewa

ma barci ya dauke shi yaji karan bude kofar daki, a hankali ya bude idanunshi yaga Nafeesah ta fito daga dakinta, da mamaki ya bita da kallo a cikin ranshi yana tambayar ko lafiya? Yanayin tsayuwar da tayi tana tapping kafafunta a kasa nervously ga waya a kunnenta ya sashi cikin tunani me ke damun Nafeesah ne haka? A hankali idanunshi suka fara yawo a jikinta, duk da babu wadataccen haske a falon amma hakan bai hana shi hango surar jikinta cikin gajeren wando da vest din data saka, wani irin tension yaji yana building a cikin jikinshi babu shiri ya rufe idanunshi da karfi yana hadiyar yawu yana gayawa kanshi it's not right! A hankali ya sake bude idanun yana kara kare mata kallo yadda jikinta yake swaying halittun jikinta suna motsi suna kara tada mishi hankali, yana so yayi motsi yadda zata san da wanxuwar shi a cikin falon, but hell! He couldn't. God Forgive him but he's enjoying seeing her in that attire, making him go mad, making him want to just drag her and kiss her senseless may be yayi wani abun worst than kiss.....! Maganar da tayi cikin fushi da daga murya ne ya dawo dashi daga tunanin da yake yi, "Muneer you evil

bastard!" yaji duniya ta tsaya mishi cak kamar an tsaida kowane wucewar minti da dakika, may be he was mistaken, ba Muneer tace ba, kila ba sunan Namiji ta kira ba, kila Muneerah tace kunnenshi yake gaya mishi Muneer. Ya sake lafewa akan kujerar da yake yana kara kasa kunne, "kasan ina son ka Muneer!! You know it all along amma what?! Aure??!...." da sauri ya saka hannu ya danne kofofin kunnenshi yana girgiza kai, no! No way!! Karya ne!!! Kwatakwata ya manta a ina yake balle yace ga abinda yake yi, wani irin rugugi yake ji yana mishi ihu a cikin kunnenshi, maganganu mafi muni da daci daya taba ji an furta a gare shi, maganganun da suka girgiza shi suka yi turning rayuwar shi up-side-down, Innalillahi Wa Inna Ilaihi Raji'un ya dinga nanatawa har yaji nutsuwa ta saukar mishi, maganganun Nafeesah sun matukar girgiza shi, the fact that tana son wata halitta, halittar ma jinsin Namiji, abu ne da bai taba zato ba, bai taba zaton cewa tana da wanda take so ba, bai kuma taba zaton cewa abun zai yi affecting dinsa sosai kamar yadda yayi yanzu ba. Yana jin lokacin data tsuguna tana kuka sosai a tsakiyar falon,

he wanted to man up yaje ya rarrasheta sai dai a halin da ake ciki shima rarrashin yake bukata, yana ji kamar shima ya fashe da kukan ko ya samu yaji sauki daga azabar zafin da zuciyar shi ta dauka, har ta gama kukan ta tashi ta koma dakinta bai iya tabuka komi ba sai bin ta da kallo helplessly. Lokaci mai tsawo yana cikin wannan hali kafin yayi karfin hali ya tashi zuwa dakinshi, alwala ya dauro ya kalli Al-Qibla ya fara jera nafilah yana mai rokon Allah akan ya mallaka masa Abinda ya jima yana kwatanta nashi ne.....!.

☆☆☆☆☆☆☆☆

A hankali na bude idanuna da nake ji sun min wani irin nauyi marar misali, na kai hannu na dafe kaina da naji yana sarawa kadan wuyana ya rike shima na kai hannu ina dan taba shi, idanuna suka sauka akan agogo, karfe shida ta wuce, da sauri na tashi tare da daddabar Hafsy ta tashi, muka shiga bandaki muka yi alwala muka fito muka yi sallah, dakinta nace taje tayi wanka ta shirya nima na shiga na watsa ruwa, nayi iyaka Kokari na

wajen mantawa da abinda ya faru Jiya da dare, bana son tunawa ko kadan. Na fito daga toilet din daure da tawul a kirjina, na tsaya a gaban mirror ina tsane lemar jikina, idanuna sun tasa sosai sunyi luhu-luhu, ni dama nasan za a rina irin kukan dana sha jiya, kayan kwalliyata na janyo na shiga shafe-shafen abubuwa amma duk kokarin da nayi idanuna basu da alamun dawowa normal dama-dama ma fuskata swollen din da tayi ya rage sosai, tsaki naja na janyo wet tissue na goge kwalliyar da nayi, nayi simple one ko janbaki ban sa ba, riga da zani na saka nayi simple daurin dankwali, na dauki jakata na jefa wayata a ciki ba tare dana damu akan in kunna ta ba. Shades na saka a fuskata wanda ya rufe idanuna da yawancim fuskata, na zura takalmi flat na fita. Yaran ne kadai a falon suna kari iyayen basa nan, naja kujera na zauna a gefen Hafsy yayin da duk suka bini da kallo, dan murmushi nayi kawai, suka gaida ni na amsa Hafsy ta jefe ni da tambayar "Yaya Nafee me ya samu fuskar ki kika sa glass?" sai da nayi gyaran murya saboda dusashewar da tayi kafin nace mata "idanuna suke ciwo, bana so in goga muku ciwon ido ne"

ta gyada kai tace Allah ya sauwake Yaya Nafee, Kai kawai na gyada mata. Muka fara cin abincin a nutse, ni kam caccakar abincin kawai nake yi duk yadda naso da inci abincin abun ya gagara, xuciyata a cunkushe take sosai, takaici da bakin ciki ya cika min ciki har babu wajen da abinci zai shiga. Suna gamawa muka fita, hango bakar Matrix da nayi nasan cewa yau Abbu ne zai kaimu kenan, mamaki ya kamani ko me ya hana shi yin break ne?? Muka shiga cikin motar, as usual a baya na zauna. Muka gaida shi ya amsa cikin wata hargitsattsiyar murya wadda tasa na kalli fuskar shi sosai kamar wadda take so ta gaskata Abbu ne ko ba shi bane? Ban taba jin muryar Abbu a hargitse haka ba, wani hargitsattsen kallo daya watso min wanda ya kada min yayan hanji babu shiri na sadda kaina kasa, ina jin Hafsy fadi ba a tambaye ki ba tana gayawa Abbu wai ciwon ido nake yi ina tsoron kar in goga musu shi yasa nasa glass, harara nake jefa mata a kaikaice sai dai wannan shine ainihin abinda bahaushe ya kira da 'harara a duhu' saboda ba gani na take yi ba. Har muka ajiye su a school dinsu ban dago kaina daga sadda shi din da

nayi ba, suna fita na tashi na koma gaba kamar yadda muke yi, Abbu ya tashi motar muka wuce su Hafsy suna dago mana hannu. A hankali yake jan motar kamar ba tafiya muke yi ba, ya juyo ya kalle ni a karo na barkatai tunda muka fara tafiyar, gudun da zuciyata yake yi ya cigaba da karuwa a duk wucewar dakika. Kamar daga sama naji ya jefo min tambayar da nake tsoron ya jefo min, "Are you ok Nafeesah???!"

Shirye-shiryen komawa gida nake babu kama hannun yaro, ganin abun nake yi kamar a mafarki. Kamar yau ne fa nake shirin tahowa Kano gashi har watanni shida sun wuce, na fada a cikin raina ina karewa akwatuna na kallo wadanda na gama shirya kayana a ciki. Hafsy ta leko dakin, gani na a tsaye ina karewa dakin kallo ta shigo ciki tare da maida kofar ta rufe, gefen gado ta samu ta zauna ta kalleni a marairaice, "yanxu Yaya Nafee gobe zaki tafi ba zaki kara mana ko kwana daya bane?" na zaro ido ina kallonta, "Lallai ma Pretty ashe baki tausayi na, ko don ke kina gaban Mom and Dad dinki ne shi yasa? Nima ina so in je in gansu saboda nayi

kewar su sosai" ta turo baki, "to ba kina zuwa kina ganin su ba duk weekend?" nace "dat's a different magana ai, so nake in koma kusa dasu gabadaya kin gane?" tayi rau-rau da idanu sai ga hawaye shar-shar, da sauri na zauna a gefenta na fara lallashinta har tayi shiru, nace "haba mana da girman ki kike kuka? Kar ki damu zan dinga zuwa kuma ina muku weekend kinji?" da sauri ta dago kanta ta kalleni, "da gaske?" na gyada mata kai ina murmushi, sai dai daga can kasan zuciyata nasan cewa yaudarar ta kawai nake yi don ta warware, ina fata idan na saka kafa na bar gidan Abbu ya zama fita ce ta har abada, ko a mafarki bana fatan in sake komawa. Da biyu nake gaggawar in koma gaban su Daddy na, ina so inyi nisa da Abbu da gaggawa, he has started putting some effects on me wanda duk iya kokarina nason ganin na hana su affecting dina abun ya ci tura, shi yasa nake so in bar gidan as soon as possible kafin abubuwan su fi karfina. Hira na fara jan ta dashi ina tsokanar ta, nan da nan ta ware ta fara dariya, tare da ita muka cigaba da shirye shirye, na fidda kaya masu dama da wasu daga cikin kayan kwalliyata na ba Harira tayi ta godiya kuwa.

Ana kiran magriba muka bar shirin muka yi sallah, Hafsy ta dauko littafan ta na taya ta muka yi bitar karatu har aka kira Ishai'i muka yi, muka fita wajen cin abinci. Muna gamawa muka koma kan kujeru muna kallo, duk da kallon daga ni sai Hafsy ne su Abdullahi wasan su suke yi abin su. Abbu da Anty Mubeenah suka yi sallama suka shigo falon, muka musu sannu da zuwa duk suka wuce dakinsu da alamun kayan jikinsu zasu canza. Anty ce ta fara fitowa, kamar yadda nayi zato ta canza kayan jikinta zuwa doguwar riga, Kai tsaye kan dinning ta wuce ta zauna. Ba a jima ba Abbu yayi joining dinta shima ya canza kaya zuwa na barci, riga da wando na M$S, muka cigaba da kallonmu har suka gama cin abincin suka dawo inda muke suka zauna. Hirar su suka fara yi su da 'ya'yansu, Anty tace "Nafeesah gobe sai tafiya gida ko?" nayi murmushi tare da gyada kai, tace "eyyah! Zamu yi kewar ki ko don dadadan girke-girken ki" Abbu ya jefa mata wani irin kallo, Qaseem yace "Yaya Nafee amma zaki dinga kawo mana ziyara koh?" nace sosai ma. Hafsy tayi caraf tace "anan ma zata dinga mana weekend koh?" na kalli su Abdullahi da suke kallona cikin zakuwa

da son jin amsa ta, murmushi nayi nace "ehh" a hankali. Suka dauki shewa suna ihun murna, kallon su kawai nayi ina murmushi. Karfe goma tana yi na tashi na musu sai da safe, Hafsy ta mike da sauri ta biyo bayana, ina ji Abbu ya tambayeta, "pretty ina zuwa?" ta juya tace "ni dai a wajen Yaya Nafee zan kwana yau" yace "a'ah zo ki wuce dakin ki, zaki takura mata" aikuwa ta bare baki zata fara kuka, nayi saurin janyota jikina, "babu komi Abbu, taho muje kinji?" ta ware hakora tana dariya, naja hannunta muka shiga daki. Brush muka yi muka fito, nace ta zauna bari inje in dauko mata kayan barci, na fita. Falon babu kowa duk sun tafi dakinsu, naje na dauko mata kayan. Na fito kenan daidai Abbu yana fitowa daga dakinshi, ya kalleni, da sauri na sadda kaina kasa nayi niyar wuce shi da sauri, cikin wata irin murya da ban taba jin ta a gun Abbu ba naji yace "Nafeesah!" na tsaya cak duk da ba haka naso in yi ba, so nayi in yi kamar ban ji ya kira ni ba in shige dakina wanda bai fi taku takwas daga inda nake tsaye ba, but damn me and my legs. Ya tako a hankali har inda nake tsaye, zuciyata bugawa take yi da sauri har naji tsoron kar ya jiyo

sautin, shiru ya biyo baya na fiye da minti biyu, jikina ya bani cewa kallona yake yi don haka naki daga fuskata balle in kalle shi. Yayi ajiyar numfashi a hankali, yace muryar shi kasa-kasa, "are you sure Pretty ba zata takura miki ba?" na tabbata ko nayi magana ma da kyar muryata ta fita don haka na gyada mishi kai kawai. Yace "umh.... Da gaske zaki dinga zuwar mana weekend?" nan ma kaina kawai na iya gyadawa. Yace "good! I'm happy to hear that. Je ki kwanta sai da safe" da sauri na wuce har kafafuna suna hardewa na fada dakin kamar wadda aka jefa, Hafsy ta daga kai ta kalleni da sauri, murmushi na sakar mata na mika mata kayan barcin ta saka nima na sa nawa, wando ne iya gwiwa don nasan ba fita zan sake yi ba da rigar vest mai budadden gaba zan iya cewa Rabin kirjina a waje yake. Na mana addu'ar kwanciya barci ni da Hafsy muka shafa, na janyo bargo na rufe mu tare da kashe mana wuta. Ban sani ba tsautsayi ne ko kuwa Kaddara ya saka ni janyo wayata na shiga social media?? Well, that was the worst moment I've regretted the most in my life!!!.

Kalmar 'Are You Ok' kalma ce da nake matukar tsoro idan ina cikin halin damuwa. I am a very emotional person, shi yasa idan ina cikin halin damuwa bana son mutane a kusa dani saboda gudun su tambaye ni lafiya? Don zan iya fashewa da kuka, ni a gare ni tambayar are you ok kamar fama min gyambo ne. Yanzu ma sai da nayi iyaka kokarin da zanyi na danne kukan da yake kokarin barke min nace "m fine Abbu, kawai bana jin dadin jikina ne" ya kalleni kawai nasan bai yarda da abinda nace ba, ban ga laifin shi ba don yadda nake a hargitsen nan babu wanda zai yarda wai gajiya ce ta maida ni haka. Ya kalleni sosai kamar wanda yake so yayi magana sai kuma kawai ya maida kallonshi ga titi, a raina naji dadin hakan nasan tambaya daya zai kara jefo min zan fashe da kuka, kuka kuma ba abinda nayi niyar in ci gaba dayi bane saboda Muneer. Har yayi parking a parking lot din dept din Microbiology, na yunkura zan bude motar ya tsayar dani ta hanyar kiran sunana, na Juya a hankali na kalleshi. Idanuwan shi fes a kaina suke, naji wani slight rawar jiki kafin in sadda kaina kasa, muryar shi a sanyaye yace "akwai abinda

yake damunki Nafeesah wanda kika ki gaya min and I wouldn't force you to tell me, kawai ina so in gaya miki cewa komi na rayuwa sai da hakuri, koma menene yake damun ki kiyi hakuri ki dauke shi a ba komi. Idan ma wani abu ne kika rasa kike ganin kamar ba zaki iya hakuri da rashin ba kada ki manta Allah yana tare da Ke. Shi ya mana alkawarin canza mana abinda yake sharri ne a gare mu zuwa ga mafi alkhairin shi don haka ki roke shi game da abinda yafi alkhairi a gare ki ba kiyi holding into something wanda yake ba alkhairin ki bane kin gane?" na gyada kaina a hankali maganganun shi sun shige ni. Abinda ya kamata in tuna kenan a lokacin da naga hoton Muneer da amaryar shi jiya, abinda ya kamata inyi kenan ba wai in kira shi ba ina kara fallasa kaina da disappointing kaina, sai yanzu naga cewar hakika abinda nayi jiya ban kyauta ba, naji kunyar kaina ta kama ni har ma data Muneer din, ko da wane ido zan sake kallonshi kuma yanzu??. Nace "na gane Abbu nagode sosai, In shaa Allahu zan yi amfani da shawarar ka" yace "good" shiru ya biyo baya a cikin motar, can naji ya sake magana cikin whisper, kamar kuma wanda

yake tsoron yin maganar, "anjima kuma sai gida koh?" na gyada kaina a sanyaye, barin rayuwar Abbu da iyalan shi!! Tunani ne mara dadi dake fadar min da gaba a duk lokacin da ya fado min a cikin raina don haka nake iyaka kokarina wajen ganin na kauda tunanin daga cikin raina. Na sake tsintar muryar shi yana tambayana, "da gaske zaki dinga zuwa kina mana weekend?" nace ehh, a cikin raina nasan fada kawai nake yi ba don zan dinga zuwa ba sai don kawai kada su dameni da tambaya. Kamar yasan abinda nake tunani, yace "da gaske kike ko kuma kina fada ne kawai?" shiru nayi wannan karon, yayi murmushi tare da kallona kawai yace na gane. Dash board ya bude ya ciro wata karamar jaka fara mai hannu ya miko min, na amsa fuskana dauke da alamun tambaya, yace "it's a small thank u gift, thank u for staying with us Nafeesah, we enjoyed having u in our life and we wish you will come back to us forever!" na dan rausayar da kaina cikin alamun rashin gane inda maganar tashi ta saka gaba, me yake nufi ne? Murmushi yayi ganin ya saka kwalwa na cikin rudani. Yayi murmushi yace "oya! Up you go! Naga abokan ki suna

jiran ki tun dazu" sai lokacin idanuna suka koma ga inda muke zaune, su Ni'ima na hango tsaye a kofar shiga lab dinmu suna hirarsu da Ramlah, cikin sauri na jefa jakar daya bani cikin handbag dita na mishi godiya tare da bude murfin motar na fita. Gabadaya kallo suke bina dashi cike da alamun tambaya nasan bai wuce na mamakin abinda muka tsaya hirantawa da Abbu bane tun dazu, naja fuska tare da kara gyara zaman gilashi na a fuskana. Tun kafin in karasa wajen su suka iso gare ni, Saadiya da Ni'ima suka kamo hannuna Ramlah kuma ta dafa kafadata, cike da damuwa suke tambayana, "Nafeesah are you ok?" ni duk sai naji sun ma bani haushi, na cire gilashin idona ina kallonsu cike da takaici, "why?? Saboda crush dina zai yi aure sai kuke zaton karewar rayuwata ne yazo ko me?" gabadayan su were relieved da yadda suka ga nayi, Ramlah tace "yeah! I thought about more than that ma, nayi zaton zan ganki kamar sabuwar kamu ne wallahi sai kuma na ganki da hankalinki dai, but are you really ok?" na gyada kaina "yeah, I am Ramlah but that doesn't mean ban ji haushin abinda Muneer ya min ba" Ramlah ta rungume

ni da sauri tana tapping bayana, "ohh my poor friend, Am really sorry. Don Allah kiyi hakuri, nasan in shaa Allah wanda yafi Muneer alkhairi a gare ki yana nan zuwa" na danyi murmushi, kwatankwacin abinda Abbu ya gama fada min. Na janye daga jikinta ina kallon su Ni'ima dake tsaye suna kallonmu nace "ba kuna da lectures ba wai me kuke yi anan?" Sa'adiya tace "wallahi Ramlah ce ta kira mu wai muzo mu tayata baki hakuri don tasan yau a hargitse zaki xo sai kuma muka ga akasin haka" ajiyar zuciya nayi nace "na hargitse kam Sady but Alhamdullillah na dawo cikin hayyaci na kuje kawai" suka mana sallama suka tafi mu kuma muka shiga lab. Ranar babu aikin da muka yi, sallama muka yi da staff da lab attendants na dept din don haka wajen karfe sha daya muka bar lab din cike da kewar mutanen da muka zauna dasu. Wajen su Ni'ima muka je na kara musu sallama, daga nan na wuce gida. Ita Ramlah tana Kano tukun.

Ina zuwa gida na kara hada kan kayana na zauna zaman jiran Daddy don yace shi zai zo ya dauke ni. Bayan an

fito daga masallaci sai gashi har da Mommy, sai da muka yi Sallar La'asar sannan muka yi sallama da iyalan Ibrahim Galadanchi cike da kewa, kauna da zullumi. Zullumin ko zan sake ganin su a rayuwata ko kuwa? Zullumin ko zan iya da korar wadannan kananun feelings da nake ji game da Abbu? Zullumin ko zan iya yin normal rayuwa kamar da wadda nake yi a gaban Iyaye na? Magana ta gaskiya watanni shida da nayi tare da Iyalan Ibrahim Galadanchi watanni ne masu muhimmanci da tarihi a gare ni, sun koya min abubuwa da dama a rayuwata, sun kuma gaya min ainihin abinda ni, Zuciya, da gangar jikina suke so da Muradi.

Na daga idanu a hankali na kalli Hafsy dake hannun Babanta tana rusa kuka da iyakar karfinta tana ihun Ita sai ta bini, na kalli su Qaseem suma duk fuskokinsu cike suke da jimami har da kwalla a cikin idanunsu, hakika bahaushe yayi gaskiya da yace 'Sabo turken Wawa' dana kalli fuskar Abbu kuwa sai da naji kamar in balle murfin motar in fito ince na fasa komawa gidan. Damuwar dake fuskar shi was obvious, na karance ta kuru-kuru cikin

idanunshi, kallona yake yi da dukka idanunshi, yanayin shi ya min kama da wani wanda yake tsoron rasa wani abu mai matukar muhimmanci a gare shi. Daddy ya bude murfin motar ya shigo ya mata key, Abbu da iyalan shi suka daga mana hannu bakinsu dauke da addu'ar Allah ya kiyaye hanyar yayin da naji kwalla ta cika min idanu, Daddy ya ja motar muka tafi. Nabi gidan da kallo idanuna cike da kwallah, Allah kenan! Kamar a ranar ne nazo gidan, na tuna sanda su Daddy zasu tafi kukan rabuwa dasu nayi, gashi yau kuma ina kukan rabuwa da iyalan Abbu. Tafi tafiya na fara bajewa daga kukan dana fara, su Daddy hirarsu suke tayi game da karamcin iyalan Abbu, ni kam kallon gefen hanya nake yi kawai. Barci ya dauke ni bani na tashi ba sai da muka isa gidanmu shima Mommy ce ta tashe ni, na fito daga motar fuskana a washe ina kallon gidanmu, Finally dai! I am back!. Muka dauki wasu kayan muka shiga dasu yayin da Maigadi ya shigo da sauran, Dakina a shirye na tarar dashi kamar ina gidan don haka ina shiga na ajiye jakar hannuna akan kujera daya dake dakin na zube akan gado ina ajiyar numfashi.

Ana kiran sallah Mommy ta leko dakina tace in fito Daddy zai ja mu sallah, sai lokacin na tashi daga kwanciyar da nayi na shiga bayi na dauro alwala na fito, dogon hijabi na dauka na tafi dakin Daddy. Wani dan karamin dakine a cikin dakin shi wanda yake aiwatar da ibadojin shi a ciki, dakin lullube yake da darduma sai tashin kamshi yake yi, shelves shelves na littafan addini a gefe a shirye gwanin ban sha'awa. Daddy ya ja mu sallah, muna gamawa ni da Mommy muka dauko littafin Arrijalu Wan-nisa'u fil Jannah Daddy ya ja mana karatu har aka kira sallar Ishai muka yi. Muka fita zamu yi dinner amma abinci fa yace sam bai ga wajen zama a cikina ba, Mommy ta kalli yadda nake ta juya cokali a cikin Irish Supper data mana wanda yana daya daga cikin favorites dina, na tabbata saboda ni tayi shi amma na kasa ci, tace "Baby lafiyan ki lau kuwa kin kasa cin abinci?" Daddy ya dago yana kallona, cikin sauri na girgiza kai nace "m fine Mom, cikina ne a cike kawai" Daddy ya tsiyayo Pineapple and coconut juice da Mommyn ta hada ya miko min, na amsa tare da kaiwa

bakina na kur6a, aikuwa har da lumshe idanuna saboda gardi da sanyin daya ratsa ni, da taimakon lemun na dan samu na kara tura abincin haka nan kafin na musu sai da safe na tafi dakina. Ina shiga na fara kokarin kimtsa kayana cikin wardrobe duk a kokarina na kauda tunanikan dake dankare a cikin raina. Na janyo handbag dita ina kokarin rataye ta a bags rack naji nauyi a ciki, cike da mamaki na zura hannuna ciki na fito da karamar jakar da Abbu ya bani da safe, a hankali na zauna a gefen gado tare da janyo dan karamin purple akwatin dake ciki, cike da mamaki na fiddo shi ina jujjuya shi a hannuna. Ina budewa na zaro idanu sakamakon wata siririyar sarka dana gani a ciki da dankunnenta har da zobe, sarka doesn't look that out of ordinary but daga ganinta kasan ba karamar sarka bace. Hannuna rawa ya shiga yi na rasa abinda zanyi, tashi nayi da dan akwatin a hannuna na fita falo, su Daddy suna zaune suna kallo duk suka bini da kallo, na zauna a gefen Daddy tare da mika mishi akwatin nace Abbu ne ya bani dazu, da mamaki Daddy ya karbi akwatin yana jijjiga shi a hannunshi yace "Shi Ibrahim

din ne ya baki wannan sarkar?" na gyada kai a hankali, ni kaina na kasa yarda da hakan gani nake kamar a mafarki, Daddy yace "amma me yasa?" na jijjiga kai "nima ban Sani ba Dad kawai bani yayi" Mommy ta karbi sarkar itama ta dudduba, ta kalli Daddy tace "da alamun sarkar Babba ce fa Habibiy, Anya zamu karba kuwa?" Daddy yace "abinda nake tunani kenan exactly..." yace min "ki je daki ki kwanta, da safe zan tuntube Ibrahim din inji" nace "toh" na musu sai da safe na wuce dakina. Ina kwanciya barci ya kwashe ni, after all it has been one exhausting and stressful day.

Washegari Daddy ya dawo min da sarkar da Abbu ya bani, ban tambayi abinda ya cewa Abbu ba ni dai yana bani na bude na zura zoben a cikin yatsa na. A ranar sai ga Anty Ameenah ta kira ni, korafi ta min akan na tafi ba tare dana musu sallama ba, hakuri nayi ta bata akan cewa Lokaci ne ban samu ba, bata hakura ba sai dana dauki alkawarin cewa zan je gidanta musamman sannan. Bayan mun gama wayar shiru nayi ina kallon wayar a raina ina tuhumar kaina akan ba mutane false

hope na ganina da ziyartar su bayan nasan cewa ba haka bane a cikin raina.

Nayi shiru akan gado duk kadaici ya ishe ni, a raina na raya da ace a gidan Abbu nake da war haka ko dai muna hira dasu Hafsy, ina kicin ina girki ko kuma muna wasa a gym kamar yadda muka saba kwanan nan idan bama aikin komi. Wayata na janyo na latso lambar Abbu, sai kuma na kasa danna mishi kiran, a raina ina mamakin kaina me zan ce mishi ne idan ya dauka? Me zan ce mishi ne dalilin da yasa na kira shi?? Kawai sai na maida akalar wayar zuwa ga Anty
Mubeenah, ta shiga tayi ta ringing amma ba a dauka ba, shiru na bata mintuna biyar ko zata kira amma bata kira ba sai na kira wayar Abdullahi, cikin ikon Allah ya dauka, cike da doki muka gaida dashi. Nace ya bani Hafsy mu gaisa yace ai tana gida yau bata je makaranta ba, nace me yasa? Yace ai Tun jiya take kukan Ita lallai sai an kawo ta wajena shine yau ta tashi da zazzabi, a raina naji ba dadi don haka nace idan sun koma gida ya kira ni yace toh. Yana kashe wayar na kira Ni'ima, muna

gama gaisawa tace "yanzu kuwa Abbu ya bar nan" nayi jim ina kokarin yin maraba da sunan shi da naji ta ambata, haka kawai naji zuciyata ta dauki bugu da karfi, "umh ya su Mama?" nayi Kokari na kauda hirar Abbu da take kokarin sakowa amma duk da haka ban tsira ba, "next week ne bikin bude kamfanin shi a Beijing, how I wish zan samu zuwa" na hangame baki cikin mamaki nace "Da gaske?" tace wallahi kuwa. Nace "Masha Allah! Lallai zan kira shi in taya shi murna, na dade da jin labarin bude kamfanin wajen Bala Malam, ni nayi zaton ma an jima da budewa ashe har yanzu?" tace "kin san dama bude kamfani a kasar waje is not something easy musamman ga wanda yake ba dan kasar ba, don ma abokin aikin nashi haifaffen Beijing din ne shi yasa" na gyada kai. Tace "Hajiyar mu tayi mamakin tafiyar ki fa dazu da Babban Yaya yana gaya mata, tayi ta korafin baki masu bankwana ba" a raina naji babu dadi, sai lokacin naji ban kyauta ba, haka na baro Kano bayan Iyalan Abbu da Anty Haleemah babu wanda na wa sallama, nace "in shaa Allah duk ranar dana kara shigowa Kano zan zo in gaishe ta" tace better! Muka dan

kara hira kafin muka yi sallama. Later in the evening Daddy ya dauke mu muka fita yawon gari, shiga nan fita nan har gidan Anty Uwani muka je acan ma muka yi sallar Magriba kafin muka juyo gida.

Sai dana gama shirin kwanciya barci misalin karfe tara na dare sannan na turawa Abbu text message, "Abbu naji ance zaku bude kamfanin ku next week, Allah ya sanya Albarka da Alkhairi.
And thank you for the necklace, it's beautiful, I like it!".
[09:16, 12/4/2017] : Minti biyar tsakani naji Wayata tana vibrating, da sauri na janyo ta, as expected; Abbu ne. Sashe daya na zuciyata cike yake da murnar jin muryar Abbu yayin da a gefe daya nake jin wata er fargaba da tsoro dana rasa ko na menene a cikin raina. Na daga wayar da sallama cikin wata siririyar murya wadda ban san ina da Ita ba. A nashi bangaren sai da yaji wani yarr! Hakan ne ya haddasa mishi sanyin jiki da sanyin murya a lokaci guda, shima cikin sanyin muryar ya amsa min, yace "Why didn't you call early?" ban fahimci abinda yace ba nace "naga dare yayi ne shi yasa

na maka text" wanda a hakikanin gaskiya ba haka bane ba, ina jin tsoron abinda jin muryar Abbu zai haddasa min a cikin jikina ne, yace "it's just nine fa, ya kike anyway?" nace "lafiya lau...... Naga sarkar daka bani, nagode sosai" ya dan yi er dariya, "shine Daddyn ki ya kira ni yau tun da safe yana interrogating dina kamar wani wanda yayi kyauta da abinda bai dace ba, sha ya bani dariya sosai ya kuma burge ni" naji na dan saki murmushi, ina so inji ana yabon iyayena, nace "sarkar ce Abbu naji Mommy tace babba ce, why would you give me such a precious thing?" na tambaye shi abinda nake ta tunani tun dazu, me yasa zai bani sarka babba haka ni ba diyar shi ba ni ba matar shi ba,in fact bamu hada ko wace irin alaka dashi ba sai ta Diyar Aboki da Abokin Uba? Ya katse ni ta hanyar cewa "Because I can ofcoure! So ya kika ga sarkar? Ina fata ta burge ki?" na kalli zoben hannuna naga yadda ta kayata hannun nawa sosai, nace "Sosai ma Abbu, zoben ya zauna a hannuna perfectly kamar don ni aka yi shi" yace "ai dama saboda Ke aka yi shi din" na danyi jim ina so kada in yiwa amsar tashi fahimtar da ba kenan ba, na maida akalar hirar

tamu zuwa wata daban ta hanyar tambayar shi ina su Hafsy! Yace "pretty ta sha kuka tun jiya har dan zazzabi tayi saboda tafiyar ki" nace "Allah sarki Hafsy! I really miss her so much!" ba zato naji yace "ni fa?!" tsit nayi ina kifta idanu, maganar tazo min a bazata, ya sake cewa "ni fa? Didn't you miss me?" cikin wata irin seductive murya, Ya Allah! Me Abbu yake nufi da innocent rayuwata ne yake min magana cikin irin wannan muryar? Na tabbata da a kusa dashi nake babu abinda zai hana ni jefa jikina kan shi, cikin rawar murya numfashi na har daukewa yake nace "Abbu... Sai.... Da safe. I gotta go" daga can bangaren shi ya dan hade ran shi, a hankali yace "you are not enjoying having my company?" nayi saurin girgiza kaina, idan da mutumin da nafi jin dadin hira dashi duk duniyar nan wanda nake ganin ko kwana zamu yi akan waya muna hira ba zan gaji dashi ba to Abbu ne sai dai ina tsoron abinda zai je ya dawo, bana fata in sake dandana abinda naji daga Muneer a wajen ko wani namiji kenan ya zama dole in janye jikina daga Abbu tun kafin inyi ending up hurting my self. Nace "m just a bit sleepy ne Abbu" yace "ok,

yakamata kiyi barci kam. Sweet dreams to you""Thanks.... And same to you!" na karasa fada more like a whisper to myself, ban sani ba ko yaji ko bai ji ba? Bana ma so yaji din ni, nayi sauri na kashe wayar. Makale ta nayi a kirjina daidai saitin zuciyata ina ajiyar zuciya idanuna a lumshe, na kwashe Lokaci mai tsawo a haka kafin in silale kan gado in kwanta. Babu abinda ya dinga dawo min a cikin kaina irin fuskar Abbu, yanayin yadda yake gudanar da rayuwar shi very cool and impressive, murmushin shi, yanayin kallon shi, zubin halittar shi.... A takaice dai da tunanin Abbu nayi barci a ranar. Wasu irin mafarkai na dinga yi barkatai kala-kala kuma cikin su babu wanda ban ga Abbu a ciki ba. Muna zaune akan wani lilo ni dashi a wani hadadden lambu mai cike da ni'imah, hira muke yi dashi duk da bana sanin abinda yake fada amma murmushi nake tayi a mafarkin har ina hadawa da dariya, ya dauko strawberry da fork ya miko min, na daga bakina kenan zan karba naji an daka min duka a kafada ba shiri na tashi daga mafarkin da nake, hannuna dafe da kafadata inda yake min xugi na tashi zaune ina kallon wanda ya aikata

wannan danyen aiki. Mommy ce tsaye a kaina tana hararata, tunda naga haka nasan abinda nayi. Da sauri na kai duba na zuwa jikina, as I expected; babu riga. Da sauri naja bargo na rufe zuwa wuyana tare da sadda kaina kasa, nasan cewa yau mai kwatana a hannun Mom sai Allah. Cikin hararar da take jifa na dashi tace "Yanzu saboda Allah Ummiey har yanzu baki daina wannan rashin hankalin da kike yi ba? Haka kika je gidan mutane dama kina musu tallar halittar jikin ki?" da sauri na girgiza mata kai, "A'ah wallahi Mom, bana yi a can" tace sai anan koh saboda kin raina ni ko" nayi saurin girgiza kai nan ma, "Allah Mommy ba haka bane, ni fa ban ma san lokacin dana cire rigar ba" tace "rufa min baki nan uwar en zagin baki tun yaushe nake miki fada game da haka Ummiey? Amma saboda taurin kai saboda kin maida ni abokiyar wasan ki baki ji koh?" tuni hawaye suka ciko min ido abinda nasan Mommy bata so kenan, cikin shagwaba nace "Allah Mommy da gaske nake. Nima fa ban san lokacin da nake cirewa ba, kawai ji nake yi kamar rigar ta na shake ni sai in kasa numfashi shi yasa nake cire rigar kuma fa na daina Allah da gaske,

ban san ya aka yi na cire jiya ba" ta kalleni kafin ta kauda kai ta juya zata bar dakin, "sai ki tashi ai kiyi sallah koh? An kira tun dazu" na bita da kallo har ta bar dakin, sighing nayi a hankali tare da lalubo rigata da nayi jifa da Ita a kasan gado na zura, saukowa nayi daga kan gadon na fada bandaki.

Anty Shafa ta fito daga dakin da aka mata masauki tana jan hannun Mukhlis, muna zaune a cikin falo Bayan mun gama cin abinci, ina gefen Mommy a zaune kawai muna hira da ita. Anty tace "Ummiey zo ki raka ni mana?" Na kalli Mommy kafin in maida kallona ga Antyn, Mommy tace "ni fa ba hana ki zan yi ba kike wani kallona, tashi ku tafi mana" murmushi nayi na tashi na shiga dakina, wandon jeans ne a jikina da shirt don haka na saka doguwar hijabi na fita muka wuce gidan su Anty. A Shagari road suke basu da nisa da inda muke don haka tricycle muka yi shata har kofar gidansu, gidan Babban gida ne da parts parts. Mahaifin su matan shi uku saboda haka gidan su gidan iyali ne sosai, Anty Shafa itace autar uwargidan Hajiya Maryam wadda ta rasu shekaru biyu

da suka wuce. Muna shiga gidan gida ya dauki sowar murnar zuwanta, da kyar muka samu muka shiga part din Hajiya Talatu uwar gida a halin da ake ciki. Muka shiga har uwar dakanta inda muka sameta akan gado a hakimce, cike da girmamawa muka gaidata ta wani amsa da kyar kamar wadda aka takurawa, dana kalleta sosai sai naga kamanninsu da gayen nan na airport na tabe baki a raina nace ashe gado yayi. Bamu yi minti goma ba muka tashi muka wuce daya part din, Ita dayar da naji suna cewa Hajiya Amarya ba laifi tana da fara'a. Anan sashen nata en sannu da zuwa suka yi ta shigi da fici. Sai wajen karfe goma na dare muka musu sallama, na saba Mukhlis dake ta shakar barci a kafadata. Muna fita waje muka jiyo horn din mota a gefenmu, muka juya. Wata jar mota er karama da Ita mai kyau, Anty tace muje, Harith ne zai mika mu gida. Sai dana turo baki kafin na bi bayanta, haka kawai naji gayen bai kwanta min a rai ba. Na bude gidan baya na zauna a gefen Anty, Harith ya juyo ya kalli Antyn kafin ya kalleni ya sake kallonta, "amma dai ina fata ba Driver zaku maida ni ba ko Sis?" Anty tace min dan Allah tashi ki

koma gaba diyata. Ba yanda na iya na fita na koma gaban, ya tashi motar muka tafi. Babu wanda yayi magana a cikinmu har muka isa kofar gidanmu, yayi parking muka fita, Anty tace mishi "sai da safe koh?" bai amsa ba sai kallona da yayi, "enmata babu godiya ne?" ban san lokacin dana wurga mishi harara ba na juya na wuce abina, na kula he's very arrogant. Anty ta biyo bayana tana ce min wai kar in damu dashi, haka halinshi yake. Ban ma tanka mata ba don a tunanina ai sai ka damu da mutum ne sannan al'amuran shi suke damun ka. Sai da muka shimfidar da Mukhlis sannan na mata sai da safe na wuce dakina, cikin mintuna sha biyar na gama duk shirin da zan yi na kwanta barci.

Washegari aka fara bikin gidan su Anty Shafa, tun da safe ta tafi ni kam ko wajen bikin ban leka ba Mommy ce ma taje. Ina gida da yamma Malamin dake koya min karatu yazo ya kara min, lokacin Mommy ta dawo muka shiga kicin muka girka Jollof macaroni da fried chicken, muna girkin nake tambayarta Mama Sauda da yake kwana biyu ta sha rashin lafiya don haka suka maidata

kauyen su tace ai taji sauki tuni, Daddy ne yace tayi zamanta a can kawai, na gyada kai.

Ni kadai ce a cikin falon lokacin da Anty Shafa ta dawo, na mata sannu da zuwa tace "tare muke da Harith wai yunwa yake ji, Allah sa akwai abincin?" na kalli dinning nace "akwai, sai dai ban tunanin zai ishe ku ku biyu" tace "nooo, ni nace abinci a gida, shine wai ba zai ci abincin biki ba, he can be picky about foods sometimes" na tabe baki nace shi ya sani ai. Anty tayi murmushi tare da juyawa don mishi iso ni kuma na leka dakin Mommy na fada mata. Ina dawowa falon yana zaune a daya daga cikin kujerun falon, Mukhlis yana cinyar shi, yaron yana ganina ya sauka daga kan cinyar shi ya rugo ya rungume ni, na tare shi ina dariya nace "mun shirya yanzu kenan?" Anty tace dama shi ai kwana daya ake Sabo dashi. Saboda idon Anty ne yasa na kalli sashen da Harith yake, "sannu" kawai nace, ban tsaya jiran amsawar shi ba na wuce dinning nayi serving dinshi abincin a plate na kai gaban shi na ajiye, kan kujera na koma na zauna na ja Mukhlis jikina ina jan shi da hira.

Ya kalleni yace 'enmata baki bani ruwa ba" sai dana kalleshi kafin na tashi kicin naje na dauko ruwa mai sanyi a fridge na kawo na ajiye mishi, yace "sorry! Bana shan ruwa mai sanyi" na ciza lebe tare da dauke goran ruwan na je na canzo mishi da mara sanyi na kai mishi ya sake kallona yace "Baku da lemu ne haka kamar fanta ko peach?" zuwa lokacin nasan cewa he's doing it on purpose, ban ko kalleshi ba na koma na zauna abina, ya kalli Anty ya wani lankwashe murya, "Anty lemu nake so" tace Bari in dauko maka to, wanne kake so? Yayi saurin cewa "no no Anty, da girman ki ki dauko mun lemu haba! Bari yarinyar can ta dauko min mana" ban san lokacin da wani irin murmushin takaici ya subucewa fatar bakina ba, lallai ma Harith! Wai yarinya! Anty da bata kula da game din da yake bugawa ba ta tashi tsaye tace "Ummiey don Allah taimake shi da lemu, bari in rage kayan jikina" ta shige dakinta ni kuma naci gaba da wasana ni da Mukhlis, kallona yayi yace "baki ji abinda Sis tace ba? Ki bani lemu!" ban kalli sashen da yake ba nace "the kitchen door is over there...." na nuna mishi da yatsa ta, "zaka iya zuwa ka dauko da kanka, m

not someone da u can be ordering around ni kuma in biye maka kamar wata er aikin ka" yayi wani irin smirking tare da dan shafa gefen wuyan shi, "seems like u r one Rude babe, I like it!" a xafafe na jefa mishi harara, "hey watch ur mouth!" ya tsuke baki yana jifana da wani irin kallo, "if not ki raba ni dashi?" tsaki kawai naja na kauda kaina gefe don na kula da neman magana ne kawai yake yi. Anty ta fito daga dakinta ta zauna a gefen Harith, ganin yadda nake jifan shi da harara ta dube shi cike da tuhuma tace "Me ka mata Harith?" ya kalleta kafin ya kalleni cikin dage gira, "Me na miki?" tashi kawai nayi na bar musu falon don na kula idan na zauna Harith zai iya sawa in zage shi a gaban Yayar shi abinda bana so kenan. Dakina na koma na fara chatting, a facebook na ga wani page da wani daga cikin friends dina yayi liking, Hon. Ibrahim Galadanchi Official Fans Page cikin mamaki na shiga page din, da gaske Abbu dinne. A Profile pic din da aka dora Abbu ne ya saka wata shadda Skye blue dinkin Abacha, shaddar ta matukar yi mishi kyau, kwarjinin shi da kyawun shi sun fito kamar ka kira shi a hoton ya amsa saboda yadda hoton ya

dauku sosai. Na kura mishi ido na dan lokaci kafin na janye kaina, jikina yayi wani irin sanyi wanda ganin hoton Abbu da nayi yanzu ya haddasa min, sai kuma wani tunani daya darsu a raina, kenan Abbu har yanzu yana kan bakan shi akan fitowa siyasa? Ni dana ji shiru kwana biyu ban ji zancen ba nayi zaton ko ya hakura ne ashe bai hakura ba. Kenan idan har na aure shi sai dai in janye kiyayyar siyasa dana sawa raina, kenan zan zama matar dan siyasa? Murmushi nake yi kamar wata doluwa da nayi wannan tunanin, na sake janyo wayata nayi liking din page din. Ranar haka na bata Lokaci na wajen saving din pics din Abbu da suke cikin page din, sai wajen karfe sha biyu na kashe wayar na kwanta.

A hankali na juya na kalleshi, ya sake wanka yasa wani wandon jeans din Vogo da rigar CK mai V-neck, ya matso kusa dani ya tsaya gab dani yana kallon Muneer fuskar shi a cunkushe, sun dauki lokaci suna kallon-kallo shi da Muneer babu wanda yayi magana a cikin su, sai da naga shirun yayi yawa sannan na daga kafa na fara tafiya, na kalleshi nace "muje koh?" babu musu ya biyo

bayana muka jera muka tafi, muna fara tafiyar ya tsaya cak tare da juyawa ya kalli Muneer da shima ya juyo yana kallonmu, yatsa ya nuna mishi cikin kashedi yace "and dude, stay out of my Fiancé side, if not....." ya juya ya cigaba da tafiya cikin takama har yana hadawa da wani bouncing, na bi bayan shi ina dan murmushin jin dadin shocked and horror expression din dana gani akan fuskar Muneer. Ramlah dake tsaye a gefe tana kallon dramar da muke bugawa ta kamo hannuna taja gefe tana tambayana wai da gaske na daina son Muneer? In ka kalli fuskarta a lokacin sai ta baka dariya, grinning take ear to ear kamar yaron da aka ba kyauta alewar bounty. Na sabule hannunta daga nawa nace mata "kinga jirana ake yi, anjima zamu yi magana" muka yi sallama na wuce na shiga motar Harith har ya tashe ta don haka ja kawai yayi muka wuce. Harara na jefa mishi, ya juyo ya kalleni "what??" nace "what was that for? That fiancé thing??" yayi rolling idanunshi, "baki gane bane? I was just trying to save you from him so that next time ba zai kara damun ki ba koda bana nan, by the way waye shi?" na danyi sighing softly kafin na

kalleshi fuskana a dan hade don ya dauki maganar da zan mishi seriously nace "sanin waye Muneer ko rashin sa babu abinda zai tsinana maka don haka stay out of it, maganar fiancé kuma kada ka kara koda cikin wasa ne kuwa ko trying to help kamar yadda kace" ya kalleni yana murmushi cikin tsokana, "ko dai baki son inji cewa crush dinki ne yayi dumping dinki kuma ya dawo yace yana son ki?" kaina na kawar gefe naki kallonshi, naki jinin a tuna min da tarin yarinta da rashin hankalin da nayi akan Muneer. Amma Harith bai kyaleni ba cewa ya sake yi "tunda baya sonki me zai hana ki zo mu sasanta dake?" a fusace na kalleshi "stop messing with me fa Harith!!" ya tabe baki, "well, m not ai dama" nace "to ni nan da kake gani na I am taken ka gane?" ya juyo ya kura min ido na dan lokaci kafin ya maida hankalin shi ga tukin da yake yi yana chuckling, ban kula shi ba na janyo wayata ina latse-latse har muka isa gida. Yau ko godiya bai samu albarkacin jin ta ba, na fita daga motar har ina banging nayi cikin gida. Kai tsaye dakina na shige, nayi jifa da jakata akan gado kafin nabi bayanta

nima na kwanta a rigingine ina tariyo abinda ya faru a makaranta ranar.

Vibrating din da wayata ya dauka daga cikin jakata ne ya dawo dani cikin hankalina, na danyi tsaki lokacin da nake laluben wayar, da kyar na iya bude idanuna da suka fara min nauyi saboda gajiya da barci na dora su akan fuskar wayar, sunan dana gani yana bouncing a jikin screen din wayar ne yasa naji zuciyata ta fara daka tsalle cikin wani irin farin ciki. Ya Allah! Yaushe rabona da inji muryar Abbu a rayuwa har na manta, Kun ganni nan kullum ina cikin page dinshi a facebook ina bibiyar rayuwar shi amma na kasa samun kwarin gwiwar kiran shi duk da cewa nayi kewar shi kuwa fiye da tsammanin mai karatu. Ganin kiran yana shirin katsewa yasa nayi saurin dagawa, sallama na mishi a nutse kuma cikin Karya murya, ya amsa cikin wannan muryar tashi cike da kasaita da wani irin huskiness daya kusa saka ni narkewa akan katifata saboda yadda naji wani electricity yana yawo a magudanar jini na. Daga can naji yana magana wadda tayi sanadiyar dawo dani duniyar Earth

daga tafiyar da nayi zuwa Mars, cewa yayi "wato Nafeesah idan shekara zamu dauka ba tare da mun gaisa ba hakan bai dame ki ba koh? Ba kya neman mutane idan ba neman ki aka yi ba koh?" da sauri nace "Abbu ba haka bane ba fa!" yayi wata irin sassanyar dariya, "to ya ne Nafeesah?" na dan sosa wuyana tare da dan gyara muryata ina kokarin boye yadda dariyar Abbu ta kassara min gabbai, nace "Abbu muna karatu ne kuma dai bana so in kira ka ko kana aiki ko wani abu in takura ka"'ina tsoron ka gaji dani, ina tsoron yin sabo da abinda zai zo yayi hurting dina daga baya" yace "that's not an excuse Nafeesah, when you feel like calling me just don't hesitate and call, zan amsa a duk inda nake no matter what m doing" na gyada kai kamar yana ganina nace "toh Abbu" ya sauya akalar hirar zuwa ta harkar karatuna, mun dauki lokaci muna hira kafin yace "Jiya muka dawo daga Beijing, nayo miki lodin tsarabar favorites chocolate crunch dinki, gabadaya na manta baki gidan ashe" nayi shiru kamar ba zanyi magana ba, wani irin dunkulallen abu ne naji ya makale min a kirji da kyar na iya danne shi na bude baki nace

"Eyyah!! How I wish ina nan" yace "that's what m saying" nace "a ba Hafsy shi kawai, Allah ya nufa ba rabo na bane shi yasa" yace "um-uhm, abinda yake naki ne dole ki zaki ci shi Nafeesah. Pretty da kowa yaci nashi don haka kema dole naki zaki ce" na saki murmushi cikin jin dadin maganar shi, a hankali kuma cike da wani irin expectation nace "to ya za ayi yanzu?" shima yayi kasa da muryar shi har tafi tawa yin low, "ya za ayi? M thinking of coming to give it to you, Personally!" na karkada kunnena kamar ban ji sosai ba, sai dana dan yi hesitating kafin a hankali na maimaita "you?? Personally???!" sai dai can kasar zuciyata tsoro ne ya cikata, ina tsoron yace ba haka yace ba kila yace ba haka yake nufi ba.... Ya wanke min zargina ta hanyar cewa "yes, I'll come to you in baki tsarabar ki Nafeesah!!". Murnar dana ji ta cika min ciki ta ware a take lokacin da confusion ya dabaibaye ni, nace "amma why would you??" yace "because.... Because...... I.......!!" numfashi na ya dauke yayi sama yaki dawowa, na tabbata zuciyata ta buga sau dari cikin sakwannin da basu fi goma ba ina jiran inji karshen maganar shi, ".....

Because I Can Of course Nafeesah!!" sai a lokacin numfashi na ya dawo kasa daga sama din da yayi, na fara yaki da zuciyata wajen ganin gudun da take yi marar adadi da numfashina da yake daidaituwa sun daidaita, a gefe guda wani irin disappointment ne ya lullube min zuciya. I'm such an idiot to think that Abbu zai fada min kalaman so! Yakamata in dawo daga duniyar Fantasy da Tunanin cewa wai Abbu zai so ni, Abbu yana da matar shi har da 'ya'ya abinsu and duk da cewa maimakon Happily, they are peacefully living together rather. Yace "besides Tu Me Manques!!" na dan yamutsa fuska, "Too mey Manqwe? Me kenan??" yayi er dariya, "just..... Sai anjima dai kawai. And please kiyi Kokari ki dinga kira na fa!" daga haka ya kashe wayar ya barni jiki a sanyaye kuma a sankame. Ajiyar zuciya na saki a hankali tare da saka kaina cikin tafukan hannuwana biyu ina jijjigawa, ji nayi xuciyata ta dauki wani irin zafi, na fara jefawa kaina tambayoyi da suka fara shirin tarwatsa min kwanya, Me ke damuna da Rayuwa ta ne? Me yasa nake son Mazan da basa sona ne? Me yasa zuciyata zata dinga jefa ni cikin damuwa ne

a koda yaushe?? Bayan son Muneer da shi bashi ma da mata balle yaya, xuciyata tayi tsalle ta koma kan mutum mai iyali kamar Abbu, Abbu da yake Abokin Daddy na. Me zan fito in gayawa duniya? Anya Duniya ba zata zage ni ba kuwa?? Na dage kullum ina kara nutsa kaina cikin son kogin Abbu ba tare da nayi la'akari da halin da zan jefa kaina da iyayena a ciki ba..... Kafadata naji an dafa, an dago da sauri na kalli Anty Shafa wadda take zaune a gefen gado inda nake zaune, na riga nayi nisa a duniyar tunani ban ma san lokacin data shigo dakin ba. Fuskarta dauke da damuwa tace min "lafiyan ki lau Nafeesah? Tun dazu nake magana a kanki amma ba kya jina" kai kawai na girgiza mata to ince mata me? 'Abokin Baba na nake so shi kuma baya so na?' nasan zagina kawai zata yi ko ta ce bani da hankali, don haka na bame bakina nayi shiru, it's better to deal with it on my own. Tace "you are lying Nafeesah! ga damuwa nan kwance akan fuskar ki ina gani, kar ki boye min komi kinji? Tell me, me ya faru?" kallonta nayi tare da sake girgiza mata kai ina jifanta da murmushin dani kaina nasan ko idanuna bai Kai ba balle xuciyata, nace "babu komi Anty,

it's just a minor headache" ta kalleni cikin rashin yarda yayin da naci gaba da haske ta da murmushi kawai, sighing tayi tare da mikewa tsaye tace Mommynki ce take cigiyar ki dama shine nace bari in leko in gani ko lafiya? Na mike tsaye nace "bari inje in ganta lafiya na lau" Anty dai ta juya ta fita, na ajiye numfashi a hankali kafin na bi bayanta.

Aunty Shafa tana ta shirye-shiryen komawa nan da kwana biyu don haka bata zama a gida, tana ta faman ziyarce-xiyarce da sallama gidan en uwa da abokan arziki. Ranar juma'ah karfe sha biyu muka gama lectures, muna fitowa ni da Ramlah daga lecture hall din na hango Harith jingine da motar shi hannunshi rike da lemun team yana sha, yana ganin fitowar mu ya dago mana hannu. Ramlah ta kalleshi ta kalleni tace "wai meke tsakanin ki da Harith ne?" na girgiza kai, "to wa ya sani Ramlah? Nima kin ganni nan ban sani ba wlh" ta tabe baki, "to Allah ya kyauta!" nace "ameeeeen". Daga nan muka yi sallama. Tun kafin in karasa ya bude min kofar motar, na shiga na zauna ya maida ya rufe. Yana

shiga motar na fara jefa mishi korafi ko bari ya tashi motar ban yi ba, "Wai Harith ba nace na yafe zuwa dauka na da kake yi ba?" sai daya tashi motar muka fara tafiya kafin yace "I was just in the neighborhood ne, nayi dropping Sister gidan Amarya Murja ne, shine nace bari in biyo in dauke ki tunda nasan kin gama lectures dinki" nace "ni ban ga kana shirin komawa ba" ya juyo ya kalleni yana murmushi, "why?? Saboda kin gaji da ganina? To babu inda zan koma, na gama karatuna ai" na juya na kalleshi sosai, "woah! Da gaske?" yayi murmushi more like a grinning, "nayi kankanta koh?" kaina na gyada mishi ina kara kare mishi kallo, dariya ya saka har yana dukan sitiyari. Yayi parking a kofar gidanmu, na dauki handbag dina na rataya a kafada nace thanks fa! Ya gyada kai, "Anytime!". Kallona ya tsaya yana yi, har na saka kafa ta daya waje na juyo ina kallonshi, "meye kake kallona?" murmushi yayi ya kalleni fuskarshi na nuna yana shirin yin serious magana ne, yace "Nafeesah! How about We come together with a plan and help ourselves??" na kalleshi cike da mamaki, "mu taimaki juna? Me kake nufi??" ya daga kafada

kamar maganar da zai yi ba mai amfani bace, "you see, there's this girl that I like....." yayi shiru yana kallona, ban ji mamaki ba haka babu shock din da naji saboda maganar shi, to ma akan me zan ji mamaki? Hankalina na mayar kan shi gabadaya ina sauraron shi, ya cigaba "she likes me too, sai dai bata son muyi aure nan kusa. Tana karatu a Turkish ne a Abuja and sai nan da shekara biyu zata gama, ni kuma na kosa... U know....!!" ya daga min gira ni kuma na Harare shi, ya kauda kai. Gyaran murya nayi a hankali bayan na gama digesting maganganun shi, nace "to daka gaya min mai kake tunanin zan yi ne??" ya juyo yana fuskanta ta sosai, "I want us to just play a game ta yadda zamu samu wadanda muke so Cikin sauki." nima na kara gyara zamana, "so??" yace "we will pretend to be lovers infront of them, I mean idan muka yi haka kishin mu zai sa su dawo kan hanya daga kaucewar da suka yi, zamu fara da Muneer ne ko menene? Tunda Ikhram 'Cara Mia' sai nan da two months zata zo gida" na hade fuska sosai, take naji raina ya wani baci, a xafafe na harare shi nace "idan har saboda Muneer kake zaton I'll be your partner

in this game then you are wrong Harith, Muneer has become 'a past' ya daina existing a duniyata!" ya sadda kanshi kasa embarrassingly, nace "But we can play it with someone, not Muneer dai" ya dago yana kallona fuskarshi dauke da murmushi, "Really Nafeesah? Oh you're really going to save my life, thank you! But waye wanda zamu bugawa wasan?" nayi rolling idanuna, "just..... By the way meye ma'anar Cara Mia din da kace?" yayi murmushi sosai, "it means My Darling in Russia" na tabe baki nace "wani fi'ili!! Ni kam bari in shiga gida toh!" muka bude motar a tare muka fita yana cewa bari ya shiga ya gaida Mommy.

A hankali rayuwa tana tafiya tana juyawa, cikin Ikon Allah minti yake shudewa ya zama awowi, awowi su koma raneku, raneku su koma satika kamar yanda satika suke juyewa su koma Watanni. Kimanin watanni biyu suka zo suka shude, ni da Harith mun yi developing wani irin shakuwa a tsakaninmu, da yawan mutane suna cewa soyayya ce a tsakaninmu ciki har da su Mommy da

Ramlah, mu kadai dai muka san menene Ainihin Akalar mu da juna.

A matukar gajiye muka shiga gidan ni da Daddy a safiyar ranar Sunday kenan muna ajiye numfashi daya bayan daya, Gym muka je wanda yake a cikin unguwar mu kamar yadda muke yi a cikin weekends. Muna shiga falon kicin na wuce na dauko mana ruwa mara sanyi na mikawa Daddy daya, nima na fara shan dayan. Sai da muka dan huta kafin muka wuce dakinmu, ruwa na watsa a jikina na saka kaya kawai na fita falo. Su Mommy har sun fara breakfast don haka nayi joining dinsu, a nutse muke cin abincin, ina jin Mommy tana gayawa Daddy bikin diyar wata Kawarta da za a fara cikin satin, tunda suka fara maganar na sha jinin jikina, a gaggauce na fara tura abincin ina so in tashi in bar musu wajen. Kamar daga sama naji Mommy ta jefo min tambayar da nake gudun tayi, "Ummiey Ke kam yaushe zaki gabatar da naki Mijin ne?" sau biyu kenan tana min maganar turo da wanda muke soyayya wanda nasan Harith take nufi, na turo baki tare da kara cusa fried

plantain a cikin bakina, Mommy ta kalli Daddy tace "Habibty kana jin mu fa!" Daddy yayi dariya yace "ina jin ku, kina bukatar bakina ne?" Mommy cike da jin haushi tace "Allah Habibty hakan bai dace ba fa! Yarinya kamar Nafeesah saboda Allah ace har yanzu tana gabanmu babu zancen aure, ina mata zancen ta fitar da miji kuma wai ka wani dinga wani tambaya na ko bakin ka nake bukatar ji?? Anya Habibty kana ma so Nafeesah tayi aure ma kuwa?" Daddy ya kalleta a hankali, duk da cewa maganar Mommy ta taba ranshi amma bai nuna hakan ba, he was very calm. Yace "kema kin san ba abunda nake nufi ba kenan Habibty, naga shi auren nan nufin Allah ne. Duk iya kokarinmu da tursasawar mu a gare ta idan Allah bai nufa ba babu yadda zamu yi. Nima ina son in ga auren Uwata saboda nasan Martaba da Mutunci 'Ya Mace suna gidan auren ta ba gidan Iyayen ta ba sai dai kin san bana so in tursasawa Uwata ko kadan. Kema din you are just desperate ne, amma duka-duka nawa Nafeesahr take? She's just Twenty Two Habibty!!" Mommy ta dafe kanta, "Ya Allah meke damun ku ne Kun kasa gane abinda nake nufi?" Daddy ya dafa

hannunta cikin sanyin murya yace "mun fahimta Habibty, sai dai muma ki fahimce mu mana. Na fada miki Auren nan...." tayi saurin cewa "naji, naji Habibty ba sai ka maimaita ba!" yayi murmushi, "ki dinga mata addu'ah kawai Habibty, amma tursasawar ki ba shine zai sa ko ya hana ba, only your prayers will" ta gyada kai gami da yin sighing cikin saddakarwa, "To Allah ya zaba mafi Alkhairi!" yace ameeen ko Ke fa Habibty? Na saki ajiyar zuciya a sace, muka ci gaba da cin abincin mu. Can kuma Mommy ta sake dagowa ta kalli sashin da nake, "amma meke tsakaninku ke da Harith ne?" na kalleta, "Mommy, sau dubu nawa kike so in gaya miki babu komi?" Mommy tace "to ku ne na rasa gane inda kuka sa gaba" ni dai na samu na lallaba na bar musu teburin kafin wata maganar ta sake bullowa. Wayata na cire a jikin Caji na shiga cikin whatsapp, dp din Abbu na daga, ya canza shi daga wani hoton shi daya dauka cikin suits bakake ya maida shi zuwa wanda suka dauka shi da 'ya'yan shi kamar a wani restaurant ne ma, na kura musu idanu ina kallo ina murmushi, precious memories dinmu dasu suka dabaibaye ni, take naji wasu irin kewar

su ta cika min ciki, har na latso lambar shi zan buga sai kuma na fasa, na sake latsawa na fasa, a tunanina idan Abbu shi yana namiji ya iya kauda kanshi daga gareni why not ni mace? Tun ranar da muka yi waya dashi bamu sake wata wayar ba sai kimanin sati biyu da suka wuce, shima tambayana yayi wai ko ina da muradin zuwa BUK inyi D.E ni kuma nace mishi A'ah, daga ranar bamu sake waya ba sai dai muna exchanging din text messages dashi. A hankali nayi tsaki tare da ajiye wayar. Littafan makarantana na dauko na fara karatu ko na samu in daina tunanin Abbu. Gabadaya lamarin shi ya fara daure min rai, idan ya kira ni a waya ko ya min text, kulawar dake cikinsu sai su sa inyi zaton so ne yasa hakan, amma yanayin yadda mu'amalar mu take ko kadan bata yi mun kama da wani abu mai kama da so ba. Yatsun hannuna na nutsa a cikin gashina ina jan tsaki ganin har lokacin dai tunanin Abbu ne a cikin raina. Tashi nayi tsam na fara canza tsarin dakina gabadaya bayan na cika dakin da sautin music har sai da Mommy ta leko ta min magana sannan na rage.

Ranar Laraba a gajiye muka baro makaranta saboda Defense din IT da muka yi, da kyar na iya kai kaina bakin gate saboda gajiya inda nayi shatar tricycle zuwa gida, Harith baya Kaduna kwana biyu kenan, yaje New York wajen hado takardun shi saboda zai fara aiki. Na tura kofar gate din gidan na shiga, yamma tayi likis lokacin. Malam Idi maigadin gidanmu yana zaune a kan dan benci yana sauraron radio, na gaida shi ya amsa da fara'ar shi gami da min sannu da zuwa kafin na wuce falo. Ina shiga sallamar dana fara yi ta kakare a makogorona sakamakon Halittar da nayi ido hudu da ita..........

Abinci nake ci amma gabadaya hankalina baya kan abincin na dai san kawai ina kwaso abinci da spoon ina saka shi a cikin bakina, tunanina ya tafi ga yadda Mommy take acting weird tun zuwan Abbu, no tun zuwan Hafsy ma. Bayan su Abbu sun tafi jiya, mun gama dinner kenan na shiga daki Mommy ta biyo bayana, sam babu alamun wasa a fuskarta ta kalleni, "Ummiey me ke tsakanin ku da Baban Hafsat?" na kalleta da sauri kuma

cike da mamaki, tambaya ce mai sauki, haka kuma amsar ta ba mai wahala bace, amma me yasa naji kamar ba'a taba tambayana tambaya mai wahala irin wannan ba? Saboda ni a karan kaina ban san me ke tsakanin mu ba. Kai na girgiza mata, "Mommy me kika gani ne?" ta Harare ni, "Ummiey ba cewa nayi ki tambaye ni ba, amsa nake bukatar ji; Me Ke Tsakanin Ku Ke Da Baban Hafsat?" na danyi shrugging kafadata ina kokarin nuna babu komi, "me ke tsakanin mu kuwa Mommy? He's just Daddy's Friend, and I stayed with them for a while I think that's all!" tace "That's all?!" na jinjina mata kai cikin tabbatarwa, "yes!" tayi shiru tana kallona kafin ta sauke ajiyar zuciya, "ko ma dai Menene Ummiey, Ina fata zaki tsaya a iya inda Allah ya ajiye ki, and alakarku ta tsaya a haka Nafeesah, No more.... Bana son wani magana ya fita daga baya kina jina??" kallonta nake cike da mamaki, me ke damun Mom ne haka yau? Duk da hakan ban fasa daga mata kai ba, sai lokacin naga tayi murmushi. "good! Hurry up and go to bed then" nan ma Kai na sake gyada mata, "sure Mom, good night" tayi murmushi ta juya ta bar dakin tare da ja min kofa. Sosai

maganganun Mom suka tsaya min a rai, ranar haka na kwanta ina nanata maganar ta, 'In tsaya a matsayin da Allah ya ajiye ni?? Kada wata magana ta sake fita bayan alakar mu ta yanzu? Tana nufin kenan ba zata amshi Abbu a matsayin miji na ba? 'Miji??' naji na sake maimaita kalmar., wa yace Abbu zai zama mijina? Ni kadai nake imagining komi a cikin raina ba tare da tunanin shi Abbu din me yake tunani ba. Ni kadai nake tunanika na na manta da cin amanar da nake shirin yi, to cin amana mana! Na zauna lafiya qalau da iyalan Abbu cikin mutunci da girmamawa, daga karshe kuma kawai sai aji na aure mai gida? Anya na kyautawa kaina dasu kuwa? Me zan ce musu to? Me zasu daukeni, maciya Amana ko me? Su Qaseem.......... Shit!!! Me zasu dauke ni yanzu? Suddenly naji wata irin kunyar kaina ta kama ni, I wasn't thinking straight and smart. Ni da Abbu belongs to different worlds, I think it's time for me to let him go., let my dreams scattered just like how I did with my first love; Muneer!! Zuciyata tayi zafi sosai, m really an unlucky being!! Me yasa ban taba samun nasara akan soyayya ba a rayuwata? I mean me

na rasa? I am a very beautiful and attractive young lady in my twenties, ina da kyau ina da diri ina da duk abinda namiji yake bukata a jikin mace but why?? Why???.......

Ramlah ta dawo da hankalina cikin restaurant din ta hanyar jijjiga ni, "hey babe!! Come back to your senses!!" na zabura ina kallonta a tsorace kafin in Harare ta, "What?!" na fada almost shouting, tace "Ke zan tambaya, you were deep in a thought and you suddenly became teary, me ke faruwa dake ne yau?" na kai yatsa na dan taba idanuna, da gaske kuwa I was about to cry ga ruwan hawaye nan ya fara taruwa a idanuna. Ta rungume hannayenta a kirji tana kallona cike da tuhuma, na sauke kaina kasa kawai ina wasa da cokalina a cikin plate, I wasn't ready to discuss the matter with anyone a lokacin, I wanted to dealt with anything on my own don haka na share Ramlah kamar ban san abinda take nufi da hakan ba har sai data kai ga yin magana, "ba zaki magantu bane har sai na matse bakin ki?" na kalleta, "Ramlah am sorry ok? When I'm really, zamu yi maganar please!!" na fada pleadingly don

nasan halinta zata iya takura ni, hakan kuwa daidai yake da saka kuka na a cikin restaurant din makarantar mu. Tace "da gaske?" na gyada mata kai, tace "ok, kar ya dade fa kin san bana son jira koh?" na sake gyada mata kai. Na dauki lemun exotic na pineapple na kai bakina, kamar ruwa haka na dinga zugar shi sai kwalin kawai na ajiye kasa. A tare muka mike muka fita daga restaurant din, muna fita naji Ramlah tana xunguri na a bayana, na harareta, baki ta tabe cikin gulma ta rada min "mutumin ki is coming" na kalli inda ta nuna min da idanunta, Muneer ne tafe shi da abokanan shi suna tahowa inda muke da alamu restaurant din zasu zo. Naji ana zancen auren shi da aka daura last week, personally ya turo min Invitation Card na bikin nashi amma a take na aika aka maida mishi Ita don ban ga abinda zan je inyi a wajen bikin ba. Tsaki naja na fara tafiya abina, Ramlah ta biyo bayana, muka yi clashing dasu amma Muneer ko glancing at our side bai yi ba. Na kara jan tsaki a raina nace "banza dan akuya!" satika uku da suka wuce he was still following me around like crazy yana begging dina akan in bashi second chance shine yanzu daga yin

aure Sati daya yana share ni irin yaji dadin Amarya dinnan, na kara jan tsaki. As if I give a damn! Kamata yayi inji da damuwata ba wai ta wani Muneer ba. Hostel muka wuce ni da Ramlah saboda bamu da lectures ranar, next week zamu fara exams already mun yi covering lectures dinmu. Muna kan gadonta muna solving din wata problem a Calculus wayar ta tayi kara ta daga, ta dauki wayar ta kalli caller ID din, "Ni'ima ce" ta daga kiran tare da sakata a hands-free, "Guess what guys??" muryar Ni'imah ta doki kunnenmu cikin farinciki, muka hada baki wajen cewa "ya ne? Bamu mu sha please!" tace "umh.... Dama......" ta fara kauce kauce, Ramlah taja tsaki, "malama aiki muke yi idan ba zaki fada ba ki kashe wayar kawai" sai data gama kauce-kaucenta sannan tace "aure aka sa mana.... Nan da one month!!""WHAT??!" muka fada cikin karaji in Unison.

"What the fk! Wannan ai rashin mutunci ne Ni'imah" inji Ramlah tana hararar wayar kamar Ni'imar tana gabanta ne, nima nace "Lallai mu da aka raina ne sai yanzu ake fada mana, ba zan zo ba don ma kiji" Ramlah ma ta cafe

nan ma muka hau korafe-korafe har sai da muka rasa abin cewa sannan muka yi shiru, Ni'imah dai saurarenmu kawai take yi, ina jiyo dariyar Sa'adiya daga background din wayar. Tace "duka-duka jiya ne aka yi abin fa!" muka yi kus, ta cigaba, "muma bamu yi zaton abun will be so soon ba kawai jin su muka yi Kun gane? Now na isar da sakon da zan isar shikenan, Kun dai san you guys are needed one week before a fara bikin ko?" muka yi dariya ni da Ramlah, "yeah of course, ai dole ne. Thank God we're finishing our exams nan da sati biyu" muka yi sallama dasu, littafin da muke karantawa muka maida gefe muka fara hirar yadda zamu gudanar da bikin, wannan hirar ita ta dauke min tunanina gabadaya akan maganar Mom da sauran su.

Daddy ya kalleni, "yanzu Har Sati daya kawai saboda biki Uwata?" na turo baki gaba, "haba Daddy, su Ni'imah ne fa, kuma lokacin muna free tunda mun gama exams dinmu fa!" ya rausayar da kai, "ai shikenan! Allah ya

kaimu" nayi tsalle akan kujera daga zaunen da nake ina clapping hannu, "nagode Daddy! That's why you're always the best!" na mishi thumbs up da duka hannuwana, yayi dariya. Naci gaba da duba littafin hannuna shi kuma ya cigaba da kallon tashar Sports. Can na tambayeshi game da DE form din da yace zai sa a cika min, yace "ni na ma manta wallahi. Bari zan sake yiwa Ibrahim Magana inji yadda ake ciki" nace "Daddy Abbu kuma? Me yasa shi? Ni da ABU nake so in cike?" yace "ba kya son zuwa BUK din ne, me yasa?" na turo baki na, "ni nafi so ina kusa daku Daddy yadda kullum ba zan sha wahalar ganin ku ba!" yayi dariya yace "Uwata kenan! To in kika yi aure kuma fa? Kin san dai dole ki bar gidan nan koh?" na sake turo wani bakin, Mommy ta shigo dakin hannunta dauke da plate wanda aka yanka fruits a ciki. Ta kalleni kafin ta maida kallonta ga Daddy, "Habibty ina fata ba gulma ta kuke yi ba koh?" Daddy yace "mun isa! Diyar ki ce take zancen bata so ta rabu damu" Mommy ta ajiye plate din a tsakiyar dakin duk muka sauka kan carpet tace "Rabuwa kuwa ai ya zama dole tunda dai ke diya mace ce kuma Aure zaki

yi"'Ai fa an tabowa Mommy inda yake mata kaikayi' na fada a cikin raina, kwana biyun nan dama Mommy kamar mai jira, da an danyi magana zata hau zancen aure da waye da waye. Sai da muka cinye fruits din tas na dauke plate din tare da musu sai da safe, na kai plate din kicin kafin na wuce dakina nayi shirin kwanciya barci. Na budo hoton Abbu a cikin gallery dina ina kallo kamar yadda ya zama Al'adar rayuwata kowane dare, na janye idanuna daga kan hoton nashi na maida su kan frame din daya bani. Ban san meye dalilin da yasa ya bani frame din ba, ban san me yasa nake jin wani irin warmness da calmness a tare dani a duk lokacin dana kalli frame din ba. Koma dai menene na yanke shawarar janye Idanuna da Zuciyata daga kan Abbu. We didn't Deserve Each Other.

Harith yayi parking motar shi a kofar gidanmu, da yake ya dawo tun last week. Yau tsokana muka fita, gidan su Ikram budurwar shi muka je da yake itama tazo hutu. Har kofar gidansu muka je aka mata sallama ta fito da saurinta ita ala dole masoyinta yazo, yadda tayi turus

ganina akan motar shi ina wasa da keys din motar shi sai daya kusa bata mana budget, kaina na kawar gefe ina boye dariyar data kama ni. Haka ta daure ta karaso wajenmu muka gaisa Harith ya gabatar dani a matsayin sister dinshi, suka dan fara hira da ita, mintuna biyar basu cika ba na kalli Harith ina hamma nace "Hari, mu tafi gida!" da sauri ya mata sallama muka shige mota muka tafi, tana tsaye a inda take har muka bar layin. Dariyar abun muke yi har muka shiga gida kamar wasu sabbin mahaukata. Idanuna suka tsaya cak akan Abbu dake zaune akan fararen kujeru inda Daddy ya saba zama yana shan iska ko karatun jarida mostly on weekends. Kamar koda yaushe, babu abinda ya canza daga bugun da zuciyata take a duk lokacin dana ganshi, rawar da kafafuna suke da wani irin doki daya mamaye ni, makaman yakin dana tanada domin yakar zuciyar dake kayata min Abbu naji sun min nauyin dauka. Idanunshi fes akan mu suke, na kalli Harith a nutse nace "ina xuwa" ya gyada min kai. A hankali na fara tafiya zuwa inda yake zaune, kafafuna rawa suke yi saboda yadda nake jin idanun shi masu kaifi a kaina, da

taimakon Allah dai na karasa inda yake. Na dan duka a hankali nace "Abbu barka da yamma" ya gyada kai, "barka dai Nafeesah. Daga ina haka?" na rasa abinda zan ce mishi saboda ba makaranta naje ba saboda ranar bamu yi exams ba, nace "mun dan fita ne" ya kalli kofar da Harith ya bi ya shiga falo ya kara kallona fuskar shi dauke da wani irin kallo daya kada min sassan jiki, "and who is he??" nima na kalli kofar, nasan da Harith yake, nace "Harith...." na rasa abin cewa saboda yadda idanunshi suke zagaye fuskata gabadaya sun dauke min kuzari, ganin nayi shiru babu amsa ya gyada kai, "well dama naso ganin Daddyn ki ne shi yasa na zauna jiran shi nayi zaton zai dawo da wuri don na biya ta ofishin shi baya nan, but bana tunanin zan cigaba da jira kam. Zan kira shi kawai" ya tashi yana gyara wuyan rigar shaddar daya saka, ya kalleni har zuwa lokacin normal kallonshi bai dawo ba, yace "Kano na nufa yanxu in shaa Allah. Nan da sati daya zaki zo bikin su Ni'imah koh?" na gyada mishi kaina a hankali, yace "good! Sai mun hadu kenan" ya fara tattaki xuwa inda ya ajiye motar shi, na samu kaina da take mishi baya har gaban motar. Ya

saka makulli ya bude motar ya shiga ya kunna, sai lokacin ya juyo ya kalleni yana dan murmushi, Ya Allah! Da ba dan motar shi dana rike da hannuna ba da babu abinda zai hana ni faduwa a lokacin, na rasa irin effect din da Abbu yake dashi a tare dani. Yace "so??" nayi saurin kallonshi saboda gabadaya hankalina ya dauke daga gare shi, nayi saurin daidaita natsuwata nace "Allah ya sauke ka lafiya Abbu, a gaida su Anty Mubeenah da Hafsy" yayi murmushi wannan karon genuinely wanda tunda yaxo sai lokacin naga murmushin shi irin haka, yace "Ameen Nafeesah, zasu ji in shaa Allah!" yaja motar shi ya tafi nima na wuce cikin gida, a bakin kofa muka ci karo da Harith zai fito, yana gani na yace "sai anjima koh babe?" na harare shi ya danyi dariya saboda yasan na tsani sunan, ya wuce abinshi ni kuma na shige gida. Sai dana biya ta dakin Mommy na gaya mata na dawo, ta kalleni fuskarta babu yabo babu fallasa, "kin ga Baban Hafsat a waje kuwa?" gabana ya dan fadi, Allah dai yasa ba wani fadan zan sha ba. Nace "ehh, ya ma tafi ai" Mommy ta kalleni cikin tuhuma, na sadda kaina kasa ina wasa da jakar

hannuna, tace "na tambaye ki abinda ke tsakaninku kin ce babu komi, yanzu kuma me ya kawo shi wajen ki?" na kalleta da sauri, "ni fa ba wajena yazo ba wajen Daddy yazo, ya gaji da jiran dawowar shi ne shi yasa ya tafi" tace "haka ya gaya miki?" nace "ehhh, ba haka bane?" ta dan harare ni na kauda kaina, tace "shi kenan je ki" kamar jira nake yi dama, da sauri na bar mata dakin na wuce nawa ina ajiye numfashi a hankali. Duk yadda Tunanin Abinda Mommy take nufi da Tunanin makomar rayuwata da Abbu suka so dabaibaye ni haka naki basu dama, na dage da karatun exams sosai. Cikin ikon Allah cikin sati daya muka gama exams dinmu, cikin lokacin mun kara zuwa gidan su Ikram sau biyu. Wato idan na tuno diramar da muka buga a zuwanmu na karshe gidansu dariyar dake kama ni koh??

Sai ana washegari a fara harkokin bikin su Ni'imah sannan na tafi Kano. Gidan Anty Ameenah muka sauka directly saboda a can amaren suke zaman biki, su Hafsy suka fito suka min oyoyo yaran sun wani kara girma, ban taba sanin nayi kewar su sosai ba sai dana dora

idanuna a kansu. Qaseem ne ya dauki jakar hannuna na kama hannun Hafsy Abdullahi ya biyo mu a baya muka shiga gidan. Tarbar dana samu daga Anty Ameenah ta bani mamaki, har uwar dakinta ta kaini inda na samu su Anty Raliya da wasu abokan su, na gaida su suka amsa Anty Raliya na min korafin na tafi babu sallama ni dai nawa bada hakuri ne kawai don nasan cewa m at fault. Na shiga bandakin ta na watsa ruwa na fito nayi sallar Laasar, kafin in gama har an shirya min abinci a tsakiyar dakin ina gamawa na zauna na fara ci. Sai dana gama sannan aka kaini inda amaren suke. Dakine guda aka ware musu inda ake musu gyaran jiki, ina shiga hayaniya ta barke kamar me. Sai a lokacin aka min kitso da kunshi Allah ma yasa na je wankin kai a Kaduna.

Washegari aka yi kamu a Triple Crown Reception Masha Allah wajen ya tsaru iya tsaruwa, mata ne zallah a wajen mun yi shiga ta gargajiya haka ma kide-kiden da aka sa na gargajiya ne zallah. A wajen kamun ne muka hadu da Anty Mubeenah, tana nan yadda take babu abinda ya ragu a yanda take. Kibar nan tata marar fasali ta karu, table daya suka ja ita da kanwar ta Anty Shakira, ta

hakimce tana ta hure-huren hanci yayin da su Anty Ameenah suke ta kai kawo suna kokarin entertaining din baki. Na ja hannun Ramlah muka nufi teburin da suke zaune, tun kafin mu karasa nake yago hakora ina murmushi har muka gaban su na musu sallama tare da gaida su, I didn't expected her to look at me with a smile on her face, tace "Nafeesah sai a haka ake ganin ku ko?" ko babu komi naji dadin yadda tayi, nayi zaton wulakanci zan sha a wajenta kam. Nayi er dariya kawai na zauna a gefen Anty Shakira ina kara gaishe su, nan muka dan yi hirar yaushe gamo kafin na musu sallama na tashi muka cigaba da gudanar da sha'anin bikin mu. Bayan mun koma gida da dare na shiga dakin Anty Ameenah zan dauko kayan barcina da yake tunda naxo kayana suna dakinta, ina yin sallama muryar Abbu ta amsa min, sai dana yi kamar in koma da baya don dai kawai nasan yaji murya ta ne shi yasa. Na shiga cikin falon a hankali kaina a kasa kamar tsohuwar munafuka, daga can gefen shi na durkusa nace "Abbu sannu da zuwa!" muryar shi tayi kasa sosai akwai alamun gajiya sosai a tattare dashi, yace "yauwa Nafeesah, bani ruwa

please!" nace toh. Na fita zuwakicin naje na dauko mishi ruwa mai dan sanyi, har zan fito na kula da farfesun kayan cikin dake cikin warmer, na koma na dauko plate na zuba a ciki na cicciba. Na dire kayan a gaban shi, ya kalleni ya Kalli abincin, fuskar shi ta nuna alamun relaxing and amusement. Ya kalleni cikin lumsassun idanunshi, "Nafeesah!!" ya kira sunana cikin muryar rada, na kalleshi a hankali ba tare dana amsa ba, it's not that ban amsa ba, nayi niyar amsawa sai dai muryata bata fita ne balle har yaji, yace "Nafeesah!! Zaki iya....." maganar shi ta katse lokacin da Anty Ameenah ta shigo falon, na kalleshi da sauri cikin mamakin dalilin tsayawar maganar shi. Anty Ameenah ta zauna a gefen shi cike da tsokana tace "ya aka yi Ibu??" na sadda kaina kasa ina kokarinboye dariyar data taso min da jin sunan da Anty Ameenah ta kira shi dashi, ya dan ja tsaki kawai ya fara cin abinda na ajiye mishi. Ganin haka na tashi na shiga dakin na dauko kayana na fito na musu sai da safe na fita, idanun su suna kaina har na fita. Na kai gadon bayana akan katifar da aka shimfida mana a tsakiyar

dakin na kwanta, tunanina a lokacin me Abbu yaso fada min dazu??

Washegari aka yi Walimah anan farfajiyar gidan Anty Ameenah. Washegari kuma aka daura aureda dare muka tafi wajen dinner. Kamar da wasa ina juyawa daga seat din da nake zaune na hango Harith da Ikram a zaune, na zaro idanuna ina kallonsu daidai lokacin da shima ya juyo, na mishi alama da hannuna alamun "ya aka yi haka?" ya danyi shrugging kafadar shi. Wayata tayi kara a daidai lokacin da sauri na daga naga Ramlah ce take kira, na daga da sauri, tace in same ta a parking lot Fiancé dinta zai tafi mu gaisa. Nayi excusing kaina wajen wasu daga cikin abokan su Niimah da muke zaune a seat daya dasu na fita. A can parking lot na same su, muka gaisa da Ayan saurayin Ramlah, (Ban fa ce na Ummu Maryam da Ihsan ba... Don kar kusa Husna tayi daidai da naman jikina, tamm). Anan na baro su su gama sallamar su. A hankali nake tafiya saboda heel din dake kafa ta, gashi dinkin skirt din dake jikina ya dan matse ni somehow don haka bana iya daga kafata sosai

inyi tafiya. Kawai ji nayi an ja hannuna anyi gefe dani, na daga baki tun karfina zan kwala ihu, aka sa wani tattausan hannu akan bakin nawa ta yadda babu yadda za ayi ihun da nayi niyar yi ya fita......

"What the....... Harith meye haka?" na fada ina hararan shi, ya sake ni tare da jingina da mota. "ina so ne muyi magana in secret, can idanun mutane yayi yawa shi yasa" nace "shine kuma sai ka tsorata ni?" ya daga kafada, "sorry ok! Ikram tana hango mu fa, muje" muka fito daga wajen da yaja mu muna dan dariya muka tsaya a daidai inda zata dinga hango mu sosai, Harith ya kai hannun shi kamar zai yi cupping din fuskata., "Nafeesah?" Husky voice din Abbu ya sankame ni a wajen, bayan kamar sakan goma na juya a hankali kuma cike da tsoron irin fahimtar da zai mana. Tsaye yake a gefen mu sanye da shadda light brown da hula a kan shi, kallonmu yake daga ni har Harith din cikin alamun tambaya da kuma bacin rai. Take naji jikina yayi sanyi, na kalli Harith da a lokacin hankalinshi ya tafi da Ikram wadda ta juya zuwa cikin hall din kamar tana share

hawaye daga karshe ma sai ya bi bayanta. Na kalli Abbu da har lokacin kallona yake yi, idanunshi suna fitar da wani irin tartsatsin abu cike da alamun bacin rai, ya dan matso kusa dani yace "me kike yi anan?" na dan ja baya kadan saboda kusancin dake tsakanin mu kafin in ce "umh, dama na fito ne zamu gaisa da saurayin......" wani irin kallo daya watso min ne yasa nayi shiru jikina ya dauki rawa, me ke damun Abbu ne yau? Na daure na karasa ".... Ramlah kawata" sai lokacin na ga ya dan sassauta muryar shiidan ban yi mistake bama har da sighing yayi softly wanda na lura dashi ta yanayin yadda kirjin shi ya sauka a hankali. Ya katse shirun da muka yi ta hanyar cewa "kin yi kyau sosai yau.... Kodayake kullum ma haka kike" nace "hmmm" kawai saboda gabadaya na rasa abin cewait's really unlike him. Na sha jin kalmar yabo daga gareshi amma ban taba jin makamanciyar wannan ba don haka naji abun so strange. Yace "zaki koma cikin hall din ne??" na gyada kaina da sauri, yace "k, ni zan koma ne yanzu" na kalli agogon hannuna kafin in kalleshi, "karfe tara ne fa kawai Abbu zaka tafi tun yanzu" yayi er dariya data saka ni

shagala da kallonshi, "ban cika halartar ire-iren wadannan abubuwan ba Nafeesah.... Wannan din ma ya zamar min dole ne, naso ganin wani very badly kuma babu hanyar ganin nashi sai ta nan shi yasa" na gyada kai kamar na fahimce shi, sai dai maganar gaskiya na kasa processing maganganun shi a cikin kaina, babu abinda nake fahimta a lokacin irin daddadan kamshin turaren shi dake tashi da yadda zuciyata take bugu. Ya zura hannu a cikin aljihu ya ciro rafar kudi sababbi kar dasu ya miko min, naki saka hannu in karba har sai da yayi magana, "kudin liki ne ba wani abu ba, karbi" da sauri na hau girgiza kaina, "ina dasu nima Abbuka bar kudin ka" ya hade fuska "akwai abinda na taba baki a duniyar nan ba tare da kin min gardama ba kuwa?" nace "Abbu Allah ba gardama bace, kawai akwai kudin likin a wajena ne nima" yace "to tunda na baki ai sai ki amsa koh?" na bude baki zan yi magana ya sake hade muryar shi, "Nafeesah karbi kudin nan kafin raina ya baci fa" yana iya? Sai kawai na saka hannu biyu na karba har da dan dukawa nace "Nagode sosai Abbu Allah ya saka da alkhairi" yace "Ameen.... Go back" ba musu na mishi sai

da safe na wuce, ina jin idanun shi a kaina har na shige cikin hall din. Na koma wajen su Ramlah na zauna, lokacin da aka kira amaren suka fita wajen rawa muma muka tashi muka je muka fara liki. Sai sha biyu saura aka tashi daga wajen dinner dinnan, an daiyi komi lafiya an gama. Kafin mu isa masauki sai wajen karfe daya aikuwa mun sha fada sosai wajen Anty Ameenah kamar me! Washegari aka kai Amaren gidajen su na aure, ita Sa'adiya tana Lamido Crescent Ni'ima kuma suna Zoo road. A gidan Sa'adiya ne muka hadu da Ikram, mun gaisa da ita sama-sama tana ta wani shan kamshi ni kuwa ina mata dariya a ciki don nasan dalilin hade fuskar, sai a lokacin naji ashe cousin din mijin Sa'adiya ce. A washegari naso komawa gida Anty Ameenah tace ina! Ai sai na cinye sati daya din da aka bani daga gida, ban yarda da gaske take ba sai data dauke min jakar kaya ta kulle a bedroom dinta, ni wallahi dariya ma ta bani. Dole haka nan na zauna, dama kwana biyu suka rage min. Naje gidan Anty Haleemah da Anty Raliya, washegari kuma direban gidan Anty Ameenah ya kaini gidan Abbu. Da yake ranar Lahadi ce na samu Abbu a

gida, na ga tarbar data bani mamaki kam. Tun daga bakin gate su Hafsy suka taro ni suna ihun murna har cikin falo. Gidan yana nan kamar yadda na tafi na barshi, matar gidan tana uwar daka. Na shiga har ciki muka gaisa na koma falo wajen su Hafsy, nan suka fara ajiye min tarkacen kayan makulashe muka shiririce anan muna hirar mu har aka kira sallar Axuhur, Abbu ya fito daga dakinshi sanye da jallabiya ruwan toka da alamun masallaci zai je, na zamo daga kan kujerar da nake zaune na gaida shi, ya amsa tare da wuce mu su Abdullahi suka tashi suka bi bayan shi ni da Hafsy kuma muka shiga dakinta muka yi tamu sallahr.

Abbu ya mana odarabinci daga restaurant muka ci namu ni da Hafsy a daki. Ina nan a gidan har yamma tayi,direban Anty Ameenah ya dawo daukata, na je nawa Anty Mubeenah sallama muka fita zuwa inda direban yake jirana cikin rakiyar su Hafsy. Abbu yana zaune akan kujera da laptop a gabanshi akan dan karamin table yana ta danne-danne a ciki. Na fasa shiga motar da nayi niyar yi na taka zuwa gaban shi, ya dago

ya kalleni yana murmushi. Na sadda kaina kasa cike da kunya, "Abbu zan wuce" ya gyada kai, "gobe zaki koma koh?" na gyada kaina, yace "nima ina so zan shiga Kadunar gobe in shaa Allah. I'll drop you off goben, that is idan tafiyar tana nan" na kalleshi fuskana dauke da alamun tambaya sai dai na basar, ai yace akwai abinda zai kaishi kuma ma cewa yayi sai idan tafiyar tana nan ne sannan zai ajiye ni. Nayi murmushi nace "to Abbu, na tafi" ya gyada kai yana jifana da murmushin nan nashi, "ok Nafeesah! Mun gode da dariya" na danyi murmushi tare da juyawa na tafi. Muka sake yin sallama dasu Hafsy na shiga mota muka tafi, daidai saitin Abbu na dan saci kallonshi, idanunshi suna kaina yana kallona da wani irin yanayi da kallo with so much affection, nayi saurin sadda kaina kasa ban dago ba har sai da muka bar layin.

Na fito jaye da trolley dina, Anty Ameenah tana zaune akan kujera a falonta ta kalleni tana murmushi, "tun

kafin yamma tayi har kin gaji damu koh Nafeesah?" na girgiza kai ina murmushi nima "haba Anty ba haka bane, karfe hudu fa tayi already kuma kinsan akwai tafiya a gaban mu" tace "haka dai kika ce. Mun gode sosai duk da haka" na fara tafiya yayin data tashi ta biyo bayana. Abbu yana tsaye a jikin motar shi Toyota yana jiran fitowar mu. Hasken ranar dake haska shi ya kara haskaka shi cikin shigar Dogon wandon jeans baki da bakar shirt, hakan ya haskaka shi ba kadan ba. Kyawun shi da cikar kamalar shi suka kara fitowa sosai, ban san cewa na shagala a kallon shi ba sai da naji Anty Ameenah ta dan zungure ni, a matukar kunyace na sadda kaina kasa. Ya Allah! Abinda Bawan nan naka yake saka ni yi!! Ya bude booth muka saka akwatina a ciki. Na bude gefen mai zaman Banza na shiga na zauna, Anty Ameenah ta leko tana min addu'ar a sauka lafiya har Abbu ya shiga shima ya tashi motar muka tafi. Tuki yake yi a nutse kuma cike da kwarewa, baka jin motsin komi a cikin motar kamar babu abu mai numfashi a ciki. Ya kunna kira'ar Sudeis cikin Suratul Maryam, na dan kwantar da kaina a jikin kujerar. A matukar takure nake

ji na, it felt so awkward for me, to be hooked up with someone you so much cherish, wanda nake hangowa a matsayin mijin da zan aura, wanda da kyar nake hana kaina throwing my self to him a duk lokacin dana ganshi, yanzu da muke tafiyar nan sai nake jin wani iri a jikina, gashi duk yadda naso koda barci ne inyi abun yaci tura. Muna barin cikin gari Abbu ya ware injin mota, lokaci zuwa lokaci za a kira shi a waya ya daga da wannan damar nake samu in kare mishi kallo. Abbu is really good looking and handsome man. Wajen karfe shida muka fara shiga Kaduna, na dan sauke ajiyar zuciya a hankali ina jin kamar in bude idona in ganni a tsakiyar gidanmu. Well, it has really been a hell of a ride (-Justin Bieber). Can u believe that tunda muka shiga mota kalma daya bata hada mu dashi ba?? Suddenly naga yayi parking din motar a gefen hanya, wani dan karamin daji ne gab da za a shiga Kaduna. Inda yayi parking din motar gaban wata korama, reflection din rana da take kokarin faduwa ya fita zane a Vikings, the view was wow! Gashi wajen babu hayaniya sai ta ababen hawa dake ta wucewa a guje. Na daga idona na kalleshi cike da mamakin dalilin

da yasa muka tsaya anan, idanun shi suna ga koramar dake gaban mu, he seems out of the world, ya shige duniyar tunani. Na dan yi gyaran murya tare da cewa "Abbu.., laa.... fiya muka.... tsaya??" a hankali, bai kalleni ba, haka bai yi magana ba. Sai na tsaya kawai ina son in ga abinda xai faru. Lokaci mai tsayi muna a yanayin da muke har hasken rana ya fara daukewa duhu ya fara shigowa, tsoro ya fara shiga ta. Abbu ya kira sunana a hankali kamar mai rada, "Nafeesah!!" na kalli sashen da yake tare da amsawa, shiru ya sake biyo baya na kimanin minti guda. Kamar daga sama, kamar a duniyar mafarki naji saukar maganar, "Nafeesah! Zaki Aure ni??!". Tsabar firgita da mamaki sai da kaina ya buge da glass din motar, ban damu da zafin da naji ba Abbu kawai nake kallo kamar wata sabuwar mahaukaciya ko kuma shine nake wa kallon sabon mahaukaci?? Ganin expression din dana nuna yasa ya dan kauda fuskar shi daga kallona, "Nasan baki taba tsammanin faruwar hakan ba Nafeesah, na sani. Ni kaina nayi hesitating fada miki maganar nan yafi sau dari, sai dai I couldn't anymore. Auren ki nake son yi

Nafeesah da gaske, ina kuma fatan cewa zaki aminta da hakan?" ya juyo ya kalleni. Allah ne kadai yasan yanayin da nake ciki a lokacin, baki nake so in daga a lokacin in amsa mishi da YES! Da duk karfin da Allah ya bani, in gaya mishi nima burina kenan sai dai ina! Na ma manta yadda ake yin magana a dan lokacin. Wasu kyawawan mintuna biyu suka wuce a haka, wasu masallatan har an fara kiran sallar magriba. Abbu yace "look Nafeesah! M not forcing you into this kin gane? Zan baki lokaci kiyi tunani da kanki don bana so in tauye miki hakkin ki Nafeesah, idan nayi haka na cuce ki. I just..... M just tired Nafeesah. I want us to get married ASAP. Hell, idan kika amsa min yanzu m ready to marry you tomorrow Nafeesah.... Na baki lokaci ki samu time ki yanke shawara akan abinda kike gani sai dai kada ya dauki lokaci pls, sannan ina so kiyi duba da Allah da soyayyar da Iyalina suke nuna miki Nafeesah, we really need u in our lives". Da wannan ya tashi motar muka kara gaba, duk yadda naso in dawo cikin natsuwata abin yaci tura, yes! I was shocked beyond my imagination. Har yayi parking a kofar gidanmu, ina jin yana gayawa Mai gadi

da yake kokarin buddy kofa ba shiga ciki zai yi ba, Mai gadin yazo ya bude saitin kofar da nake yana jera min sannu da hanya. Kamar wadda aka daddaba daga barci, sai lokacin duniyata taci gaba da juyawa da dai tsayawa tayi cak. Na zura kafana daya waje da niyar fita, Abbu ya tsayar dani ta hanyar kiran sunana. Na dakata ba tare dana juya na kalleshi ba, bani da kuzarin kallon shi, ina tsoron abinda kallon fuskar shi zai haddasa min. Nasan zan iya amsa mishi da yes a take a lokacin. Yace "please think about US carefully Nafeesah, ina fatan jin daddadan labari daga gare ki" na karasa cira daya kafar na fita daga motar. Mai gadi ya maida mishi murfin motar ya rufe, ya sungumo trolley dina ya biyo ni dashi. Da kyar nake daga kafa ta. Taimakon Allah ne kadai ya kaini cikin gida, Mommy ta fito da saurinta tana min oyoyo, gani na a haka sai data yi turus. Ta matso tana tambaya na lafiya na lau kuwa? Da kyar na iya daga baki nace mata "gajiya" tace "shine kuma kika yi zuru-xuru haka? Wuce kije kiyi sallah kici abinci sai ki kwanta" babu musu na shige dakina. Na dauro alwala nayi sallah, yadda nake jin cikina a cike nasan babu abinda zan iya

ci a lokacin. Ko kayan jikina ban cire ba na haye gado tare da lashes wutar dakin. Ina jin lokacin da Mom ta leko dakin ta maida min kofar dakin ta rufe. A gajiye nake, barci nake ji, sai dai awa daya kenan da kwanciyata babu alamun barci a tattare dani. Maganganun Abbu suke replaying a cikin kwalwa ta over and over, for once in my life da naji farin ciki yana so ya saka ni kuka, sai dai shima kukan yaki zuwa. Ya Allah!! What in the world am I suppose to do??! Ranar nasan dama babu barci, ina zan iya barci dama idan har na cigaba da hango ni zaune akan gado a cikin gidan Abbu lullube da gyale???

Da murmushi na tashi akan fuskata, rabon da inyi barci mai dadin na yau har na manta. Naje nayi brush na fito falo, babu kowa a falon dama nasan ba lallai in ga kowa ba saboda karfe goma sha daya na safe ne lokacin. Break fast na fara yi kafin na shiga dakin Mommy na gaida ta. Tace inje in shirya zata aikeni gidan Aunty Uwani, da saurina naje na watsa ruwa na shirya na fito. Turaren wuta ne da kayan labule da bed sheets ban san

dai kona waye ba sai da naje can take ce min na diyar kanwar mijinta ne. Can kuryar dakinta na shige na nade akan gado ina kara tunanin makomar zancen Abbu a cikin raina, wani bangare yana shawarta ta da in kira shi a yanzu in fada mishi na amince, wani kuma yana gaya min hakan bai dace ba, wani kuma yana ce min in dan bashi lokaci dai gabadaya na rasa wanda zan dauka, a haka barci ya dauke ni saboda rashin barcin da ban samu a daren jiya ba, sai wajen karfe uku Anty Uwani ta tashe ni nayi sallah, bayan la'asar na musu sallama na wuce gida. Ina zuwa na ba mommy sakon data bani in kawo mata na wuce daki, ba a jima ba na fito muka shiga kicin da ita muka fara girki.

Kamar yadda yake Al'adar gidan mu, bayan an gama muna haduwa a dakin Daddy a yawancin darare, wani lokaci muyi kallo wani lokacin hira, sometimes ma musamman idan daddy yana ayyuka zaku ga kowa abinda ke gaban shi kawai yake yi. Ina zaune a kasan kujera ina browsing Mummy kuma tana kan kujera a xaune, Daddy ya fito daga bedroom din shi ya zauna a

kusa da Mommy. Daddy ya kira sunana in a serious tone, "Uwata" na amsa a nutse tare da kallon shi, yace "last two weeks da suka wuce Ibrahim ya same ni da wata magana mai Muhimmanci" yayi shiru yana kallona yayin da zuciyata ta hau duka kamar zata fado kasa, ya cigaba da magana "Yace wai Yana So Ya Aure Ki! Ni kuma nace mishi sai naji daga bakin ki don bana son tursasa ki akan abinda baki da niyar yi, me kika ce? Zaki Auri Ibrahim?" Na sadda kaina kasa ina wasa da yatsun hannuna, ban san abinda yakamata in ce ba, ina son Abbu kuma Ina son Auren shi? Ina son Abbu amma ina tunanin auren shi is not a good idea? Ko kuwa me zan ce?? Mommy tayi saurin riga ni magana, "Haba Abban Ummiey, kaima kasan cewa wannan ba abu bane mai yiwuwa. Shi bai yi tunanin abinda zai zo ya dawo bane ya kirkiro wannan magana? Wannan abu ba zai yiwu ba sam!" duka ni da Daddy muka kalleta, fuska a hade sosai take yin maganar, daga ganin yanayin idanunta nasan cewa she is strongly against it, sai jikina ya kara yin sanyi akan na da. Daddy yace "me kike cewa ne haka Habibty?" tace "Abinda ya kamata mana, Idan shi

idanun shi sun makance da cin Amana bai kamata naka su rufe ba Abban Ummiey. Haba! Ace daga tura yarinya yin IT na wata shida kawai sai aji wai ta buge da aure mai gida? Kaima kasan cewa wannan ba abu bane da zai yiwu ba, sai dai idan so kake ka saka mu a bakin duniya kuma" Daddy ya danyi murmushi, "sai dai idan basa son junan su Habibty, amma idan suna so then who cares about what people will say? Su mutane ai aikin su kenan ina tabbatar miki idan kika ce zaki biye ta mutane to numfashi ma sai sun miki izinin kiyi kenan?" Mommy ta hade fuska "na kula ga gaskiya nan kana gani kuru-kuru amma kana takewa, son Kai ne ko me? Aure dai Nafeesah da Ibrahim babu shi!! Ba zan taba bada hadin kaina ga cin amanar wannan da kuke shirin yi ba" Daddy yace "ke kuma kin ki fahimtar abinda soyayya zata yi da wannan ba zata iya ba, baki tsaya kinji ta bakin yarinya ba kin zauna kina ta tada jijiyoyin wuya, be it zaman aure ko cin amana kamar yadda kika ce don ni dai ban ga komi ba a ciki, ina ga ai ya rage ga yarinyar koh?" Mommy tace "ni nasan Ummiey ba zata taba aminta da hakan ba, ga samari nan bila adadin suna karakaina a

kanta sai ta buge da wani can, ga mata ga 'ya'ya, abokinka kuma for that matter, anya Abban Ummiey ka duba maganar nan sosai?" Daddy ya kalleni yace "Uwata!" na daga kai na kalleshi, yace "kada ki damu da abinda take fada kin ji? Just tell me idan kina son Ibrahim kuma zaki iya auren shi" na kalli Daddy na kalli Mommy, toh fa! Ga sanyin Idaniyata guda biyu a gabana, ko wanne ya zuba min ido yana jiran amsa ta wanda nasan cewa amsar da zan ba daya daidai take da bacin ran daya, abinda na tsani gani da ji kenan a duniyata ace daya daga cikin Iyayena yana cikin bacin rai sabida ni. Abinda Mommy take fada gaskiya ne, shima Daddy akan gaskiyar shi yake, to me zan yi kenan? M I going to disappoint one of them? Ya Allah!! M extremely confused! Na samu kaina da girgiza kai wanda ni a karan kaina ban san dalilin yin hakan ba, Daddy yace "me kike nufi da girgiza kai, eh ko aah??" na sake girgiza kaina, "ban sani ba Daddy!" Daddy ya kura min ido na tsawon lokaci, yace "tashi ki tafi kawai Uwata, Allah ya zaba mana mafi alkhairi" ba musu kuma ba tare dana kara uffan ba na musu sai da safe na wuce

dakina. Hannu dafe da kai na fada kan gadona na kwanta, na gaji! Na gaji haka nan. Haba! Kwana biyun nan kaina har ciwo yake yi tsabar tunanika da suka hana ni sukuni, abin ya ishe ni haka nan. Tashi nayi na fada toilet na dauro alwala na fito na haye kan Abin sallah, sallah na fara jerowa, dana gama na roki Allah akan yayi mun zabin abu da yafi alkhairi a cikin rayuwata, na gama nayi shirin kwanciya barci na kwanta zuciyata cike da sake-sake.

Tsawon sati guda Daddy bai sake min zancen Abbu ba Mommy ma haka, haka a tsayin lokacin nan ban sake ji daga Abbu ba. Mun koma makaranta don dama ba wani hutu aka bamu mai tsayi ba. Ranar Asabar ina kwance a dakina da hantsi, mun gama waya da Harith kenan yana gaya min yadda suke shan fada shi da Ikram akan wai ni budurwar shi ce ni kuma ina ta shan dariya, na ajiye wayar tare da kurawa ceiling ido ina kallo. Wani kiran wayar ne ya dawo dani cikin hankalina, na mika

hannu a sanyaye na dauki wayar. Ban san lokacin dana zabura na tashi zaune dangargar ba, Abbu. Kallon wayar kawai na dinga yi har kiran ya kusa karewa, in daga in ce mishi me? Koda yake na riga na gama yanke shawarar abinda nake ganin daidai ne a rayuwata so let's just finish this once and for all kawai, na karfafawa kaina gwiwa. Nayi gyaran murya tare da daga kiran na kara wayar a kunnena......

Assalamu Alaikum" sansanyar muryar shi ta doki kunnena, duk wani karfin gwiwa dana tanada da kaudin da nake na cewa Abbu ya daina firgita ni ashe aikin banza nake yi, a take muryar shi tayi raga-raga da naman jikina, yayi gyaran murya tare da ambatar sunana, na amsa a nutse kuma a hankali cikin muryar rada, shiru ya biyo bayan hakan na lokaci mai tsayi, baka jin komi sai karan iska dake wucewa ta cikin wayar. Yace "Nafeesah! Ya muka kare da maganar mu ne?" nayi shiru ina zare idanu, da me na shirya zan ce ne? Gabadaya komi ya fita daga cikin kwakwalwata, yace "umh?! Ina sauraron ki" na bude baki zan yi magana sai

dai sautin dake fita kawai shine "ermm.... ermmm" na kasa yin takamaimiyar magana. Abbu ya tausasa murya,

"look Nafeesah. I don't have much time yanzu, mintuna kadan suka rage min in tashi zuwa Vancouver zan yi wani four months course acan so please do tell me, me kike tunani? Ina son ayi ayi auren mu dana dawo Nafeesah, da so samu ne a gare ni da tafiyar nan dake zan yi ta a matsayin mata ta Nafeesah don ba wani tsayawa zan yi bata lokaci wajen soyayya kamar yaro ba, kin san na tsufa da hakan koh?" wata hudu a Vancouver? A perfect timing!! Yace ina jin ki Nafeesah, an fara kiran fasinjoji, me kike tunani? Zaki iya aure na??" na lumshe ido a hankali zuciyata na suya a kirjina kamar an tsoma ta a ruwan zafi, "I Am Sorry Abbu...... I can't!" shiru ba magana daga bangaren shi yayin da kowace wucewar dakika zuciyata take nunka gudunta har na fara tunanin idan na kara minti daya a wannan lokacin zata iya bugawa gabadaya. Bayan kaman wucewar lokutan dana kasa lissafawa, yayi gyaran murya, muryar shi lullube da wani irin embarrassment

da daci yace "zan kira ki idan muka sauka Nafeesah" a hankali hannuna da wayar suka sauka akan gadona kamar wadda aka zare mata numfashi. Nayi imanin da ace Duniya da lokaci suna tsayawa da sai ince nawa sun tsaya, komi nawa ya tsaya cak. Bana fahimtar komi sai daci da sanyin jiki dana ji suna fita daga bakin Abbu, ban yiwa kaina adalci ba, sai dai ina bukatar sanyin rai dana zuciya. Ina bukatar farin cikin iyayena, nasan cewa definitely Mommy zata yi farin ciki da hakan Daddy ne dai ban sani ba, ni kuma I only need those four months, In shaa Allah kafin lokacin ya cika, "I'll over come it!" na fada a fili cikin karfafawa kaina gwiwa. Karan bude kofa yasa nayi firgigit na kalli kofar, Mommy ta shigo tana kare min kallo, tace "kin yi bakuwa Ummiey" na kalleta da sauri, "bakuwa, wacece?" ta dan maida kanta wajen kofa tare da furta "shigo" Ikram ta shigo dakin bakinta dauke da sallama, da sauri na tashi tsaye ina amsawa, iso na mata zuwa gefen gadona ta zauna, Mommy ta juya ta fita ta barmu muna gaisawa, ruwa da lemu na dauko mata a fridge na dawo, muka zauna shiru a dakin saboda ba wani sabo muka yi da ita ba dama, can na

katse awkward silence din nace "so???" ta sadda kanta kasa tana wasa da yatsun hannunta ta kasa magana, na dan yi murmushi nace "Kina son tambayar Abinda ke tsakani na da Harith koh?" ta kalleni cikin mamaki kafin ta gyada kai, nace "magana ta gaskiya Ikram babu abinda yake tsakani na dashi, duk abinda kika ga mun yi was just a plan, yana so ne yayi provoking dinki" ta nuna kanta da yatsa, "ni kuma? Why??" na zayyane mata labarin duk abinda kenan, Ikram tayi shiru kanta a kasa har na gama. Tace "yaki ya fahimce ni ne kawai, shekaru biyu kadai suka rage min a karatuna, menene a ciki idan ya hakura zuwa shekarun biyu?" nace "Ikram kina son Harith shima yana son ki saboda haka ni ban ga abin tada jijiyar wuya a wannan maganar ba. Shawarar da zan baki shine to just go for it, karatu baya hana aure kamar yadda aure baya hana karatu idan har kika maida hankalinki akan hakan" tayi shiru kamar mai tunani kafin ta kamo hannuwana ta rike, "nagode sosai Nafeesah. In shaa Allahu zan zauna in duba hakan, nagode" na danyi rubbing hannunta dake kan nawa ina murmushi. Mun dan kara hira da ita kafin ta min sallama

ta tashi, na raka ta har bakin titi ta samu abun hawa ta tafi ni kuma na koma gida. Da dare Daddy yake gaya min an sai min DE form a BUK, na turo baki nace "Daddy ni fa ABU nace maka ina so" yace "sun riga sun rufe saida basically ne shi yasa nasa aka nema miki BUK din" nayi shiru ina tunani, wannan shine kaka-kara-kaka din fa, ina gudun Abbu shi kuma yana kara bibiyata, nace "ni dai kawai na hakura sai next year" daga Mommy har Daddyn kallona suka yi, Mommy tace "sai mu saka ki a gaba munakallo har shekara koh?" Daddy yace "Duk maganar zama bata ma taso ba, tunda an samu admission din ki daure ki tafi can din kawai" nace "amma a cikin hostel zan zauna koh?" Mommy tace "to in ba can ba ina? Dole can zaki zauna" Daddy ya daga baki kamar zai yi magana sai kuma yayi shiru kawai. Daga haka aka fara processing din nemar min admission a BUK. A gefe daya kuma naci gaba da karatu na.

Sati daya, biyu, uku suka shude babu alamun kiran Abbu a cikin wayata, ban kuma sake jin magana game dashi ba. Tunanika iri-iri game da hakan babu kalar Wanda

ban yi ba da wasi-wasi, kila ya hakura ne, kila maganar da nayi ta bata mishi rai, kila dama ba sona yake yi ba.

So sai kawai kika yi rejecting din golden opportunity like that?" cewar Ramlah. Zaune muke a lecture hall dinmu bayan mun gama lectures. Kwana biyu bana cikin natsuwata, walwala ta min kaura kamar yadda fara'a tayi kaura daga fuskata., a duk lokacin dana samu na kebance babu abinda nake yi sai tunani, Ramlah ta kula da yanayin da nake ciki yau dai ta rike ni sai dana fada mata abinda ke faruwa, ko babu komi naji dadin fada mata din da nayi. Tunda abin ya faru babu wanda yaji maganar, ni kadai nake juya abun a cikin raina. Fadar irin mamakin da Ramlah tayi ma bata baki ne, data hangame baki sai dana cika mata shi da popcorn sannan ta rufe. Na kai popcorn bakina tare da gyada kai, "babu wani zabi daya rage wannan Ramlah, kema kin sani" ta kura min ido, "akwai so many and n much more choices Babe, ke ce dai baki so zaba ba". Muka yi shiru na dan lokaci, ta sake cewa "wai ba kince kina son shi ba?" na gyada mata kai, "then why did you do it? Bayan kin san

zaki kasance cikin damuwa?" na kalleta sosai, "Ramlah, ina cikin rudani wallahi" ta girgiza kai, "no! Ki kike confusing din kanki dai, wannan abu ne mai sauki da cikin kiftawar ido zaki magance shi. Kina son mutum, then marry him mana, meye matsalar ki wai? You once fall for the wrong person yanzu kuma right person din yana sonki kina gudu da kafafun ki? Me kike so ne?" nace "so, kulawa, zaman lafiya Ramlah" tace "A cikin abinda kika lissafo wanne ne ba zaki same shi ba wajen Abbu?" nace "duka..... Ban sani ba ko Abbu yana so na ko baya sona ba. Ban sani ko dangin shi zasu karbe ni ko ba zasu karbe ni ba, ban sani ko iyayena zasu yi farin ciki da haka ko ba zasu yi ba...." ta katse ni, "wait don Allah. Shi Abbu da bakin shi yace baya son ki?" na girgiza mata kai, "ko Kadan. Yanayin acting dinshi towards me ne yake nuni da hakan. Ki duba ki gani tunda muka yi maganar nan dashi yau an wuce wata biyu amma koda wasa bai kira ni, bai taba nuna yana sona ba, bai taba furta cewa yana so na ba, a haka zan aure shi kuma? To ince nayi auren me?? Bayan haka alakar shi da matar shi is not in a good condition wanda

hakan ya saka ni zargin cewa saboda ita yake so ya aure ni...." na zayyane mata duk irin yanayin zaman su dana sani da challenge dinsu akan karo aure, tayi shiru tana saurare na har na dasa aya. "shine nake jin tsoron na amince dashi kuma daga baya in zo ina dana sani" Ramlah hararata take yi kamar wata wadda na kashe mata da, tace "kin san Allah? Da ba don ke bace? Da sai na dalla miki mari. Wai me yasa ke kullum tunanin ki daban yake dana normal mutane?" nima na harareta, "kin fara ko? Meye laifina anan to?" ta dafe kai, "saboda kin kasa fahimta. Sai me idan Abbu baya son ki? At least yana so ya aure ki which means ko yaya ne yana admiring dinki., kuma ko ba jima zai fada tarkon son ki girl balle ma na riga dana san tuni ya fada" nace "me yasa kika ce haka?" tace "yadda ya dinga kallonki with so much tenderness and affection in his eyes ranar dinner din su Ni'imah, ke ko ba wannan ba kallon da mutumin nan yake miki da gaske na so ne" na girgiza kaina, "I doubt it Ramlah" wayana tayi karan shigowar sako, na ciro ta daga cikin jakata tare da bude sakon bakuwar number ce kuma har da karin alamun + wanda

yake nuni da cewa sakon daga wajen Nigeria ne, cewa aka yi., 'Let's have a talk later please, I'll call you nine pm on dot in shaa Allah.-Galadanchi' hannu yana rawa nayi niyar maida mishi amsa Ramlah tayi saurin rike min hannu, na kalleta "meye?" tayi rolling idanu, "haba babe! Bashi kamar minti goma mana zuwa ashirin kafin kiyi reply?" nace "ban gane ba? He sent me a message, let me reply please" ta kwace wayar daga hannuna, "kin ce kin fada mishi baki son shi, then me kike so yayi tunani yanzu? Ya turo miki text, within a second kin maida reply as in you care dinnan, kinsan Allah mazan yanzu ba a musu haka koda kuwa wanda yake son ka ne balle ke da kike ikirarin kina son shi" na sadda kaina kasa, "Ramlah kin san halina sarai. Ban iya boye so ba kamar yadda bana iya boye ki, bazan iya yiwa Abbu haka ba" tace "at least try mana. Be like the classy girl you are, wannan yana da banbanci da son da kike yiwa normal mutane, ina gaya miki ta haka ne kadai zaki gane yana son ki ko baya son ki" na gyada mata kai a hankali. Ta dafa kafadata tana dan bubbugawa, "ban san irin son da kike mishi ba Nafeesah, amma zan baki

shawarar ki dinga Addu'ah. In shi alkhairi ne a gare ki Allah ya baki shi, idan kuma ba alkhairin ki bane Allah ya canza miki da mafi Alkhairi" nace ina yi wallahi Ramlah, tace sai kici gaba dayi. Na gyada kai, "in shaa Allah, nagode sosai. Baki ji dadin da naji ba dana gaya miki wallahi" tace "kar ki damu, what are friends for after all? Naji ance BUK zasu fara registration da lectures dinsu next month, haka ne?" hirar mu ta koma ta makaranta, da yake ita university of Abuja zata koma, mun dan kara mintuna kamar ashirin muna hira kafin muka mike, na mata sallama na wuce gida ita kuma ta wuce hostel.

Ban maidawa Abbu reply dinshi ba, amma tun kafin karfe tara ta cika na samu waje na zauna ina jiran shigowar kiran Abbu. Kamar yadda yace, karfe tara tana cika kiran shi ya shigo wayata. Na daga wayar tare da mishi sallama ya amsa, a nutse na gaida shi nan ma ya amsa tare da tambayar karatuna, ya dan ja ni da hira kadan kafin ya dulmiya cikin maganar data saka shi kira na. "Nafeesah ranar nan muna waya na katse sai kuma

ban sake kira ba, na kara miki lokaci ne wanda zaki yi tunani a nutse don a tunani na a wancan lokacin baki zauna kinyi tunani bane shi yasa. Ina fata in ji different amsa daga gare ki wannan karon". Nayi shiru ina tunani, wata marubuciyata tace wai 'Opportunity comes once (Dama tana zuwa ne sau daya -Takori)' ni kam yau dai ina so inyi wasa da tawa damar. Masu karatu kar kuga laifina. I am a girl in her twenties, a irin wannan age din babban abinda 'ya Mace take bukata daga kowane namiji shine kalmar so, sai dai ni yana proposing din aurena ne kawai ba tare da nasan ainihin abinda yake cikin ran shi ba. In amince da auren shi ince nayi auren me? I can't risk my happiness akan son zuciya irin nawa. Nayi gyaran murya a nutse nace "kayi hakuri Abbu, ina kan bakana har yanzu" ina dire aya ya tare ni, "why?" nayi shiru, yace "me yasa baki son Aurena ne?" nace "it's obvious, saboda kai baban Hafsy dasu Abdullahi ne, kai Mijin Aunty Mubeenah ne, you are Niimah's brother, Abby you Are My Father's Friend.... How are you expecting me to accept your offer?" yace "just because of that?" na gyada kai kamar yana gani na, "yace but is

it a sin? Abubuwan nan da kika lissafo dukan su ba wasu obstacles bane da zasu hana ni auren ki Nafeesah! Just tell me ba kya so na shi yasa ba zaki iya aure na ba" nayi shiru zuciyana tana bugawa, ina zan Iya furta wadannan maganganu? Yace "tell me Nafeesah!" cikin husky voice nashi wanda ya fara gauraya da bacin rai, nan ma shiru kawai nayi, zan iya karya akan komi amma banda karyar kin Abbu, ba zan iya ba. "Goddammit Nafeesah! Me kike son nayi for goodness sake?!" wannan Karon bacin ranshi ya fito baro-baro, ya cigaba "kina bukatar ki ganni akan gwiwa na ina rokon ki akan ki aure ni? Ko kuma so kike yi in dinga binki sahu-sahu kamar yaro ina shelantawa duniya ina son in aure ki sannan zaki yarda?" na danyi chuckling a hankali, that is so childish. Yayi shiru kafin inji ya fara magana wannan karon a hankali kuma very calm, "ok, ok. Maganar su Hafsy da kike yi Nafeesah ina tabbatar miki they will be more than happy idan suka ji cewa zaki auri baban su saboda suna Son ki Nafeesah, sun dauke ki da muhimmanci sosai fiye da tunaninki, haka ma su Ni'imah, Dad dinki kuwa has already given us his

Blessings. M just trying to be a nice guy anan kin gane? Bana so ne a miki abinda ba kya so ne kawai shi yasa, Mubeenah kuma wannan ba damuwar ki bace, ba lallai sai da blessings dinta ne zamu yi aure ba, Are we good now?" nace "still Abbu....." ya katse ni, "kina da wanda kike so ne?" nayi shiru ban amsa ba, jin shirun da nayi yasa ya sha jinin jikin shi, "akwai kenan koh?" nan ma nayi shiru, yayi kwafa "just wait till I come back. I will not let you go that easily Nafeesah, Aure a tsakanin mu kamar an daura ne Nafeesah coz you are mine! Saboda ni aka halicce ki ba dan wani ba. Zan baki sauran watanni biyu da suka rage min anan don ki tsara yadda Rayuwar ki a gidana zata kasance. Ina dawowa daurin auren mu ba xai dauki lokaci ba Nafeesah in shaa Allah.... Bari in barki haka, sai da safe" da kyar na iya daga baki nace "A tashi lafiya" kusan a lokaci daya muka katse wayar dashi. Na kai hannuwana duka biyun na tallabo kumatuna dasu, Abbu da gaske yake. Wani bangare na zuciyata yana murna da hakan yayin da wani sashen yake jimami da tantama, tantama akan in

amince ko inyi akasin haka? Jimami kuma na ya makomar rayuwata zata kasance idan na amince din???

Daga wannan ranar kusan kullum sai mun yi waya da Abbu, yawancin lokuta zai kira ya tambaye ni karatuna da sauran su, bai sake tada min zancen auren ba, hakan shi yake kara jefa zuciyata cikin wasi-wasi. I mean yadda nake ji ana fada ko kuwa dai mostly yadda ake yi a cikin film, a situation irin haka zaku ga Namiji ya shiririce a gefen mace going to the moon and black, proposing ta hanyoyi daban-daban, amma shi Abbu babu alamun haka a tattare dashi. Idan text ya turo min babu kalmar so ko daya da nake tsinta a ciki haka ma idan muka yi waya dashi, amma kulawa kam ina shan ta, kullum cikin tambayar lafiyata da Al'amuran rayuwata yake. Hakan shi yake kara jefa ni cikin tunani., Abbu Wane irin mutum ne shi kam??

High waist blue jeans, shabby coffee color T-shirt, black veil rolled, black and white kimono, jakar poshter rataye

a kafada, one last look a jikin mirror na tabbatar dana fita yadda nake so. Yau ne ranar da zan zana exam dina na karshe a Kasu, probably rana ta karshe da zan taka kafana zuwa cikin makarantar idan ba da wani dalili ba dai. Na saka sneakers a kafada baki tare da daukar wayar hannuna na fita, karfe tara lokacin dana fita bakin titi, kafin in isa Kasu tara da rabi tayi already don haka exam hall dinmu kawai na wuce. Kyawawan awanni biyu suka wuce kafin mu fito, daga nan bankwana muka yi da abokanan nan mu muka wuce gida, Ramlah tun a ranar ta wuce Kano zata je ta fara shirin wucewa Abuja. Nima nasan lokacin da nake dashi a Kaduna ba mai yawa bane kafin in wuce Kano saboda BUK tuni sun fara lectures dinsu tun kimanin satika biyu da suka wuce. Na koma gida na samu tarba ta musamman a wajen Iyayena, wata kwaryar liyafa suka hada min inda en uwa suka taru wajen taya ni murnar kammala karatuna, I didn't expect it but I was happy and touched. Soyayyar da Iyayena suke min abu ne mai matukar wahala in iya fayyacewa masu karatu irinta. Kwana biyu ina gida bana fita ko nan da can ina aikin barci da relieving din stress

din exams. Bayan na huta completely na fara shiryeshiryen wucewa BUK tare da iyayena. Ranar Lahadi da misalin karfe hudu na yamma, tafe muke a kan titin daya dauki hanyar fita Kaduna zuwa Kano a cikin motar Daddy Hillux, tare da Mommy, Anty Uwani da Sultan. Duk wasu abubuwa da zan bukata suna bayan motar da muke ciki, komi game da karatuna ya riga ya hattama a waje guda, abinda ya rage kawai shine shiga dakin daukar lacca a gobe litinin. Anty Uwani da Mommy bakinsu yaki rufewa wajen bani lecture Akan zamantakewar cikin makaranta, rayuwa ce da zan hadu da mutanen da ban sani ba kuma inyi rayuwa dasu, nasihohi da shawarwari dai. Mun shiga cikin BUK da misalin karfe biyar da rabi. Mommy da Anty Uwani suka taya ni shirya dakin da aka kaini, mun samu occupant daya a dakin luckily musulma ce kuma bahaushiya da alamun kuma zata yi kirki. Su Mommy suka taya ni gyara kayana da hattama su waje guda. Sai bayan sallar Magriba sannan suka juya, ni da Firdausi roommate dina muka musu rakiya har parking lot. A gabanmu Daddy yaja motar suka tafi muna daga musu kallo, ina kallon

su har Motar ta bace mana daga gani. Iyayena suka tafi suka barni a bakon gari, bakon waje, again, for the second time. Na kai yatsa na dauke siririyar kwallar data tarar min a ido, wannan yana daya daga cikin challenges da 'ya mace take fuskanta a rayuwarta, wannan temporary ne ma fa, zan iya zuwa in gansu a duk lokacin dana ga dama kuma na bushi iska, to ina ga nayi aure kuma? Muka juya muka koma cikin hostel Firdausi na min dariyar kukan da nake. Sallah muka yi naci abinci na jira aka kira isha'i nayi kafin nayi shirin kwanciya barci na kwanta. Sai dana janyo wayata kafin naga alamun shigowar sako, ban san yaushe ya shiga ba amma ina tunanin lokacin da nake sallah ne. Zuciyata ta shiga bugu da tsallen murna lokacin dana ga sakon daga Abbu yake, yaushe rabon da inji muryar shi? Tunda muka fara exams ya daina kirana sai dai yana turo min text akai-akai. Yau ma kamar koda yaushe ko ince ko wane lokaci, ya nake? Ya su Daddy na? Ya kara da min lale maraba da zuwa makarantar BUKsai abu d'aya daya kara, cewa yayi;"Kar in saba da zaman hostel dinsu da wuri, saboda soon.... Very soon zan bar hostel din,

saboda yana dawowa zai dauke ni daga hostel din" na turo baki kamar yana ganina, "wai ya daukeni kamar wata er tsana" sai kuma na kwashe da dariya ina birgima akan gadona, Abbu bai san cewa nima jiran dawowar tashi nake yi ba ne kome? He kept bragging about it, koda yaushe cikin zancen in jira dawowar shi yake making me go curious akan me zai faru idan ya dawo din. Ina lissafe da kwanan wata, ya daura akan wata hudu din da yace zai yi. Mommy ta kira ni muka gaisa tare da tambayata yanayin wajen nace mata lafiya, bamu yi wani hira ba saboda yadda nake jera hamma tace inje in kwanta kawai, nan muka yi sallama tare da kashe wayar. Addu'ar kwanciya barci nayi tare da lumshe idona, a tunani na barci zai kwashe ni a take saboda yadda nake a gajiye amma ina! Rayuwata a gidan Abbu, iyalinshi dashi kanshi, tun daga ranar dana fara ganin su har zuwa yau ta fara min yawo a idanu, nayi juyi akan gadona a karo na barkatai ina tambayar kaina tambayoyin dana kasa samun amsar su suma a karo na barkatai, will it be okay? Zan iya kuwa?

Muna fitowa daga lectures masallaci na shiga nayi sallar La'asar daga nan na wuce flower Garden. Anty Ameenah tana zaune a daya daga cikin kujerun da aka tanada, tana hangoni ta fara waving dina tana murmushi, nima murmushin nayi na karasa gareta, kujera naja na zauna ina fuskantar ta, na gaisheta ta amsa tana tambayata abinda nake so a kawo min nace a bani egg roll da lemu don tun safe da zan fita dana sha shayi ban kara komi a cikin cikina ba, aka kawo mana egg roll, meat pie burger da lemun peach. Anty ta kalleni tace "Allah yasa ban takura miki ba da nace ina son ganin ki?" nayi saurin girgiza mata kai, "haba ko kadan wallahi" tayi murmushi tare da gyara zamanta akan kujera, "da farko ban yi niyar sa baki ba akan maganar wannan sai dai ina ga lokaci yayi daya kamata in saka baki, ba shisshigi nake miki ba amma ina so inji inda maganar ku ta kwana?" na dubeta cikin mamaki, "Anty wace magana kenan?" tace "maganar ku da Ibrahim mana!" sai dana kusa zubdo da abinda nasa a bakina saboda maganar da naji cikin bazata. Ta miko min tissue na goge bakina tare da korawa da ruwa, Anty Ameenah tace "m sorry idan

baki so hakan ba" kai kawai na girgiza mata, amma a kasan raina ina mitar me yasa don kawai Abbu yana son aurena sai kowa a cikin dangin sa ya sani? Kamar wadda take karanta mind dina, tace "kada fa kiyi zaton Ibrahim ne ya gaya min ko ya turo ni, bashi bane. Kwanakin baya dai ya taba neman shawarata akan cewa yana so ya aure ki, me nake gani? Naji dadin hakan sosai, wallahi abu ne wanda ya jima yana min amsa kuwwa a cikin kaina, tun ranar farko dana fara ganin ki Nafeesah na yiwa Ibrahim sha'awar kasancewar ki matar shi, sai dai sanin halin Ibrahim yasa na kame bakina nayi shiru. Ba tun yau ba nake mishi maganar kara aure amma sai ya wawantar da maganar, ba ni Kadai ba Hajiyar mu ma tayi nata kokarin ganin irin zaman da yake yi da matar shi but to no avail. Amma jin da kanshi yazo yana ce min yana sha'awar kara aure nasan cewa da gaske yake, Ibrahim baya nuna bukata akan abinda yasan baya so, musamman akan zancen nan Nafeesah, I've seen something different in him. To kuma tun daga lokacin har yanzu ban sake jin yayi magana game da hakan ba, last time dana mishi maganar ma sai ya sake wawantar

da ita, ni kuma gaskiya na kasa mantawa da zancen shi yasa nace bari in tuntube ki da kaina inji" nayi shiru tare da sadda kaina kasa, ince me? Tunda ni a karan kaina ban san ya muke ciki ba. Anty Ameenah ta kamo hannuna ta rike cikin nata, "look Nafeesah! I am not trying to persuade you or something else.... I just.... I mean ina cikin eagerness nason ganin rayuwar kanina tayi haske, ya samu farin ciki da kwanciyar hankali a cikin rayuwar auren shi. It has been good thirteen years tun auren shi da Mubeenah, aure ne aka musu na zumunci, ita diyar wani abokin Alhajin mu ne. Tun daga auren su Ibrahim ya rasa farin cikin shi, he was young, amma bai dandani abinda matasa kamar shi suke dandana idan suka yi aure ba. Ya rasa jin dadin yarintar shi a wajen yarinyar da bata san darajar shi ba saboda kawai bata son shi. A matsayin Ibrahim na namiji ya hakura da auren dole din da aka mishi amma ita ta kasa hakura, a wajen Mubeenah ne kadai na karyata maganar bahaushe da yace duk kiyayyar da mace take wa namiji da sun fara haihuwa take dawowa so, a gareta kam sai kiyayyar ta koma har kan 'ya'yan shi. You wouldn't

believe me Nafeesah, lokacin da ta samu cikin Abdullahi da kyar ta iya haifeshi, Allah ne kawai ya nufa zai zo duniya amma sai da tayi attempting din zubar da cikin sau biyu, haka aka zo aka sha dabi da cikin Qaseem, daga haihuwar Hafsat taje aka saka mata loop a cikinta ba tare da sani ko yardar Ibrahim ba. Bata dauke mu a tsiyar komi ba, sai mu hadu da Mubeenah a hanya idan ba dama ta gani ba ba zata mana magana ba, idan mu mun mata sai ta ga dama take amsawa. Babu yanda bamu yi da Ibrahim ba akan ya kara aure amma ya ki, yace baya so yaci amanar da marigayi mahaifin Mubeenah din ya bar mishi akan ya kula da ita da farin cikinta, shi a ganin shi cin amana ne idan ya kara aure. Haka Ibrahim ya rayu tsayin shekarun nan, ya danne farin cikin shi saboda matar da bata san yana yi ba, wadda bata appreciating dinshi da dangin sa har ma da 'ya'yan shi. Wallahi baki ji farin cikin da nayi ba lokacin da naji cewa ya shirya fitowa daga cikin ukubar daya sa kanshi a ciki ba, shi yasa kwata kwata naji na kasa yin hakuri in zuba ido ki kubuce masa Nafeesah" jikina gabadaya yayi sanyi, ban taba sanin cewa irin rayuwar

da Abbu yayi ba kenan, koma yake kan yi. Anty Mubeenah kam wace irin mace ce? Anya akwai sauran mata irin ta a duniyar mu ta yanzu? Anty Ameenah ta shafa hannuna tace "kinyi shiru?? Baki son shi ne ko kuma ya miki tsufa??" na girgiza kaina ina dan murmushi, "ban taba mafarkin kasancewar wani mutum a matsayin mijina ba sai Abbu Anty" farin cikin dana hanga a cikin idanuwanta abun baya misaltuwa, na sadda kaina kasa cike da kunya ina jin kamar kasa ta tsage in shige. Tace "amma me yake hana ki cika burin ki?" nace "ina jin tsoron abinda zai je yazo ne, my mom seems to be strictly against it. Sannan ban san me zai je yazo ba a rayuwar auren Abbu da Anty ba, bana son abinda zai tarwatsa musu rayuwar auren su da kan iyalinshi" Anty tace "believe me Nafeesah! You are not. Allah kadai yasan iya ceton ran da zaki yi, wallahi babu abinda zai faru a rayuwar gidan Ibrahim sai ma farinciki dana san zai wanzu in shaa Allah, ke kadai ce wanda zaki iya yin wannan aikin saboda na tabbata Ibrahim yana son ki. This the first time in my life da naga Ibrahim wanting something very badly kamar ki, na tabbata idan

ya rasa ki sauran rayuwar shi will be shattered to pieces. Naji dadin wannan lamarin sosai, ina tabbatar miki da cewa you are the perfect match for Ibrahim. You suits each other, na tabbatar da zai kula dake, zai so ki. Kada kiyi zaton saboda shi kanina ne wai nake koda shi, ba haka bane. Saboda na yarda da Ibrahim na kuma yarda da halayen shi. Ki kwantar da hankalinki In shaa Allah babu abinda zai faru sai Alheri, in shaa Allah ba zaki taba yin nadamar Auren Ibrahim ba kamar yadda na tabbata zaki kasance a cikin farin ciki matukar kina amsa sunan Matar shi.So dear, stop holding yourself in and just go for it, kiyi abinda kike son yi kafin lokaci ya kure miki, Allah ya Albarkaci rayuwar ki" na sadda kaina kasa ina jin wani irin confidence da kwarin gwiwa yana shiga ta. In shaa Allah ba zan kara rike kaina ga yin abinda nake son yi ba, da yardar Allah zan zama mallakin Abbu tun kafin ya subuce daga hannuna ya sa in tagayyara. Anty Ameenah ta kara bani shawarwari kafin muka mike muka fita daga cikin garden din, har inda tayi parking din motar ta na raka ta. Ta bude motar ta shiga, ta mika hannunta baya ta dauko Leda mai dauke da tambarin

kamfanin shop rite Ta miko min, naso nokewa in ki karba amma ya kamo hannuna ta dora min ledar a tafin hannu dole na karba tare da mata godiya, tace "babu komi Ameenah, and please make sure to make it very fast" na sunne kaina a kasa ita kuma ta tashi motar ta tafi.

Tarkacen kayan makulashe ne ta kawo min, dambun nama, cookies da tarkacen biscuits sai turare masu kamshi a cikin ledar. Na bude biscuit din short bread na kai bakina na cinye tare da korawa da lemu, kwana biyun nan abubuwan dana mayar abincin cina kenan. Bayan nayi sallahr Isha'i na gama shirin kwanciya, na kwanta akan gadona tare da janyo pillow na rungume a kirji na, Maganganun Anty Ameenah suka fara dawo min a cikin kaina. Na tsinci kaina cikin mutuwar jiki tare da jina ina narkewa akan katifar da nake kwance. Allah sarki Abbu! Ban taba zaton cewa rayuwar auren shi munin ta yayi yawa har haka ba, na kara juyawa a akan gadon. Poor Abbu! Da yardar Allah sai na zama dalilin sharewar hawayen shi da yayi ta zubarwa a shekarun baya, in Allah ya yarda sai na zama haske da fitila a cikin

rayuwar Auren shi. Da haka na lumshe idanuna barci ya dauke ni, idanuwa brown masu sheki da kyalli suna gagari a cikin duhu.

Da kuzari sosai na tashi a cikin jikina ranar, tunda nayi sallahr Asubahi ban koma barci ba saboda ina da laccar safe, nayi wanka na shirya abin karyawa kafin na shirya jikina cikin riga da siket na leshi ruwan ganye dinkin yayi min cif a jikina, shi bai yi yawa ba kuma bai yi kadan ba. Ina cikin karyawa dinne na kira gida muka gaisa dasu, anan ne Daddy yake fada min cewa result dinmu na KadPoly ya fita kuma yayi kyau sosai, nayi hamdala tare da godewa Allah. Yace ya riga daya turawa Abbu da result din don a kammala shigar da takarduna a cikin BUK tunda dama awaiting result ne, nace mishi babu damuwa, daga nan ya ba Mommy muka gaisa da ita har take fada min ansa auren Hansa'u diyar Kawun su Daddy nan da watanni hudu, na musu fatan alkhairi sannan muka yi sallama da ita. A gurguje na karya naja gyale

yellow mai yalwar fadi da flat din takalmi shima yellow sai jakar littafai da wayar hannuna na tafi. Kimanin mintuna arba'in muna jiran zuwan Mrs Adayi matar da take daukar mu Intro. Physiology amma shiru bata zo ba har karfe tara tayi laccar daya kamata ace tun karfe takwas aka fara ta. Na kalli agogon hannuna tare da dan jan tsaki, bana son abinda zai bata min lokaci duk da cewa bani da wani class din sai two, amma ina son ganin Abbu kafin ya tafi gida wanda nasan cewa muddin ta shigo sai ta cinye lokacin data batar a waje. Wajen karfe tara da rabi class rep yayi announcing din isowar lecturer din, nan da nan ajin yayi shiru daga hayaniyar daya dauka. Kofar hall din ta bude aka shigo, cikin takun nan nashi mai cike da kasaita da natsuwa ya taka har zuwa gaban allo. Ina jin irin sautin woah! Daya dinga fita daga bakin mates dina mata da kuma kus-kus din da suke yi sai dai hankali na baya kansu, yana gaban allo ina kallon halittar dake tsaye, sanye cikin suits navy blue da farar shirt sai navy blue din neck tie kafar shi sanye da bakin cover shoe, fuskar shi mai cike da kwarjini da ilhama tana ta shinning a cikin hasken ranar daya shigo, nasan

dole dama enmatan ajinmu su rikice da ganinshi a yadda yayi kyawun nan, looking soo take away. Daga sama na dinga jin muryar shi lokacin da yayi introducing kanshi as Doctor Ibrahim Galadanchi, zan koya mana course din a madadin Mrs Adayi wadda ta samu accident din mota a daren jiya, zai daukeni course dinne har zuwa lokacin da zata warke. Ya lalubo idanuna ya rike da nashi idanun na en sakanni kafin ya janye idanunshi zuwa ga sauran dalibai yana wani smirking, "alright, can we start now?" gabadaya ajin ya dauki sowar "yes" Ya Allah! Ni kam na kasa tantance a wata duniya nake, har ya gama gabatar da darasin ranar cikin kwarewa da tataccen turancin nan nashi babu abinda na iya tsinta sai idanunshi dake karakaina a jikina suna kara hana ni natsuwa, A Father's Friend! A Lecturer! Way to go Nafeesah!! Ta yaya zan iya dealing da responsibilities dinnan?? Ya rufe littafin hannunshi tare da maida marker dinshi cikin cover dinta yana kallon en ajin, "let's call it a day here" kowa ya fara maida littafin shi cikin jaka, ba bata lokaci ya dauki brief case dinshi ya tunkari kofa bayan ya haske ni da wani irin kallo wanda yasa naji

gabban jikina sun koma kamar ruwa, Abbu will really be the death of me!! Dalibai suka fara fita daga cikin class din amma ni ina zaune kikam kamar gunki, sai da Jalila wadda muka zauna seat daya da ita ta dan daddabe ni sannan na dawo cikin natsuwata, tace "Nafeesah lafiya? Tun dazu na kula kamar baki cikin natsuwar ki" na girgiza mata kai, "lafiya ta lau, kawai na dan gaji ne" tace muje koh? Na jinjina kai tare da mikewa tsaye, ina tashi karan shigowar message a wayata ya tsaida ni; Abbu ne. Cikin rawar hannu na daga, "meet me at room 13, Dept of Physiology, lecturers lounge" abinda yace kenan, na kalli Jalila ina dan murmushi nace "sorry, ku tafi kawai, akwai inda zan biya yanzu" tace ok, tare da wucewa. Ni kuma na tafi zuwa kiran Abbu. Ofishin shi shine na karshe cikin jerin offices din lecturers din dake wajen, na tsaya a bakin kofar ina kara kallon name tag dinshi dake rataye a jikin kofar an rubuta 'Dr. Ibrahim Mas'ud Galadanchi' na shafi sunan da hannuna tare da lumshe idanuna ina dan murmushi, Abbu! What have you done to my innocent soul?? A hankali nayi knocking a bakin kofar, cikin husky voice dinshi yace "yes come

in please" na tura kofar a hankali na shiga, kafafuna suka nutse a cikin wani tattausan zagayayyen carpet an rubuta welcome a jiki, tattausan kamshin air freshener da sanyin split suka doke ni har sai dana saki ajiyar zuciya saboda sanyin dadin daya ratsa ni. Yana zaune a gaban desk top yana aikin typing, ya cire suit din jikin shi sai shirt din kawai ya bari, you have no idea irin kyawun da yayi mun a lokacin. Ofishin nashi babba ne, shelves shelves ne na littafai tun daga na bokon har na Arabi a kowace kusurwa ta Ofishin, sai desk da dai duk wasu tarkace da zaka samu a cikin Ofishin manyan laccarori da boko ta gama ratsa su. Ya dago kyawawan idanunshi daga kan desk top din da yake aiki a kai ya kalleni, murmushi ya saki mai sanyi wanda ban san lokacin dana mayar mishi da martani ba. Ya nuna min kujera alamun in zauna, ba musu naje na dan dosana kamar wadda za ace mata ar! Ta karta a sukwane. Na nutse nake bin Ofishin nashi da kallo, baby wasu tarkace da zasu saka mutum ciwon kai, komi a shirye kuma cikin tsari. A hankali ya daga baki yace "plss make me a cup of tea" na daga kai na kalleshi a hankali, ya wani

langwabar da kai gefe kamar wani karamin yaro saura kiris in kwashe mishi da dariya. Na ajiye jakar hannuna akan kujerar na mike na kunna electric kettle dana gani a jikin socket, ya nuna min inda cups da sauran kayan shayin suke ruwa yana tafasa na hada mishi na kai na ajiye mishi, ya kalleni "thanks.... Ke fa?" na girgiza mishi kai. Aikin shi ya komawa yana yi yana dan sipping din shayin nima na koma na zauna. Ban jima ba naji ya kashe computer din, karan matsawar kujera alamun ya tashi daga inda yake, ya zauna akan kujerar shi wadda take fuskantana. Shayin shi yaci gaba da kurba idanuwan shi suna kaina, kaina yana kasa ina wasa da yatsun hannuna, ji nake kamar wanda rami zai bule daga cikin fatar fuskana saboda zazzafan kallon Abbu a kaina. Ya ajiye cup din akan teburi tare da dan matsowa daga kan kujerar da yake, yace "toh Nafeesah, yau dai ina so inji abinda kika yanke game damu, ya ake ciki? Na fada miki na gaji da jiran ki haka nan, na gaji da yawo da hankalin da kike min. This is the last time da zan tambaye ki, bayan shi ba zan kara ba Nafeesah I promise you don ni dai ba karamin yaro bane, so m

asking you, me kike yanke game damu??" Zuciyata was beating very fast and erratically kamar wadda tayi gudun marathon, kaina, yatsa, gangar jikina da komi ma na jikina sun yi mun wani irin nauyi marar misaltuwa amma duk da hakan ban fasa daga kaina na nake jin ya koma kamar wani gingimemen dutse ba na kalleshi, fuskar shi was mixed of emotions, fargaba, hope, plead, idanunshi da suke matukar burge ni sun shige ciki, nasan da ace idanu suna magana dasu ne zasu yi rokon da nake gani akan fuskarshi tunda bakin shi ya gaza furtawa. A lokacin na gama yin concluding cewa farin cikina koma ince namu a yadda na karanci fuskar Abbu a lokacin, yana tattare damu ne, yayin da makullin kofar take hannuna, that means ni kadai ce zan iya bamu farin cikin da muke bukata kenan??
A hankali na sadda idanuna kasa, na tattaro duk kwarin gwiwa na tare da gyada kaina a hankali.....

Na kasa tantance abinda ke zane akan fuskar Abbu a lokacin, murmushi yake yi sosai, amma zan iya rantsewa akan cewa na hango alamun moistness a cikin

idanunshi, ban san me zai faru ba nan gaba, ban san ya zamu kare da Mommy ba sai dai irin farincikin dana gani a tattare da Abbu yasa naji duk wata fargabata ta barni, idan dai har zan dinga ganin irin wannan kallo daga Abbu to ban damu da duk abinda zai faru ba, nasan cewa murmushin Abbu ya ishe ni. Ya dauki mintuna da dama bai yi magana ba ina jin yana containing farin cikin dake cin shi ne, yayi gyaran murya yace "nagode sosai Nafeesah, amincewar ki da yardar ki a gare ni sun dadada min sosai you have no idea, in shaa Allah na miki alkawarin ba zaki yi nadamar aurena ba, Mrs. Ibrahim Galadanchi!" na kai hannuna biyu na rufe fuskata dasu ina dan murmushi yayin da naji Abbu yana er dariya, yace "why? Baki son sunan ne ko me?" naki bude fuskata balle in kalleshi, yace "idan baki son sunan it's okay, but bude mun fuskar ki plss" na kara kankame fuskar tawa, ina zan iya fuskanta Abbu a yanzu? Ina jin lokacin daya tashi daga inda yake ya dawo gefena ya zauna kamshin turaren shi ya cika min hanci, yace "zaki bude da kanki ne ko sai na janye da kaina?" a hankali na janye hannuwan nawa sai dai fuskana tana kasa, a

yadda nake jina a lokacin nasan ba zan taba iya hada ido dashi ba. Ya rankwafo da kanshi saitin fuskata, da sauri na daga kaina na kalleshi cikin sa'a muka hada idanu dashi, wayyo Allah! Kasa tsaye in shige. Ban taba ganin Kwarjinin da yayi mun a lokacin a tattare dashi ba, wani irin magnet naji ya fara fuzgata yana kokarin hada ni dashi, da sauri na mike tsaye ina lalubar jakata tun kafin in kai ga yin abinda zan zo ina dana sani gwara in bar office din. Abbu ya bini da ido yana frowning, na tsaya a gaban shi ina rataye jakata a kafada kaina a kasa, nace "umh.... Zan tafi... In... na da class anjima" ya kalli agogon hannunshi tare da dan jan siririn tsaki, "so nayi mu tattauna game da yadda zamu tsara rayuwar auren mu dake fa, amma ba komi there's always a second time. Amma zan sanar da Daddynki dai" na kalleshi da sauri ina zaro idanu, "tun yanzu?" yayi scrunching din brows dinshi, "tun yanzu? Me kike nufi?" nayi kasa da kaina "na ga kamar yayi kusa ne" ya girgiza kanshi "bai yi kusa ba Nafeesah, na gaya miki na kagauta ki zama mallakin, ni da so samu ne ma sai ince satin sama a daura mana aure in killace ki a gidana, Ya

Allah! Na tabbata burina ya gama cika, I wouldn't ask for anything sai dawwama dake a gidan Aljannar Firdaus" sai kawai na daga kafa na fara tafiya, Anya Abbu ne? Ban san me ya shiga kan shi da kwalwar shi ba a Kwanakin nan sai ya dinga min wasu maganganu da suke saka ni cikin ramin matsananciyar kunyar shi. Ya mike tsaye, "tunda baki son yin hira dani bari in maida ki hostel to" na fita na tsaya a bakin kofar Ofishin ina jiran shi, ya fito daga ciki ya rufe office din yayi gaba na bishi a baya har inda yayi parking din motar shi. Muka shiga yaja motar, a hankali muke tafiya yana ja na da er hira. Duk yadda nake kauce-kauce da kare-karen fuska sai dana dawo ina dariya, kafin mu karasa hostel na sake daga awkwardness din daya dabaibaye ni, a cikin motar ma mun jima muna hira a gaban hostel dinmu har sai da aka fara kiran sallar azuhur sannan muka yi sallama. Na bude murfin motar ina ce mishi ya gaida su Hafsy, yace "me zaki ce musu bayan tunda kika zo baki ziyarce su ba? Fushi ma take yi dake don ki sani... Koda yake ai na kusa ciccibar ki in kai mata ke cikin gidan gabadaya, ki fara haifo mata kanne nasan

zata yi farin ciki sosai, zan gaya mata ta daina fushi dake haka nan" ni dai na ida sa kafata waje na fita ina dan murmushi, da gaske Abbu ya canza daga cool and calm Abbun dana sani zuwa Romantic, wanda yake fadar duk maganganun da suka zo bakin shi ba tare da yayi la'akari da cewa sun girmi kunnuwana ba. Ya dan leko da kanshi ta cikin motar, "baki ce komi ba fa" na dan juyo na kalleshi tare da haske shi da murmushi na juya na shige cikin hostel, ina jin hot gaze dinshi a kaina har na yi nisa a cikin hostel din, na tura kofar dakin na shiga. Firdausi na zaune akan kujera da littafi a hannunta tana karatu, ta dago tana min sannu da zuwa na amsa, kallona ta cigaba dayi kamar wadda taga wani bakon abu a jikina, na rataye jakar hannuna a jikin hanga na kalleta, "wannan kallon naki lafiya dai koh?" tayi murmushi tace "you are blushing! Did someone propose to you??" na kalli kaina a cikin madubi, I couldn't help the chuckling daya fito min, na kalleta ina murmushi "Ina ga dan zafi zafin da ake yi ne kawai" ta kalleni tana murmushi tare da gyada kai ta maida Idanunta ga littafin hannunta. Nima nayi murmushin na fita naje nayi

alwala na dawo nayi sallah, kafin in gama Firdausi ta dafa mana indomie ina gamawa muka ci na sake fita wajen lecture.

A daren ranar sai ga wayar Daddy ta shigo, na daga wayar cikin sanyin jiki da faduwar gaba. Ina gaida shi ya amsa ya dora da fadin, "Ibrahim ya kira ni yanzu yana fada min wani labari" na sadda kaina kasa kamar ina gaban shi, "kayi hakuri Daddy" ya danyi murmushi, "meye kike bani hakuri dear? I just call to know that you are okay with it. Are you sure zaki iya?" na gyada kaina amma ban yi magana ba, yace "naji dadin zabin da kika yanke sosai Uwata, naji dadin cewa mutumin da kika zaba ya zama abokin rayuwar ki Ibrahim ne, naji dadin cewa zan barki a hannu na gari kuma na kwarai, nasan ba zan taba yin fargaba game da yadda kike ba saboda na yarda da Ibrahim. Allah ya miki albarka Nafeesah" naji hawaye suna kokarin cika min ido, da ace ina kusa dashi da sai na rungume shi, nace "I love you Daddy, nagode" yace "You are all we have Uwata, dole mu so farincikin ki, ina Alfahari dake" nace "nima haka

Daddy.... Amma Mommy fa?" yayi kasa da murya nasan sirri yake nufi, "Mommy dinnan taki fa sai a hankali, tun dazu take hawa tana kumbura kamar fulawa daga mata maganar wae ai ita bata yarda ba cin amana zata yi, shine nace mata idan haka ne itama za a turo mata yarinya kamar ki idan tayi watanni sai in aureta, don Allah ba anyi 1-1 ba?? Sai kawai ta hau kumbure-kumbure, yau ko magana bata min ba dana dawo daga aiki" duk da banji dadin abun ba sai dana yi er dariya nace kai Daddy! Yace "it will be better idan baki kira ta ba for two days, zan yi kokari in ga cewa na ganar da ita abinda take fahimta" nace toh Daddy. Yace good girl, kije kiyi alwala ki kwanta, nasan kina da darasi da safe nace "exactly Dad, goodnight" muka yi sallama na ajiye wayata jikina a sanyaye. Na jima a zaune ina tunanin yadda zan yi idan Mommy taki bamu albarkarta game da auren nan, ni dai nasan cewa ba zan iya auren Abbu ba tare da yardar Iyayena ba gaskiya. Na tashi naje na dauro alwala nayi shirin kwanciya barci. Dana daga wayata naga message din da Abbu ya turo min mintuna biyar da suka wuce, cewa yayi; "A lokacin da kowa yake

neman makwanci da niyar warware gajiyar data addabe shi, a daidai lokacin bawan Allah Ibrahim yake karawa kan shi wani tarin gajiyar, why? Saboda bashi da makwanci kwanciya balle filon tada kai. Ina fata wadda take karanta sakon nan zata yi gaggawar kasancewa tashi ko zai samu sanyin rai dana zuciya a tare dashi. Sai da safe, lots of love and kisses" n zan iya rantsewa naji saukar lebba a kumatuna, na kai hannu na dafe wajen ina duba gefe na, dariya na saki tare da dan dukan goshi na, silly me! I am even expecting him to kiss me, woah!! 'Goodnight' kawai na tura mishi as a reply na kwanta tare da lumshe idanuna. Barci mai dadi cike da kyawawan mafarkai ya daukeni ni. ~So how are you doing outta there Abbu and Nafee's fan??

Kwana biyu kuwa ban yarda na latsa sunan Mom a wayana da sunan kira ba sanin halinta na sauka daga fushi da kanta idan ta hau don sau tari idan tana fushi bata cika son ana bin kanta ana bata hakuri ba ma, she prefers a kyaleta har sai ta sauka don kanta, don haka

ban tarki kiranta ba sai dai na tura mata text message which of course bata yi replying ba.

Ina fitowa daga class na koma daki, su Ni'ima suka kira ni suka ce suna dakina. Ina shiga suka tare ni da shewa ni har suka sa gabana ya fadi ina tunanin ko zancen mu da Abbu ya kai kunnensu ne, sai da muka gaisa har muka fara hira naga basu yi maganar ba sannan na dan saki jikina. Na kunna stove ina kallonsu, "me zan dora muku?" Ni'ima tace Indomie noodles, Sadiya kuma tace Spaghetti, na kallesu "guys, idan zaku daidaita akan abu daya ku daidaita don kun san bani da lokacin yin girki biyu" suka kwashe da dariya, Sadiya tace "dora mana noodles, wannan maman Babyn ba zata barmu mu shaki iska mai dadi ba idan ba a dafa noodles dinnan ba" nace "kema ai Maman Babyn ce" ta wani zare ido, wa?? Muka kwashe mata da dariya ni da Ni'ima.

Nan da nan na dora Indomie na ta dahu na juye mana a tray muka fara ci. Muna cikin ci kiran Abbu ya shigo wayata, na kalli wayar tare da kallon su Ni'ima dake kallona suma, na ci mur tare da janye wayar na kife ta akan gado, suka yi sharing glancing a tsakaninsu.

Sadiya ce tace "wai ni me ke tsakanin mutanen nan biyu ne? I've started putting a big question mark a tsakanin su" Ni'imah tace "kamar kin shiga zuciyata wallahi... Ni kaina na kasa fahimta" na kara hade fuska ina cusa indomie bakina ba tare da nayi magana ba, sam bana so maganar mu da Abbu ta fita ta shiga cikin dangin sa don tsakanina da Allah ban san da wani ido zan kallesu ba, ban shirya ba. Ni'imah tace "idan tayi wari dai mun ji" ni dai na kyale su ban tankasu ba. Muka gama na wanke kwanuka na kai mana soft drinks muka sha, daga nan na koma class bayan nayi sallah na bar su a dakin, dana dawo ban same su ba sun bar mun sako dai kan cewa sun tafi. Da dare Abbu ya sake kirana, na daga wayar da sallamata ya amsa ya dora da cewa "me bawan Allah yayi aka ki daga kiran shi dazu" nace "bana kusa da wayar ne Abbu.... Ina yini?" ya amsa, anan yake fada min wae washegari zai tafi Ilorin zai yi sati daya a can. Yace "me zai hana idan na dawo kawai a daura mana aure Nafeesah?" nace "Abbu baka tunanin it's too sudden?" yayi sighing,

"Nafeesah, y do u always keep saying yayi sudden? Kina tunanin haka zan ci gaba da kallonki Ina kauda kai har zuwa yaushe? Har ki gama makaranta ko me?" nayi kasa da murya nace "at least in dan yi nisa a karatu na mana!" yace "really? Kin san? Ko session dinnan ba zan bari ya kare ba ba tare dana aure ki ba Nafeesah, idan kuma ba so kike yi in..... God! Nafeesah wae me kike nufi da rayuwata ne??" muryar shi ta dan fara yin sama alamun ranshi ya fara baci, nayi shiru ban bashi amsa ba. Lokacin dana gama yanke shawarar yarda da Abba, kamuwa da son shi da amincewa akan cewa zan aure shi, ban yi tunanin zancen aure ba, ban yi tunanin cewa zai taso zancen aure nan kusa ba, ban yi tunanin zai so ya aure ni ina cikin karatu na ba, nayi tunanin zai bar ni in karasa karatuna ko kuma at the very least ya bari sai na kusa kammala karatuna sai kuma gashi yana zancen aure in the next two weeks when I'm not even ready for it, hell ban ma san meye ma'anar auren ba, me zan yi kenan?? Ga zancen mu da Mommy ga.... Ya katse ni ta hanyar cewa "just forget about it Nafeesah, bana son tursasaki yin abinda baki yi niyar yi ba. Na hakura da

zancen auren, idan muka ci gaba da zama a haka ma ya ishe ni, I want your happiness" naji kwallah ta tsattsafo min a idanu, nace "Abbu kayi hakuri" yace "don't mind Amour, na fahimce ki" nayi murmushi mai sauti wanda na tabbata ya jiyo sautin shi, ya maido min da martanin wani wanda yasa naji gwiwoyin kafana sun yi wani sanyi, yace "Pretty na tana ta cigiyar ki, yaushe zaki zo ki ganta?" na zaro ido kamar yana gabana, har sai da naji gabana ya fadi nace "ni?? A'ah gaskiya" ya danyi er dariya, "tsoron me kike ji ne? Na manta ma dazu in fada musu you are now my wife to be" nayi saurin cewa "pls Abbu no! Don Allah ba yanzu ba!" yace y? Na dan turo baki, "ni dai don Allah a'ah" yace "naki, sai na fada musu" na kula tsokana ta kawai yake yi don haka na kyale shi yayi ya gaji sannan muka danyi hira kafin muka yi sallama na mishi Allah ya kiyaye hanya muka ajiye wayar. Abin mamaki sai ga kiran Mommy ya shigo wayana, nayi tsuru Ina kallon wayar kamar ba zan daga ba, Ina tsoron abinda zai faru idan na daga kiran. Sai daya kusa tsinkewa sannan na daga, a hankali kamar mai tsoronta nayi sallama tare da gaida ta, cikin usual

tone dinta ta amsa yadda take min, ta tambayeni karatu da sauran abubuwa duk na amsa mata da lafiya lau, tace "naji abinda kika yi Nafeesah, kina ganin daidai ne hakan?" nace "Mommy kiyi hakuri don Allah" tayi shiru kafin tayi ajiyar numfashi, "to tell you the truth naji haushin Abin daga farko, daga baya sai naga cewa abinda kike so kenan and I don't have the right da zan hana ki yin auren da kike so ba Ummiey. I really hope decision din da kika yanke shine daidai kuma zai kawo miki farinciki mai dorewa a cikin rayuwar auren ki" naji zuciyata tayi wani irin sanyi, na saki sansanyar ajiyar zuciya Ina jan hamdala a cikin raina, nace "Mommy nagode sosai" tace "Ni me ma zaki ce mun ne? Kwana biyu baki kira ni ba saboda kina gudun kar in hana ki yin soyayya ko?" nace "mommy ba haka bane" tace "idan haka ne ma ya zanyi? Tunda daddyn ki ya kitsa miki kin hau kai kin zauna, ina jinshi ai yana baki shawarar kar ki kira ni shine ke kuma kika ki kirana" na sake cewa "kiyi hakuri" ina danne dariyar data taso min, ta kuta, "he was even threatening me wai zai iya karo aure, bai san cewa abinda matar shi Ibrahim din zata yi da halin

da zata shiga idan taji zancen auren bane nake gujewa ba, yayi zaton son raina ne nake shirin shiga tsakaninki da abinda kike so ba. Ummiey mata da kike gani baki san irin tashin hankali da fargaba da suke shiga idan suka ji zancen kishiya ba balle ita data zauna dake a gida daya ta rike ki cikin amana, dare daya ace zaki aure mata miji kin san ba zata ji dadi ba dai koh?" jikina yayi sanyi na sadda kaina kasa, wannan yana daya daga cikin abinda ya saka ni hesitating at first amma ya zamu yi? Ba zamu danne farinciki cikinmu don faranta ran wadda bata san namu farin cikin ba. Mommy tace "kada ki damu fa, kuma kada ki saka maganar a cikin zuciyar ki babu abinda zai faru da yardar Allah. Amma ya miki zancen aure? Yaushe yace za ayi?" nayi wuri-wuri da ido, tace "baki sani bane? Zan yiwa Daddyn ki magana, ya kamata ace anyi auren nan kawai" nayi saurin cewa, "Mom, ba zaku bari in gama karatu bane?" shiru ya biyo baya kafin tayi magana, "kina da hankali kuwa Ummiey? Shekaru nawa suka rage miki kafin ki gama karatunki, kina tunanin zamu zuba miki ido ko kuma shi Ibrahim din ne yace sai kin gama karatu?" nace A'ah, tace "to ai

ko shine Ummiey ba zamu zuba miki ido ba, zan yiwa Daddynki magana a zauna ayi maganar auren ku don gaskiya hankalina ba zai kwanta ba kina karatu a Kano shima wanda ke son naki yana Kano mu muna nan Kaduna bamu san abinda ke faruwa ba a yadda duniyar nan ta baci" nace "Mommy baki yarda dani bane?" tace na yarda dake Ummiey, nasan irin tarbiyar dana baki, but still, hankalina ba zai kwanta ba gaskiya" nayi rolling eyes, "ai shikenan Mom" tace "zan dai tuntubi Daddynki inji, goodnight baby" na mata sai da safe tare da kashe wayar.

Babu ranar da bamu yi waya da Abbu ba tunda ya tafi, idan ma bamu yi wayar ba muna tare ta hanyar text message yana kashe ni da dadadan kalamai da suke kara narka zuciyata zuwa gare shi. Sai a dan tsakanin na fahimci ainihin ma'anar Soyayya, ashe da shirme nayi, ashe ba son Muneer nake yi ba tunda ko a lokacin dana yi tashen son shi ban taba kawowa raina bazan iya rayuwa idan babu Muneer ba, amma a yanzu, na tabbata cewa muddin babu Abbu a cikin rayuwata to tabbas

rayuwa ba zata yiwu a gare ni ba, ko zan yi ta to mara gardi da dandano ce. A yanzu bana taba iya tunanin runtsa idanu matukar ban ji muryar Abbu a yini ba saboda nasan cewa ba zan iya barci ba, nayi wani irin sabo da muryar Abbu wanda sau tari hakan yake bani mamaki. A kowace rana kuma a kowane lokaci wata kofa a cikin zuciyata sai ta bude da sunan Abbu rubuce a jikinta Ina da tabbacin nan da dan lokaci kankani kila numfashina ma idan aka kula sunan Abbu ne zai dinga fita daga cikin shi. Duk da dai ance wai sanin gaibu sai Allah amma zan iya cewa ta bangaren Abbun ma hakan take koma fiye da haka. A yadda na fahimce shi cikin dan lokacin, yana daga cikin mutanen da baiyana halin da zuciyoyin su ke ciki abu ne mai matukar wahala da wuya a gare su, sai dai su baiyana shi through their actions kawai. Baya zama yana wani tsara min kalamai na soyayya kamar yadda yace bai iya irin wannan Abun ba but I am comfortable da yanayin yadda yake tafiyar dani, yadda yake tattalina da yadda yake nuna kamar duk duniyar nan babu wata 'ya mace mai gashi a cikin idanun shi sai ni, wannan kadai ya ishe ni numfashi mai

dadi a rayuwa sanin cewa abinda nake matukar so da qauna shima yana sona da kaunata equally. Shi yasa ko a lokacin da Mommy ta sake tuntuba na da zancen aure a karo na biyu, tace "bikin Hansa'u yana matsowa, me zai hana a hada auren ku gabadaya kawai a daura a can Malumfashi? Bai fi watanni biyu ba za a daura in yaso ko bayan kun karar da session dinnan ko semester din sai ayi biki da tarewa ko?" nace "Mommy sai wani saurin ku aurar dani kuke yi kamar wadda kuka gaji dani? Wane irin aure ne kuke shirin yi mun haka daura aure kafin tarewa?" tace "to ai gani nayi hakan zai fi mana sauki da mutanen da zasu zo daurin auren, ace anyi aure da wata daya wasu ko gama kafe gajiya basu yi ba a sake juyowa yin wani auren kin ga ai akwai takura, ba gwara ayi a wuce wajen ba?" nace "Mommy ni bani da zabi, kuyi duk abinda kuke ganin daidai ne" tace "to Allah ya miki albarka, Yasa hakan shi yafi alkhairi.... Oh su Ummiey za a zama matar aure!" da sauri na kife wayar a kan gado na fara juyi akan gadon idanuna akan fuskata kamar Ina gaban ta. Abbu ya kira ni a daren ranar cikin tsananin farin ciki da murna, yace "kin gama

yi mun komi Nafeesah, kin saka zuciyata cikin farincikin da bata taba shiga ba, Allah ya miki albarka Nafeesah! I'll definitely compensate you Amour, yau zan ma iya barci kuwa saboda murna?" da wadannan kalamai nashi na kwanta suna min amsa kuwwa a cikin kaina, tabbas I'll be the luckiest bastard on earth matukar na auri Abbu, Abbu!! Allah ya nuna min ranar da zan zama matar shi lalle zan kere sa'ah.

Bayan kwanaki biyu Abbu ya dawo daga Ilorin, da yake dawowar safe yayi gida ya wuce ya dan huta ya shirya kafin ya shigo cikin makaranta, lokacin muna cikin lab muna practical don haka yace in same shi a office dinshi idan mun gama. Sai karfe biyar muka fito, ban tsaya yin komi ba na tunkari ofishin Abbu cikin wani irin doki, ji nake kamar in yi fuffuke ko in bude idanuna in ganni a gaban shi, in dora idanuna akan kamilalliyar fuskar shi mai saka ni cikin nishadi, nayi kewar shi, ban taba kewar abu a rayuwata har nake ji numfashina yana daukewa saboda rashin wani abu kamar yadda nayi kewar shi ba, how I can survive without Abbu a rayuwata yanzu, only

Allah knows. Jikina har rawa yake lokacin dana hau corridor da jerin offices yake ba, naja nayi burki a kofar ofishin shi Ina kokarin saita kaina kila idan na shiga kai tsaye a yadda nake zai iya zaton ko gudu nayi naxo gare shi. Na daga hannu da niyar yin knocking na jiyo wata murya tana magana, cikin Jan hankali, cikin kissa da kisisina, cikin wata murya dake baiyana tsananin bukatuwa da roko..... Zuciyata ce ta bada wani irin sauti da naji shi tamkar saukar aradu......
~Me kuke tunani game da chapter din Yau?
~Mommy fa? Ya kuka gani? Ta burge ku??

Dr. Ibrahim baka tunanin lokaci yayi da xaka yi recognising din soyayya ta zuwa gare ka? Kana sane da halin da ruhina yake ciki saboda kai, soyayyar ka na azabtar da zuciyata a kowace rana amma kayi kunnen uwar shegu dani kana nuna kamar baka san komi ba, haba Ibrahim, ka tausaya min mana please!!" kafafuna suka shiga rawa na kasa yin knocking din da nayi niyar yi, a hankali na matsa ta jikin tagar office din da yake a bude take. Abbu yana tsaye ya juyawa tagar baya, ya

rungume hannayen shi a kirji yana fuskantar ta yayin da ita kuma take fuskantar tagar duk da cewa dai bana iya hango fuskar ta amma yanayin shigar da tayi m not satisfied with it. Ko dai tayi kwalliya ne don tayi seducing din Abbu na ko kuma ta saba yin tambadaddiyar shiga ta marasa mutunci kamar yadda tayi yanzu. Abbu yace "Dr. Luba Ina ga wannan abu ai yana gare ki ne, ba tun yau ba na riga da na fada miki cewa Ina da aure har da 'ya'ya...." ta katse shi, "nima ai nace maka zan iya aurenka a hakan, meye hadina da matar ka ni? Kai zan aura ba ita ba!" yace "am getting married, in the next two months in shaa Allah!" ta laulayo wani ashar ta maka,"says who? Karya ne Dr Ibrahim, wallahi Karya ne! Babu 'ya macen data isa ta aureka Ina tsaye Ina kallo, idan ma wasa kake yi tunda wuri ka fadi kafin in aikata abinda ran mu ba zai mana dadi ba" yace "me yasa zan miki wasa? Ba tsoron ki nake ji ba kuma ba shakkar ki nake yi ba, ban san ko sau dubu nawa kike so in fada miki cewa bana son auren ki ba, you are not my type Ramlah" tace "but you are my type, and there's no way da zan zauna ina kallo a gaban idona wata ta

dauke abinda nake so ba, Karya ne wallahi...." ta kara taku zuwa gaban shi ta kai bakin ta daidai kunnen shi, ban san me ta rada mishi ba, naga dai taja da baya yayin da Abbu yayi shiru kawai, can kuma naji yace a hankali, "get out please Dr Luba" tace "ba kai kace in zo ofishinka ba ra'ayin kaina ne, don haka idan zan fita ma yanzu sai nayi ra'ayi, gashi kuma ban gaji da ganin fuskar ka ba, ya za ayi kenan?" na hangame baki cike da tsananin mamaki, lallai duniyar Allah mai fadi, xaka ga mutane daban-daban masu hali iri-iri, ita kuma wannan wacece? Zuciyata ta hau wani suya kamar zata fito daga kirjina, ji nayi kamar in banka kofar ofishin in shiga in jawo ta by her hair in fada mata Abbu nawa ne, in ma ta kai ga tofa mata yawu a fuska duk zan yi matukar zata fita daga cikin rayuwar Abin sona. Na koma ga kofar na fara knocking da karfina kamar zan balla ta, Abbu ne ya min izinin shiga. Na tura kofar na shiga with full of attitude and Charisma, so that wadda take ikirarin mallakar Abbu na ta karfi da yaji taga cewa am not the type of people da ake musu kwacen abinda suke so, abinda suke Jin cewa ba zasu rayu ba tare dashi ba right in front of their

eyes ba tare da sun yi abu ba. Abbu ya juyo yana kallona, murmushin daya saki kadai yasa naji wani irin kwarin gwiwa ya mamaye ni, naji duk wata fargabar kada fa matar dake gabanshi ta kwace min shi ta tafi ta barni a take, tabbas Abbu shine mahadin rayuwata. Nima na mayar mishi da martanin murmushin wanda yake kunshe da zallar so da nuna tsananin kewar shi da nayi kafin idanuna suka sauka akan matar dake ikirarin claiming din abinda yake nawa. Ta sha uwar kwalliya a fuska saboda tsabar kwalliya ba zaka tantance ainihin kala ko kamanninta ba, tasha adon izgar doki wanda ya sauko a kafada da gadon bayanta, wani material ne a jikinta an mishi wani irin watsattsen dinki na Allah wadai wanda ya fito da shafaffen kirjinta kamar shafaffen silifas, dinkin ya matse ta tun daga kirjinta har cinyoyinta, ta wani kalleni tun daga sama har kasa yayin da nake kallonta disgustingly cikin nuna kyama kamar wadda taga abin kyankyami wanda na tabbatar da cewa sai ya kada mata 'ya'yan hanji. Abbu ya katse mana kallo-kallon da muke wa juna ta hanyar cewa "Dr Luba meet my dearing wife, Nafeesah. Nafeesah she's my co

worker" nace "sannu, ya kike?" ta tabe baki tana wani yamutse fuska, "wannan abar ce dama kake wani tada jijiyoyin wuya kana cewa wai zaka aura? Me ta fini dashi?" Abbu yace "ko zaki iya bamu waje, Ina son sirri" ta buda kofofin hanci har suna naso, "ko baka ce ba yanzu zan bar maka ofishin ka kafin ka wulakantani a gaban wannan er yarinyar, sai dai kada kayi tunanin na hakura ne, ko ta halin yaya sai na mallake ka Ibrahim saboda kai nawa ne!" ta warci jakar hannunta ta fita tana murguda kugu kamar wani shafaffen plate saboda rashin cikowar shi, na bita da kallo Ina murmushin mugunta, matar nan ta rainawa kanta hankali da yawa, ni ta kira da yarinya koh? Allah ya kara hada ni da ita wani lokacin, ni kuma nayi alkawarin nuna mata aikin yarinta. Na maida kallona ga Abbu lokacin data fita daga office din ta maida kofar tayi banging kamar tashin duniya. Murmushi na sakar mishi softly, duk da cewa har zuwa lokacin zuciyana tana itching game da Luba ce ko Bana yace sunanta? Bana so in sani. Yaja kujera ya zauna a kusa dani tare da nuna min wata kujerar nima na zauna, yace "kiyi hakuri da abinda ya faru, kada

kuma ki sa maganar ta a cikin ranki, ta saba irin wadannan maganganun duk burga ce da tauna tsakuwa don aya taji tsoro" nace "wai wace? Ni ban ma fahimci abinda take fada ba balle in saka shi a cikin raina...," ya kura min idanu yana murmushi, "kin san abinda yasa nake kara jin ki a cikin raina kenan? Nafeesah my other being" na sadda kaina kasa Ina dan murmushi, Abbu with his flirtations, a hankali nace "sannu da dawowa, ya hanya?" yace "it was tiresome, amma yanzu na dawo normal dana gan ki, my wife!" wayyo kunya! Na rufe fuska ta da hannuwana ina er dariya, shi kuwa dariya ya saki sosai, a tausashe. Nayi shiru Ina jin dariyar da yake yi, he sound so relieved and happy, and I feel proud knowing that ni ce sanadin farincikin da yake ciki.

Cikin barci na kai hannu kasan filona na lalubo wayata dake vibrating, duka-duka karfe goma ne da rabi na safiyar ranar Assabar, da yake ranar hutu ce kuma ban samu nayi barci da wuri a
daren jiya ba shi yasa na ke jina kamar wadda ta kwanta a lokacin saboda tsabar barci. Ban ko tsaya duba caller

ID ba na dauka, muryar Sadiya ce ta doki kunnena, "Asslm, Nafeesah hope ban katse miki barci ba?" cikin muryar barci nace "kin katse min mana" tace "sorry, dama muna nan AKTH ne shine zan fada miki" na tashi zaune a sukwane nace "Teaching Hospital kuma? Waye babu lafiya?" tace "Ni'imah ce wallahi, ta samu miscarriage yau da safen nan" jikina yayi sanyi sosai, Allah sarki Ni'imah. Nace "ki turo min da number din dakin da kuke, gani nan zuwa" na ajiye wayar tare da dirowa daga kan gado. Wanka nayi na fito na Karya, ban wani tsaya yin kwalliya ba na saka kayana kawai na fita, sai a cikin mota ne na kira Ramlah Ina fada mata, tayi jimamin abin sosai tace zata kira ta mata jaje. Ban samu Sadiya ba a dakin da aka ajiye su lokacin da naje, Anty Ameenah da Anty Rayyah suna nan a dakin tare da wata dattijuwa sai kannen Bashir mata su biyu, Ni'imahr na kwance tana barci an sa mata drip, ta wani dashe tayi fari tas kamar wadda babu jini a tattare da ita. Muka gaisa dasu Anty Ameenah cikin mutunci har tana bani hakuri akan wai an taso ni daga makaranta, nace a kunyace haba Anty, Ni'imah tafi karfin haka a wajena

ai.... Allah ya mayar mata da mafi alkhairi, suka amsa da ameen. Sadiya ta shigo dakin hannunta rike da na Jameel dan Anty Jameelah wanda yake tafiyar ta-ta-ta, muka gaisa da ita itama na musu jaje, naja Jameel a jikina ina tambayar shi inda yaje yana ta min gwaranci ina murmushi. Ni'imahr bata farka ba sai bayan azuhur, su Anty Ameenah suna waje suna sallah da yake ni fashin ta nake yi, na matsa gefen gadonta Ina mata sannu tare da tambayar ta abinda take bukata? Kuka kawai ta saka tana shafa cikinta, na rungumo ta a jikina ina dan jijjigata kamar nima in rushe da kukan nake ji, it's not easy ka dauki cikin abu ka raine shi, bayan ka gama kwallafa ranka a kanshi kuma sai Allah ya jarabce ka da rashin sa, hakika Allah kadai yasan irin sakayyar daya tanadarwa irin wadannan matan. Nace "kiyi hakuri Ni'imah, haka Allah yaso. In shaa Allahu zai kawo miki mafi alkhairin sa, stop crying please kinji?" ta jijjiga kanta. Naje na xubo mata ruwa a cikin cup ta kurba, lekawa nayi na gaya musu ta farka sai gasu sun duro cikin dakin, kowa sannu yake jera mata tare da nasihar fawwalawa Allah lamuranta, nan aka zuba mata abinci

muma muka zuba namu muka ci. Da yamma sai ga Bashir din yazo ashe ma baya gari saukar shi kenan daga Abuja, bawan Allahn nan har da hawayen shi abin gwanin ban tausayi wallahi. Bayan Magriba su Anty suka yi haramar tafiya gida, Anty Rahina tace in zo ta sauke ni a makaranta mana nace mata ai ni anan zan kwana, tace inah! ga Sadiya nan da Gwoggo Hinde sun isa in zo ta maida ni makaranta kawai, nace mata ni fa anan nayi niyar kwana. Tayi shiru tana kallona ganin na kafe kafin tace "kin fadawa iyayen ki?" nace "zan fada musu anjima dai" tace ai shikenan, Gwoggo Hinde zo mu wuce gida dake kawai. Da haka suka mana sai da safe suka tafi bayan sun ajiye mana duk abinda zamu bukata. Na shiga bandaki na gyara jikina, ban taho da panties bama sai dana fita waje na sayo wasu pad ce ma ban nema ba da yake ni ma'abociyar ajiyar su ce a cikin jakata saboda emergency. Na fito daga bandakin ina gyara zaman rigar jikina, daidai lokacin Abbu yayi sallama ya shigo cikin husky voice din nan nashi Hafsy na biye dashi a baya, zuciyata tayi wani irin fari da ganin shi kamar zata haske duniya da abinda ke cikinta, gabadaya ranar ban ji

muryar shi ba mun dai yi exchange din messages a tsakaninmu da rana, fuskar shi ta nuna zallan mamaki da ganina kafin baiyanannen farin ciki daya kasa boyuwa ya nuna akan fuskar tashi, na ja kujerar kusa da gadon Ni'imah din na zauna. Na Kalli Hafsy dake tsaye a bakin gadon Ni'imah na mika mata hannu alamun tazo ina murmushi, ta makale kafada tare da kara lafewa a jikin Abbu alamun ba zata zo ba, na janyo ta jikina tana kokarin kwacewa amma na hana ta, nace "haba Hafsy na ni dake bata baci, Waye ya tabo min ke?" ta turo baki tana nuna ni da yatsan ta, nace "ni da kaina? Me na miki?" tace bake bace ba kike kin zuwa ki gaida ni, kullum sai nace kizo ki ganni amma baki taba zuwa ba! Na dan saci kallon Abbu dake gaisawa da kannen shi amma idanuwan shi suna kanmu yana mana dan murmushi, na janye tare da kallonta nace "kiyi hakuri kinji? In shaa Allahu zan dinga zuwa Ina ganinki, so stop frowning and smile kinji?" tace "promise?" na gyada mata kai. Aka kwala kiran sallahr Isha'i a daidai lokacin, Abbu ya zube min wayoyin hannunshi a gabana ya fita da niyar yin sallah

Kwanci tashi asarar mai rai, biki yana ta kara matsowa yayin da muke ta shirye-shiryen rounding off din semester dinmu. Tuni Ni'imah ta warware har ta fara shigowa school abinta, cikin Sadiya yana ta kara fitowa ni kuwa gandoki har na fara tanadar kayan jarirai, lol.

☆☆☆☆☆

Cikin mamaki na daga wayata dake ringing bayan na duba sunan wanda yayi kiran, “Yau ko dai batan lamba waya kayi Harith?" tunda ya samu aiki a Ibadan ya tarkata ya tafi zumuncin dake tsakaninmu yayi kasa, shi aiki ni kuma karatu don haka we were not in contact recently, yace “haba Nafeesah, har ke kina da bakin magana? Sau tari zan tura miki sako ta whatsapp amma bana ganin reply dinki, anya idan da amana ruwa ya dafa kifi??" nayi dariya nace “kasan rayuwar dalibai sai a slow wallahi, shi yasa. Ka yini lafiya?" yace “yeah, Alhamdulillahi..." nan muka gaisa dashi da tambayar juna kwana biyu, yace “Sis take fada min ranar nan wai

ai an saka miki ranar aure, shine nace bari in kira in tambaya inji laifin me nayi da ban samu labari ba?" nayi murmushi nace "to kuma kawai daga sa min aure sai in hau shela? Kaima ai naji ance ka kai kudin aure gidan su Ikram" yace "yeah... Amma ya aka yi kika sani? Ko abokaina basu san da labarin ba" nace "nima a gari naji, amma daga majiya mai tushe, Ikram din ce da kanta take fada min" yace "iye lallai naga nuna wariyar jinsi, so u guys have been in contact with each other amma shine kike fada min wai wani rayuwar dan makaranta and stuffs ko?" nayi dariya nace "ai kasan zumuncin mata ko ta yaya dai in a week ba su rasa yin waya shi yasa... So what's up?" yace "mun shigo workshop ne cikin Kano, shine nace bari in tambaye ki idan ziyara is allowed, zan leko mu gaisa" nace "why not? You are welcome!" yace "to ba laifi, goben idan zan shigo I'll inform you" daga nan muka yi sallama kowa ya ajiye wayar. Firdausi ta dago kanta daga typing din da take yi a cikin laptop dinta ta kalleni, tace "ni yanzu meye makomar ki idan an miki aure? Zaki ci gaba da zama cikin hostel ne ko kuma zaki zauna tare da kishiyar ki ne

tunda har yanxu ba a gama gyara inda zaki zauna ba?" na zauna a gefen gadona ina sighing, “ban sani ba nima wallahi, but kila, may be in ci gaba da zaman hostel" tace anya? I doubt idan mijin nan naki zai yarda, na harareta “me kuke nufi wai? Abinda Sadiya da Ramlah suka ce kenan dama" tayi dariya, “to ai yadda yake nunawa ne, he's barely holding it in, a dokance yake kuma a kagauce da auren nan, azo kuma ace an daura amma ya barki ki zauna a hostel? Ni dai a ganina da kyar ya bari" na dauki dan karamin filo na jefeta dashi, “ke fa m dinki karama ce wallahi, sam baki da kunya" ta fashe da dariya ni kuma na maida bayana kan gado na kwantar ina kara juya maganganunta a cikin raina, gaskiya a son samuna koda ace gyaran gidan da za a ajiye ni bai kammala ba to Abbu ya barni in ci gaba da zama a cikin hostel abina har sai an gama don ni fa har ga Allah ban shirya fuskantar Anty Mubeenah a matsayin kishiya ba balle har ta kaini ga zama a gida daya da ita a matsayin kishiyoyin juna, woah! Ko ya zaman zai kasance?? Na gyara juyawa a kan gadon tare da janyo face mask na rufe idanuna, a hankali barci ya dauke ni.

Washegari lecture din Abbu gare mu, da wuri na tashi na shirya cikin jallabiya brown mai kwalliyar light ash a jikinta, ban yi wata kwalliya ta sosai ba na yi rolling gyale ash mai dan fadi, na zura takalmin vincci flat na fita da dan saurina, takwas saura ina cikin hall din, nayi ajiyar numfashi lokacin da nake zama a kan seat, Abbu baya tolerating late coming ko da wasa, minti biyar ya kara akan karfe takwas to ka hakura da lecture dinshi na ranar kawai, na tuna lokacin dana taba yin nauyin barci ban tashi da wuri ba, na isa wajen six minutes past eight na tarar da kofa a rufe, kuma fa Abbun yana kallona a tsaye a kofar class din amma yayi biris dani tare da sauran dalibai abokan latti na, haka muka gaji da jira muka kama gaban mu.... Na ciza bakina cike da takaici, har yau idan na tuno abinda ya faru sai naji kamar inyi me, kuma fa sabida shi nayi makarar, shi ya kira ni a daren ranar ya tsare ni da hira har dare ya tsala., ai kuwa dai da kyar ya samu ya shawo kaina. Na saki dan murmushi a hankali dana tuno irin bidirin da muka sha a lokacin. Ajin yayi tsit lokacin da Abbu ya turo

kanshi cikin ajin, yayi shigar wani danyen vowel ruwan hanta, bai saka hula ba sai dai ya taje sumar kanshi da yake shi ba ma'abocin saka hula bane. As always, yayi kyau kamar ka lashe shi. Ya fara searching din hall din da idanun shi a hankali har ya lalubo ni, ya sakar min murmushi very soft and lovely, ban bata lokaci ba wajen mayar mishi da martani, yayi gyaran murya amma fa jefi-jefi idanunshi kan kalloni kamar yadda koda wasa nawa basu bar shi ba.

Muna gama lectures muka fita, tun saura minti sha biyar mu gama dama Harith ya min text kan cewa ya shigo cikin makatantar ina zai sameni, na tura mishi text din inda muke yace xai zo, don haka muna fita na hange shi inda ake ajiye motoci. Murmushi nayi na karasa wajenshi, ya wani kara fari ya kara zama magidanci kamar ba Harith din dana sani ba watanni hudu da suka wuce, shima mamakin da yake yi kenan yace wai na kara yin kyau nayi fresh, nan muka tsaya muna gaisawa sosai mun fara hira sama-sama ya kalli agogon hannunshi yace “I gotta go, Abuja zan wuce daga nan"

nace "za aje a ga Amarya kenan? A gaishe ta" kamar ance in waiga bayana, ina juyawa na hango Abbu yana nufo mu, na zaro ido tare da juyawa ina kallon Harith dake kallona shima, fuskar nan ta Abbu a hade take murtuk, lallai yau kishin maza ya motsa. Sam banyi zaton har lokacin yana cikin department dinmu ba saboda ban ga motar shi ba, ai da banyi gangancin tsayawa da Harith a wajen ba. Harith yace "da alamun wanda zaki aura ne ke tunkaro ku" nace "ya aka yi ka gane? Ka san shi ne dama?" yace "not at all, but hararar da yake jefo min kamar zai kawo min naushi irin wadda nake wa duk namijin dana gani tsaye da Ikram" nayi er dariya, "he's cute, isn't he?" daga bayana naji anyi magana, "well, look who's calling who cute" he sounds so close alamun yana bayana kenan, na ja gefe da dan saurina ina dariya cike da jin kunya, Abbu ya mikawa Hatith hannu fuskar shi babu yabo babu fallasa babu fara'ar nan dake tattare a fuskar shi, "Ibrahim Galadanchi" abinda yace mishi kenan coldly, ina ganin yadda yake glaring din Harith da hot gaze dinshi wanda zai iya grilling din kifi, da sauri Harith ya mika mishi

nashi hannun suka yi musabiha yace “Harith, fiancé din Ikram cousin din Sulaiman mijin Sadiya" sai lokacin fuskar Abbu ta dan warware kadan daga hadeta din da yayi amma bata koma normal ba har lokacin, suka dan gaggaisa a tsaitsaye ya dawo da kallonshi gareni da tun da naja gefe ban yi magana ba, kallon daya jefe ni dashi sai da yasa naji alamun kadawar ‘ya‘yan hanjina, yace “ki same ni a mota" da kyar na samu na iya daga mishi kai, ya wa Harith sallama ya nufi wata bakar Land Rover dake kusa da inda Harith yayi parking din tashi motar, haba ba mamaki ashe ya canza mota ne? Na kalli Harith daya jefe ni da murmushin mugunta, na harare shi ya wani yi shrugging yana daga gira sai kawai na girgiza kai don bani da lokacin biyewa tsokanar Harith, godiya na mishi muka yi sallama na wuce inda Abbu yake jirana na bude motar na shiga. Ina shiga yaja motar muka fara tafiya ba tare da yace uffan ba, na kalli fuskar shi har lokacin babu fara'ah a tattare dashi, da alamun na bata mishi rai sosai. Jikina yayi sanyi, na maida kallona ga tagar motar ina jin kamar in fita ta ciki, da alamun yau Abbu na baya cikin walwala, duk saboda ni!!

Suka kalli juna kafin suka kalleni, Sadiya ta dage gira daya "me kenan?""me fa??" na tambayeta ina wani fuskewa ni ala dole ban fahimceta ba. Tace “ki wani daina fuskewa malama, mun san abinda ke faruwa tsakanin ku biyun nan" na kada mata idanu innocently, “ni da wa??" ta kai min duka a kafada, “zaki sani ne maras M, ace kamar mu kuna cikin relationship da Yayan mu mu kasa sani?" na kallesu su duka biyun ina so in karanta yadda suka amshi zancen, ban karanci komi ba sai dai murmushin dana gani kwance akan fuskar su na farin ciki ne bana embarrassment kona takaici bane, naji sanyi ya lullube min zuciya, at least abotar mu dasu tana nan. Ni'imah tana murmushi tace “Sady ke kike wani tsayawa ma kina neman karin bayani, ni fa dama tun ba yau ba na harbo jirgin su ita dashi, they were making it obvious shi yasa ni ban tsaya jira a fada min ba nayi jumping into conclusion" na dan harareta cikin wasa nace “ni kar ki mun sharri wallahi" tace “ba wani sharri sai gaskiya. Irin kallon da kuke wa juna dama tun ba yau ba be it kuna cikin mutane ko ku kadai ne wallahi

na soyayya ne, ai Anty Rahina tace an kusa yin auren" na dafe kirji ina zaro idanu, nace “su Anty har sun sani??" dariya suka saki suna kallona kamar wata kuntacciya dinnan, “Allah kina kwafsi matar Babban Yaya, tunda har muka sani ai dole su Anty su sani kuwa" na rufe fuskana ina diddira kafafuwa a kasa, “Ya Allah! Da wani idanu zan kallesu ni kam?" suka sake kwashewa da dariya har da tafawa, na hade fuska ina kallonsu, “this is not funny fa!" na fada in a serious tone don su san ba wasa nake yi ba, amma ko a jikinsu sai ma wata dariyar da suka kara sawa. Ganin zasu sa min ciwon kai naja Hafsy data fara gyangyadi a zaune muka koma kan spare gadon dake dakin na zauna ita kuma ta kwanta kanta a kan cinyoyina. Hira nake janta dashi duk don in janye hankalina daga shakiyancin dasu Sady suke min, cikindan lokaci barci ya dauketa. Na maida hankalina wajen buga game bana ko kallon inda suke, har suka gama shiriritar su da tsara yadda bikin zai kasance suka yi shiru, dinner ma sai da aka tsara kala biyu, luncheon da parties kuwa wai har da Tea Party, fruits party, Arabian nightsdasu Fulani day da tarkace, ina jinsu dai

ban saka musu baki ba sai dariya da nake musu kasa-kasa, da alamu wani noti a kansu ya kunce kila saboda murnar auren Yayan su ne ko wani abu? Muna nan su Abbu suka dawo daga masallaci shi da Bashir, sallama ya musu ya matso inda muke ya dauki Hafsy a kafadanshi ni kuma na kara gyara zaman gyalena na kwashi wayoyin shi nabi bayan shi. Ya bude seat din baya ya kwantar da Hafsy, ya maida seat din ya rufe tare da jingina da motar yana kallona, na sadda kaina kasa ina dan tapping kafafuna a kasan, akwai wadataccen haske sosai a wajen shi yasa naji na kasa sakewa in kalleshi, tunda maganar auren nan ta shiga tsakaninmu na kasa sakewa in kalleshi sosai koda yake ko a da can dinma idan muka yi kallon ido da ido sai dai by mistake, balle yanzu. Yace “gobe in Allah ya kaimu zan samu Alhaji Babba yayan Alhajinmu da maganar zuwa a tambayo min auren ki, zasu kai kudin na gani ina so za kuma a saka ranar auren gabadaya” nayi shiru kaina a kasa, me zan ce mishi? Shi Abbu bai san irin matsananciyar kunyar shi da nake ji bane da zai dinga zama yana tattauna maganar aurena dani ba. Ya kara

jingina da jikin motar yayi alamun tagumi, “ni ai shikenan tawa ta same ni kuma. Son maso wani nake yi ko kuma ba a shirya aurena har yanzu bane?" na saci kallonshi, ba karamar dauriya nayi wajen danne dariyar data taso min ba, ya wani yamutse fuska kamar yaron dake shirin fashewa da kuka, nace “me nayi ni kuma?" yace “baki son maganar auren mu mana. Da nayi sai ki wani hade fuska kamar wadda ake tursasawa, ji yanzu ma na gaya miki magana maimakon ko ameen ki ce shine kike wani sadda kai kasa" na girgiza kaina ina dan murmushi, Abbu da rigima yake wani lokacin kamar karamin yaro haka yake. Kwanan nan haka yake, gaba daya ya zama very open to me, baya shakkar fada min duk maganar data fito bakinshi, wata rana ta saka ni jin kunyar shi duk da cewa abin yana burge ni kuma na kula hakan yana kara ja na zuwa gare shi. Nace “to ameen Abbu" yayi murmushi, “datz you my Amour.... Amma tsaya...." na kalleshi, yayi frowning face “yaushe ne kika ce kin daina kiran sunana da wani Abbu? Na gaya miki Abbu na yara na ne ba naki ba" nace “ai nace zan daina fa! amma ba yanzu ba" ya wani langwabar da kai, “har

sai yaushe?" nayi shiru, ya sake cewa “ko sai mun yi aure?" na gyada mishi kai, yace “ba laifi, ni ai bawan Allah ne I can wait" nayi dan murmushi, “datz you kaima.... Wai don Allah meye ma'anar Amour?" yace “Love in french" na sadda kaina kasa ina blushing, da gaske ni Love dinshi ce? Nace “amma sauran messages da kake tura min shima French ne? Me suke nufi?" ya girgiza kai, “naaa! Ba zan gaya miki yanxu ba, zan dai koya miki French din sai ki karanta da kanki. Idan muka yi aure ma a Kasar Faransa zamu yi honeymoon dinmu ai, kila kafin mu dawo sai kin koyi yaren sosai, sai mu dinga canza yare a gaban mutane abinmu koh?" na kai hannu ina rufe fuskata ina dariya, can kasan zuciyana kuwa fata nake ina ma zan bude ido in ga har watannin da suka rage in zama mallakin Abbu sun zagayo? Ya kara jingina da jikin motar yana murmushi “ke da kunyar nan taki kuna birge ni, sai dai it's way too much gaskiya, kiyi kokari ki rage ta ko kuma ni da kaina inyi wannan aikin...!" na kara dukunkune fuskana wannan karon a cikin gyale ma. Yayi dariya son ranshi kafin yace “ina tunanin raba muku gida ke da Mubeenah, me kike

tunani?" nace “idan hakan yayi maka bani da damuwa da hakan nima" amma a can kasan raina ba karamin dadin hakan naji ba, har ga Allah dama can bani son zama gida daya da Anty Mubeenah har yanzu ina jin kaina guilty wani lokacin, har yanzu kuma ban san da wane ido zan kalleta ba balle har inyi tunanin zama a gida daya da ita, duk lokacin da nayi tunanin na kan ji hankalina bai kwanta da hakan ba. Yace “hakan ya min perfectly, zan samu inci amarcina cikin dadin rai da kwanciyar hankali abina. Amma na dan lokaci ne fa, don tuni an fara mana sabon gini" nace “sabon gini kuma?" yace “yeah, inda zamu koma da zama mu dukan mu har yaran da zamu haifa nan gaba. Da wancan gidan na gina shine a matsayin inda zan rayu da matar aurena ne, ban taba kawowa raina kara yin aure ba sai da kika shigo cikin rayuwata sannan na fara samun second thoughts. A yadda nake so kuma ki cika min gida da yara inda muke zaune yanzu ya mana kadan. Ina so iyalina su tashi da hadin kai ba tare da banbancin komi ba Nafeesah, ina fatan zaki bani goyon baya wajen ganin hakan ya tabbata?" muryar shi ta tabbatar min da cewa

da gaske yake, tausayin shi ya kama ni Allah sarki Abbu na! Da haka yaso ya karasa rayuwar shi cikin takaici da rashin kulawar matar aure? Ta wani fannin sai na tsinci kaina da godewa Allah daya kawo ni cikin rayuwar su, ko babu komi nasan zan kawo haske cikin rayuwar Abbu kamar yadda name tabbata cewa shima zai kawo haske a tawa rayuwar. Nasan cewa shawarar daya yanke is not a bad idea, ni kaina nasan ba zan juri ganin rabuwar kan yayanmu ba kuma da yardar Allah ba zan bada gudunmawa wajen ganin rabuwar kansu ba kamar yadda wasu iyalan suke, na gyada kaina nace “In shaa Allah Abbu, zan yi iyaka bakin kokarina" yace “Nagode sosai Nafeesah. Allah ya bani ikon faranta miki rai kamar yadda kike iyaka bakin kokarinki wajen ganin cewa kin faranta nawa ran" na sadda kaina kasa ina murmushi, daya daga cikin halayen Abbu dake matukar burge ni kenan, saukin kai da saurin fahimta. A kasan raina kuma na amsa Addu’ar da yayi da “Ameen”.

Bamu ankara da lokaci ya ja ba sai da muka ga Basheer ya fito zai tafi sannan Abbu ya duba agogo yaga karfe goma ta wuce, Abbu ya kama baki cike da tu'ajjibi yace “haka lokaci yake gudu dama?" na sadda kaina kasa ina magana a hankali yadda ba zai ji ba “kaine dai baka kula da lokaci yana tafiya ba saboda love ya rufe maka ido" ya mikawa Basheer hannu suka yi musabiha na mishi sai da safe nima ya karasa wajen abin hawan shi ya tafi, Abbu ya bude motar ya shiga ya zauna, ya kalleni yana kokarin yiwa motar key, “naji abinda kika fada sarai, zaki zo hannu ne ai zaki yi bayani by then" na ja da baya ina er dariya, na maida mishi murfin motar na rufe, yace “any thing for me?" na girgiza mishi kai, “babu, sai da safe Abbu na!" na juya da sauri na fara tafiya ba tare dana jira abinda zai ce ba, ina jin shi yana en maganganu har na mishi nisa kafin naji alamun yaja motar, na saki dariya a hankali. Ina shiga daki suka min caaa da magana, ni dai er dariya kawai na dinga yi da kyar na samu na kashe musu baki, Sadiya ta miko min leda mai dauke da gasasshen kaji da yoghurt, na zauna ina ci muna hira dasu har wajen karfe goma sha biyu

Ni'imah tayi barci, sannan ne muma muka kwanta don dama duk saboda ita ne muke yin hirar don kar muyi barci mu barta ita kadai kadaici ya dameta, muka gyara daya gadon muka kwanta mu ma. Washegari wajen karfe goma Basheer ya kawo mana abin kari da kayan da Ni'ima zata canza, bayan su Anty Rahina sun zo mun gaida su nabi Sadiya gidanta muka je muka yi wanka muka canza kaya, sai kayan Sadiya na saka saboda ban tafi da wanda zan canza ba. Muna komawa muka tarar an sallame su, nan muka hada kaya muka wuce gidan Ni'imah. Muka gyara mata gida da komi muka mata girki, su Anty Ameenah ana kiran sallahr la'asar suka wuce, ni dai daga nan na musu sallama don a ranar zan koma makaranta. Sai bayan tafiyar su ne sannan na kira Mommy na fada mata abinda ya faru, sai da nasha fadan wai ban gaya mata da wuri ba sannan tace in hada ta a waya ita da Ni'imah, no dai na bata hakuri kafin in ba Ni'imah wayar Mommy ta mata jaje tare da kara mata da nasihu daga nan ta maido min wayar, na amsa, anan take fada min cewa wakilan Abbu zasu je gida Malumfashi tambayar aurena, nayi shiru ina gyada kai

kawai, ta mim addu'ar Allah ya sanya alkhairi muka yi sallama da ita. Nima ba a jima ba na musu sallama na koma makaranta. Bayan kwana biyu aka sanya ranar auren mu ni da Abbu watanni biyu masu zuwa yayin da biki da tarewa kuma za a bari sai na gama exams dina. Wannan kenan!!

Shiru muna cin abinci a cikin restaurant din da muke zuwa lokaci zuwa lokaci, baka jin karan komi sai karan cokali da plate din dake gaban Abbu yana cin abinci yayin da na kurawa nawa plate din idanu kawai, duk yunwar da nake ji sai naji ta tafi, babu space din komi a cikina a lokacin sai na numfashin da nake shaka. Fushin Abbu ya takura ni, ya tsorata ni, gabadaya na rasa abinda yake min dadi a lokacin. Tunda ya sadda kanshi ga plate din gabanshi bai dago idanunshi ba, na kula yana gudun kallona ne kamar yadda na kula cusa abincin kawai yake yi ba wai don yana jin dadin shi ba. A hankali nace “Abbu!" ya dakata da cin abincin da yake yi kafin ya dago ya kalleni, kyawawan idanuwan shi da a koda yaushe suke farare tas-tas suna sheki suna

kallona cike da so da kulawa, sun rine daga ainihin kalar su zuwa ja-brown, gaba na ya fadi sosai ban taba ganin wannan kamar ta Abbu ba, ya maida kanshi kasa ya cigaba da cin abincin. Nace “Abbu don Allah kayi hakuri kar kayi fushi dani, kawai Harith yazo ne mu gaisa ba wani abu ba please" bai yi magana ba kamar yadda bai dakata da abinda yake yi ba, na sake cewa “kaji?? Please Abbu na!!" duk da cewa sau tari ya kan nuna bai son sunan amma na kula jin sunan daga bakina yana dadada mishi rai sai dai da alamun hakan bai yi tasiri ba yau, babu murmushin nan daya saba yi, bai yi scowling dinnan ba yana kallona dangerously kamar zai zuke ni da idanunshi, instead sai kawai ya kalleni yayi wani murmushi da bai ma gama hade fatar bakin shi ba balle fuskarshi, muryar shi tayi can kasa kamar wanda yake suffering daga cutar mura yace, “eat, Nafeesah!" ya cigaba da cin abincin, sai kawai naji gwiwoyina sun sage, me ke damun Abbu ne yau? Gabadaya ya wani rikice min kamar ba Abbun dana sani ba, ban taba ganin wannan Abbun da yake gabana ba don haka ne naji nima na gigice sosai. Na xuba duka tafukan hannuwa na biyu

a cikin kumatuna kawai na kura mishi idanu, ban damu da cewa hakan zai takura shi ba ko kuma idon mutane dake cikin restaurant din, ni dai fata na da burina shine in karanto abinda yake damun Abbu inyi gaggawar magance mishi koma meye sai dai ban karanci komi ba, ya gama cin abincin ya dago ya kalli plate dina sai kuma ya tashi, yaje ya biya kudin abincin suka dawo tare da yaron wajen aka maida nawa abincin cikin take away muka fita daga restaurant din. Ko a cikin mota ma haka tafiyar ta kasance, yayi wani kicin-kicin da rai kamar wanda aka aikowa da sakon mutuwa. Har muka je bakin hostel ya samu waje a parking lot yayi parking. Na dan saci kallonshi kafin na yunkura da niyar fita daga cikin motar ya katse ni ta hanyar kiran sunana, “Nafeesah!" na dakata amma ban juya na kalleshi ba, na tsani ganin expression din fuskar shi kamar yadda na tsani mutuwata. Murya a hankali yace “kiyi hakuri don Allah" cike da tsananin mamaki na juya na kalleshi, fuskar shi nuna how apologetic he was, nace “me ya faru?" ya girgiza kanshi, “na saka ki cikin damuwa saboda son rai irin nawa, you didn't do anything wrong amma na saka

ki gaba ina hade miki fuska, na..." ya sadda kanshi kasa saboda maganar data kakare mishi ni kuma na kura mishi idanu, he looks soooooo lovely and adorable, Anya soyayyar Abbu zata barni in rayu cikin dadin rai?? Ya sake dago kanshi ya kalleni, wannan karon babu bacin rai dake tattare dashi sai idanuwanshi dake nuna tsananin so, kauna, kulawa da wani abu kamar tsoro? I'm not sure. Yace “I was afraid" cikin mamaki na kalleshi nace “of what?" ya girgiza kanshi, “I don't know. Kawai tunda na ganki da wani a tsaye naji wani tsoro ya dabaibaye ni, I really cherish you alot Nafeesah, I was afraid of you leaving me ko wani ya juye miki tunani daga gareni, idan hakan ya faru ban san ya zan yi ba!" wannan ba Abbu Baban su Hafsat da Abdullahi bane, wannan Ibrahim ne a zamanin da yake kan ganiyar kuruciyar shi, na muskuta ta yadda zan fuskance shi sosai, “ni ko wanene kwanakin baya yake cewa ba zai zauna yana soyayya irin ta yara ba? I wonder ko wace kalar soyayya ce wannan?" ya dan jefe ni da harara, na danyi murmushi kafin nace “nima idan hakan ta faru ban san yadda tawa rayuwar zata kasance ba Abbu, idan

hakan ta faru I'll be more shattered than u, gwanda kai kana da mata da ‵ya‵y'a ni kuwa dama daga kai sai Mommy da Daddy nake dasu" ya kura min idanu kaman wanda yake kokonton abinda nace, na saki murmushi reassuringly “kada ka damu Abbu, in shaa Allahu abinda kake tsammani ba zai taba faruwa ba, I am yours, and I'll always be in shaa Allah!" ya lumshe idanunshi for a second, daya bude duk wani duhu da rikicin dake cikin idanunshi sun yaye, damuwar data lullube shi ta tafi, Abbuna ya dawo kamar yadda yake, ya saki kayataccen murmushin nan nashi, “you are almost mine dai but at least am relieved, God! Kin tsorata ni wallahi, amma do you really mean what you said?" wai sai a lokacin naji kunya ta dabaibaye ni, nayi gaggawar Kai hannu na rufe fuskata, ina jin er dariyar da yayi, “ana so ana kaiwa kasuwa.... Zaki yi bayani ne idan aka miki snatching" fuskana na cikin tafukan hannuna nace “ai babu wanda ya isa ya kwace min abinda nake so!" ya rankwafo kanshi kusa dani yana wani smirking, ina kallonshi ta yatsun hannuna, yace “Ashe dai ana so na?" da sauri na bude murfin motar na fita na barshi yana dariya, da

alamun abin ba karamin dadi yake mishi ba, haka kawai naji murmushi ya subuce min. Ya fito daga cikin motar shima, “tambayar ki fa nayi baki amsa min ba" inaa, ai nayi gaba abina. Yace “to tsaya ki amshi abincin ki" naja tunga na tsaya, ina ji ya bude motar ya dauko takeaway din ya tako zuwa inda na tsaya ya miko min, nasa hannu na

karba ina wani sinke fuska, ya wani kuta kamar gaske “zaki yi bayani ne wallahi, sai ki wani dinga sinke fuska kina cuta na wai ke kunya, Allah ya kaimu ranar da zaki shigo hannuna" na saki murmushi, yace “dariya ma kike yi koh? Allah Nafeesah kina bukatar in gyara miki zama, dazu kin ce wai I was cute, yanzu kince ina soyayyar yara and ina magana kina dariya koh?? Sai na tabbatar dana hukunta bakin nan naki da baya jin magana wata rana" dariya na dan saki kasakasa, da alamun yau en rigimar ne akan Abbu. Naci gaba da tafiya abina, ya tsaya a inda yake yana magana cikin korafi, “wato ma tafiya kika yi kika barni koh? Ba komi, sai kinyi sati biyu baki sake ganin mai kama dani ba, kai sai ranar auren mu zaki sake ganina ma" na juyo ina kallonshi nace “to

ka gaida gida dasu Hafsy" yayi wani irin chuckling daya sa ni bude baki ina kallonshi, ji nayi kamar in ruga da gudu in fada cikin faffadan kirjin shi, sai nayi murmushi kawai tare da girgiza kaina na wuce cikin hostel. Kafin in karasa daki kiran Anty Raheena ya shigo wayata, na daga muka gaisa da ita. Tace wai kira tayi in fada mata size dina zasu siyo under wears da za a saka a cikin kayan lefena, ni wallahi kunya ma ta bani. Da kyar na iya bude baki na fada mata, ko sallama bamu yi ba na kashe wayar.

Bayan kwana biyu aka kai akwatina gidanmu, guda takwas sai kit, sai ta waya Anty Uwani ta turo min akwatunan na gani, wasu azababbun akwatuna kirar kasar Italy na zallan fata kalar pink ne, kayan dake ciki kuwa kama daga shadda, lace, materials, atamfofi, takalma ma kadai daga na kamfanin vincci, dg, poshter, ga jakunkuna da jewelries duka babu kanana gaskiya ba karamin kokari Abbu yayi ba wajen hada kayan nan, na dinga gyada kai kawai lokacin dana dinga duba kayan, 'kaya kam sun yi kyau gabadaya babu na yar wa sai dai fatan in more su a gidan aurena cikin tattali da soyayyar

juna ni da mijina'., a cewar Anty Uwani, ni kam na amsa da ameen a cikin raina.

☆☆☆☆☆☆

A hankali ya gangara motar shi cikin gareji yayi parking, “Amour, sai anjima, take care" nace “toh Abbu na, take care too" yace “mimm, wai Abbu"dariya kawai na saki wadda nasan tana saka shi cikin nishadi na kashe wayar, yayi murmushi yana bin farar Toyota data shigo cikin gidan tayi parking a daidai inda yayi parking din tashi motar. Saddiqa babbar Yayar su Mubeenah ta fito daga cikin motar, shima fita yayi ya gaidata cikin girmamawa, ta amsa a tsaitsaye tana kumburi kafin ta wuce shi fuu, ya bita da kallo cike da mamaki, matar tana da kirki unlike sauran kannen Mubeenah da ita kanta Mubeenar, duk cikin danginta daga ita sai Shafa'atu ne masu sanyin hali a cikin su, yau kam ko mai ya hau kanta? Ya tabe baki ya wuce wajen maigadi suka dan yi en maganganu ya shige cikin gida. Tun daga cikin falo yake jiyo

hayaniyar dake tashi daga can dakin Mubeenah. A can dakin na Mubeenah kuwa akwatuna ne a tsakiyar dakin manya har guda shida, Saddiqa na tsaye a gabansu ta kama kugu tana kallon Mubeenah dake kwance akan gado tana latsa waya, tun kayan barcin ranar data tashi dasu ne a jikinta bata canza ba gashi lokacin har karfe hudu na yamma, gashin kanta ya cukurkude ya cure waje daya, Saddiqa ta saki kugu data kama ta fara tafa hannayenta tana sallallami bayan ta gama saurаren abinda kanwar tata Mubeenah ta fada mata, “Innalillahi.... Mubeenah?! Anya kina da hankali kuwa? Kishiya ake shirin miki amma what?? You are cool with it?? Wai ke wace irin mahaukaciyar yarinya ce Mubeenah??" ta dago ta kalli Yayar tana gunaguni, “ni fa wannan aure za zai yi gaba ya kaini ba baya ba, kina kallon akwatunan daya zube min shake da kaya a matsayin kayan fadar kishiya, 5 millions ya bani in kara jarina bayan haka yana nan yana sake gina mana sabon gida kuma ya min alkawarin zai canza min kayan daki sababbi, bayan haka ita yarinyar da zai aura ta zauna damu anan, na riga da nasan halayenta ciki da bai na

tabbata da cewa ba zata taba cutar dani ba balle ‵ya‵ya na ke in fact na tabbata Ibrahim ba wai don yana son ta zai auro ta ba sai don kawai ya bani haushi kamar yadda yake fada tun ba yau ba, to kin kuwa ga menene nawa na yin fushi ko in wani kama bori kamar yadda kike cewa inyi? Kin ganni nan wallahi ko a kwalar rigata, in dai aurene yaje yayi tayi ga fili ga mai doki" bayani take zubawa tun karfinta babu ko digon aya balle comma, yayin da Saddiqa ta sake baki da hanci tana kallon kanwar tata kamar wadda tayi gamo, ta jijjiga kai cike da takaici tace “naji dai ana cewa ke mahaukaciya ce, amma ban taba zaton cewa haukan naki ya kai mataki na farko ba sai yau. Ke don kaza kazar ki, (ta kawo zagi ta lailaya mata), kowace mace tana shiga cikin tashin hankali da fargaba idan za a mata kishiya, amma ke kina zaune hankalinki kwance kina gaya min wai an baki jari kuma za a miki sabbin kayan daki. Kudin banza kudin wofi? Ke don ubanki kin manta yadda muka sha dabi da amaryar Abban mu?" ta kuta, “koda yake kina yarinya dama ya za ayi ki tuna? Ga kuma wata irin kwalwa ta kifaye da Allah ya halitta miki?" ta wani cuno baki gaba,

“Na gaya miki yarinyar tana da kirki sam ba halinta daya da sauran matan da kike fada ba..." Saddiqa ta warci kofin dake kan mirror ta saita bakinta ta jefeta dashi Allah yasa ta kauce da sauri, da sai ya dauke mata hakoran gaba biyu, Saddiqa tace “banza mahaukaciya wadda bata san inda yake mata ciwo ba. Kina ta daga murya kina wani fadan cewa kin san yarinya, kin san halinta ko tasan naki halin? Tazo gidanki ta zauna ta gama sanin sirrinki dana gidanki ciki da bai, taga weakness dinki taga komi naki, taje ta gama damarar kwace miki miji daga hannun ki amma kina zaune hankalinki kwance har kina da confidence din daga min wannan bakin naki ki ce wai kin san halinta?" da alamu ko kadan maganganun Saddiqa basa shiga kunnen Mubeenah, tace “ke ce kika kasa fahimtata dai, ni nasan Abinda nake yi. Da wadda ban sani ba ai gwara wadda na sani, ko babu komi yarinyar tana da biyayya sau da kafa, hakan zai bani damar juyata yadda nake so!!" Saddiqa ta dafe kanta da hannuwa biyu kamar zata kurma ihu, Mubeenah ta kalleta cikin mamaki, “wai ni kam don Allah menene damuwar ki akan maganar auren

nan, ke za a yiwa kishiya ko ni?" Saddiqa tace “Yi miki kishiya fa kamar yi mana ne, kin sani kamar yadda nima na sani, Ibrahim zama yake yi da ke kawai ba wai don yana jin dadin zama dake ba, kin sani" Mubeenah ta katse ta, “ni nasan Ibrahim yana so na" Saddiqa ta daka mata wata tsawa data sa tashi zaune dangargar akan duwawunta babu shiri, tace “ki min shiru Mubeenah!! Ke ce banza da kika kasa tantance so da dole, idan kika kuskura kishiya ta tako kafarta cikin gidan auren ki wallahi ina mai tabbatar miki da cewa kashin ki ya bushe, idan kin san ma'anar OUT to tsab zata yi waje dake kuma ina mai tabbatar miki da cewa idan har kika sa kafa kika bar gidan Ibrahim to ki tabbata cewa kinyi sallama da aure, I am as sure as hell babu wanda zai yi marmarin daukar ki a matsayin mata a yadda kike dinnan, wallahi Ibrahim kadai ne rufin asirinki" Mubeenah tace “Ibrahim yana so na, ku daina cewa wai baya so na, auren da zai yi babu abinda zai ragu daga son da yake yi min" Saddiqa ta juya ta kara juyawa a cikin dakin kamar wadda take fareti, “idan na gama da case din auren ki I'll make sure to take you to

psychiatrist for sure. Amma kafin nan bari inje in samu Haja (mahaifiyar su) babu macen data isa ta shigo gidannan wallahi" ta sa kafa ta bar dakin fuuu a matukar fusace kamar guguwa, Mubeenah ta daga kafada ta koma ta kwanta abinta. Saddiqa na fita taci Karo da Abbu a tsakiyar falo, bata damu da cewa yaji maganganun su ba ko bai ji ba ta shura kafa ta bar gidan. Ya girgiza kan shi a hankali yana murmushi amma fa can kasan xuciyar shi ji yake murmushin yafi mishi madaci ciwo, zuciyar shi kamar ana diga masa ruwan dalma saboda yadda take azalzalar shi da kuna, me yafi ciwo irin kaji cewa matar aurenka bata kishin ka??

~So what did you think about today's chapter?

~Kuna tunanin akwai mata irin Mubeenah a cikin duniyar nan kuwa? Idan akwai, wane irin hukunci kuke ganin ya dace da ire-iren su??

Na cewa Jalilah class mate dina, “ki wuce hostel kawai, akwai inda zan je" tace toh sai kin dawo. Har ta fara tafiya sai kuma ta juyo tace “naji wani rumor yana yawo

a cikin class dinmu, wai zaki yi aure?" na dan jijjiga mata kai ina murmushi, tace "amma gaskiya ban ji dadi da baki fada min ba" nace "sorry, auren ne kawai za a daura kin gane? Shi yasa ma ban wani yi shela ba saboda ina makaranta ma za a daura" ta matso da bakinta saitin kunnena cikin rada, "amma naji ana cewa wai wani lecturer ne anan zaki aura, da gaske ne??" na zaro ido cike da mamakin yadda aka yi zancen ya isa garesu, koda yake dama an ce zancen duniya baya buya. Nace mata "rumors ne kawai amma ba haka bane" tace "idan ma hakan ne meye na wa ko na mutane a ciki? Allah ya baku zaman lafiya mai daurewa" na mata murmushi ina kokarin boye dariyar data ciwo ni don nasan magana ce ta fada min, nace Ameen. Ta juya ta tafi abinta. Na duba agogon hannuna naga karfe sha daya ne da rabi lokacin, da sauri na dauki hanyar da zata kaini ofishin Abbu don nasan yana can yana jira na, ranar juma'ah ce ga masallaci ga kuma cinkoson ababen hawa. Na tura kofar office din na shiga fuskana dauke da murmushi, duk lokacin da zan ga Abbu sai in dinga jin wani irin doki da farin ciki a cikin raina kamar wadda ta shekara bata

ganshi ba, alhalin duka duka jiya alhamis har karfe tara na dare muna tare dashi, ranar ta Jumma'ah da safe wayar shi ta tashe ni daga barci, muka gaisa ya maimaita min how eager he was to have me as his, farin cikin da yake ciki saboda samuna da yayi a cikin rayuwar shi. A gare shi wadannan kalmomin kamar wasu routine words ne da ya saba fada min a duk sanda muke tare, a gare ni kam they were far more than golden and diamond words, suna saka ni cikin tsananin farin ciki da jin dadi, suna hana duk wata damuwa da bacin rai samun matsuguni a cikin raina, they were my remedies. Ya juyo daga gaban book shelves din dake kusa da desk din computer dinshi, wani tattausan murmushi ya sakar min da suka sa naji alamun butterflies na yawo a cikina, sanye yake da wandon jeans blue da knit shirt mai kama da sweater, irin shigar da naga samarin zamanin nan nayi kenan a wannan lokacin, shima sai ta maida shi kamar wani saurayin bayan kyawun data mishi, Abbu yasan kan fashion kamar wani fashionista shi yasa ko wane irin kaya ya sanya suke haska shi. Ya maida littafin dake hannunshi cikin jerin littafan dake cikin shelves din,

ya juyo gareni gaba daya yana murmushin nan nashi dai, kallona yake kamar wanda zai tsuke ni ta cikin idanuwanshi, it was so intense and disconcerting sai dana ajiye idanuwa kasa ina jin kamar kasa zata tsage in shige, yace “tun dazu nake jiran ki yanzu nake shirin biyawa ta library din in duba ki" nace “ban kula da cewa lokaci yaja bane, sorry!" ya dauki wata jaka mai kama da box dinnan akan tebur ya miko min, nasa hannu na amsa ina kallon shi cikin alamun tambaya, ya dan jingina jikinshi da teburin yace “akwai reception da aka hada mana ranar Sunday, kayan da zaki saka ne" na bude jakar na kalli kayan ciki, shadda ce bugaggiya ruwan kasa mai haske sai jaka, takalmi, da gyale su kuma dark brown kalar zaren da aka yi amfani dashi wajen yin surfani, na kara kallon shi nace “ranar Monday fa zamu fara exams dinmu" yace “ba zai taba karatunki ko jarabawar ki ba I promise, ni kaina ban san da zancen ba sai da suka riga suka shirya komi sannan suka sanar dani. I don't want to disappoint them, please help Nafeesah kinji?" yadda ya wani rausayar da kai yana kallona pleadingly, who m I to say no to him a yadda

yayi dinnan taking my breath away?? Sai kawai na girgiza kai ina murmushi, nace “Allah ya kaimu ranar" yayi murmushi “Ameen Amour.... Mine" na sunke kai a cikin hijabina, ya wani kuta, “just wait till tomorrow, war haka kin zama tawa, mallakina ta har abada, wannan kunyar taki sai nasa kin neme ta kin rasa" ya saki murmushi mai sauti, “Allah ya kaimu goben nan dai, I really can't wait baby" na kara kanannade fuskata a hijabin, jin abin nake yi kamar a mafarki, mafarkin ma wanda ba zai zama da gaskiya ba, wai goben ne daurin Auren mu? Oh, zan zama matar Abbu, Abbu na wanda so da qaunar sa suka mamaye jini da jijiyoyin jikina, na kauda tunanin daga cikin raina bana so in fara fayyace matsayin da gobe take a gare ni don nasan ba zan gama da wuri ba. Ya dauki key din motar shi muka fita, na jira ya rufe office din kafin muka fara tafiya a hankali zuwa inda ya ajiye motar shi. Ya bude motar ya shiga ciki ya juyo ya kalleni, “sorry, bazan iya maidaki hostel ba saboda sai na biya na dauki su Abdullahi sannan mu wuce masallaci" nace “babu komi, a gaida su" ya gyada kai, “zan kira ki anjima" na maida mishi murfin motar na

rufe, ya mata key ya tafi ina daga mishi hannu, sai dana ga fitar shi sannan na daga kafa da niyar tafiya. Kamar daga sama naga tsayuwar mutum a gabana, naja baya a dan tsorace har ina dafe kirji ina jan salati, Matar nan da muka hadu da ita a ofishin Abbu ranar nan ta bayyana a gabana, da alamu shigar rashin mutunci da na ganta da ita ranar a jininta take don kuwa lokacin ma irinta ce a jikinta, zan iya cewa ta ranar tafi ta waccan lokacin bayyana surar jiki ma. Hararata take yi tun karfinta da gwala-gwalan idanuwanta da suka sha uban eye shadow da girar kanti in ka ganta kamar wata doll. Nima na mayar mata da kwatankwacin hararar da take jifana dashi, “Malama lafiya zaki tare min hanya?" ta kama kugu tana wani jijjiga jiki, “ina so ne in fada miki ki rabu da Ibrahim" nayi fuskar alamun tambaya “me yasa?" ta dan daga murya, “saboda nawa ne! Na sha alwashin babu wadda ta isa ta aure shi muddin ina raye" nace “da alamu baki samu labarin cewa gobe ne daurin auren mu dashi ba, na tabbata da kin sani kam da ba zaki tare ni a hanya kina barking kamar tsohuwar karya ba" a girmame matar ta girme ni nesa ba kadan ba, sai

dai ni a rayuwa na sau daya zaka zubda daraja da kimarka a idona, abin na matar yayi yawa, ko a lokacin da nayi shirmen son Muneer ban taba tunanin zan yi kwatankwacin abinda take yi yanzu ba, bin kan namiji yana wulakanta ni kamar karya amma in ki in hakura har ta Kai ni ga bibiyar wadda zai aura ina threatening dinta. Fuskar ta tayi looking so pale saboda maganar da nayi, "ni kika kira da karya? just wait, in har ina raye sai na mayar dake abin kwatance, sai na muzanta ki fiye da kare, I'm warning u, ki fita daga rayuwar Ibrahim kafin in mayar dake abin kwatance!!" na daga kafada, "I'm not stopping you from doing whatever you will do, kawai abinda nake so yanzu shine ki matsa ki bani hanya in wuce" ta hasala iya hasala, hannu ta daga kamar zata mare ni, kallonta nake yi kamar wata kayan kashi a yatsine, ita da kanta ta janye hannunta ta maida shi kasa, nayi murmushin mugunta nace "kece kike ta shirme kina bin namijin da yake kin ki, tunda yace baya yi let him be, ana so dole ne malama?" ta wani zare ido tare da buga tsawa "ke...!!" nayi saurin katseta kafin ma ta gama fadin abinda tayi niyar cewa ta hanyar zare ido

nima, nace “malama kin ganni nan ban yi kama da matan da threats dinki zasu yi tasiri a kan su ba, kiyi duk abinda zaki yi wanda kike ikirarin mallaka ba zaki taba mallakar shi ba saboda ba don ke aka yi shi ba, a shawarce zan gaya miki ki fita daga rayuwar shi, Idan kuma kin ki ji sai dai kiyi mutuwar da kike ikirarin yi! Abbu ne kamar na aure shi na gama" naja tsaki tare da zagayawa ta gefenta ta wuce abuna ina muttering kalmomin dani kaina bansan me nake fada ba duk don in yi provoking dinta, na kuwa yi nasara. Ina bada baya naji sautin karan data saki cike da takaici, na kuwa saki murmushi kamar zan sheke da dariya.

Washegari da misalin karfe daya aka daura auren a babban masallacin juma'ah dake garin Malumfashi. Muna zaune a dakinmu Ni'imah ta kawo wata yarinya tana min kunshi wanda hakan umarnin Abbu ne, text dinshi ya shigo wayata. Na mika hannu na da nake jin shi kamar ba a jikina yake ba na dauki wayar, kai gabadaya ma sauran sassan jikina haka suke tunda garin ranar ya waye, ina ji Niimah da Firdausi suna ta

hira amma na kasa saka musu baki duk da cewa rabin hirar a wajen tsokanata ne. Text din cewa yayi, “Alhamdulillah. Yanzun nan aka shafa fatiha, kin zamo tawa ta har abada. Ina taya junanmu murna da farin cikin mallakar junanmu, Allah ya bani ikon rike ki cikin amana da kulawa Nafeesah" sai kuma wani da yace, “Wannan ranar rana ce da ban taba tunanin zata Riske ni ba, ranar dana mallaki abinda ban taba kawowa raina zan mallake shi ba. Jina nake kamar wani sabon halitta saboda tsananin farin cikin da nake ciki wanda na kasa misalta shi, Nafeesah kina da gurbi mai matukar girma da fadi a cikin zuciyata, na roki Allah mai Girma akan ya bamu zaman lafiya mai dorewa. You've Completed My Puzzled and Shattered Life, I really Cherish You Nafeesah" naji hawaye sun cika min idanu, nayi saurin runtse idanun ina kokarin maida hawayen, Allah abin godiya da Girmamawa, wai ni ce yau na zama matar Abbu?? Naji ina narkewa kamar wata jelly akan kujerar da nake zaune, na tabbata da ace ina tsaye ne da sai na fadi. Rangadediyar gudar da Ni'imah ta rangada ce ta dawo dani cikin tunani na, guda take tun karfinta da

waya a hannunta ta hau kiran waya tana bada albishir din an daura aure. Wayana ya shiga kara na daga, Daddy ne. Cikin rawar hannu na daga, “Uwata! Amarya!!" abinda na fara dokar kunnena kenan, na kasa magana sai kai dana jijjiga, yace “Nagode Allah da yasa naga wannan rana, ranar dana damka amanar ki a hannun wanda na tabbatar zai rike ki dari bisa dari, dama babu burin duk wani uba na kwarai daya wuce wannan. Yau dai kin zama matar Ibrahim, kin fita daga karkashin kulawar mu kin koma karkashin shi, yanzu shi zai yi sanadiyar ki zuwa gidan Aljannah wadda nasan babu haufi zaki sameta da yardar Allah uwata, Allah ya miki Albarka, Ya Albarkaci Rayuwar Auren ki, Allah ya baku zuriya Dayyiba!" muryar shi tayi kasa can kamar wanda yake so yayi kuka, ni kam kasa daurewa nayi kawai na fashe da kuka, gabadaya wani iri nake jina a tunanina idan nayi kukan zan samu sanyin zuciya. Ya shiga lallashina har na samu nayi shiru kafin ya min sallama. Yana kashe wayar kiran Mommy ya shigo, itama dai Addu'ah ta min kamar yadda Daddy yayi, zuciyar Mace mai rauni, sai tasa kuka, nima kukan nake

yanzu sosai su Ni'imah na aikin bani hakuri, ina ji daga wayar Anty Uwani da muryar wasu mata suna ba Mommy hakuri, Anty Uwani cikin fada tace “sai kisa hankalinta ya tashi ai, gashi nan itama kin sata kuka, ina amfanin haka?" tace “kukan farin ciki ne" tace “ai godiyar Allah ya kamata kiyi ba wai kuka ba, shima Abban nata yanzu na baro shi a waje yana share kwallah Allah yasa ba ita ya kira yana kukan ba.... Wannan ai sai ku sanyayar mata da gwiwa...." daga haka dai suka kashe wayar. A hankali nima nawa kukan ya fara yin kasa har ya dawo shessheka kafin nayi shiru ina ajiyar rai. A ranar dai har ba zan iya lissafa iyaka mutanen da suka kira ni suna taya ni murnar yin aure ba, tun daga kan abokaina da yan uwa har wasu daga cikin abokan Mom. Da yamma sai ga Ramlah ta dira a Kanon kamar daga sama, muka yi tsalle muka rungume juna ni da ita muna ihun murna, watanni biyar ciff tunda muka rabu da ita bamu sake haduwa face to face ba sai dai a Video call. Muka zube akan gado muna maida numfashi daya bayan daya, kallona take tun daga sama har kasa ta kyalkyale da dariya, “kaga Amarya a gidan Ibrahim

Galadanchi, kin ga wani kyau da kika yi kuwa??" na kai mata duka ina dariya, “meye haka zuwa babu sanarwa?" tace “surprise, dazu na dawo har mun yi hutu abinmu" nace “kun huta ku kam" nan muka shiga hirar yaushe gamo, tana nan tare dani har aka kira sallar magriba, ganinta ne yasa na warware har na samu naci abinci. Nan dai ta min sallama ta tafi akan cewa zata dawo Washegari, bayan na rakata zuwa bakin kofar hostel din na koma daki nayi sallar isha'i, bayan na gama na zauna nayi ta jero addu'o'i game da neman albarkar Allah da zaman lafiya a cikin sabuwar rayuwar da nake tunkara a cikin rayuwata. Abbu ya kira ni yace yana jirana a parking lot inda muka saba tsayawa, na tsinci kaina cikin faduwar gaba da sanyin jiki, cikin sanyin jikin na tashi na gyara zaman hijabin jikina na sauka kasa. Jingine yake da motar shi yana danna wayar shi, sanye yake cikin shadda ruwan Makuba yau kam har da hula a kanshi, akwai wadataccen haske a wajen hakan ne ya bani damar ganin fuskar shi sosai kamar cikin rana. Tunda na hango shi naji kafafuna sun fara hardewa, ban taba tsintar kaina cikin fargaba da tsoron fuskantar Abbu

ba tunda nake a rayuwata sai ranar, da kyar na iya karasawa gaban shi ina maida numfashi kamar wadda ta sha gudu, babu abinda yayi motsi a jikinshi sai idanun shi da suke kare min kallo tun daga sama har kasa, kafafuna ba zasu taba iya daukana a haka ba sai nima na jingina da jikin motar ina kallon zara-zaran yatsun kafar shi da suka fito ta cikin kyakkyawan bakin budadden takalmin kafar shi yana ta sheki.....

~Yau dai Allah yayi Dare Gari ya waye An Daura Auren Nafeesah da Abbu, Woah!

~Me zaku ce game da Shafin yau??

A hankali ya sauke ajiyar zuciya wadda take nuna tsananin farin cikin da yake ciki, “Hii there My Queen, My Happiness, My Amour, My Bride! Sunayen naki suna da yawa fa, amma kullum zan dinga kiran ki da guda daya wanda nasan sai mun dauki shekara basu kare ba, how are you?" kunya ta kama ni na sadda kaina kasa, yau ko sallama ban iya nayi ba balle in gaida shi, haka kawai naji wani nauyi da matsananciyar kunyar shi sun dabibaye ni.

A hankali kuma kamar wadda aka tursasa na bude baki nace "Ina yini Abbu?!" ni kaina sai da nayi mamakin muryata, it was very low kamar wadda take rada, ban yi tunanin yaji abinda nace ba sai da naji yaja wani sharp breath har yana hadawa da lumshe ido, "Masha Allah!" ya furta a hankali yana kallona da lumsassun idanuwan shi, ya Allah!! Da ace yasan yadda kallon yayi affecting dina da yayi gaggawar dauke idanunshi daga kaina saboda nasan ba zai so amaryar shi ta zube kasa kila hakan yayi sanadiyar karyewar kafarta ba, sai ya ci gaba da kallona kawai. Na samu nace "Ya hanya?" duk don in katse kallon da yake jifa na dashi da kuma hirar da zukatanmu suke yi, yace "Alhamdulillah, akwai gajiya kam amma tunda mun iso lafiya ai shikenan, besides ni tunda na ganki ma naji ni kamar an dauke min duk gajiyar dake tattare dani" nayi kasa da kaina, yace "Dad dinki ya bada sakon gaisuwa a kawo miki, ya damka min amanar ki har sai da sashen karbar sakonni a kwalwata ya cika, he even threatens me, heol!!" ya wani yi rolling idanu tare da dan chuckling, na kalle shi ya haske ni da murmushin nan nashi da yake sa ni yin abin da ban

shirya ba, ba shiri na sakar mishi murmushin. Yayi cocking kanshi gefe guda, “ko ke fa! Keep smiling like that baby, yau fa rana ce ta musamman a gare mu bai kamata ace murmushi ya kau daga kan fuskar ki ba.... Hmm, how I wish gidana za a kaiki yau din nan, da sai na nuna miki kaunar da babu namijin daya taba nunawa wata ‘ya Mace a duniyar nan, na saka ki a cikin farin cikin da baki taba tsintar kanki a ciki ba, amma tunda hakan ba zai samu ba zan rike komi har sai an kaiki gidana baby, ranar...." sai kuma yayi shiru yana girgiza kai, “it will be a surprise, sai kin zo kawai zaki gani" ya duba agogon hannunshi, motar ya bude ya fito da leda ya miko min, tun kafin in amsa nasan ko menene a ciki, kaza ce gasasshiya sai tashin kamshi da tururi take yi, yace “bana son farin cikin ciyar da amaryata a daren aurenmu ya wuce ni duk da cewa ba ni da kaina zan ciyar dake ba" nasa hannu na amsa tare da mishi godiya, yace “you must be tired, jeki ki kwanta, nima zuwa zan yi inyi barci don ji na nake yi very exhausted Allah ma dai yasa in iya yin barcin" ni dai ban tanka

mishi ba na daga Baki da kafa a lokaci guda nace “sai da safe".

Suddenly naji an janyo hannuna an dawo baya dani, kafin inyi yunkurin kwace hannuna da kaina gabadaya ko kuma ma in tantance abinda ya faru na tsinci kaina akan faffadan kirjin Abbu, yasa hannu daya ya dago habata ya kalli tsakiyar idanu na, abubuwan dana karanta a idanunshi a lokacin suna da yawa, zallan so, tsabar kawa, raw lust Ya Allah I couldn't take it, idanuwana na kame don ba zan iya cigaba da karbar sakonnin dake fita daga cikin idanunshi ba, naji hucin numfashin shi akan fuskana ban taba kawo komi ba sai da naji bakin shi akan nawa, it was as if duniya ta tsaya cak da juyawa, ya dago ya kalli fuskana da idanuwan suke rufe yace “it's something that I've wanted to do decades ago but being the good man I am holding it in, I Love You Nafeesah!!" abubuwan sun yi wa kwalwa ta yawa a lokacin har na rasa da wanne iri ne zan ji, his sudden kiss ko kuma sudden kalmar yana so na daya furta?? Na daga idanuna da suka min nauyi na sauke su a fuskar shi, kallona yake fervently, sai naji ni kamar

wata danyar nama a gaban zaki, da dan sauri na janye hannuna daga nashi hannun, cikin sauri na juya na fara tafiya ina jin kamar wadda ake turawa don har ga Allah ban san ina nake jefa kafa na ba, ni kaina nasan ikon Allah ne ya kaini daki, nayi jifa da ledar daya bani akan slab na zube akan gado kamar kayan wanki na rufe kaina rikib da bargo, Firdausi ta bini da kallo baki a bude naji dadi da bata yi magana ba. Allah kadai yasan lokacin dana share a kwance a cikin bargon nan, daga karshe dai na mike saboda ihun da cikina yake yi na yunwa, tun macaroni din da muka ci da Ramlah da rana ban kara cin komi ba, na sauka daga kan gadon na dauki plate na bude ledar har da yoghurt a ciki mai sanyi duk da zafin kazar ya rage mishi sanyi, na dora ta akan plate da fork da er wuka na kai kan dan karamin bench da muka mayar kamar dinning na dora, na dauko kofuna da yoghurt din suma na ajiye, da hannu na wa Firdausi nuni alamun ta taso don ba zan iya daga baki in mata magana ba ma. Ta taso ta zauna a gefena tana wabi smirking, “Anya zan iya cin kazar amarcin nan kuwa? Idan aka tashi tambayana ita ya zan yi kenan?" nayi banza da ita

na fara cin kazar, itama ta fara ci. Tace “ni naga kin wani firgice ne ko dai anyi abin ne?" na harareta tayi dariya kasa-kasa tace “dama sai dana gaya miki ai, mu dai ki rufa mana asiri ki bari sai mun kaiki kafin ki samu ciki kinji??" nan ma ban tanka mata ba, to ai ko nayi niyar tanka mata ma bani da kuzarin yin hakan. Ita kanta kazar jin ta nake yi tayi wani iri na bakina bana jin dadinta, sai yoghurt nayi ta kwankwada don shine mai sauki tunda hadiya kawai zanyi, sauran kazar Firdausi ta nade a cikin takardar ta ta saka a cikin fridge dinta. Littafai na dauko na dare kan study table ni ala dole zan yi karatu, koda na zauna babu abinda yake yawo akan littafin sai fuskar Abbu da murmushin shi, duk yadda naso inyi karatu a daren ranar abin yaci tura dole na hakura na koma kan gado na kwanta hannuna dafe da lebena wanda har lokacin nake jin tausasan lebunan Abbu akan su, it felt so awkward yet so good my body was shaking with desire.

Sai bayan da nayi sallar asubahi sannan na samu na kara bitar karatu. Karfe tara muka fara exam dinmu

muka fito kafin sha biyu, daga nan barci nayi don jiya kam ban samu nayi barcin kirki ba. Sai da su Ni'ima suka zo sannan na tashi daga barci lokacin wajen karfe biyu ne, sai da nayi sallah sannan muka shiga shirye-shiryen zuwa wajen Reception din. Suka wanke min kai suka kafar dashi kafin suka gyara min shi sai sheki yake yi da tashin kamshi, nayi wanka na fito nan ma aka shiga yin kwalliya kuma. Da aka kira la'asar muka yi saurara muka yi sallah sannan muka ci gaba, na zura doguwar rigar shaddar da Abbu ya kawo min, Ramlah ta daura min dankwalin rigar yayi kamar gwaggwaro, na saka dankunne, sarka da awarwaro masu ratsin brown a ciki, muna cikin yin shirin wanda aka turo ya dauke mu ya yi waya yace ya iso, da yake suma a shirye suke sai duk muka rankaya muka tafi. Wata er ubansun Range Rover ce baka tana ta sheki tazo daukar mu, aka bude mana muka shiga maza biyu ne a gaban motar don haka muka shiga baya muka tafi, daya daga cikinsu ya juyo muka gaisa har da yin shakiyancin su na abokanan ango, su Firdausi ne masu tare min ni kam kaina yana kasa, duk inda muka wuce sai an bimu da kallo wanda probably

nasan cewa motar suke kallo don kuwa haduwarta ya wuce misali.

Tafiya muke yi a hankali har Hotoro, aka yi horn a kofar wani gida aka bude muka tura hancin motar muka shiga, anyi decorating din wajen da kayan ado da ake yi wajen bukukuwa ga kujeru an shirya, wajen cike yake da mutane ana ta hada-hada, aka yi parking sannan muka fita. Wasu mata gungu guda suka zo suka ja mu har wajen da na tabbatar saboda ango da Amarya aka yi shi saboda wajen ya fita daban, wasu royal kujeru guda biyu a kasan canopy an sa tuntu akai a kasa kuma an shimfida wani babban carpet me fadi da laushi. Mai gayya mai aiki Abbu yana zaune a kujera daya, munyi anko da kayan jikinshi shadda light brown mai surfanin zare dark brown, leather brown cover shoes da hular zanna bukar itama brown, kaina a kasa yake ban yi gigin daga ido na dubi Abbu ko tarin mutanen da hankulan su ya dawo gare mu har suka taimaka min na zauna a kujerar kusa da Abbu, in a wink sun bace daga wajen, photographer yazo ya fara haskemu da flashes ya dauki kamar guda goma kafin ya tafi. Abbu ya dan matso saitin

kunnena ya rada min “kin yi kyau sosai amaryata" na danyi murmushi ina wasa da yatsun hannuna. Mutanen wajen basu da yawa duk da haka na hango wasu daga cikin dangina na Malumfashi mazan, Aminu, Haruna da Samir duk diyan kanne da Yayin Daddy ne, a matan wajen kuma na hangi Anty Amina da Anty Rahina, Sadiya, Saratu, Da Halima su kuma cousin din su Sadiya dinne, sauran matan kuwa da zasu kai guda goma ban san su ba na dai yi zaton kila matan abokan Abbu dinne. Ba wani bata lokaci aka fara gabatar da walimar, wani daga cikinsu ya bude taro da addu'ah, ya mana fatan alkhairi ana yi ana raha ana ta shan dariya saboda jokes din da mutumin ya dinga cracking, daga nan kuma aka yi en ciye-ciyen snacks da aka raba da kuma drinks, daya bayan daya suka dinga zuwa kowa da matar shi, mu gaisa dasu su mana fatan alkhairi su bamu kyauta, wani a cikin wrapping sheet wani kuma a envelope har su Anty Aminah dasu Ni'imah, daga nan kuma aka shiga daukar hotuna kamar me?! A haka har duhu ya fara shigowa, sannan ne fa aka kara rufe taro da addu'ah muka fara sallama dasu suna shiga motocin su suna

tafiya, kafin dai a kira magriba an barmu daga mu sai mu, su Anty Ameenah ma suka mana sallama suka tafi, su Ni'imah sun bi mazajen su sun tafi sai Ramlah tabi bayan su Sadiya. Muka shiga falon matar gidan mai suna Farha ta mana jagora ni da Firdausi har cikin bedroom dinta muka yi sallah, matar tana da fara'ah ga kirki, muna gama sallah muka fara hira wadda yawancin ta akan rayuwar aure ne, challenges din dake cikin shi da shawarce-shawarce akan zamantakewa da kuma wasu shawarwarin da suka sa ni sunke kaina cikin gyale na, tace "kunya kike ji? Wallahi idan kika ce zaki saka kunya cikin rayuwar aurenki to zaki samu cikas kuwa more especially ke mai kishiya, ai wallahi dagewa zaki yi ki cire kunyar nan ki kama mijinki tsam kafin kishiya ko wata a waje ta miki kwacen shi" na gyada kaina cikin yarda da maganganunta. Su Abbu basu shigo gidan ba sai bayan sallar Isha, Farha tayi-tayi damu akan mu tsaya mu ci abinci muka ce a'ah, ta bude wani karamin Kit, tana bude shi wani kamshi mai dadi ya hade dakin, ta dauko kwalaben humra guda biyu ta bani ita kuma Firdausi ta bata turare, tace min "sai dai humra din nan

ki bari sai kin tare kafin ki fara amfani da ita Zai fi" muka mata sallama muka fita waje inda Abbu yake jiranmu, muka sake sallama da Farha da maigidanta muka shiga mota muka tafi. Babu wanda yayi magana a cikin motar har muka isa makaranta, Abbu yana yin parking Firdausi ta bude motar ta fita bayan ta wa Abbu sai da safe shi kuma ya mata Allah huta gajiya. Tana fita kamar wanda yake jira ya kamo hannuna, bai damu da yadda nayi gaggawar kwace hannuna ba ya sake janyo hannun nawa yana caressing da thumb dinshi, “kunshin nan yayi kyawu sosai, idan ya goge ki sake yin wani kinji? Shima idan ya goge ki sake wani, I'd like to be seeing it kinji??" na gyada mishi kai a hankali, yayi murmushi “good girl, amma ni sai wani noke-noke kike yi da wani kauda fuska, kin daina min magana, laifin me na miki iye?" ban yi magana ba sai kaina dana girgiza yace “ikon Allah! Aikuwa ba zamu yi haka dake ba, za kina bude baki ne kina min magana idan ba haka ba kuma raina zai baci fa, and u wouldn't like me idan hakan ya faru, ok?" na sake gyada kai, sai kuma nayi sauri nace “toh" yace “na fara nema mana visa fa, wani gari kike so kije for our

honeymoon?" na dan zare ido, “honeymoon?" yace “ehh mana, da kin gama exams kin koma za a dawo min dake daga nan kuma zamu tafi honeymoon dinmu" nace “amma da aka ce sai session dinnan ya kare?" ya wani zaro ido kamar wadda ta fadi wani sabo, “ses... me? Ni dai nasan da bakina baki ji na fadi haka ba koh?" nace “ai nayi zaton haka ne" tun kafin in gama yake girgiza kai, “no! Ba haka bane. Gidan da zamu zauna is ready, komi ya riga ya kammala, kun gama jarabawar ku to me zan jira kuma? kin dai san ba zan barki kici gaba da zaman hostel ba kuma yanzun ma don we've already agreed on it ne shi yasa kika ga nayi shiru amma maganar gaskiya ban jin dadin zaman ki anan" na wani yi rau-rau da idanu, ya dage gira, “Allah baby kina jin dadin ki, kuka zaki yi kuma, me na miki?" ya kai hannunshi na dama ya tallabo kuncina dashi yana caressing din kuncina, hannunshi was very warm, na lumshe idanu na a hankali, na jiyo yatsar shi a saman idanu na yana shafawa, “zan ga yadda zamu kare da rigimar ki baby, dama ana haka ne? Daga magana sai ki kama kuka irin daddyn ki ya shagwaba ki koh?" na turo

baki tare da janye fuskata daga hannunshi wadanda suka fara sanya min sayingsanyin jiki, murmushi kawai yayi. “Wadannan kyautukan da kika samu ban san ya zanyi dasu ba, do u have any idea ko wajen da zaki ajiye su?" nace “ka ajiye min su a wajenka" yace “to shikenan, zan kaisu gidanmu in ajiye, idan kin zo sai mu bude tare koh?" na rufe fuskata shi kuma yayi dariya, “nasan akwai kudi a ciki su kuma zan saka su cikin account ko ya kika ce?" nace hakan ma yayi, nan ma yace ok. Muka dan yi shiru na dan lokaci kafin ya duba hadaddiyar agogon fata dake daure a lallausan hannunshi, “to nine, yakamata kije ki kwanta yanzu koh?" nace “to, sai da safe" dama duk a wani takure nake ji na, na kama murfin motar zan fita ya sake janyo hannuna da bai jima da saki ba ya juyo dani, “not so soon baby, babu ko sallama?" na danyi frowning in confusion, wace sallama yake so muyi bayan wadda na mishi yanzu? Ban kai ga furta abinda nayi niyya ba naji ya hade goshina da nashi waje guda, irin sallamar jiya ya min sai dai ta yau tafi zurfi da demanding, ya sake ni a hankali idanunshi a lumshe, har lokacin goshin mu a hade yake, numfashi

yake ajiyewa a hankali can kuma sai ya sake ni gabadaya, “Goodnight Amour" ya fada cikin whisper, cikin salubewar jiki na fita daga cikin motar. Ina shiga daki text dinshi ya shigo wayata, “make sure to eat something kafin ki kwanta, sweet dreams" na girgiza kai kawai na ajiye wayar akan gado na fara zare kayan jikina, ruwa na watsa na dawo nayi shirin kwanciya barci. Ba wata yunwa nake ji ba don haka na kwanta kawai, Abbu da Al'amuran shi masu ban mamaki suke min yawo a kwalwa, abubuwan da yake min were very new to my innocent life, ban san ya zan kamanta abinda nake ji a cikin raina ba amma ina jin kamar abin is wrong, anya ban yi kuskure ba kuwa?? Nayi juyi akan gado tare da tura kaina cikin pillow.

I love you so much Baby na Abbu na

Ranar Talata bamu yi exams ba sai ranar Laraba. Misalin karfe tara muna cikin exam hall muna jiran invigilators su shigo, sanye nake da doguwar riga dinkin Stella sai

mayafi dana yafa mai yalwar fadi, fuskata daga hoda sai kwalli ko janbaki ban shafa ba saboda a sukwane na fita ranar don na kusa makara. Much to my surprise na tsinci Abbu cikin invigilators din, idanunshi suka zagaye ajin har sai da suka lalubo ni ya sakar min kyakkyawan murmushin shi da sai da yasa naji gwiwoyina sun sage, a dan kunyace na maida mishi martani tare da sadda kaina kasa ina tuno yadda muka rabu dashi a jiya da yamma da yazo wajena, yana insisting lallai sai munje ya nuna min gidan da zan zauna ni kuma nace mishi ba sai na gani ba, da yaga alamun ba zan bishi ba sai ya fara min abubuwan nashi da har lokacin kwakwalwata ta kasa daukar su ko sabawa dasu, da kyar na samu na zame na tsere.

Lokacin dana sake kallon inda yake hararata yake yi kasa-kasa fuskar shi na nuna bacin rai, gabana ya fadi, crap! Me nayi? Ko dai tun laifin jiya ne har yanzu yake fushi dani don naga tun daga lokacin bamu sake waya ba kamar yadda bai turon text ba duk da cewa dai na tura mishi wani yau da safe amma bai turo min da reply ba. Aka fara raba mana answer booklet ya dauki wasu

yayi row din dake gefenmu na dama, yadda na bishi da ido haka na tsinci idanun yawancin ‘yanmatan ajin suna bin shi da kallo, naji wani takaici da bacin rai yana lullube ni, meye nasu na

Kalle min miji? Sai naji kamar in tashi in fidda shi daga cikin ajin, na dai daure ban yi anything silly ba har ya juyo ta bangarenmu. Yazo saitina ya tsaya yana kokarin ciro booklet din, kamshin turaren Armani Code ya mamaye wajen naja na shaka har da lumshe ido, a hankali nace mishi “Abbu good morning!" lokacin daya danyi leaning akan desk din da nake ya ajiye mun takardar, “me yasa kika fito da wadannan kayan a jikin ki?" ya fada muryar shi na nuna bacin rai da distaste, na kalleshi tare da kallon kayan jikina, saboda Allah meye aibun su? Gyalena mai fadi ne ya rufe duk inda ake bukatar ya rufe, kafin in samu ince wani abu ya kara gaba zuwa ga desk din bayana, na danyi shrugging slightly na fara rubuta sunana akan takardar.

Ana bamu question paper na fara rubutu, Abbu ya jingina da window din gefenmu na hagu saitina, duk da ban daga kai na kalleshi ba amma nasan da cewa

idanuwanshi a kaina suke don kuwa naji su, don haka zan iya cewa jarabawar ranar cikin takatsantsan nayi ta, ko motsin kirki ban yi ba. Ranar ni na fara submitting, ban tsaya jiran komi ba na bar hall din a tunani na zan iya tsere mishi kafin ya fito, sai ganin shi nayi ya wuce ta gabana, "follow me!" kawai yace yayi wajen parking lot, na sadda kaina kasa in surrender, nabi bayan shi na bude motar daya riga ya mata key na shiga, ina zama ya juyo glaring at me, "na tambaye ki baki bani amsa ba, nace me yasa kike yawo da wadannan kayan?" na daga gyalen jikina ina kallonshi, "naga fa gyalen bashi da matsala babba ne, kuma ya rufe min jiki meye marabar su da hijabi?" yaja motar muka tafi, "it's transparent for Goodness sake, ki duba kiga dazu da muka shigo, hannu da wuyanki duk a waje suke. Maza nawa na gani suna kallonki kina a matsayin mata ta?" juyawa nayi na kalleshi, ashe muna taya daya, "daga yau na hana ki saka gyale ko wani iri ne, be it mai kauri ko transparent I don't care, wear hijab wadda zata dinga rufe miki dunduniya!" na zaro ido, "to ai ni hijabai na gabadayansu ma basu kai biyar ba kuma da guda biyu

kadai nazo makaranta" ya daga baki cikin mamaki kamar zai yi magana sai kuma ya rufe bakin, ya sake budewa yace “akwai hijabai a cikin kayan lefenki, idan kin tare ma zan dinka miki wasu for now sai kiyi amfani da wadanda kike dasu kafin ki koma" nace “Abbu....?" ya juyo ya kalleni fuskarshi na nuna rashin jin dadi, “r u arguing with me Nafeesah?" nayi saurin girgiza kaina, “to meye?" sai kawai na sake girgiza mishi kai, muka cigaba da tafiya ba tare da munyi magana ba, wani tunani ya darsu a raina. Na hade fuska tare da turo baki nace “to in dai haka ne sai dai kaima ka daina sa irin kayan daka sa yau, Allah kadai yasan iya adadin matan da suka dinga kallonka yau, kai duka ‘yanmatan ajinmu were looking at you with interest in their eyes" daidai lokacin yayi pulling motar zuwa cikin lot din dake gaban hostel dinmu yayi parking, ya kwashe da dariya cikin farinciki da wani abu mai kama da humor, na kura mishi ido ina kallonshi relieved and amazed, at last! Yayi more than murmushi.

Sai da yayi dariyar ta ishe shi sannan ya kalleni, “ni kuma meye aibun tawa shigar?" Armani pants ne a

jikinshi da open neck top, ire-iren kayan da suke boye shekaru da girman da yayi su fito da xallan yarinta da kyawun shi. Na turo baki ban amsa ba, hannuna ya kamo ya rike a cikin nashi yana caressing, “girl, Ashe kema kin iya kishi? Ni indai nine baki da matsala dani, ki fadi duk irin kayan da kike so in dinga sawa zan sanya babu musu, m all urs Amour" na sadda kaina kasa ina blushing, na duba naga duk cikin irin kayan da yake sawa babu wanda basu mishi kyau, sai na kauda hirar na fara kokarin janye hannuna daga nashi wanda ya fara sa min tashin tsigar jiki. Ya kalleni fuskar shi a dan hade, “na kula baki son ina rabar ki kwana biyun nan Nafeesah, mai yasa?" duk da maganar da yayi sai dana janye hannuna daga nashi na saka su cikin gyalena, shiru nayi kawai, to in ce masa me? Ina jin kaina kamar wata traitor ko mai laifi idan ya taba ni, I'm feeling awkward idan ya taba ni, feelings ne da ban saba jinsu a cikin rayuwata ba hakan yasa na fara having second thoughts, ko dai don yana abokin Dad ne na kasa sakewa da Al'amuran shi? Ya kuta kawai, “zaki gama kewaye-kewayen ki ne ma ki dawo hanya Nafeesah, ina

so zan wuce gida yanzu, me kike so in kawo miki anjima?" nayi saurin girgiza kaina, “babu komi" frankly speaking zan fi so ace ba ma sai ya dawo ba, ya tabe baki “sai wani guduna kike yi fa, kin manta cewa komi wayon amarya sai an sha man ta?" na kalle shi, wani murmushin mugunta ne akan fuskar shi da yasa naji wani tsoron shi yana shiga ta, ya kamo hannuna duk nokewar da nake yi sai da ya kai bayan hannuna saitin bakin shi ya sumbata, nayi saurin bude motar na janye hannuna na fita, sai dana fitan sannan na leka ta tagar motar nace “Abbu a gaida su Hafsy, sai anjima" yayi murmushi kawai yana gyada kai, na juya da sauri na wuce.

A haka har muka gama exams dinmu, ina ta kauce-kauce yayin da Abbu bai fasa abin shi ba sai ma abubuwa da suke karuwa kullum. Kwana biyun nan ya dameni akan wai shi fa lallai sai ya kaini naga gidan mu, ni kuwa nasan muddin na taka kafa naje gidan to sunana sorry, kila warning din dasu Ni'imah da Firdausi suke yi mun na in daure kar in tare da ciki ya tabbata. Tun a

ranar da nayi exams dina na karshe na fara hada kayana, na kira Daddy a waya yace washegari zai turo a zo a dauke ni saboda ranar sai da yamma muka gama exams din, nace mishi don Allah ya turo direban tun da safe mu tafi, a matukar kagauce nake da in tafi gida, I have to clear my thoughts and brain kuma nasan gidanmu ne kawai zai bani wannan natsuwar, ga kewar su Daddy da nake yi kamar me, hakika nayi kokari, watanni biyar rigis ba tare dana saka su a cikin idanuna ba. Na kira Ramlah da tace tare zamu wuce Kadunar da ita na sanar da ita, tace zata shirya sai mu biya ta gida mu dauketa nace to muka yi sallama.

Karfe tara na safe kayana sun kammala waje daya, nayi wanka na shirya cikin riga da siket na atamfa, hijabin data zame min mayafi na ajiye a gefen gado a linke, na dauki wayata na fara buga game don ya dan kashe min time kafin direba ya zo. Kiran Abbu ya shigo wayata, gabana ya fadi sosai gabadaya na manta bamu yi sallama dashi ba saboda doki, na dauki wayar na kara a kunnena, "meet me at my office" kadai yace ya kashe wayar, na bi wayar da kallo kamar ba zan tashi ba, can

kuma na mike na saka hijabina, Firdausi bata dakin taje rubuta jarabawa don haka na rufe dakin na fita. Zaune na same shi akan kujera fara dake a tsakiyar ofishin da alamun jirana yake yi, na maida kofar na rufe na zauna akan kujera dake fuskantar shi na zauna, fuskar shi sam babu yabo babu fallasa hakan yasa naji sanyin jiki ya mamaye ni, Allah dai ya taimakeni muyi rabuwar aminci yau don na kula da cewa rigima yake ji yau. Murmushi nayi a sanyaye nace "Abbu ina kwana? Ka tashi lafiya?" yace "ke zan tambaya ai, amma ni kin tambayeni tashina lafiya bayan kina neman hana min abinda yake nawa ne?" na dan zamo daga kan kujerar da nake zaune nace "don Allah Abbu kayi hakuri, idan kayi hakuri ma duka kwanaki nawa suka rage kafin a kawo maka ni gabadaya kayi yadda kake so dani?" ya lumshe idanun shi tare da maida kanshi ya jinginar da kujerar da yake zaune, "I tried Nafeesah, I really do. But I can't anymore, all I ask for u is just half an hour, please ki zo muje gidana, I so badly want you Nafeesah!!" na kura mishi idanu, idanun shi a lumshe suke har lokacin, Abbuna ne a gabana yake rokona, da ace zan iya da na

mishi abinda yake so domin samun farin cikin rayuwar shi, sai dai ba zan iya din bane, I'm still not ready for it. Mikewa tsaye nayi a hankali, hanya mafi sauki in bar mishi ofishin kafin in kara bata mishi rai, nasan ba zai fasa tambayana ba, ni kuma in yaci gaba da tambaya it's either inyi abu daya cikin biyu; ko dai in sallama mishi ko kuma inyi denying wanda duka cikin biyun babu wanda zai mun dadi, nace "Abbu don girman Allah kayi hakuri, kayi hakuri na wata da watanni ma balle na en kwanaki? I am very sorry, zamu wuce Kaduna yanzu don Allah kar kayi fushi dani Abbu..." na juya cike da sassarfa zan fita. Ban ji lokacin daya tashi tsaye ba sai maganar shi dana jiyo daga bayana, "Please Mana Nafeesahh!!" Ya fada cikin wata irin murya wadda ta narke cikin tsantsar qauna da soyayyah. Kaina na fara girgizawa a tsorace, "Bazan iya ba. Kai fa Abokin Babana ne please kayi hakuri,bazan iya ba wallahi!!" idanunshi ya zuba min wadanda suke a lumshe kamar na mashaya, dama a yawancin lokuta a haka suke, sai dai na yau sun banbanta dana sauran lokutan. Na yau cike suke da wata irin soyayyah, zallar qauna, pure lust, I

can sense them radiating from his body. Muryarshi ta kara yin kasa sosai “ina tunanin mun riga da mun gama wannan maganar Nafeesah? saboda Allah mutane nawa kika san sun yi aure irin namu kuma suna zaune lafiya har ma da zuria a tsakaninsu, ko a cikin tarihi ki duba fa, Sayyadah Aisha RTA diyar Sayyidina Abubakar ce wanda ya kasance babban Amini makusanci a wajen manxon mu (S. A. W) nasan kin san da haka ba sai na sake gaya miki ba" maganganun shi haka suke sai dai na kasa convincing kaina da zuciyata" nace “yeah, I know.., I just need time please kayi hakuri" ya girgiza kai, “na gaya miki ba zan iya bane Nafeesah, it's not as if wani sabo ne nake shirin aikatawa" Kai na ci gaba da girgizawa hawaye na sauka akan kumatuna, ya zanyi da raina da rayuwa ta ne ni kam? Ban san ya aka yi ba sai ganin shi nayi a gabana, kafin inyi wani yunkuri yayi pinning dina da bangon ofishin, "I love you Nafeesah....I want you n I know you do, u just don't want to admit it!""no.... No... I... I" na fara fada cikin in'ina kafin inji wasu tausasan lebba sun hana ni karasa maganar. Lebena na kasa ya kamo ya fara tsotsa cikin wani irin

passionate kiss, a hankali na lumshe idanuna tare da kamo nashi leben na sama nima na fara tsotsa, ya saka hannu daya ya zagaya dashi ta kuguna ya kara matso dani zuwa gare shi tare da zura harshen shi cikin bakina muka fara hadamammen kiss, ihu ake a cikin kaina da kwalwata, "Ya Allah! What am I doing? He's my father's Friend for Heaven's sake!! Cewar wani sashe na zuciyata, but hell! I couldn't let him go, sai ma kara rike shi da nayi tsam....

Karan da wayata ta dauka baby kakkautawa ne ya dawo da hankulanmu cikin ofishin, a matukar kunyace na janye jikina daga nashi yayi saurin janyo ni ya rungume a cikin kirjinshi, duk yadda naso in kwace abin yaci tura ina ji ina gani haka na Hakura har wayar ta gama burari ta katse, numfashi yake saukewa a hankali har ya dawo cikin natsuwar shi, ya hade goshina da nashi yana kallona ni kuwa naki hada idanu dashi, murmushi ya saki a hankali, "kin gani koh? We need each other Nafeesah, amma kina hana kan ki abinda zuciyar ki da gangar jikinki ke so, why?" a hankali na daga baki nace "kayi

hakuri" ga mamakina sai naji yace “na hakura Nafeesah" na daga kai cikin mamaki na kalleshi, ya daga kafada, “to me zan yi idan ba hakurin ba? Kin san cewa ba zan taba tursasa ki ga yin abinda baki so ba, zan jira har a kawo ki din sai dai kada ma ki roke ni wani abu a wannan lokacin don ba zan ji ki ba...., muje in kaiki hostel din" ya zari makullin mota ya fita, na bishi da kallo ina murmushi, saukin kan Abbu yana burge ni sosai da sosai, Allah ya yaye min fargabar nan da wasi-wasi da nake ji ko na samu na faranta mishi rai kamar yadda yake kokarin faranta min. Na bi bayanshi na fita daga ofis din ya rufe muka tafi. Koda na duba miss call din da aka min direban da daddy ya turo min ne, na kira shi ya sanar dani ya iso nace mishi gani nan. Koda muka isa mun dauki lokaci muna hira da Abbu kafin muka yi sallama dashi akan cewa zamu yi waya, ya kama hannuna yayi kissing bayan hannun kamar yadda ya mayar dashi al'adar shi tun ina jin abun banbarakwai har nazo na saba da hakan yace “m gonna miss you baby" nace “me too" a kunyace, yayi murmushi, da haka yaja motar shi ya tafi. Firdausi ta taya ni dauko kayana muka

lode su a bayan booth, daga nan muka yi sallama da ita ita sai nan da kwana biyu zata gama nata exams din, na shiga mota direba yaja muka wuce Kaduna bayan mun dauko Ramlah. Karfe biyu a Kaduna ta mana, da gudu na shiga gidan ina ihun kiran Mommy, ta fito daga kicin tana goge hannunta da kicin towel, na tafi da guduna na rungumeta ina murna, ta janye ni daga jikinta tace “ke tafi can ni, wannan yarinya ban san yaushe zaki girma ba ni kam" na kara shigewa jikinta ina tsalle abina, sai da Ramlah ta shigo sannan na sake ta. Suka gaisa da Mommy kafin muka shiga dakina muka yi wanka muka yi sallah, sai a lokacin na kira Abbu na sanar dashi mun sauka, nan muka danyi hira muka yi sallama sannan muka fita falo muka ci abinci. Da yamma Daddy ya dawo muka sha hira da murnar ganin juna, ko da dare ma dai hirar muka yi har sai da dare yayi sannan na musu sallama na wuce dakina. Washegari Anty Uwani tazo ta daukemu ni da Ramlatu muka tafi gidanta bayan ta sa mun dauki kayan sawar mu kala biyar, ban san me zamu yi ba na dai ji suna maganar Gyaran jiki ita da Mommy

ni kam ban maida hankali wajen sanin lallai sai na san me zamu yi ba.

Munyi nisa sosai kafin kukan da nake yi ya dauke, Anty Shafa ta miko min handkerchief na share fuska ta dashi, ta bude Jakarta ta ciro kayan kwalliya ta juyo da fuskata ta gyara min kwalliyar dana bata, na juya kaina ga window din motar na fuskanci waje zuciyata cike fal da tunanika iriiri. Karfe shida muna cikin Kano, kai tsaye unguwar Galadanchi aka wuce damu gidan su Abbu. Can muka tarda mutane na jiran isowar mu, dakin Hajiya Siyama Mahaifiyar su Abbu surika a wajena muka sauka, aka damka musu Amana ita da Dattijan da muka samu a dakin nata, daga nan kuma aka kaini dakin Hajiya Fati nan ma dai gaisuwa da bada amanar ne, bayan an gama aka dauke ni zuwa wajen mahaifin su, ya mun nasiha sosai mai shiga jiki tare da addu'o'i, ya bada abin Sallah, Carbi da Turare aka bani a matsayin tsarabar gidan aure daga nan muka koma cikin mota sai gidan Aurena a Sharada phase 2.

Gida ne flat mai kyau, dakuna uku manya duk an yi jere, akwai toilets a cikin kowane daki, kicin, sai toilet daya a cikin falo kila na baki ne.

Su Ni'imah sune en jagora har zuwa dakina, sai da muka shiga daki Anty Ameenah ta yaye min gyalen kaina duk da haka kin daga kaina in kallesu nayi, Su Anty Shafa daya dakin aka kaisu ni kuma su Ramlah suka zauna a tare dani, nan dai muka dauro alwala muka yi sallah, kasancewar lokacin Sallar Isha'i yayi yasa muka yi har Isha'i din. Muna gamawa aka dire mana plates din abinci, Macaroni jollop da lemuka, tsakanina da Allah cikina a cike yake shi yasa na dinga tsakurar abincin, Sadiya data fara nauyi haihuwa ko yau ko gobe duk da ita aka yi jigilar gaisuwa da ita ko nauyin cikinta bata ji, tace "Amaryar Babban Yaya ya dai baki cin abinci ko dai kazar amarcin kike jira?" na harareta kasa-kasa ganin gasu Anty Ameenah a gefenmu suna zaune, Ni'imah tace "ta fa riga da taci kazar amarcinta tun ranar da aka daura aure, muma ba har muka ci saura ba?" na kuwa kai mata mintsini a cinya tayi tsalle gefe guda tana sosa wajen, Ramlah tace "ku kyale yarinyar nan, tun

dazu take nuku-nuku kamar ba ita bace tace tana son auren, lokacin da yunwa zata taso mutum ya nemi abinci kuna ihu?" duk suka sa ihun, "Gida!!" tace "kun gani?!" ni kam sai na tashi na bar musu wajen kawai, na koma kan bencin dake gefen gado na zauna ina satar kallon kayan dakin, komi na ciki silver ne da black, gadon irin kananun Italian beds dinnan ne medium king size sai wardrobe data kusa cinye bangon dakin na gefen dama, dressing mirror, end of bed table, rug carpet, labulaye silver, sai sauran kananun tarkace da ba za a rasa ba amma kayan sunyi kyawu sosai, babu wata hayaniya irin ta kayan dakin zamanin nan.

Su Anty Ameenah suka mana sai da safe suka tafi suka barmu da su Anty Shafa da Ramlah, er hirarraki muka yi kafin Anty Shafa tace yakamata mu kwanta haka, ni na fara shiga toilet nan ma kayan ciki har ba a magana, katoton Jacuzzi tub, sinks, akan canters kuma mayuka ne tun daga na gyaran fata har na gashi ne da turaruka abin ba a cewa komi, na tari ruwan dumi na dan yi relaxing saboda warware gajiya kafin na dauro babban

towel na fito na danyi en shafe-shafe na fita, Ramlah ta shiga.

Wardrobe na bude da niyar duba kayan barci, baki na bude a tsorace ina kallon cikin wardrobe din. Layi daya atamfofi ne wasu ma ko dinga su ba ayi ba, sai daya na laces, daya nasu jallabiya ne da dai dogayen riguna, daya nasu materials, saitin kayan barci kuwa sai da suka kwashe biyu, na zaro riga daya na daga ta sama, it looks more like a lingerie yawancin kayan barcin duk ireiren su ne.

Na juya da rigar a hannuna ina nunawa Anty Shafa, “meye haka Anty?" tace “kayan barci mana" na kara kallon kayan, “you didn't mean... Ni zan saka su koh?" ta harareni, cikin gatse tace “a'ah ni zan sa..., ko kuma shi mijin naki!" na gumtse dariyata nace “amma Allah Anty kayan suna nuna jiki da yawa fa" tace “yi mun shiru malama, don suna nuna jiki sai me? Ina ce dai hakan ba Zunubi bane? Idan kin san ta yadda aka yi kayan nan suka zo nan ba zaki zauna kina ce mun wai suna nuna jiki ba, I specially went to Kamfanin da suke sarrafasu na bada oda, don haka tun kafin raina ya baci ki saka

kayan nan, besides kayan nan na arziki ne idan kika yi comparing dinsu da wasu kayan, koda yake ke da kanki zaki san amfanin su kizo kina nema na" sai na gumtse baki na juya na maida rigar na fara laluben kayan sa wa, da kyar na lalubo riga da wando suma dai sai a hankali, wandon 3q, rigar mai hannun vest gasu silk, lokacin Ramlah ta fito nan muka bi lafiyar gado. Anty Shafa kuma ta ajiye katifa a tsakar dakin muka yi light off muka kwanta, kamar jira yake, sakon Abbu ya shigo.

“Sleep??" nayi gaggawar tura mishi da, “about to.... How was your day?" ya turo “dama nasan ba zaki iya barci ba baby na, tun yau fa baki ji murya ta ba balle kiga text dina, nima ina kewar ki baby na nasan da kyar barci ya dauke ni yau, amma kar ki damu, na yau ne kawai..., daga gobe babu wanda zai sake shiga tsakaninmu da yardar Allah" lokacin dana karanta sai da er dariya ta kufce min, kai Abbu is full of self confidence. Na tura mishi “says wanda yake da mata., plus ni fa barcin ne kawai bai zo ba amma babu wanda nake kewa sai Mommy da Daddy na!" na tura ina dariyar tsokana,

nasan kila har gari ya waye yau muna musayar sakonni ne, sai kuma har barci ya dauke ni bai dawo da reply ba.
 Sai da muka tashi sallar Asabar naga amsar daya maido mintuna kadan da fara barci na, "zaki ce haka ai tunda har yanzu baki zo hannu ba, gobe war haka ki maimaita abinda kika fada yanzu please...." nayi murmushi kawai na maida wayar kasan filo na fada toilet. Muna gama Sallah muka koma wani barcin, sai karfe tara na safe muka tashi. Muka yi wanka muka kimtsa, an kawo mana abinci daga gidan su Abbu muka fita parlour muka karya. Falon madaidaici ne wanda ya dauki wasu rantsattsun beige couches guda biyu an jera su daya ta kalli gabas daya kuma ta kalli arewa, sai wasu Everette chairs navy blue guda biyu suna fuskantar couch daya, a tsakiya kuma an saka babban teburin gilashi kasan shi wasu woods ne suka tokare shi, a sama kuma an dora flower base mai kyau, sai lamp mai kama da bishiya, kasan parlor hardwood flooring aka yi, kai komi dai na falon ya fita very unique, muka hau kan dinning mai cin kujeru takwas muka karya.  Dakina muka koma Anty Shafa sai cafta take sauke min tana karawa duk da wasu

abubuwan duk tuni ne take yi mun. Karfe daya munyi sallar Azzuhur sai ga Abbu shi da abokan shi biyu, nayi sauri na dauko hijabi na dora akan kayana, falo muka fita muka gaisa dasu, ban yi gigin daga ido na kalli kowa ba. Ramlah ce tayi jigilar entertaining dinsu, ni kam suna fara cin abubuwan data kai musu nayi wuf na fada daki. Gefen gado na samu na zauna, ban jima ba sai ga Abbu shima ya shigo. Kai tsaye inda nake zaune shima yazo ya zauna a gefena, hannuwana duka biyun ya kamo da daya hannunshi, dayan kuma yayi amfani dashi wajen dago kafadata, ya wani rausayar da kai, "me nayi ne yau kuma Babyn? Babu gaisuwa, babu murmushi, babu kallo?" na sadda idanuna kasa tunda ya rike fuskar, duk yadda naso in daga baki in gaida shi kasawa nayi, wani irin nauyi da kunyar shi da ban taba ji ba naji sun dabaibaye ni, ya nisa, "bari in maida su AbdulHameed gida in kuma dauko direban da zai maida Anty gida sai in dawo gare ki gabadaya koh?" ya kai hannuna bakin shi yayi kissing as usual kafin ya fita.

Yana fita su Anty suka fara shirye-shiryen tafiya, nayi rau-rau da idanuna nan Anty ta samu abin fada, abin

mamaki kuma bayan kamar awa daya da taji direba yazo sai kuma ta hau sharar kwallah, nan na rungumeta ina kuka, Ramlah ma tana gefe tana matsar kwallah, Abbu da kanshi ya leko ya sanar da ita zuwan direban. Ta mike tana share hawayenta tare da rataya jakarta, ta kamo hannuna ta rike cikin nata, “to Nafeesah, sai watarana, Allah ya baku zaman lafiya da maigidanki da abokiyar zaman ki, hakurin nan dai da kowa yake gaya miki kiyi da biyayya shi zan kara jaddada miki, sai kinyi exercising hakuri sannan ne zaki ci ribar rayuwar aure duk da nasan ki da hakuri amma dole sai kin kara kinji? Allah ya miki Albarka" na gyada mata kai ina hawaye. Ta sa kafa ta fara tafiya Ramlatu ta bita a baya nima na bisu, a bakin falo Abbu ya dora min hijabin dana saka lokacin da abokan shi suka zo, muka karasa fita har shi. Ina tsaye har Anty Shafa ta shige mota Ramlah ma ta shiga different mota tunda ita gidan Anty Haleemah ta nufa. Direba ya tashi motar suka tafi muna daga musu hannu har maigadi ya maida gate ya rufe, wasu hawaye suka kara gangaro min a kumatu, shikenan an tafi an barni ni kadai. Abbu daya tsaya a bayana ya sakalo da

kanshi ta wuyana tare da zagaye ruwan cikina da hannuwanshi, duk da halin da nake ciki sai da naji wasu abubuwa na min yawo a jikina, a hankali yake magana, “m sorry Baby, In Shaa Allah ni zan maye miki gurbin su Daddy dinki kinji? Stop crying kinji? Yau ce rana ta farko fa da zamu rayu karkashin rufi daya a matsayin ma'aurata, rana ce mai matukar muhimmanci don haka babu kuka ok?" na gyada kaina a sanyaye, ya sake ni ya juyo dani ina fuskantar shi, hannu yasa ya goge hawayen fuska ta, ya kama hannu na yana min murmushin nan nasa mai kwantar min da hankali muka koma cikin falo. Muna shiga aka kira sallah, ya shiga dakina yayi alwala ya tafi masallaci ni kuma na tada kabbarar tawa a daki abina.

Bayan na gama sallar falo na koma na zauna ina kallace-kallace har Abbu ya dawo daga masallaci Maigadi ya biyo shi a baya da kuloli a hannunsa, na tashi na karbi kulolin na shiga kicin na fito na plates da cokula, Abbu yana kan dinning table a zaune naje ina wani sunke-sunken kai na zuba mishi abincin na tura gaban shi, nima na zuba

nawa naja kujera da take fuskantar shi na zauna. Tsam naga ya mike dauke da plate dinshi a hannu, na bishi da ido cike da mamakin abinda zai yi naga yaja kujerar gefena ya zauna, abincin plate dina ya juye a cikin nashi plate din, yace “daga yanzu we share one plate, spoon, and if possible har kujerar zama kin gane?" ni kam dai nawa gyada kai ne, jina nake kamar wata sabuwar halitta. Cikin sanyin jiki muka fara cin abincin, idan yaci sai in karbi cokalin shi nima inci haka har muka gama cin abincin na tattara kayan na kai kicin na wanke kafin na koma falon, yana zaune yana waya ya miko min hannu, a kunyace naje na zauna a gefenshi, yaci gaba da amsar wayar shi ni kuma naci gaba da kallona, ya gama wayar ya janyo hannuna cikin tafukan hannayen shi duka, kunshin da aka sake min yake shafawa da alamun yana son kunshi sosai, ya fara ja na da hirarraki duk don in samu in sake dashi amma ina, na kasa. Yau dai gabadayan shi ya koma min kamar wani bako, irin awkwardness dinnan da ake ji when you were stuck up with a total stranger a waje daya shi nake ji, bai takura akan lallai sai na saki jiki dashi ba.

Sai da aka kira sallah sannan muka tashi, yace min sai bayan sallar Isha zai dawo nace toh. Daki na shiga nayi Alwala na fito nayi sallah, akan abin sallar na zauna ina tilawa har aka Isha na tashi nayi na hada da Shafa'i da Wutiri.

Gefen gado na koma na zauna na dauko wayata, babu caji ma a ciki. Anty Shafa na kira na tambayeta ko ta sauka lafiya, nan muka gaisa da ita ta ba Mommy wayar muka gaisa kafin Anty Shafa ta sake amsar wayar, wata riga ta kwatanta min a cikin kayan barci na tace ita zan saka idan zan kwanta nace mata to, kafin muyi sallama ta kara jaddada min in saka rigar fa nace mata to dai. Bayan mun yi sallama da ita Ramlah na kira, ta daga da shakiyancin ta wai ina na baro angona nake danna mata kira da dare? Nan muka fara hira har Abbu ya dawo daga masallaci misalin karfe tara, na mata sai da safe na ajiye wayar ba tare dana kula da tsokanar da take jifana dashi ba.

Dangin fruits ne ya dawo dasu sai gasasshiyar kaza, na dauko plates da wuka na kawo, muka zauna muka ci duk da dai tsakura kawai nayi fruits dinne ma dai na ci sosai,

ya tsiyaya fresh milk mai sanyi a cikin cup ya miko min shima ya zubawa kanshi, na amsa na kafa kai na shanye ta ban bar ko digo ba. Ya kalleni "kin koshi?" na gyada kai, yayi hamdala shima ya karasa shanye nashi madarar. Na hada komi na kai kicin, na wanke na wankewa, sauran fruits da kazar kuma nasa a fruit. Ya leko kicin din ya tsaya a jikin kofa yana kallona, jin idanunshi a kaina yasa na juya, murmushi yayi yace "have you prayed?" na gyada kai, ya rausayar da kai gefe, "idan kin gama kije ki dauro alwala ki same ni a dakina" ya juya ya tafi ya bar ni ina zare idanu.

A sanyaye na gama shirya kayan na koma daki, wanka na fara yi na daura alwala ba shafa lotion mai kamshi na fito, cikin wardrobe na lalubo rigar da Anty Shafa tace in saka. Wata silk trim gown light purple wadda ta kai rabin cinyoyina, gabadaya saman rigar lace ne mai kama da net, na zura rigar ina karewa kaina kallo ta cikin mirror, gabadaya cinyoyina a waje suke kamar yadda ilahirin kirjina yake waje kai har ma cibiyata, ta yaya ma zan iya fita gaban Abbu a haka? Ni kaina kunyar kaina naji, nayi kamar in cire rigar sai na fasa, after dress na laluba

na dora, na dauki hijabi na saka na fesa turare a jikina tun daga na jiki har na kaya.

Kafewa nayi a tsakiyar daki ina tunanin ta yadda zan karasa dakin Abbu, inje in ce me? Ni ba wawiya bace, nayi karatu daidai bakin gwargwado na kuma san muhimmancin sallar dana yiwa alwala yanzu kamar yadda nasan abinda zai biyo bayan hakan. Gabana yayi wani irin bugu just for the mere thought of it, me zai faru yau kam? A dan tsorace na kalli kofa jin ana taba ta, Abbu ya shigo dakin amma ba gabadayan shi ba, ganina a tsaye ya dan yi frowning, "me kike yi? I've been waiting for you fa" nace "ai.. Ehh dama yanzu zan zo ai!" ya kara bude kofar alamun in wuce, ba musu na bi ta gefenshi na wuce gabana na dukan tara-tara, ina jin lokacin da ya kashe wutar dakin tare da rufo kofar, gabana yaci gaba da luguden daka da yake yi har kafafuna na rawa. Yayi gaba na bishi a baya kamar wadda take jan kafar ta. Dakin shi shima ba wasu tarkace bane, daga gado wanda zai iya kwasar mutane uku, sofa, bedside table da lamps, walk-in closet sai toilet. Dakin zagaye yake da rug carpet mai zane baki

da fari kamar jikin zebra. Ya shimfida mana abin sallah ya umarce ni da in bi bayan shi, Nafila ya fara jerawa sai da muka yi raka'ah takwas, ya fara jero mana addu'ah samun zaman lafiya mai dorewa da zuri'ah mai Albarka a rayuwar auren mu ina amsawa da ameen a cikin raina. Ya tashi ya nade abin sallar, ban yi yunkurin mikewa ba ina zaune a inda ya barni ina satar kallon shi, dakin kayan shi ya shiga, ba a jima ba ya fito sanye da pyjamas na Marks and Spencer masu taushi ash color, ya latsa wani abu mai kama da remote hasken dakin ya dauke ya fara kawo wani jan haske an jima kadan sai blue ya kawo. A hankali naga ya daga kafafun shi ya fara takowa inda nake zaune, duk taku daya sai bugun zuciyata ya karu. Yasa hannuwanshi biyu ya daga kafaduna tare da mikar dani tsaye, hijabin jikina ya cire ya ajiye akan abin sallar, ya kai hannu yana kokarin balle maballan doguwar rigar jikina, da sauri nasa hannu na rike, daya hannun ya saka ya rike min hannun ya cigaba da balle buttons din rigar, ina jin lokacin da rigar ta sulale daga kafaduna ta sauka akan tafin kafata, da

sauri na rufe idanu na don nasan ba zan taba iya hada idanu da Abbu ba.

Hancin shi ya kai cikin gashin kaina ya shaki kamshin, a hankali kanshi ya fara gangarowa har ya kawo wuyana ya fara wani shinshinata, “Masha Allah baby! I like this scent.... Really!" ya fada cikin wata irin murya da ban taba jin shi da ita ba, faduwar gabana ta karu, rawar jikina ta linka ta da, a hankali naji wani abu mai sanyi da lema yana tracing din ilahirin wuyana da samar kirjina, a rikice naji kafafuna sun fara sulalewa kasa yayin da gangar jikina ta bisu zamu zube gabadaya, ji nayi an daga ni sama cak an dora akan gado, ba bata lokaci ya biyo bayana ya dora leben shi akan fuskata ya fara bin ilahirin fuskata da ruwan kisses har da lasa kamar wata alewa har ya gangaro wuyana, ai gabadaya wuta dauke min tayi, na manta a duniyar da nake, na kasa tuna a inda nake, babu abinda nake fahimta da ganewa sai lebuna, harshe da hannuwan Abbu da suke yawo a gabadayan sassan jikina. Haka kawai naji hawaye suna zubo min wanda ban san dalilin su ba duk da dai nasan cewa hakan baya rasa nasaba da sabuwar

rayuwar da Abbu yake kokarin jefa ni ciki. Goshina ya hada da nashi yayin da hannun shi yake share min hawayen dake gangarawa suna shiga har cikin kunnuwana, “why baby??" ya rada min a kunne, tsikar jikina ta tashi a take rawar jikina ya karu, wasu hawayen suka kara zubo min, yace “nooo baby, don't cry please. Please kar ki hana ni mallakar ki Nafeesah, I really want to do this please??" ni wacece da zan hana shi abinda yake mallakinshi ne, ni wacece da zan hana shi samun farin cikin shi?? A hankali nayi nodding kaina, yace “thanks baby... I won't hurt you I promise, I'll be gentle In shaa Allah! I love you" hannu nasa na rungumo shi kawai ina hawaye, and that is the invitation he needed, ya hade bakina da nashi yana tsotsa exploringly kamar zai hadiye ni.

Ba a dauki lokaci mai tsayi ba dakin ya cike da sautin shesshekar kukana, tun ina daurewa tsananin azabar da nake ji har na saddakar na bude baki na fara kuka da magiya har ina kokarin ture shi daga kaina, abin yafi kafin tunani na duk da cewa bai kai ma rabin zafin da nake hangowa ba irin wanda naji ana bada labari, amma

azabar is still unbearable. Sai daya nutsu ne ya ankara da kukan da nake zubawa kamar wadda ake zarewa rai, ya fara jijjiga ni a hankali yana tafin bayana ba tare da yayi magana ba. Sai da numfashin shi ya dawo normal naji yayi magana, “I am sorry, did I hurt you?" a hankali na girgiza mishi kai, duk da akwai zafi amma nasan bai kai wanda za ace yaji min ciwo ba. Ya gyara min kwanciya a jikin shi tare da janyo bargo ya rufe mu, “ok, yi barci baby" muryar shi was soft, very soothing. Na lumshe idanuna ba bata lokaci barci yayi awon gaba dani. Cikin barci naji lokacin daya tashi ya shige toilet, na kara kudundunewa a cikin bargo.

Sai da asubahi sannan na farka shima wasu tausasan hannuwa ne naji suna shafa min kumatu, na bude idanuna inda naci karo da fuskar smiling Abbu, “Hii sleeping cutie pie, a tashi koh?" na dan motsa, slight pain din da naji ya ratsa ni yasa na maida kaina cikin bargo a sukwane, sai lokacin kwalwata ta tariyo min daren jiya. Yayi chuckling kafin naji an daga ni sama daga ni har bargon na fara wutsilniya amma bai dire ni ba sai cikin bath tub wanda aka tara ruwa mai dumi a

ciki. Ya zare bargon jikina ya ajiye akan dressing table, ya dawo ya fara kokarin min wanka. Duk yadda naso ya fita ya kyaleni sai hakura nayi, ya taimaka min nayi wanka tare da dauro alwala, ya dauko towel mai fadi ya nade ni a ciki ya kara ciccibana muka koma daki. Rigar jiya ya dauko ya saka min kaina yana kasa na kasa hada idanu dashi duk da tsokanata da yake yi, nan ya tafi masallaci ya barni na lallaba na hau kan abin sallah na tada kabbara. Ina gama sallah na koma kan gado na sake nadewa saboda barci, ina jin sanda Abbu ya dawo ya hau kan gadon ya nado ni cikin jikinsa, na kuwa kara shigar da kaina cikin faffadan kirjin sa na lafe.
~Hahhh, If you were ask to say One Word for this night, what will you name it?
~Wa zai iya shiga kwalwar Abbu ya fada mana abinda yake cikin zuciya da Ruhin shi??

Hasken rana daya haske min idanu ne ya katse min daddadan barci mai cike da natsuwa da nake yi. Na bude idanu na a hankali na sauke su akan agogo, karfe tara da kwata. Na maida dubana zuwa ga curtains din dakin

wadanda aka daga sama, hakan ya ba haske da zafin rana damar lekowa ta cikin manyan windows din dakin. Abbu baya kan gadon kuma nasan da kyar idan yana toilet, ko ina ya shiga? Na tashi a hankali na nufi tagar da niyar rufewa, wani dan guntun murmushi ya subuce min lokacin dana yi tozali da terrace garden a bayan dakin, shuke-shuken roses da different flowers and plants ne wadanda suka kawata wajen matuka, ga wooden couch nan mai raga-raga kamar anyi saka a tsakiyar wajen inda zaka zauna ka huta, naja numfashi na shaki kamshin furannin har ina lumshe ido, sai dana gaji da tsayuwa sannan na saki curtains din, komawa nayi na yaye zanin gadon na je dakina na dauko wani na dawo na shimfida shi kuma dayan na jefa a cikin washing machine na shanya shi a nan cikin toilet din wajem da aka tanada musamman for laundry. Kayana na tarkata na wuce dakina, na jiyo motsi a kicin amma ban leka ba. Ruwa na tara mai dumi na shiga na kara gasa jikina don har lokacin ina jin zafin wajen, na daura babban towel a jikina na fito na zauna a gaban dressing mirror nayi goge-goge da shafeshafe, kwalliyata nayi

kamar yadda ya zame min Al'ada, na fesa turaruka masu kamshi mai kwantar da hankali, jiya naga Anty Shafa tana jera su a kan dresser din nasan ita ta sai min tunda Arabian perfumes ne ita kuwa yawanci irin turarukan da take amfani dasu kenan.
Kofar dakin aka turo aka shigo, cikin sakan daya na juya na kalli wanda ya shigo na maida kaina kasa na dukunkune a tsakanin cinyoyi na. Ya tako a hankali har ya iso gare ni, kaina ya dago nufin shi in kalle shi amma na jimke idanuna, murmushi yayi mai sauti, "yau kuma a haka zamu gaisa Baby na?" nayi shiru ina kokarin janye fuskata amma yaki bani damar hakan sai ma mikar dani tsaye da yayi ya kalmashe ni a cikin jikinsa, ya dora habar shi a kan gashin kaina yace "babu gaisuwa ne yau?" kaina na kan kirjin shi na girgiza alamun a'ah, kaina ya sake dagowa nayi saurin kara rufe idanuna, peck naji ya bani a kunci da lebena kafin ya sake ni gaba daya, "it's okay, na fahimta. Kunya ta ake ji ko?Yanzu zan fita a dakin, yi sauri ki shirya kizo mu yi break fast, yau da kaina na tattare hannun riga ta na hada miki break fast" idanuna suka yi walai cikin rashin sanin nayi

hakan da tsananin mamaki, dariya yayi tare da dan jan hancina, “thank goodness I've got to see this beautiful eyes, yes ni na hada break fast now yi sauri kizo muci kafin ya huce, ko In zo in shirya ki da kaina?" wayyo nayi saurin girgiza kaina, yayi er dariya ya fita. Wardrobe na bude na ciro wani tausassan yadi ruwan madara riga ne da siket na saka, na lalubi silifas mai taushi na zura tare da yafa dankwalin a kaina da yake babba ne na fita.

Yana zaune akan kujera yana duba waya ina fitowa ya tashi tsaye tare da wucewa wajen dinning nima na bi bayan shi, kujera yaja min na zauna a darare shima yaja ta kusa dani ya zauna. Kwallin kula daya ce a wajen sai flask na ruwan zafi da cups da kayan shayi. Ya hada mana tea tare da daukar plate ya bude kular ya juye abundance ke ciki, nayi shagaraa da baki ina kokarin tantance abinda yake gabana. What did you expect? Konanniyar wainar kwai ce tayi bakikkirin da ita, yasa fork ya yanki kadan ya kai bakinshi kamar mai testing, yace “kar ki samu da bakin da tayi pa, bata yi komi ba" a sanyaye na dauki fork nima na kwaikwayi yadda yayi,

abu na farko daya fara ratsa min harshe shine dan banzan gishiri sai kuma dacin konewar da tayi ya biyo baya, ganin yana kallona yasa na takura tun karfina na hadiye kwan, take zuciyata ta tashi, ya daga min gira, "ya??" na dage tun karfina na kakaro yaken tare da mishi alamun good, yayi murmushi. Wata na sake cirowa na kai baki, wannan karon na jima a bakina kafin na iya hadiyeta. Na ja kofin shayin na fara sipping, gani ba gwanar shan shayi da madara bace. Shi kanshi daya kai loma ta biyu gani nayi ya dakata yana kallona, "kamar gishiri yayi yawa koh?" nace umh. Ya kara kai ta uku bakinshi na bishi da kallo tsigar jikina har tashi tayi, ba shiri ya furzar da ita ya lalubi kofin tea ya kora dashi. Kallona yayi yace "sorry baby, ko zaki zan sama mana wani mu ci? Da alamu na manta yadda ake girki ko don na jima ban yi ba?" kamar jira nake, na tashi na hade kan kayan na nufi kicin. Store dinmu shakare yake da kayan masarufi wanda nasan kila zai iya daukarmu shekara kafin mu ci rabin kayan, murmushi kawai nayi tare da girgiza kai, Daddy!.

Cikin mintuna talatin na gama soya chips da plaintain, nayi vegetables sauce na dauka na kai mana muka yi break. Na tashi na hade kayan waje guda Abbu ya biyo ni da wasu. Na ajiye kayan tare da juyawa, da sauri Abbu ya riko hannuna, ban kalleshi ba na sadda kaina kasa, yace “are you ok Nafeesah?" na gyada mishi kai a hankali, yace “please Ki daina jin kunya na haka Baby, kin riga da kin zama ni kamar yadda na zama ke. I need you to be free, frank and comfortable idan muna tare, bana jin dadin hakan da kike yi. I know it'll be awkward, but still kiyi trying mana kinji?" na gyada mishi kai, yace “noo, amsa min da bakinki" na daga bakin da kyar nace “toh" ya kai bakinshi kan nawa ya dan tsotsi leben nawa kafin ya dago yana murmushi, “datz you baby...., zan fita yanzu me zan kawo miki?" nace “babu komi" yace “k, ki kunna kallo ko ki shiga dakina a study room akwai kayan exercise ko kuma just do anything so that you won't be bored don zan dan jima, sai na dawo" nace “a dawo lafiya, Allah ya kiyaye hanya" yace “Ameen Nafeesah ta" ya juya ya fita bayan ya bani peck a goshi. Ni kuma na fara wanke kayan da muka karya dasu.

Yinin ranar a kiraye-kirayen waya da chatting nayi shi, babu wanda ya leko gidan kamar yadda ban ga kiran kowa a waya na ba sai na Abbu yana tambayana me nake yi? Lokacin ina study room dinshi bayan na gama gyaran dakinshi da nawa dama gidan gabadaya, sai kuwa Anty Shafa data kira bayan rana ta daga sosai tana sanar dani a ranar da dare zata bi jirgi ta koma gida, na mata godiya game da Alkhairanta a gare mu, muka yi sallama da ita tana jaddada min in fa dinga shiga ruwan zafi har naji kunya ta kama ni. Daga nan naci gaba da gudanar da harkoki na. Abbu bai shigo gidan ba sai bayan la'asar, sai lokacin nayi lunch ko ince muka yi. Ba laifi na dan sake dashi ranar, ba wani awkwardness da strange feelings irin na jiya sai er kunya wadda itama kafin dare yayi na neme ta na rasa, not that I care don ni fa duk abinda zai saka Abbu na cikin farin ciki shi nake aiming yayin da yace shi fa kunyar nan ta dame shi don haka na jefa ta cikin kwandon shara.

Ranar ma a dakin shi na tarda shi bisa umarnin shi bayan nayi wanka na wadata jikina da turare, ya mana light off

tare da jana cikin jikinsa ya fara lalubata at first shiru yayi, but lokacin da naji hannunsa a kan kirjina and things started becoming steamy, sai nayi sauri na janye bakina daga cikin nashi, jikina yana er rawa saboda tunano wahalar daren jiya, a hankali nace “Abbu ban warke ba fa!" muryar shi was hoarse and low at the same time yace “I know... Babu abinda zan miki baby, just a good night kiss" sai daya gama samun natsuwar shi ta hanyar ‘good night kiss' kamar yadda yace sannan yayi cuddling dina a cikin jikinshi kanshi a tsakiyar kirjina barci mai dadi ya dauke mu.

Ranar kam ya daga min kafa, wadda ta biyo bayanta kuwa yaki daga kafar despite magiyata da kukan shagwaba wadanda daga baya na fahimci cewar su suka kara karfafa mishi gwiwa ma, ranar data biyo baya ma haka and the day after that.... Soon, na zama gogayyiya kuma expert a cikin sabuwar rayuwar da Abbu ya bude min kofar ta. Mun kara karfafa Rayuwar aurenmu ta hanyar girmama Juna da shimfida kyakkyawa kuma tsaftacciyar rayuwar aure, kulawa da junanmu da tausayawa. A cikin en kwanakin kam duk wanda ya

ganmu yaga wadanda suke kan ganiyar cin amarcinsu, na dan rame kadan amma still na kara yin fresh saboda kwanciyar hankalin dana samu. Abbuna kuwa ya kara kiba, jikinshi ya kara yin fresh ko ba komi nasan dadadan girke-girken da nake mishi kadai sun isa sa shi yayi kiba.

A kwana na biyar da tarewa ta, har ranar babu wanda ya leko gidanmu, Abbu ma bai cika fita sosai ba. Ina zaune da safiyar ranar a falo sanye da wasu Pakistan riga da wandon su, na gyara gashina ya kwanto har gadon bayana yana ta sheki da kamshi. Gate naji an bude, nayi murmushi nasan Abbu ne ya dawo daga fitar da yayi. Na kara gyara zamana ina fuskantar mota, yana shigowa na tare shi da murmushi. A bakin kofar ya tsaya shima yana murmushin, hannu ya mika min alamun inje, babu musu na tashi na fara tafiya cikin jan hankali ina jujjuya jikina kamar wadda take rawa, kasa daurewa yayi in karasa ya taka da sauri ya taro ni tare da rungume ni. Sai daya gama welcome kiss dinshi and stuffs sannan ya umarce ni da in dauko hijabi zai nuna min abu a waje, na shiga daki na saka na fita na same

shi yana jirana, hannuna yaja muka fita compound din gidan, dalla-dallan motoci biyu Land Rover Discovery fara da Vibe ja daga ganin su sabbi ne saboda yadda suke ta sheki a cikin soft hasken ranar ta alhamis. Ya miko min keys guda biyu, cike da tsananin mamaki nake kallon su kafin na maida kallona ga motocin, da kyar na iya kakaro "wadannan keys din fa Abbu?" yayi murmushi much like a grinning, "for you baby!" na zaro idanu na cikin mamaki, "duka?" ya zagaya ta bayana tare da rungume ni, "wannan..." ya nuna min jar vibe din, "is from me.... Wannan kuma..." ya nuna farar Discovery din, "is from your Daddy" nace "Dad kuma?" ya daga kafadar shi, "yanzu aka kawo ta daga can Kaduna, sai dana fada mishi cewa na sai miki amma yace shima tunda ya siya sai ki hada duka biyun kiyi amfani dasu" Daddy, my Dad! He's really the best. Ban fada mishi ba amma already ya riga yasan da irin motar da nake muradi, nayi tsalle na juya tare da rataye hannayena a wuyan Abbu ina dariyar dake nuna tsananin murna da godiyar da nake mishi duk da bakina bai furta ba. Ya miko min kumatun shi ba bata lokaci na bashi peck a

kunatun, peck din daya koma deep mouth to mouth French kiss in a wink, in another wink na tsinci kaina a tsakiyar gadon Abbu, kayan sawa suna yin koina a cikin dakin....

Later da yamma na kira Daddy na mishi godiyar Mota, “Haba Uwata bari mana kar ki bata min rai? Meye abin godiya dan uba yayi wa diyar sa abinda yake responsibility dinshi ne? Beside saboda wa nake neman kudin idan ba ke ba uwata? All I wish for you is to be happy kin gane? Sannan zan tura miki da kudin sadakin ki ta account gobe in shaa Allah" nayi saurin cewa “Daddy ka bar su a wajenka pls" yace “aah, ai hakkin ki ne Nafeesah kuma ma ni bana son kudin ki" nace “to a ba Mommy" yace “itama bata so" ba shiri na saki dariya, nan muka yi sallama dashi.
Washegari kuwa ya turo min da kudin, dubu dari biyu bayan dubu dari ne sadakin, na kira ina tambayar shi dalili sai cewa yayi ai sabida in dinga ba baki da kuma sauran kashe-kashe saboda baya son in cika tambayar mijina, sai kawai nayi murmushi tare da mishi godiya.

Ina zaune Abbu ya fito daga dakinshi yana gyara karin hularshi cikin shirin tafiya masallacin juma'ah. Na tashi na taya shi kafa hular tare da raka shi har bakin kofa, yace “In kawo miki su Hafsy ne su miki yini?" da sauri kuma cike da doki nace “ehh, please Abbu" yayi dan murmushi tare da juyawa ya tafi ina mishi Allah ya kiyaye hanya. Yana tafiya na fada kicin na hau shirya musu cookies da kayan motsa baki ga kuma abinci, ina kicin din ma suka shigo gidan su da Abbu da ihun su suna kiran sunana, da sauri na fita waje nan suka kwashi ihu suka rugo suka rungume ni, nima na rungume su ina murnar ganinsu, sai da muka nutsa sannan na dago kai ina kallon Abdullahi dake gefen Abbu a tsaye, na mishi dan murmushi ba tare dana damu da yadda bai yi joining dinsu ba. Daga baya dai muka tashi muka koma cikin falo, na dauko musu duk abubuwan dana shirya musu nan fa hira ta barke, bayan mun ci abinci Abbu ya tafi daki ya dan kwanta kafin a kira la'asar ya barmu muna ta hirarrakin mu, har baya muka fita muka danyi wasanni kafin muka dawo falon. Yini guda suka mana sai bayan magriba Abbu ya maida su gida, don Hafsy ma

da kafewa tayi anan zata kwana sai da kyar Abbu ya lallasota ta hakura suka tafi. Na hada su da tarkacen sweets, chocolates da tarkace dai iri-iri suka tafi.

Ban sani ba shagala ce ko kuwa mantuwa? Zancen cewa angwaye kwanaki bakwai suke yi a dakin amaren su su koma na uwargida, kai in fact na manta cewa ma ina da abokiyar zama kwata-kwata a lokacin, na manta cewa bani kadai bace wadda take da Abbu, na manta cewa Abbu yana da wasu iyalan daya kamata ya kula dasu. Muna cikin cin abinci yake fada min cewa washegari idan zai je gidan Mubeenah zai dauko cousin dinsu Zaynab diyar wata kanwar mahaifiyar su zata dinga zuwa tana taya ni kwana. Na maida spoon cikin plate dina na ajiye ina kallonshi cikin alamun tambaya, and that was when it downed on me, ranar na cika sati daya cif da tarewa which means washegari zai fita daga dakina. Jikina yayi wani irin sanyi har yana hadawa da rawa na dai daure na cije na gyada mishi kai naci gaba da tura abincin da taste dinshi ya bace a bakina.

Duk yadda naso na daure in nuna mishi hakan bai dame ni ba kasawa nayi, sai daya fahimci sanyin da jikina yayi. Ya riko hannuna ya zaunar dani akan cinyar shi tare da dago fuskata, na daga idanuna da suka fara cika da ruwa na kalleshi, yace “come on mana baby kar ki bayar dani, meye kwanaki biyu kadai? Besides, zan dinga zuwa kullum ina ganinki kinji? Kuma zamu kasance a waya a koda yaushe don haka ki daina bata ranki, ni naki ne ok? Oya, give me that gorgeous smile of yours baby" na kuwa saki murmushin tare da dora kaina akan kirjin shi.

Washegari da safe ya tattara ya tafi bayan ya jira Zainab tazo, yarinyar tana da kirki ga fara'ah, na dan girme mata da shekaru tunda shekarunta ashirin. Na raka Abbu har bakin mota duk da sallamar da muka gama yi a daki, yaso ya kaini gado a lokacin nace a'ah, ba zan shiga hakkin abokiyar zamana ba don nima bana so a shiga nawa hakkin. Haka ya tafi ina daga mishi hannu har sai daya fita daga gidan maigadi ya maida gate ya rufe kafin na juya cikin gida cike da kewar Abbu, zama nayi muka dan yi hira da Zaynab kafin na shige dakina

na kwanta don jiya Abbu bai barmu mun yi barcin kirki ba.

☆☆☆☆☆

“Wannan yace a cikin abinci kamar miya ko fate zaki zuba mishi yaci, manta kowa kenan. Ina mai tabbatar miki da cewa idan har yaci wannan maganin to wallahi sai dai uwarshi ta sake haihuwar wani, kin dai ga yadda mijin Umaimah (er autar su) yake mata, uwar shi ma yanzu sai Umaimah taso yake ganinta balantana wata banzar bazara wai ita kishiya, kema to haka zaki mallakeshi..., wannan kuma...." Saddiqa ta fito da wani ruwa a cikin kwalba tana nunawa Mubeenah, “...a cikin ruwan wankan shi zaki zuba mishi, shi kuma zai sanya mishi matsanancin son ki ne, ya zama babu wata ‘ya mace a cikin idanuwan shi sai ke ina fada miki, boka Saddar ya bani tabbacin a ranar zai dankarawa ita waccar banzar kishiyar taki saki uku, shi da kara aure kuma sai a lahira. Don haka ki kula sosai, ki bi komi a hankali yadda ya dace don hakan mu ya cimma ruwa kin

gane?" kamar wata kadangaruwa ta gyada kai, “yauwa, ina turaren dana kawo miki last week nace kiyi tsuguno dashi?" Mubeenah ta gyada kafada, “turare? Na ma manta inda na jefa shi" Saddiqa ta maka mata harara, “wai ke banzar wani gari ce? Duk inda yake ki lalubo shi kiyi tsuguno dashi yau ba gobe ba, yaushe girkin ki zai fita?" tace “gobe da safe" tace “bamu da lokacin batawa kenan, yau yakamata yaci maganin, yayi wanka kuma ya kusance ki kina jina? Abubuwan nan da muke yi is all for u Mubeenah, kin dai san kaf danginmu babu mai kishiya sai waccan banzar yarinyar (Shakira) don kishiyar Umaimah hoto ce, don haka kema ba zaki biyo sahu ba kin gane??" Mubeenah tace “ehh".

Tayi murmushi, “yauwa., kudin aiki dubu dari da hamsin tashi maza ki dauko min" Mubeenah ta zaro ido, “dari da hamsin?" ta harareta, “to meye dari da hamsin matukar an samu biyan bukata?" Mubeenah ta gyada kai, “hakane kam. Sai dae babu kudi a hannuna sai dai idan Ibrahim ya dawo sai in amsa a wajen shi" Saddiqa ta yago hakura, “to babu damuwa, amma to dari biyu zaki

tura min tunda dai nasan kema in kika tashi ba a dari biyun zaki tsaya ba" suka kwashe da dariya.
Nan taci gaba da kitsawa Mubeenah abubuwa har yamma ta gabato sannan ta mata sallama ta tafi bayan ta kwashi manyan atamfofi biyu da lesuna cikin kayan da aka kaiwa Mubeenah na fadar kishiya bayan ta gama kwashe musu albarka, ji fa!. Mubeenah ta dawo daga rakiyar ta ta tsaya ta leka dakin Abbu, tun jiya daya dawo daga gidan Nafeesah ya leka ya gaya mata ya dawo tare da fada mata ya raba musu girki kwanaki bibbiyu bata sake ganin shi ba. Yanzu ma baya nan gashi akwai maganganu da take so suyi.

Dakinta ta koma, magungunan da Saddiqa ta kai mata suna zube akan gado, ta zauna a gefen gado tare da kura musu idanu kamar wadda take muhawara, ta saki ajiyar numfashi tare da tashi tsam ta dauki magungunan. Toilet ta shiga ta zazzage su a cikin masai tare da yin flushing, dama turaren data kai mata Harira ta ba ta jefa shi cikin kwatami. Daya daga cikin manyan abubuwa da Mubeenah bata so kuma bata ma yarda

dasu ba shine bin malamai da bokaye, tana mamakin yadda mata suke yarda da karerayi da soki-burutsun bokaye da malamai, a ganinta in kura na maganin zawo to tayi wa kanta mana?? Shi yasa tasu ta matukar zuwa daya da Shakira kanwar su, sam bata cikin harkar bin malaman da sauran en uwansu suke yi, ta kan ce ita tafi ganewa tayi yaki akan abu ta yadda idan ta mallakeshi zata yi alfahari da cewa saida ta share zufa ta sha wahala kafin ta same shi ba wai a ruwan sanyi ta hanyar bokaye da yan tsibbu ba, kuma gaskiyarta.

Tunda gari ya waye take leke-leke da zarya daga falo zuwa dakinta. Ta kula kwata-kwata ya daina zama a cikin gidan, tana mamakin inda yake zuwa cikin kwanaki biyun daya mata. Tana nan zaune a daki taji tashin muryoyin su dasu Qaseem wadanda suke hutun makaranta ranar, Sai data ji shiru alamun ya shiga dakinshi sannan ta tashi tsam!.

"ok baby sai na iso, kar ki manta anjima da yamma dai zamu fita in fara koya miki tuki" na danyi tsalle daga zaune din da nake, "yeyh! Abbu na, sai kazo. Please ka

taho da wuri fa!" yayi er dariya, “missing me that much??" dariya kawai nayi na kashe wayar. Shima dan murmushi yayi ya ajiye wayar yaci gaba da shirya takardu a cikin brief case din shi.

‘Baram!! Karan sautin turo kofar dakin nashi kenan kamar tashin duniya. Tun kafin ya juya yasan ko waye ya shigo, haka take shigowa dakin babu knocking balle sallama, kofar dakin ma haka take turo ta, duk ranar data shigo a hankali to ranar nema take a wajen shi.

Bata yi magana ba ta coge a bakin kofa, shi kuwa yaki daga kai ya kalleta yaci gaba da abinda yake yi har ya gama ya rufe brief case din. Wardrobe ya bude ya fara ciro kaya, ta kankance idanu cike da masifa ganin yadda yake abubuwan shi kamar bai san da Allah yayi ruwan tsirarta a cikin dakin ba.

“Ibrahim! Ina so muyi magana da kai!" ta fadi kanta tsaye cikin izza, ya juya a hankali tare da kallonta. Wani malulun bakin ciki da bacin rai suka kawo mishi wuya, wasu pyjamas ne a jikinta daga ganinsu sun dauki lokuta ba a wanke ba, ta kawo wata hular beanie ta maka a kanta fara ce amma tayi bakikkirin ta dafe alamun ta

kwana biyu, gashin kanta da yayi cukus-cukus a cikin hular ya maida ta kamar irin sababbin kamun nan. Ya hade fuska sosai wadda tasa ta shiga hankalinta ba shiri amma hakan bai hanata yin dibar albarkar data kawo ta ba. "Ibrahim mai kake nufi da nine, an kawo amarya ban ga kalarta ba, ka kama ka killace ta a waje guda saboda ita er goal ce, er nasiha ta hadin kai da naji mazaje na hada matansu waje guda su musu kai baka yi hakan ba, ka dawo daga gidanta kaxo nawa amma har ka gama kwanakin ka amma sau daya na saka ka a cikin idanuna, anya Ibrahim baka dauko hanyar da amaryar ka zata raina ni ba kuwa??" ya jingina da jikin wardrobe din yana watsa mata kallon uku-taro, sai data dire aya sannan ya ajiye numfashi, "killace amarya kamar yadda kika ce nayi sabida ta kai matsayin a killace ta dinne, Nafeesah ba er gwal bace er diamond ce Mubeenah. Kawo amarya gidanki damka amana ni na hana saboda ban ga dalili ba, ke kanki ya kike kula da taki rayuwar balle har ki kula da rayuwar er wasu? Maganar rashin gani na da baki yi ina ji kin manta ne, dama can muna daukar satika ma bamu ga juna ba alhalin muna gida daya yanzun ma

ina ga ai bata canza zane ba koh?" tayi tsuru tana zare idanu, maganar daya fada haka take, ita kanta bata san dalilin sako maganar ba, kawai maganar has been eating her brain ne dole ta fade ta ko ta samu sawaba.

Tayi gyaran murya tare da cewa “whatever! Amma kasan dai saboda Allah baka kyauta ba, kuma naji ance ka sai mata manyan motoci har guda biyu bayan ni ka bar ni da tsohuwa ina fama, tun kafin tafiya tayi nisa zaka fara shimfida rashin adalcin da ake cewa dama a jinin ku maza yake?" yayi murmushi cike da takaici, dama yasan duk inda zata je ta dawo dai maganar kenan. Ya daga kafada, “mota yeah, ni na sai mata daya Daddyn ta ya sai mata daya, ina ce kema lokacin da aka kawo ki an sai miki mota?" “karya ne!" ta fadi cikin hargowa, “karya kake yi kai ka sai mata, motar da kake fada ai Mahaifinka ne ya sai min da kudinshi ba naka ba mai ya hana kai ka saya min da kudin ka ko kuma yanzu daka sai mata nima ka sai min idan ba rashin adalci ba??" Ranshi ya baci sosai, ya sha daukar fiye da haka daga wajen Mubeenah, ya sha jin munanan kalmomi daga gareta duk yana shanyewa amma yau baya jin zai

iya shanyewa. Yana da hakuri sosai, sai dai duk ranar da aka kai shi bango akwai matsala. Tun daga tsawar daya daka mata Mubeenah tasan cewa ranar ta tsallake layin hakurin Abbu. Idanunshi sun juye saboda bacin rai, “enough Mubeenah! Ya ishe ki, ya ishe ni haka nan. Mota bani na sai mata duka biyu ba amma da ace idan nayi hakan Nafeesah zata karba happily da wallahi sai na sai mata fiye da mota biyu. Kin san saboda me? Saboda Ina Son Ta!! Saboda tana kula da farin cikina, saboda ita kadai nake kallo in san cewa yes! Ina da mata, in san cewa akwai wani da zan ba umarni kai tsaye yayi, akwai wadda bata zartar da komi sai da yawuna, akwai wadda zan bugi kirji ince Matata ce in kuma nuna ta a koina cikin duniyar nan ba tare da fargabar zata muzanta ni ba. Saboda ita kadai ce take bani hakkina ba tare da na biya ta ko sisi ba, saboda itace matar da nake sa ran zata haifa min yara ta kuma shayar dasu ba tare dana biya ta kudin shayarwa ba!! Saboda... Nafeesah itace komi nawa!! Zaki ga laifina idan na sayi jirgin sama na damkawa wannan matar kuwa?".

Mubeenah tayi shiru kanta a kasa, tunda take dashi bai taba mata ihu irin na ranar ba, bai taba daga murya kamar haka ba, duk abubuwan daya fada ta aikata har da ma wadanda bai fada ba duk tayi kuma sun faru, kalma daya data doke ta... “Kana Son ta?? Ni fa?! That means baka so na kenan?" without second thought ya gyada mata kai, “kwarai Mubeenah!Ni dake duk mun san cewa zaman hakuri da zaman ‘ya‘yanmu muke yi, amma zancen ‘so' kin san cewa babu shi a tsakaninmu" ta fara girgiza kai, bai jira mai zata sake ce mishi ba ya warci brief case dinshi a fusace ya ratsa ta gefenta zai fita, kofar dakin ma ko albarkacin ta rufe ta bata samu ba, tsoron shi daya Allah yasa cikin yaran babu wanda yayi over hearing din conversation dinsu yasan may be ya saka confusion a cikin kansu. Ranshi ya kara baci da wannan tunanin, daga bayan shi ya juyo muryarta a kausashe “Nafeesah!...." tun ma kafin ta gama fadin abinda tayi niyya ya juyo a fusace, “don't you ever dare drag her into this, ba irinki bace ita saboda haka ke kici gaba da laluben duniya ki barta taci gaba da laluben lahirar ta!" ya juya a fusace ya bar gidan zuciyar shi na

azalzalarshi cike da bacin rai ko sallama bai wa yaran nashi ba da suke dakinsu suna kallo.  Mubeenah ta bishi da kallo cikin bacin rai na maganganun daya yaba mata yanxu, fargaba da tsoron anya bata bari kwabarta tayi ruwa ba kuwa? Dana sanin ina ma tayiamfani da magungunan da Saddiqa ta kawo mata???

Muna gama waya dashi falo na koma ina jiran karasowar shi. Ina cikin zaman jiran ne Zaynab ta fito daga dakin dana ware mata a sukwane tana ihu, “Anti Nafeesah.... Anty Sadiya ta haihu yanzu!!" nayi ihun nima tare da direwa cikin murna, sai da muka gama iface-ifacen na tambayeta abinda ta haifa tace Mace. Ba bata lokaci ta shirya ta tafi ganin baby. Na zauna ina jiran dawowar Abbu impatiently ina jin kamar inyi fuffuke inje inda suke. Ina dakina ina canza kaya daga shigar da nayi ta wani mini daya tsaya min a gwiwa da half vest mai hannu daya ta taryar Abbu zuwa riga da zani na atamfa, ban san ya dawo gidan ba sai dana leka waje naga motar shi a fake sannan. Abin ya bani mamaki, nayi tunanin

zai shigo dakina direct idan bana falon kamar yadda yake yi, ban kawo komi a raina ba na nufin dakin da saurina cike da doki. Na tura kofar ko sallama doki bai bani damar yi ba na fara zuba mishi bayanai, “Abbu yanxu Sadiya ta haihu, kazo ka kaini in ga baby ka ji??" kwance yake yayi rub da ciki ya tura kan shi cikin filo, na zauna a gefen gadon ina dan jijjiga shi alamun ya tashi, “Abbu.... Abbu kaji?" nan ma shiru babu magana, ban sani ba common sense ne ya dauke min ko kuwa? Ban yi tunanin ina takura mishi ba ko barci yake yi naci gaba da jijjiga shi, “Abbu kazo ka kaini in ga baby kaji? Abbu??" Juyowa yayi a fusace, cikin muryar dake hauhawa da bacin rai yace “Oh God Nafeesah!! Will you please justshut up and leave me alone??" jikina yayi sanyi ganin yadda fuskar shi take cike da bacin rai, “amma Abbu.." na fara magana in protest, “leave me alone!!" ya fada cikin karaji, sai kuma naga ya dafe kanshi da sauri, ya lumshe idanunshi na en sakanni kafin ya bude su, “please!!" ya fadi cikin sanyin murya wannan karon. Jiki na rawa na tashi na fita daga dakin ina tambayar kaina me ya hau kan shi??

Kujera na laluba na zauna cikin tsananin sanyin jiki, ban iya daurewa kwallar data taran min ba sai data gangaro kan kumatuna, gabadaya sai na dora laifin fushin Abbu a kaina. Watakila ni na dame shi da hayaniya har ranshi ya baci, kila barci yake yi na tashe shi da hayaniya kun san yadda mutane kan zama moody idan sun tashi daga barci balle shi da naje ina jijjigawa abinda Anty Shafa tace mata basa tashin mazajen su daga barci ta wannan hanyar. Ko kuma yana bukatar kadaici ne ni kuma ban kula da hakan ba? Idan haka ne kuwa ai laifi na ne. Tashi na sake yi na koma dakin, lekawa nayi kamar munafuka wannan karon yayi rigingine, na shiga dakin a hankali tare da maida kofar na rufe, barci yake yi. A hankali na dauki bargo na rufa mishi, na juya kenan naji an riko hannuna na juya da sauri. Ya bude idanunshi da suka shige ciki har sun canza kala ya kalleni dasu, take naji wani irin bacin rai na shige ni. Na samu kaina da tuhumar kaina da responsibility na bacin rai da yake ciki, a hankali nace mishi “kayi hakuri Abbu!" janyo ni yayi na fada kan gadon tare da jana jikinshi ya rungume ni, ina jin yadda zuciyar shi take bugawa da sauri, yace

“noo, am sorry! I shouted at you bayan baki yi mun laifin komi ba" na kwantar da kaina akan kirjinshi ina shafa saitin zuciyar shi da hannuna, “Allah ya huci zuciyar ka Abbu na. Wanda ya bata maka rai bai kyauta min ba ni kam tunda nima yasa nawa ran ya baci" kuma gaskiya na fada, raina ya baci kwarai daga ganin bacin ran dake dankare akan fuskar shi. Yayi dan murmushi tare da jan bargo ya rufe mu dashi muka shiga barci.

Koda muka tashi ran shi wasai babu bacin rai a tattare dashi. Da yamma na lallaso shi da kyar muka je gidan Sadiya muka ga baby don da cewa Yayi wai ya za ayi in fara fita ina amaryar sati daya? Da kyar da jibin goshi ya bar ni bayan na dauki alkawarurruka da dama wadanda sirrin mu ne, daga can muka wuce ya fara koya min mota sai gab da magrib muka koma gida. Kwana biyu da yin haka visar mu ta fita kasashen ketare yawon bude ido (honey moon) ta fita. Da kaina na zauna na fitar da kasashe biyar wadanda nake matukar so da burin ziyarta a rayuwata. Muka fara shirye-shiryen tafiya amma fa bayan anyi sunan Sadiya.

A rana ta uku da haihuwar na kara komawa gidan Sadiya daga can bayan Abbu yaje ya dauke ni da dare muka biya ta can babban gida gidan su Abbun muka gaida iyayen shi, Hajiya Siyama mutuniyar kirki ta amshe mu da hannu bibbiyu har da dan guntun fadanta wai me yasa ya barni na fara fita yanzu? Har tana karawa da cewa wai ai su a zamanin su amarya sai tayi rabin shekara kafarta bata taka kofar gidanta ba., na kama baki a raina na kara da lallai kuwa! Bayan mun gaisa ta saka mana albarka muka wuce sashen Hajja Fati itama muka gaida ta. Nan ta hada ni dasu tarkacen daddawa da sauran su. Mahaifinsu kuwa kwaryar zuma farar saka mai kyau ya bani, daga nan muka juya gida hannu riki-riki da tsaraba.

Ranar sunan kuwa da safe na tafi. Muna ta ayyuka da tsare-tsaren wajen da baki zasu zauna bayan falo. Sai bayan la'asar su Anty Mubeenah suka iso gidan ita da yaranta lokacin muna can bayan gidan muna suyar samosa wadda ake ba baki.

Ni'imah data kai wa su Anty Ameenah wadda muka soya ta dawo, ta daddabo ni tare da rada min “ga fa uwargidan ki can tazo!" naji kamar zuciyata zata faso kirjina saboda bugawar da tayi, ganin yadda nayi kuru-kuru da ido yasa tayi dariya, “haba babe cool mana, sai kace wadda zata cinye naman jikin ki?" nayi murmushin yake kawai.
Ni'imah ba zata gane halin da nake ciki ba, ba wai tsoron Anty Mubeenah nake ji ba, kawai ina fargabar yadda karon mu da ita zai kasance a matsayina na matar Abbu-Mijinta a halin yanzu, nasan ko kallon banza ba zan samu ba wannan karon, fatana daya mu rabu da ita lafiya ba tare da rayuka sun baci ba. Don haka nayi gefe daya da tunanin naci gaba da rolling din da nake yi. Har inda muke Hafsy ta lalubo ni, nan ta zauna tana ta zuba min labarai har muka gama, aka shiga da wadanda muka yi ciki mu kuma muka shiga BQ muka yi wanka muka gyara jikinmu.
Wata uwar sun shadda muka saka a matsayin ankon suna, dark purple ta sha aikin pink din zare, Ya Allah! Zo kuga yadda na fita a cikin kayan nan. Kyawuna ya fita

sosai kamar ka sace ni ka gudu, muka tsaya muka dan karkashe flashes kafin muka koma cikin gida. Bayan dogon hesitating da tunanin zanyi ko ba zan yi ba, daga karshe dai nayi sallama dakin maijego na shiga cikin dakiya duk da cewa zuciya na wani mayen tsere take yi a cikin kirjina.

Ina shiga muka hada idanu da ita kamar wadda take jiran isowa ta, ni da ita muka yi stilling a waje guda, ni na fargabar abinda zai je yazo ni yayin da a nata 6angaren ban san dalili ba.  Ta janye idanunta a kaina, yayin dana daga kafa da kyar na karasa shiga cikin dakin. Gefen gado kusa da maijego na zauna nesa da inda Anty Mubeenar ta zauna ita da kanwar ta Shakirah wadda sai dana zauna na kula da ita a wajen hakan ya kara min fargabata, a tunani na ko taron dangin cin kaniyata suka yi.

Da dan murmushina cike da yake na dubi inda take zaune nace "Anty Mubeenah ina yinin ku?" ta dage kai sama yadda kasan ba da ita nake ba, sai Shakirah ce ta amsa da er fara'arta har da cewa "su amare ne?, Ai naso

lekawa har gidan naki mu gaisa Allah bai nufa ba tunda bamu samu zuwa biki ba, Allah ya sanya alkhairi!" na amsa da "Ameen" a hankali kuma a dan kunyace ina satar kallon inda Anty Mubeenah take a zaune koma ince a hakimce, to ta dare kan gado tare wani baje-baje yadda kuka san kan gadonta tana kallon kowa daya bayan daya kamar wasu bayinta ko irin en duniya dinnan da daurin kallabinta ture-ni-kaga-tsiya dinnan wanda ya fito da daddagaggiyar keyar ta gashi duk a cunkushe, sosai matar take bani mamaki. Kamar ta ace tana da saloon guda amma gashinta bashi da maraba da wata Inna ko Goggo a kauye wadda bata san menene ma'anar Relaxer, Shampoo ko Stretcher da stuffs dinnan ba.

Tashi tsaye tayi tana jan hannun Shakira tana magana kamar mai gunaguni, "Malama tashi mu tafi koh?" Shakirar ta maida ta ta zaunar tace "haba ke kuwa, ba mu jima da zuwa ba fa! Bari mu dan jima mana" ta koma ta zauna tana wasu guna-guni, fuskar nan tayi wani sha6ar babu kyawun gani, na kauda kallona daga gun su kafin cibi ya zama kari kuma.

Anty Ameenah ta shigo dakin, “Nafeesah kin ci abinci kuwa?" na dan girgiza mata kai, “A'ah Anty, bana jin yunwa ne" ta dan hade fuska, “a‘ah ban yarda ba, maza-maza tashi ki nemo abinci.... Ko don ma ina zuwa" ta juya ta fita daga dakin.

Tana fita su Hafsy su duka ukun suma suka shigo, dama kai tsaye Hafsy wajena ta taho, su kuma biyun sai da suka matso kusa sannan suka lura dani. Qaseem ne yayi tsallen murna ya karaso wajena shima yayin da Abdullahi yayi gefen mahaifiyar shi. Yaran suka zauna a gefena muka gaisa da Qaseem, na kalli inda Abdullahi yake zaune cikin er tsokana nace “su Abdullahi babu magana ne??" ya kalleni sosai kafin ya dauke fuskar shi ba tare da yayi magana ba. A take na sha jinin jikina, tun ranar da suka je gidana na kula da wasu canje-canje a tare dashi dama kawai ban yi tunanin wani abu bane mai girma amma yanzu kam, na hangi babban lamari a tare da yaron.

Muna nan Anty Ameenah ta dawo dakin hannunta dauke da plate shake da fried rice, coleslaw, da naman kaza a

sama ta miko min plate din, na zare ido cike da mamaki na kalleta nace “Anty ina zan kai wannan abincin?" tace “cikin ki mana! Ni anya ma kuwa kina cin abinci yadda yakamata Nafeesah?" na sadda kaina kasa ina dan murmushi kawai. Ta zauna a gefen gado sai a lokacin ta kula dasu Mubeenah a zaune, Shakirah ce ta fara gaida ta, tayi dan murmushi ta amsa ta dauke kanta ga mayar da bakin da suke cikin dakin. Na jijjiga kai a hankali ina kara jinjina halin Mubeenah a cikin raina.

Ni dasu Hafsy muka fara cin abincin, har ga Allah turawa kawai nake yi. Ga rashin jin yunwa, ga tunanin sauyawar dabi'un Abdullahi a gare ni, abin ya daure min kai sosai. Muna cikin cin abincin naga ya tashi ya fita daga cikin dakin, da sauri na tashi na bi bayan shi.

A can bayan gidan wajen wasu shuke-shuke na same shi a zaune, ya kurawa shukokin idanuwa very lost in his thought, sai dana zauna a gefen shi sannan ya kula dani. Yayi saurin dauke kanshi ya sadda shi kasa. Dan murmushi nayi tare da gyara zama na sosai. Muka yi shiru muna kallon shukokin, can nace mishi.,

“Ka tsane ni koh Abdullahi?" da alamun tambayar tawa ta bashi mamaki sosai, da sauri ya dago ya kalleni yana girgiza kai alamun a'ah, sai dana sake ajiyar zuciyar relief a hankali kafin nace “kar ka boye min komi Abdullahi. Nasan cewa dama dole zaku tsane ni, nazo na aure muku mahaifi na zama kishiyar mahaifiyar ku, ko ba haka ba?" nan ma ya girgiza kai da sauri.  Nayi shiru tare da kura mishi idanu, idan ba haka bane ba to menene? Na juya na fuskance shi sosai tare da riko hannayen shi nace “to idan ba haka bane ba Abdullahi menene? Me yasa kake avoiding dina? Last time da kuka zo gidana dama haka kake sakewa kamar ni bakuwar ka ce wadda baka taba gani ba, you hurt my feelings you know... Now, gaya min, ni ce koh?" ya sake girgiza kai, a hankali kamar mai tsoron yin maganar yace “Abbu ne!!".

Na zaro ido cike da mamaki ina kallon shi, “Abbu da kan shi? Me ya maka? Fada min zan mishi magana kaji??" ya kura min idanu kamar ba zai yi magana ba, can kuma yayi maganar da tasa na kusa sakin fitsari a wando saboda tsananin mamaki. “cewa yayi baya son Mommyn

mu!!" ya fada muryar shi na dan rawa yayin da idanun shi suka cika da hawaye.
Da gaske gabana ya fadi, duk wata kalma ta bace daga cikin kaina. Cikin sanyin jiki na kura mishi idanu nace “shi Abbu din ne ya fada maka haka da bakinsa?" yayi saurin girgiza kai, “a'ah, Mommy ya fadawa. Ni kuma lokacin naje dakin shi ince ya kai mu gidanki mu yini, shine naji yana gaya mata cewa baya son ta ke yake so!" na dafe saitin zuciyata dake bugawa, ba wai na jin dadin maganar ko fluttering ba, na takaici da wani dan tsillin jin haushin abinda Abbu yayi. A tunani na sai mazajen da basu san inda yake musu ciwo bane suke irin wadannan halaye, ashe ba haka bane.

A lokacin na fahimci cewa wasu iyayen su suke sa ‘ya‘yan su su tsani kishiyoyin iyayen su. Babu yadda za ayi ace a yabi wata ba uwar yaro ba, ko a fifita wata akan uwar yaro bai ji haushin abin ba koda uwar tashi bata da kyawun hali kuwa. Kamar dai abinda yake faruwa yanzu, wanda ba zan taba bari hakan ya faru ba. Mun gina amintacciyar rayuwa ni da yaran, they trust

me, suna so na, suna girmama ni, ba zan taba bari hakan ya taba amintar mu ba.

Nace “shi yasa ka tsane ni kenan?" yayi shiru kan shi a kasa, “lokacin da naji labarin zaki auri Dad dinmu, frankly naji haushi. Me yasa muna kallon ki a matsayin yaya a gare mu zaki buge da auren Abbu? Daga baya kuma sai na fara tunanin hakan ai ba laifi bane ba, kuma zamu zama muna tare dake a koda yaushe saboda believe me muna son ki wallahi. Har lokacin da muka zo gidanki ina cikin confusion, daga karshe dai nazo nayi concluding cewa Kaddarar ki ce hakan don haka na kauda tunanin komi a cikin raina nayi niyar rungumar ki da zuciya daya. Saboda haka ne ma nayi niyar sa Abbu ya kaimu gidan ki mu yini in kuma baki hakurin abinda ya faru ranar farko da muka je gidan ki. Sai kuma na kare da jin maganganun dasu Abbun suke yi..., I was afraid! Naji tsoron cewa zaki iya sa wa Abbu ya tsani Mommy ya daina kula ta, muma yazo ya tsane mu ya daina son mu sai ke da baby idan kin haihu..., irin yadda Daddyn su abokina Ameer ya musu lokacin daya kara aure!".

Na fahimci irin tsoro da fargabar da yake ciki, na matsa tare da kamo hannun shi sosai. Nace "look Abdul, ni ba irin matar Baban su Ameer abokin ka bace kaji? Ba zan taba bari wani abun cutarwa yazo kusa da ku ba balle in cuce ku da kaina. Sannan Abbun ku yana son Mommyn ka kaji?" yaron ya kalleni sosai with so much hope in his eyes sai da naji kamar zan yi kuka. Fuskar shi ta washe da murmushi, "da gaske Anty Nafeesah?" na daga mishi kai da sauri, "sosai ma. Yafi son ta akai na ma. Kawai ranar ai ya fada min, yana so ne yaga abinda zata yi ne shi yasa yace haka. Wasa yake mata!!" na karasa maganar cikin cije baki.
Yayi ajiyar zuciya, "har naji dadi wallahi, da har na fara ji Abbu ya fara bani haushi!" da sauri nace mishi "kul! Kar ka sake maimaita irin haka kaji Abdul? Ko me iyayen mu suka mana bamu da damar jin haushin su a cikin ranmu kana jin mu? Duk abinda zasu yi suna da dalili don haka mu dinga musu uziri ka gane?" ya gyada kai cikin fahimta, "na gane. Nagode sosai Anty Nafeesah! Kiyi hakuri kuma" na shafa tattausar tattaurar sumar kanshi ina murmushi, "are we good now?" shima ya

gyada kai yana murumushi. Nace "zo mu koma cikin gida kaga yamma tayi kila su Mommyn ka suna neman ka. Kada fa ka sanya damuwar komi a cikin ranka kaji?" ya gyada kai. Naja hannun shi muka tafi.

Aikuwa su Anty Mubeenah na waje suna neman shi, ganin mu tare fuskar ta ta danyi frowning da ban san ko na menene ba. Na daure duk da sanyin da gwiwa ta tayi muka karasa har gaban motar su, wanda kafin muje sun shige ciki, Abdullahi ya bude baya ya shiga na leka ta jikin taga ina musu Allah ya kiyaye hanya, Anty Shakira da yaran suka amsa cikin fara'ah yayin da mai gayya Mubeenah ta dauke kai gefe, ni dama nasan za a rina. Suka ja motar suka tafi, na sauke ajiyar zuciya a hankali na juya zuwa cikin gidan, lokacin an fara kiran Sallar Magriba.

Bayan Isha'i Abbu yazo ya dauke ni, na wa su Anty Ameenah sallama na tafi suna ta min godiyar hidimata a gare su, daga ta gangar jikina har ta jakata. Na bude murfin motar gefen mai zaman banza na zauna, Abbu ya kalleni da murmushi a fuskar shi. "ya ne baby?" na

kakaro murmushin yake kawai, yayi zaton gajiya ce don haka ya tashi motar muka tafi.

Muna zuwa gidan na dafa mishi jollop din Spaghetti, ban zauna ci ba don cikina a cike yake already. Daki na shiga na watsa ruwa, na dauro alwala na yi sallar Isha'i tare da yin Shafa'i da Wutiri. Yan shafe-shafe nayi tare da zura kayan barci. Wando iya gwiwa da riga mai budadden wuya, har yau ban warke daga cuta ta ta jin suffocation idan na kwanta da riga ba, saukin dana samu shine Abbu baya ma bari na na kwana da riga, idan ya tafi gidan Anty Mubeenah ne nake amfani da riguna irin wadannan saboda ina sakewa a cikin su.

Nayi sallama a nutse na tura kofar dakin, yana kan sallaya yana Nafilfilin shi na duk dare daya saba yi. Na wuce kan gado tare da kwanciya na juya baya daga inda yake sallar na kalli bango zuciyana cike da sake-sake, ina so inyi mishi maganar ina kuma tsoron abinda zai auku ko yaje ya dawo, amma a ganina yin maganar kamar ya zama dole ne.

Ina jin lokacin daya gama sallar ya wuce gaban dresser yayi shafe-shafe da feshe-feshen turaruka kafin ya

kashe wutar dakin. Ya hawo kan gadon ya kwanta a bayana tare da janyo ni jikinsa, hannunsa ya fara laluba na yayin daya kai bakinsa gadon bayana yana manna short short kisses zuwa bayan wuyana, kafin in lalubo hanyar yin protesting ya san yadda yayi ya batar min da hankali, da sauri na juya na sarkafe hannuwana a wuyan shi tare da sakar mishi jikina gabadaya, ina nufin mallaka mishi....

Yayi rigingine akan gado yana ajiyar numfashi, kaina yana kan kirjinshi yana shafa gashin kaina a hankali. “as usual, that was amazing baby, I love You!" ya fada tare da kissing din kaina. Ire-iren kalaman shi kenan a yawancin dararen ko ince lokutan da duk muka kasance tare dashi. Duk yadda naso kar inji dadin kalmar hakan bai yiwu ba, naji zakin ta tamkar zuma. Na kara shigewa cikin jikinshi tare da dora lebbana a tsakiyar kirjinshi na sakanni da basu fi biyar ba na kara maida kaina na kwantar a kirjin shi.
Wucewar mintuna masu dama, mun yi shiru ne kawai babu wanda yayi magana. Wata masaniya ta taba bani

shawarar cewa lokuta irin wadannan wato lokutan bayan gama Auratayya, lokuta ne da suke kawo fahimtar juna da kara sa shakuwa a tsakanin ma'aurata, I tried, n it really works. Wani lokaci mu kan tattauna game da feature dinmu, rayuwar mu, idan ma da matsala sai mu tattauna akan ta mu warware ta. Na jefa mishi tambayar “me yasa kake so na Abbu?" maganar taje mishi a bazata saboda shirun da yayi na dan lokaci kafin yace “I don't really know, amma kyawawan halayen ki, kulawar ki a gare ni da tausasawar ki ina ji sune jigon abubuwan da suka ja ra ayina game da ke" nayi dan murmushi kawai, “I am sorry to say, but idan zaka rike son da kake min a cikin zuciyar ka zan fi son hakan" yayi shiru na dan lokaci kafin yace “saboda me?" nayi shrugging, “ina so in samu farin ciki mai dorewa da kai Abbu, ina so in rayu da iyalan ka cikin aminci da lumana da yarda da juna, idan kana fadawa kishiyata kana so na a gabanta me kake tunani hakan zai jawo min??" tashi zaune yayi sosai, nima na zauna tare da jan bargo na rufe jikina.

“me kike nufi? Kun hadu da Mubeenah a wajen suna ko? Me ta fada miki? Tana kokarin ta raba ni da wadda take

so na ko? That..." nayi saurin katse shi, “ba ita bace, yes mun hadu da ita amma ko kalma daya bata hada mu da ita ba" ya kalleni sosai, “idan ba Mubeenah ba a wajen wa kika ji maganar?" nace “kayi hakuri, amma ba zan iya fada maka ba" ya kalleni, “daya daga cikin yaran ne koh?" shirun da nayi ne yasa ya gaskata zarginshi, hannu ya kai yana yamutsa sumar kan shi, “God!! Abinda nake jin tsoro kenan".

Na kara matsawa kusa dashi, “saboda haka ne nake so plssss ka daure, kada kayi sanadin da zai sa yaran su tsane mu daga ni har kai. Kaga hakan ba zai mana dadi ba" muryar shi cike da bacin rai “no way! Ita bata so na sai kuma ta hana ni son wanda yake so na??" nace “babu wanda ya hana ka son abinda ke son ka Abbu, amma kaje kana ihun kana son kishiyarta a gabanta da yayanta, hakan babu kyau. Zai jawo consequences masu dama wanda hakan ba zai mana dadi ba" ya dan girgiza kai, “I was angry!" nace “shi yasa Annabin mu SAW ya umarce mu da yin shiru idan muna cikin fushi, you should've just keep quite ko ka bar inda take lokacin da ranka ya fara baci. Ni dai don Allah kada ka sake yin

hakan kaji Abbuna??!" na fada cikin sanyin murya mai dauke da roko, ya kura min idanu cikin duhun dakin kafin ya sake ajiyar zuciya., “naji! Na fahimta, hakan ba zai sake faruwa ba. Na gode, Allah ya miki albarka!" matsawa kusa dashi nayi na dare kan cinyar shi na kamo fuskar shi na rike cikin hannuna, “har kullum fahimtar ka a gare ni da saukin kan ka su suke kara saka min natsuwa da jin dadi Abbu na, Allah ya barmu tare ya kara mana son juna" yayi murmushi, “if you are that happy then show me!" ba bata lokaci na hade bakina da nashi. Kafin wani lokaci na tsinci kaina a karkashin shi, “you up to another round??!" ya fada hoarsely idanunshi na sheki da farin ciki da sha'awa, na daga baki zan bashi amsa but instead na buge da furta “Abbu....!!".

Washegari ya koma gidan Anty Mubeenah, Zaynab ta dawo da yake idan ya tafi can ne take zuwa, ranar da zai dawo kuma sai ta koma gida. Naje gidan su Anty Ameenah na musu sallama har can babban gida sai da naje, ranar daya dawo gidana da dare jirginmu ya daga zuwa Las Vegas, Paris.

Cikin tsakiyar dare muka isa birnin Las Vegas, already mota daga hotel din da Abbu ya kama mana tana jiran mu a airport din, muka zuba abubuwan da muka taho dasu a bayan motar muka shiga direban yaja muka tafi sai Bellagio Hotel, babban hotel ne dake tashe a cikin birnin LV musamman kasancewar shi a cikin tsakiyar manyan waje na shakatawa da wasanni.

Garin ko ina haske tal kai kace ranar Allah Ta'ala ce, mutane suna ta shige da ficin su suna gudanar da al'amuran rayuwar su kamar ba tsakiyar dare bane.
Muna zuwa babu bata lokaci receptionist din wajen wata farar yamutsattsiyar baturiya mai fara'ah ta bamu keys da number din dakinmu dake can sama, kayanmu tuni suka riga mu isa don haka muma muka shiga elevator muka tafi har hawa na goma na biyu, dakin babba ne living room da bedroom duk a hade suke waje guda sai babban toilet dake hade da dakin, komi na ciki guda biyu ne alamun it was meant for couples.

Muka rage kayan jikinmu muka fada bandakin muka yi wanka da ruwa mai dumi don warware gajiya, muka yi alwala muka fito Abbu yaja mu muka yi Shafa'i da wutiri daga nan muka haye kan babban gadon dakin ko abinci bamu nema ba don ma wai mun ci abinci a cikin jirgi, ba bata lokaci kuwa barci ya dauke mu.

Washegari misalin karfe goma na safiyar ranar acan, mun tashi mun yi wanka mun shirya, muna zaune akan daya daga cikin sofa din dakin daya daga cikin ma'aikatan wajen ya kawo mana abincin da muka yi oda, nan muka zauna muka karya. Muna gama karyawa Abbu ya sauka kasa yace zai je ya dawo.

Na leka ta babbar tagar dakin ta gilashi wadda ta kusa cinye rabin bangon dakin, curtains din kuma anyi gefe dasu hakan ya bani damar hango titin kasar a cikin safiyar ranar, mutane da suka koma min kamar kwari da ababen hawa suna ta kai komon su, na sarkafe hannuna a kirji ina kallon su ina sake-saken abubuwa a cikin raina har Abbu ya dawo.

Ya zauna akan sofa tare da mika min hannunshi alamun inje, babu musu na tafi na zauna akan cinyar shi. Ya danyi kissing gashin kaina da goshina, nayi murmushi kafin ya ciro Sim Card wanda ake amfani dashi a kasar sabo ya bani, dama nashi tun a washegarin ranar da safe ya saka nashi a waya ya kira yaran har ma muka gaisa dasu. Tsallen murna nayi a jikinshi na rukunkume shi ina murna, dariya kawai ya dinga yi. Tashi nayi na saka a wayata na kira su Mommy da yake akwai credit a ciki, na sanar dasu mun sauka lafiya, na kira su Ni'ima da Ramlah muka shiga hira har sai da Abbu yazo ya kwace wayar sannan na kashe. Yinin ranar a daki muka yishi Abbu bai sake fita ba. Sai da yamma yace in shirya mu fita, na shirya cikin rigar jallabiya ocean blue, na dora gyalenta a kaina nayi rolling, Abbu kuma yasa pants na KC da riga body hock muka jera muka fita bayan mun rufe dakin.

Idan ka ganmu a lokacin kasan cewa kaga perfect match couple wadanda suka dace da juna ta kowane fanni. Hannuna yana sarke ana Abbu muka fita wajen hotel

din, a hankali muke tafiya ta gefen titi inda aka tanada saboda masu tafiya da masu tuka keke. Yanayin weather din surrounding din gwanin dadi da burgewa, iska mai sanyi yake kadawa yana wasa da tufar mu, wani dan karamin garden ne muka je, wajen yana ta kamshin furanni da shuke-shuke iri-iri, it was breathtakingly beautiful! Masha Allah!! Abinda na dinga maimaitawa kenan bakina a bude, Abbu dariya ya dinga min da alamun ba sau daya yazo wajen ba. Yaja hannuna muka shiga zagaya wajen, wajene na shakatawa sosai, ga masu sayar da kayan makulashe iri-iri, jefi-jefi zamu ci karo da gungun mutane a waje, either wasu suna kide-kide da raye-raye ko kuma wasu suna su karate, wasa da wuta, da sauran abubuwa dai masu kayatarwa da birgewa, mu kan tsaya mu dan yi kallo ko mu sayi wani abun na motsa baki. Da lokacin magrib yayi muka samu kebantaccen waje Abbu ya tada sallah muka fara, abin mamaki wasu couple suka yi joining dinmu, bayan mun gama muka gaisa dasu nan muka tashi muka cigaba da zagaya wajen dasu, matar Hanan shi kuma mijin Amir mutanen Syria ne, suma sun zo yawon bude idanu ne,

gasu da fara'ah da son mutane nan da nan muka saba dasu.

A wata karamar restaurant muka dakata, a tsakiyar garden din take ga haske yanayin setting din wajen kanshi abin kwantar da hankali ne. Babu wasu mutane masu yawa a wajen, ga kida a hankali dake tashi daga background din wajen, very romantic. A table daya muka zauna dasu Hanan, nan ma'aikatan wajen suka zo, mazan suka yi placing order yayin da ni da Hanan muke ta kashe selfies abinmu.

Muna hira a hankali dasu har muka gama cinye Chicken pepper soup, potato chips and salsa da Rich Maccaron da suka mana oda, bayan mun gama sun dauke kayan aka kawo mana chocolate cake guda biyu, Ya Allah! Ban san lokacin dana fara tafi ba ina giggling lokacin da naga cake dinmu dauke da sunana ni da Abbu, ansa Happy One Month Marriage Anniversary a jiki, kafin ince me! Amir ya tattaro mutanen wajen wai su zo su taya mu murna, nan suka zagaye mu suna tafi da er wakar su,

muka bushe lights din candle din kafin muka yanka, Abbu ya saka min a baki nima na saka mishi, daga nan ya kama hannuna muka fita filin wajen muka dan juya haka nan, m not fond of waltz bama iya taka ta nayi ba haka nan dai nabi bayan Abbu, hannunshi daya ya rike kuguna dayan kuma ya rike hannuna na dama ya rike da nashi, yayin da nawa hannun na hagu yake kan kafadar shi, a hankali yake juyawa damu yana bin tattausan taushin kidan dake tashi, I was happy, really! Murmushi nake kamar wata sakara, Ya Allah! Farin cikin da nake ciki a lokacin ban taba tsintar kaina a makamancin shi ba, har ban so kidan ya kare ba, Abbu yaja hannuna muka koma seats dinmu, tafi da shewa da mutanen wajen keyi ya ragu kafin su koma wajen zaman su, nan muka karasa cinye cake din muka yi Sallar Isha'i kafin muka yi sallama dasu Hanan bayan mun yi alkawarin zamu hadu dasu washe gari.

Nayi zaton daki kawai zamu koma mu kwanta, ga mamakina koda muka shiga hotel din wani wajen muka nufa, mutane na tsaitsaye sun zagaye wani abu mai

kama da round about, wajen babu wadataccen haske sosai amma hakan bai hana ka ganin mutanen dake wajen. Abbu ya janyo ni jikinshi sosai, bakinshi ya kai saitin kunnena ya rada min “are you ready?" na bude baki na a hankali nace “for what?" kafin ya bani amsa kawai naga ruwa yayi fitar burgu daga round about dinnan yayi sama, Ya Allah!! 'watching fountain show at Bellagio Hotel with Husby!' abinda ya fara fado min a rai kenan a matsayin status daya dace ace nayi a lokacin, na rukunkume Abbu cikin tsananin farinciki har ma na rasa kalmar mishi magana, kyawawan mintuna shida ruwan nan na sama da kasa in a waves, wasu nata daukar hotuna da videos mu kam muna tsaye muna ta kallo har show din ya kare. Abbu ya sake ja na muka tafi cinema dake nan cikin hotel din, muka sayi popcorn da soft drink muka sayi tikitin romance movie muka shiga, sai karfe goma sha daya muka koma dakin mu, kafin mu yi wanka, Shafa'i da wutiri da sauran abubuwa sha daya da rabi tayi already.

Na kwantar da kaina akan gado idanuna a lumshe ina tariyo abubuwan da suka faru ranar, Abbu ya hayo

gadon tare da janyo ni jikin shi, kaina ya dora akan kirjinshi yana shafa gashin kaina a hankali na kara lafewa a jikin shi, “how was today?" naji ya tambaye ni, na zagaye kugun shi da hannuwa na, “it was wonderful and unforgettable Abbu" ya danyi murmushi, fuskata ya dago daidai saitin fuskar shi, “am relieved to hear that baby!" ya fada a hankali kafin ya hade bakina da nashi....

Kwanan mu biyar a Las Vegas, mun je wajaje masu dama na shakatawa da bude ido irin su HooverDam, The Venetian, mun je The Freemount Street mun kalli light show dinsu, tafiyar mu dai kam tayi yadda ya kamata, mun huta sosai mun kuma darji soyayyar mu, a kwanan mu na shida muka wuce zuwa Paris. A can muka bar su Hanan da tuni muka saba dasu, kaya da tsarabobin da muka saya kuwa Abbu ya tura mana su zuwa Beijing inda can ne kasa ta karshe da zamu ziyarta.

Muna kwance a dakin Hotel din da muke tunda muka isa Paris yau kwanakinmu biyu kenan, kaina yana kan

cinyar Abbu shi kuma yana duba jarida, na dago na kalleshi, “wai ni Abbu ya zancen siyasar da ake cewa zaka fita naji shiru har yanzu?" ya kalleni yace “ai tuni na janye" na gyara kwanciyata a jikinshi, “me yasa Abbu?" yace “kawai.... Abin ne kawai naji ya fita daga kaina, dama kuma tun farko Hajiyar mu bata yi na'am da abin ba.... Ya ne?" nayi saurin girgiza kaina, “babu komi Abbu na... Kayi tunani me kyau sosai da kayi hakan" yayi kasa-kasa da idanuwanshi yana kallona cikin alamun tambaya, murmushi nayi tare da shafo tattausan sajen fuskar shi nace “da gaske babu komi Abbu, nima bana son siyasar nan fa!" yayi murmushi, datz very good ai. Nace “yau kuma ina zamu je Abbu?" shiru yayi kamar mai tunani, can ya duko saitin kunnena kamar zai min rada, “surprise!" baki na turo cikin shagwaba, “kai Abbu!" yayi dariya tare da maida kanshi ga jaridar hannunshi, ni kuma na lalubi wayata na kira Hafsy muna hira tana bani sakon abubuwan da zan sayo mata.

Ranar bamu fita ba sai da yamma, muka shirya muka fita kasan hotel din wanda bashi da nisa da Eiffel Tower, daga cikin dakuna ma kana hango tower din kamar ka mika hannu ka taba ta. Tunda muka zo nake so muje amma Abbu yana cewa ba yanzu ba, mun dai yi yawace yawace sosai mun je manyan restaurants, wajajen shakatawa dana hutawa, har wani Modern Museum of Art muka je Center George's Pompidou muka kalli hotuna iri-iri, mun shiga wata karamar Art Market inda masu zane suke baje basirar su a wajen nan aka zana hoton mu ni da Abbu, ko a haka muka tsaya it was really worth it.

Muna sauka kasa muka hadu da Vincent wadda take guiding dinmu idan zamu fita, mata ce mai fara'ah da ban dariya wadda tasan kan aikinta sosai, cikin harshen turanci muka gaisa da ita yayin da suka juya yare ita da Abbu zuwa French. Na turo baki na tsaya a gefen shi har suka gama maganganun su kafin ya kamo hannuna yana dan murmushi, “can we?" na maida mishi martanin murmushin. Vincent na tafe muna binta a baya har

gaban Tower din, lokacin dana ganni a gabanta I couldn't believe my Eyes!! Na kai hannuna daya baki yayin dana kankame hannun Abbu da dayan cikin tsananin farin ciki, Abbu bai gajiya da bani mamaki da farin cikin dake gigitani tunda muka baro Nigeria. Sai dana yi calming down Vincent nata mun dariya, sannan ta mana nuni da matakalar da ake hawa can sama, tace “mu je!" na zaro ido ina kallonta tare da nuna mata elevator da mutane suka yi cunkuso a wajen, nace “ba dai steps dinnan kike nufi zamu hau ba koh?" tayi murmushi, “dear, believe me it's worth it. Mutanen nan da kika gani kila sai muje mu dawo wasu basu samu sun je ba, kuma idan kika hau elevator dinnan babu abinda zaki gani ki bada labari... Mu je!" na kalli Abbu ya min murmushi, a hankali muka daga kafa muka bi bayanta..

Kafin mu karasa sama na jigata kwarai da gaske, hawa steps din bene dari bakwai da hudu ba abu bane mai sauki lol, wai don ma muna dan tsayawa mu huta, ko kuma mu dan yi hotuna a wajajen da suka burge mu. At last! Bayan lokutan da suka fi awa biyu sai gamu on top

of Eiffel Tower! Dana leka kasa ko tracing din mutane ba ka gani, sai kayi zaton cewa dots dots ne, but it was amazing really!! Na daga kai na kalli sararin samaniya, yadda ta zama soo close dani kamar in mika hannu in kamo kyakkyawar rana da take shirin faduwa saboda kusancina da ita. Mun jima a gun sosai, sai da muka huce har lokacin Magrib yayi sannan ne muka bi ta elevator muka sauka kasa, sai lokacin na yarda da maganar Vincent, sam banji dadin tafiya ta cikin elevator ba.

Sai data raka mu har hotel kafin ta mana sallama ta tafi, muka tsaya a wata restaurant anan wajen Hotel din, na zauna a lounge wajen da aka tanada don hutu yayin da Abbu ya tafi yayi sallah kasancewar ina fashi, bayan ya dawo muka ci abinci, Bhajia, steak da lemu mai sanyi. Daga nan muka sake komawa kasan Tower din inda bamu fi minti biyar da zuwa ba aka fara Fire Work! Woah, sai lokacin na fahimci dalilin da yasa Abbu yake ce min in jira ashe saboda show din ne. Naji dadin hakan sosai kuwa ba kadan ba, ban taba ganin abinda ya burge

ni ba kamar kallon fireworks dinnan, idan ina kallo a cikin film jikina har rawa yake yi don burgewa, yau da aka yi displaying abin a gabana sai naji na rasa bakin magana in fayyace wa Abbu halin da nake ciki, kawai na sarkafo wuyan shi na hade bakina da nashi, ina ji ya fahimci sakon da nake son isar mishi, ya rungume ni sosai yana shafa bayana, a hankali na janye daga jikinshi ina dan murmushi cike da jin kunya, sai lokacin da ihu da iface ifacen mutanen wajen ya shiga kunnena na tuna inda muke, nan na karkata hankalina ga display din.

Bayan mintuna sha biyar aka gama display din muka koma dakinmu, Abbu yana Sallah na kira Daddy na fara bashi labari, ranar kam har sai daya gaji da saurare ya min sai da safe, na turo baki nace “Daddy har ka gaji dani koh?" dariya yayi yace ni na isa in gaji da jin story daga bakin Uwata? Na gaji ne, ga kuma Mommy dinki can tana jirana mu ci abinci" nace “to Daddy sai da safe, a gaida Mommy" muka yi sallama na ajiye wayar. Toilet

na shiga na yi wanka na fito na shirya, already Abbu na kan gado don haka na bi bayan shi muka kwanta.

Daga Paris muka wuce Sao Paulo, Brazil. Kwanan mu biyar a can muka wuce Amsterdam, can kuma muka yi kwana hudu muka karasa Beijing. Kwananmu biyu a can bana lekawa ko can da nan saboda tsananin gajiya, sai a kwanaki na uku muka fita muka je kamfanin su Abbu.

Babban Kamfani ne Masha Allah! Shi kanshi ofishin Abbun wani wawakeken ofishi ne daya isa ace an gina wani karamin gida. Muna zuwa suka shiga meeting, ya hada ni da PA dinshi, Chao Shang muka zagaya kamfanin wanda ya dauke mu lokaci mai tsawo sosai kafin muka sake komawa ofis dinshi, har sai da nayi barci akan kujerar hutu kafin ya dawo, nan ya tashe ni muka koma hotel din da muka sauka.

Mun sha yawo a Beijing kamar Hauka, satin mu daya, mun je kananun garuruwa da kauyukan su mun bude idanu, mun shiga kasuwa mun yi siyayyar tarkace iri-iri

da kayayyaki, Abbu dai duk inda muka je kayan jarirai ne yake saya unisex har da kayan wasanni inyi ta mishi dariya. Satinmu daya cif muka hada namu-i-namu muka dawo bayan Abbu ya hada mana kayayyakinmu an auna su a container amma fa sai da muka biya ta Bangladesh wajen Aminu kanin su. Kamanninsu da Abbu har ta baci, gashi da fara'ah da dan banzan tsokana, yana karantar Mechanical engineering ne a nan University dinsu. Already ya mana booking daki a hotel, don haka yana dauko mu daga airport can ya wuce damu, muka yi wanka muka yi Sallah muka yi abinci muka kwanta. Ranar duk nacin Abbu sai kyaleni yayi don ina jin kaina akan gado barci yayi awon gaba dani, ina jin yana lalubata amma na ma kasa daga hannu balle in maida mishi Martani, ina ji yayi kuta tare da furta bashi naci kafin ya janyo ni jikinshi. Aikuwa sai daya biya bashin nan da asubahi har sai daya kara min da alakoro.

Kwananmu biyu a can muka harhada namu ya namu muka wuce Najeriya cike da kewar Aminu da muka saba dashi sosai, shi ya zama idanun mu a can duk da cewa

ba wasu yawace-yawace ne muka yi a can ba na azo a gani.

Saukar dare muka yi don haka muna yin Sallah sai barci, washegari aka yi ta zuwa sannu da zuwa da ganin gidan Amarya da wasu basu zo sun gani ba. Tsawon kwanaki uku ana ta shiga da fita kafin kafa ta daga, na tunkari Abbu da zancen ina so in je gida in ga su Daddy, idanu ya kura min a nutse lokacin kwanan shi daya a gidana, kamar ba zai yi magana ba can kuma yace "yaushe kike son zuwa?" nace "idan ka tafi gidan Anty Mubeenah gobesai in tafi in dawo jibi" idanu ya xubo min sosai yana kallona kamar wadda notin kanta ya kunce dinnan, "haba Nafeesah! Kwana kuma? A'ah sam ban yarda ba gaskiya, za dai kije ki yini a can wannan kam na yarda amma ban da kwana" na turo baki gaba, "haba don Allah ka bar ni, yaushe rabon da in gansu har na manta fa, kuma ma sai fa nayi ziyarce-ziyarce idan naje can" yace "gaskiya ba zan iya ba Baby, kawai kije ki yini sai ki dawo" tashi nayi ina dira kafafu ni ban yarda ba nayi fushi na fada daki, ya bini da kallo yana dan murmushi.

Da yake dare ne mun gama cin abinci already, wanka na shiga nayi na shafa lotion mai kamshi sosai na aloe Vera, na shafa wani Arabian perfume mai kamshi sosai na fito dakin daure da towel a kirjina, Abbu yana zaune a gefen gado cikin pyjamas ya rungume hannuwa a kirji yana kallona, dauke kai nayi naje na bude wardrobe na fara binciken kayan barci, ban ji lokacin daya tashi daga kan gadon ba sai ji nayi an daga ni sama cak! Na dan saki kara cikin tsoro tare da kara rukunkume shi, kan gado ya dora ni tare da biyo bayana. Na fara mirginawa zan sauka yayi saurin janyo ni tare da pinning dina akan gadon ta hanyar rike min hannuwa. Kallon juna muka tsaya muna yi, a hankali ya saukar da bakinshi kan nawa ya fara tsotsa a hankali, da fari mutsumutsu na fara amma daga baya, wadannan effects da charming na Abbu a duk lokacin da fatar shi ta hadu da tawa suka sa na manta da zancen fushi na biye mishi...

A hankali yace “kiyi hakuri" nace “umh?" cikin daukewar hankali don bansan akan abinda yake ba da hakuri akai

ba, yace “maganar xuwan ki gida, please ki daure kije ki musu yini kawai kinji Baby, please?" nayi shiru ina sauraren bugun da zuciyar shi take yi a hankali, numfashi naja nace to shikenan! Ya kara jana cikin jikinshi sosai, “oh Nafeesah! Shi yasa nake kara sonki a cikin raina kullum. Jibi zaki tafi da safe sai ki dawo da yamma ya miki?" na gyada mishi kai tare da kara shigewa cikin jikin shi.

Ranar Assabar muka dauki hanya ni dashi sai Kaduna. Misalin karfe Goma muna cikin gidanmu, kasa bari nayi mu shiga tare, na bazama da gudu nayi cikin gidan ina kwalawa su Daddy kira, a kofar falo muka ci karo dasu, nan na hada su duka su biyun na rungume a jikina, sai lokacin nasan ashe ba karamar kewar su nayi ba, har da yan guntun hawaye na. Sai da muka gama murnar ganin juna sannan muka karasa cikin falo, Daddy ya fita suka gaisa da Abbu wanda yace xai je ya dawo da yamma mu tafi, ya tafi bayan ya sauke tulin tsaraba da nayo musu daga sassasassa na garuruwan da muka da muka je.....

Yinin ranar dungurungum a tsakiyar Mommy da Daddy nayi shi, sai bayan Azuhur ne naje gidan Anty Uwani, daga gidan Anty Uwani na lelleka gidajen kawaye na da abokan Mommy muka gaggaisa, bayan La'asar na koma gida inda muka sake dasa wata hirar dasu Dad, har wajen karfe biyar da rabi sannan Abbu ya dawo daukana. Gabadaya ji nayi yinin ranar yayi min saurin karewa, nan nayi narai narai da idanuna kamar zan saki kuka, Mommy taja hannuna muka shiga daki muka bar su Abbu da Daddy suna hira. Mommy ta saka ni a gaba tana bani shawarwari da tambayana game da rayuwar aurena, Daddy ya leko yace in tashi mu tafi, Mommy ta ciro ingantattun turaruka da magunguna ta bani a cikin leda tace sauran bayani zata kira ni. Haka muka yi sallama dasu Daddy kamar kar mu rabu dasu, muka shiga mota suna daga mana hannu muka tafi. Sai gab da Isha'i muka karasa gida kuwa....

Washegari.....!

“Yauwa, datz good.... Oya, juya shi a hankali mu karya kwanar can....." a nutse, hankalina gabadaya a kanshi

nake bin instructions din da yake bani. Wai mota ce yake koya min duk da cewa dai dama ko a gida Daddy ya fara koya min motar dama, ban dai maida hankali bane wajen koyon kawai. A haka yana bani instructions har na maida mu gida, bayan maigadi ya bude mana gate mun shiga, na yi parking tare da kashe motar na juya ina kallon Abbu da yake kallona yana grinning ear to ear, thumbs up ya min nayi giggling, ya kamo hannuna yayi kissing bayan hannun yace "you are really a fast learner Amour, da alamu gobe da kan ki zaki je ki dawo" murmushi nayi na shafa bayan hannunshi dake rike da hannuna tsam nace "ai dama fa kaine kaki yarda, amma tuni na kware, n yes, I'm a very fast learner, always smart!" ya wani yamutse fuska tare
da scrunching hanci, "anya?? Akwai abinda na koya miki amma har yau kin kasa kwarewa" baki na daga zan yi musu kafin na tuna abinda yake nufi, da sauri na bude murfin motar na fita a kunyace, bayana ya biyo yana "tsaya mana baby" amma ban tsaya ba sai a cikin daki, ya shigo yana er dariya kasa-kasa, baki na turo ina kallonshi, ya tsaya a gefena tare da kamo fuskana ya

rike, “fushi kika yi koh? Ai gaskiya na fada ko karya nayi?" na ciza lebena na kasa, “haka kace koh? Ni kuwa sai na baka mamaki" gira ya dage sama alamun yana challenging dina, “oh really? Bring it on then" murmushin mugunta na saki tare da matsawa gaban shi seductively ina kallon fuskar shi, ga kunya ina ji amma I don't want to lose don haka na jefa kunyar a cikin kwandon shara na rufe for the time being, in yaso daga baya na dauko ta sai in wanke...

Bayan kamar awa daya na fito daga bayi ina goge jikakken gashina da towel, yana zaune a gefen gadona yana kallona cikin murmushi. Naja kujera na zauna tare da jona dryer ina kafe gashin kaina, yayi gyaran murya, “I admit" na juya na kalleshi tare da yin murmushi cike da kunya, “na fada maka ai!" yayi er dariya “yes Babe, shi fa dayan?" idanu na zaro sosai, ya daga min gira yana er dariya, wani dan tuntu mai kama da soso na dauka na jefa mishi, ya cafe tare da komawa kan gadon rigingine ya kwanta, na girgiza kai tare da cigaba da goge gashina.

Cikin kwana biyu kuwa na kware sosai, yau da kaina na kai shi gidan Anty Mubeenah da yake ranar girki yake komawa hannunta, bata nan ma lokacin da muka je sai yaran, bayan mun gaisa da Harira na dauki yaran muka je gidan Anty Rahina data sha zazzabi kwana biyu muka duba ta, daga can muka wuce gidan Ni'imah dake ta laulayi, muka karasa gidan Anty Ameenah, a takaice sai da yamma na maida su gida har lokacin kuma Anty Mubeenah bata dawo ba. Na musu sallama na wuce gidana inda na tarda Zainab tana jirana.

Bayan sati daya muka koma makaranta, da kaina nake tuka kaina zuwa lectures wata rana kuma Abbu ne yake kaini. Yanxu en class dinmu duk sun san wanda na aura, na share kwanaki kafin su daina tsokana, shakiyanci da taya ni murnar aure, a haka dai muka ci gaba da karatun mu.Yau Abbu zai yi wata tafiya zuwa birnin Ikko taron karawa juna sani, daga wannan taron ne muke fata za a

bashi matsayin Professor idan ya dawo. Da yake kwana na ne ranar ni na taya shi hada kayan shi wadanda zai bukata. Tafiyar kwanaki shida ce zai yi. Ni na raka shi har airport, sai da naga tashin jirgin su sannan na koma gida cike da kewar Abbu na, har yau na kasa sabawa da rashin shi a kusa dani.

Kasancewar muna waya dashi, chatting, sometimes ma har video call, shi yasa ban ga tsayin kwanakin da yayi ba, kwanaki shidan na cika kuwa ya dawo, zai karasa kwana daya a gidana kafin ya koma gidan Anty Mubeenah. Na tare shi da murnata da tarin delicious abinci dana hada mishi kafin muka dire a gado inda muka nunawa juna tsananin kewar juna da muka yi. Washegari ya koma gidan Anty Mubeenah.

Muna gama lectures da misalin karfe biyar na ranar Alhamis, na fito daga class din a dan gajiye na nufi parking lot inda nayi parking Vibe dita, na bude murfin

motar kenan zan shiga naji an kira sunana, “Malama Nafeesah??" na juya ina kallon matashin saurayin daya kira sunana cikin mamaki da alamun tambaya, nace “na'am, lafiya??" Wata envelope brown ya miko min, “sako ne?" na kalleshi “sako? Daga wa??" ya girgiza kai, “I was just asked to pass it to you" na jijjiga kai, hannu nasa na amshi envelope din tare da mishi godiya, “ok thanks" yayi nodding kan shi kawai ya juya ya tafi. Na bishi da kallo kafin na gyada kaina kawai na bude motar na shiga tare da mata key bayan na jefa envelope din a bayan motar, ina kokarin yin kwana na juya na dan kalli gefe na na dama kadan kafin na wuce.

Koda na isa gida wanka na fara yi tare da dora abinci naci, Abbu yana gidan Anty Mubeenah Zainab kuma taje gida da yake yanzu na saba da zama ni kadai. Da dare Abbu ya leko ya min sai da safe kafin ya tafi da yake sai washegari ne zai dawo gidana. Yana tafiya na kashe wutar gidan naje na kwanta. Haka kawai envelope din da aka bani ta fado min a rai, na tsinci gabana da faduwa sosai. A raina na raya sai washegari zan duba.

Washegari Abbu ya dawo, da yake sai karfe goma nake da class bayan mun karya ya wuce dani makaranta. Da aka tashi sai na biyo adaidaita ya dawo dani gida don shi Abbu ya wuce masallaci.

Zan wuce ta gaban motar idanuna ya sauka a bayan motar na hangi envelope din nan, motar na bude na dauki envelope din na shige cikin gida, abincin rana na daura bayan na gama nayi wanka na kimtsa jikina na zauna jiran Abbu. Out of frustration na jira, na janyo envelope dinnan na bude. Hotuna suka fado daga ciki lokacin dana bude ta, na dauki hoto daya na bude. Abbu ne sanye da kayan dana gane su riga shirt brown mai bakaken lines da wando trouser baki, suna daga cikin kayan dana hada mishi lokacin da zai tafi Lagos. Yana zaune a wani waje kamar na shakatawa suna magana da what? Wata Mace ce amma ta juya bayan ta don haka babu fuska, na dan yamutse fuska tare da bude wani hoton, su dinne dai a waje guda amma a tsaye da alamu zasu tafi, na bude wani, ido na zaro ganin matar nan a jikin Abbuna!! Ya dora hannunshi akan kafadar ta, cikin

rawar hannu na bude wani hoton... Da sauri na runtse idona ina jin ana min wani lugude a kirjina, Abbu shi da wata kwance a kan gado babu riga a jikin su, Abbu shi da wata kwance akan gado wata Watsattsiya tana shafa shi da filthy hannuwanta, Abbu na!! Abbu na.... Abbu dai mijina shi da wata akan gado.... Gado dai a kwance wata banzar bazara ta dora filthy mouth dinta akan precious and luscious lips din Abbu na!! Innalillaahi Wa Inna Ilaihi Raji'un..... Na kwala ihu tare da yin watsi da hotunan suka zube a tsakiyar dakin ko wanne yayi nashi wurin, wasu zafafan hawaye suka shiga zubo min a kan kumatuna..., does that mean Abbu has been lying to me?? Haba, biri yayi kama da mutum, sau tari na kan tambayi kaina taya Abbu mutum mai matsananciyar sha'awa yake iya rike kanshi daga matan banza bayan baya samun yadda yake so daga wajen matar shi?? Na yarda dashi, nayi amanna dashi, nayi zaton cewa idanun shi suna ga halalin sa ne, Ashe......!!

Lokacin da aka kira sallar La'asar lokacin ne hankalina ya dawo cikin jikina, na tashi da kyar da bin bango ina

jin jiri na shiga toilet nayi alwala na fito nayi sallah, akan abin sallah naci gaba da zama na kurawa hotunan dake watse a tsakiyar dakin idanu gabadaya kwalwata ta kasa nema min mafita akan abinda ya kamata inyi.

Nayi tunanin in jira Abbun ya dawo in kwashi hotunan in watsa mishi a fuska, wata zuciyar tace shake shi zan yi har sai ya gaya min gaskiyar abinda ya faru, wata tace kawai in tashi in bar mishi gidan shi bai kamata in ci gaba da zama da maha'inci ba, tunanika barkatai har ta kai ga bana fahimtar abinda zuciyoyina suke kullawa da warwarewa. Cikin wannan halin na jiyo karar mota alamun dawowar Abbu daga masallaci, na tashi da kyar naje bakin kofa na tsaya ina hangen shi yana fitowa daga cikin mota hannunshi dauke da leda, agogo na duba. Awowi uku da suka wuce ya kamata ace ya dawo gidan, ina ya tsaya? Na samu zuciyata da saka tunanika marasa dadi, ina kallon shi ya taho da waya makale a kunnenshi, at the last step da zai hada shi da kofar falon, wani tunani ya dar su a cikin raina. Abbu na ne fa? Abbu na dai the gentle and good man dana sani ba wani ba,

mutumin dana zauna a gidan shi na tsayin watanni shida ba tare daya taba rike yatsan Hannuna idan ba mistake ba, da ace dan iska ne kamar yadda nayi zato anya zai iya kyale ni kuwa bayan da ace yaso ya lalata ni da tuni yayi hakan? Mutumin da ko bayan aurenmu sai daya jira da ixini na da komi kafin ya kusance ni?? Dana kara tuno wasu abubuwan sai na samu kaina da sake kallon hotunan idanuna na hango katon question akan kowannen su zuciyata na tamvaya na anya kuwa babu lauje a cikin nadi??.

Da sauri na koma na hau tattare hotunan na janyo drawer ta gefen gado na watsa su ciki tare da fadawa toilet da sauri na,dole in zauna in sake tunani kafin in yanke hukuncin abinda ya dace inyi, ina rufe kofar bayin naji shigowar Abbu dakin....

Ganin bana dakin yasa ya fita daga dakin tare da maida min kofar dakin ya rufe. Na kurawa kaina idanu a jikin mirror ina kallon reflection dina, kwalliyar da nayi ta hade da ruwa da hawaye ta maida ni kamar zombie.

Ruwa da sabulu nasa na wanke fuskana na kara yin wata kwalliyar kafin na fita, akan kujera na gan shi a zaune. Yana ganina ya saki murmushi mai taushi, yayin da naji gabana ya fadi sosai, anya zan iya daurewa kuwa? Don a daidai lokacin zuciyata tana kitsa min in ci kwalar shi ne kawai. Na daure na kakalo murmushi wanda nasan ko fatar bakina bai gama hadewa bama, a sanyaye na karasa kusa dashi na dan duka tare da cewa “Abbu sannu da zuwa" ya amsa yana murmushi, “kin ga na dade koh?" na gyada mishi kai kawai, yace “wai gidan Rahina na biya, shine ta hado ni da kaya ma tace in kawo miki" ya miko min ledar daya shigo da ita na amsa tare da dubawa, turaren wuta ne sai wani kamar na tsuguno idan ban manta ba naga irin shi cikin kayayyakin da aka hado min daga gida. Na maida ledar na rufe tare da kallon shi nace “abinci?" ya lumshe idanu tare da gyada kai, “please, m hungry... Very" da ace zuciyana cikin kwanciyar hankali take da babu abinda zai hana ni kamo fuskar shi in bashi sumba a baki, a yanzu kam koda tunanin ya fado cikin raina I found it disgusting sosai.

Sai kawai nayi wajen dinning table ban ko yi magana ba yayin da naji lokacin daya tashi ya biyo bayana.

Abincin na hau zuba mishi, gabadaya cikina a cushe yake nasan sam babu abinda zai shiga cikina a lokacin don haka na zuba mishi iya wanda zai iya ci kawai, ina gamawa na tura mishi su gaban shi na juya da niyar tafiya yayi saurin sa hannu ya riko hannuna, ji nayi kamar garwashi ya taba ni, kallona yayi sosai, "ina zaki je haka? Ba zaki ci abincin bane?" na girgiza kai tare da kallon shi, "naci tun dazu da naga baka dawo ba" ya kara kallona kamar wanda bai yarda da abinda nace ba kafin naga yayi murmushi tare da jan kujerar gefen shi tayi baya ya zaunar dani, "ok, zauna ki taya ni hira toh, kin san cewa dai bana jin dadin cin abinci idan ba kya gefena koh?".

Haka na zauna tare da kurawa kasan carpet din idanu ina ta saka da warwara, ban san lokacin daya gama cin abincin ba, ya juyo dani na fuskance shi, "baby, me ke damun ki ne?" ya fada cikin nuna damuwa da halin da

rashin walwalata a gare shi, nima nasan cewa yaudarar kaina kawai nake yi idan har nace wai zan iya pretending inyi behaving kamar yadda na saba.

Na girgiza kaina kawai, "babu komi Abbu, bana jin dadin jikina ne kawai" da sauri ya dora hannun shi akan goshina yaji babu zafi, ya dawo dashi wuya nan ma komi normal, yace "amma jikin ki lafiya lau... Are you sure ba sai mun je asibiti ba??" nayi saurin gyada kai, "m ok" yace "idan kin ji da wani abu don't hesitate fa, ki sanar dani" na gyada mishi kai, yayi murmushi tare da cewa "good girl" fuskana ya matso daidai tashi tare da kawo bakin shi saitin nawa, ina fahimtar abinda yake shirin yi nayi saurin kauda kaina gefe ta yadda leben shi ya kare da sauka akan kumatuna ba lebe na ba, ya dago ya kalleni cike da alamun tambaya, da sauri na tashi na tattara kayan da yayi amfani dasu na kai kicin. Wanke su nayi tare da dora abincin dare, ya leko kicin din ganin ina girki yazo ya kashe gas din, a hankali na dago na kalleshi amma ban yi magana ba, kafada ya daga cikin alamun tsokana "hey chill! Ba sai kinyi girki ba yau, zan

fita in sayo mana abinci" sai kawai na juya na sauke tukunyar dana dora na zubar da ruwan tare da rabawa ta gefen shi na fita.

Ina gaban wardrobe dina ina shirya kayan ciki wadanda na ciro su daga ciki musamman saboda in dauke hankalina daga tunanika, Abbu ya sake shigowa dakin. Gefen gado ya samu ya zauna yayi tagumi tare da zuba min idanu wadanda seriously na dinga jin su a cikin jikina kamar me?? Kokari nake kawai naci gaba da aikina. Can kasan zuciyata ina so in mishi maganar, sai dai ina matukar tsoron abinda xai fito daga bakinshi, ina tsoron ya amsa min da ehh shine don a hakikanin gaskiya ban san ina zan jefa rayuwata idan hakan ta kasance ba.

Haka muka wanzu har aka kira sallar Magrib, Abbu ya tashi ya shiga toilet dina ya fito daure da alwala ya wuce masallaci, sai dana ga fitar shi sannan ne nima na dauro alwalar naxo na tada kabbarar sallah, anan kan sallayar na zauna bayan na gama ina laxumi har aka yi Isha'i

nayi sallah. Tashi nayi na nade abin sallar, ina ta en kimtse-kimtse na wanda a zahirin gaskiya basu da amfani ina yi kawai don kada su dauke mun tunani, Abbu ya dawo daga masallaci. Dakin kawai ya leko yace in fita mu ci abinci. Na fita falon na same shi har ya fiddo plates waje, naje gefen shi na zauna kawai.

Gashin nama ya xuba mana cikin plate din da yoghurt a cikin cups, na sa cokali muka fara ci daga cikin kwano daya. Ba wai don wani abu ko yunwa nake cin abincin ba, kawai saboda bana so Abbu ya dame ni da korafi ne don a lokacin ko kadan bana so inyi magana, gabadaya raina a jagule yake. Abu na karshe da nake bukatar yi shine in kadaice a waje guda in nemi mafita a cikin rayuwata data aurena gabadaya.

Duk da halin da nake ciki hakan bai hana ni jin dadin naman ba har ma ban san lokacin dana bude ciki naci naman sosai ba, sai dana ji cikina ya cika kafin na kora da yogurt din, lokacin Abbu ya ture kwanon gefe alamun ya koshi don haka na tattara kayan na kai kicin, sauran

kayan duk na saka su a cikin freezer na fita falo. Abbu yana zaune akan kujera yana kallon labaran kasa, na shige shi zuwa dakinshi da yake yanzu yawancin kayana ma suna dakin don ragewa kaina wahalar je ka dawo daga wannan dakin zuwa wancan. Toilet na shiga nayi brush na fito na shirya cikin kayan barci tare da fesa en turaruka na kwanta. Not that barci nake ji ko kuma gajiya, kawai ina gujewa Abbu ne.

Misalin karfe tara Abbu ya shigo dakin, ina jin alamun shigowar shi na kara lafewa akan gado kamar mai barci. Ina ji ya gama duk abubuwan da zai yi kamar su brush, shafa turare, sa kayan barci da sauran su. Ina jin lokacin daya kashe wutar dakin kafin inji alamun hawan shi kan gadon, na kara sakankance jikina sosai. Ina jin lokacin daya janyo ni jikinsa, duk da ihun da naji ana min a kunne akan in kwace jikina sharewa nayi, bana so inyi abinda zai sa Abbu yayi zaton idanu na biyu. Ina jin shi yana lalubata wanda da da ne tashi zanyi koda barcin nake yi in shige cikin kirjin Abbuna mai fadi, yau kam ban yi hakan ba.

Bayan lokaci mai tsayi naji alamun yayi barci, a hankali na zare jikina daga nashi tare da juya mishi baya, wasu siraran hawaye suna gangaro min a kumatu, ban san yaushe barci ya kwashe ni ba. Da asubahi Abbu ya tashe ni daga barci ya wuce masallaci. Ina kan sallaya ina karatu lokacin daya dawo daga masallacin, kan gado ya hau ya kwanta rigingine, ban motsa daga inda nake ba har sai da gari yayi sha, na rufe al-qur'anin na mayar dashi inda ake ajiye shi na fita daga dakin. Kicin na shiga na fara shirya break fast.

Abbu ya shigo kicin din, ina tsaye ina wanke hanta a jikin sink, ya tsaya a daidai gefena na dama. Kwana daya kacal daga ni har shi mun yi wani zuru-zuru damu, hannu yasa ya kamo habata a kokarin shi nason mu hada ido, sai nayi kasa da nawa idanun na hana shi ganin kwayar idanu na. Muryar shi tayi kasa sosai cike da damuwa yace “hey, me ke faruwa da ke ne Nafeesah?" na kara yin kasa da kaina na kasa magana, ya kara matsowa kusa dani sosai har ina jin saukar

numfashin shi a kaina, fuskana ya sake dagawa sama, “talk to me Nafeesah please..... Look at me" yadda yayi maganar kamar wanda yake rokona yasa na daga idanuna na kalli nashi idanun, tsananin damuwa da kulawa dana hanga a cikin idanunshi suka sa ban san lokacin da hawaye suka zubo min ba, sai dana ji dumin su akan kumatuna sannan na ankara...
Abbu ya ida hade er tazarar dake tsakaninmu tare da rungume ni kam a jikinsa, a hamkali ya kai hannu bayana yana shafawa a hankali alamun rarrashi, hakan ya kara karya min xuciya sosai... Na zagaye hannuwana a bayan shi tare da fashewa da kuka ba tare dana shiryawa hakan ba.....

Bayana yake tapping a hankali ba tare da yayi magana ba, ina jin yadda zuciyar shi take bugawa da sauri ban sani ba bacin rai ne ko tausayi na? Shi dai ya bar wa kan shi sani. Hannu yasa ya kashe gas din dana kunna, yaja hannuna ba musu na bi bayan shi muka fita daga cikin kicin din. Daki ya kaini ya zaunar dani a gefen gado

yayin da shi kuma ya zauna a kasa a gabana ina fuskantar shi.

Sai dana gama shesshekar kukan da nake yi da komi, ya tashi yaje kan mirror ya dauko tissue ya miko min, hannu nasa na amsa na goge fuskata dashi. Wajen daya tashi ya koma ya zauna ya kalleni..., “ok, ina sauraronki. Fada min, me ya faru??".

Idanu na kura mishi cikin tunani, shin in gaya mishi ko kuwa in yi shiru? Shin in nuna mishi hotunan ko kuwa zan ci gaba da boyewa ne ina kwarar mu?? Ganin nayi shiru ba tare da nayi magana ba yasa ya kara matsowa gab dani, ya kamo hannuwana ya damke cikin nashi tare da dora su akan cinyata, murya can kasa wadda ta dakushe cike da damuwa yace “Kalle ni Nafeesah!" na dan yi hesitating na en dakikai kafin na daga kai a hankali na kalli kwayar idanun shi, take jikina yayi sanyi sosai, na kasa daurewa kallon tsananin kulawa, so da kauna da suke cikin idanun shi sai na kara yin kasa da kaina.

Yace “Nafeesah, idan ban manta ba na fada miki cewa babu boye sirri a tsakaninmu, ba zamu boyewa junan mu Abu ba komi tsananin munin shi kuwa, amma meye yanzu kike yi? You are hiding something from me Nafeesah, kin saka ni cikin damuwa gashi na rasa gane matsalar balle in magance miki ita, please tell me Nafeesah, tell me me ke damun ki??" rikon da yayi min a hannuna ya kara karfi, ajiyar zuciya na sauke a hankali. That's it! I couldn't do this anymore, kawai bari inji ta bakin shi in yaso komi ta fanjama shi kenan.

Naja numfashi a hankali tare da tashi cikin sanyin jiki bayan na zare hannuna daga cikin nashi, ya juya ya bini da kallo. Drawer din na bude na ciro hotunan cikin faduwar gaba na koma inda yake, sai dana lalubi gefen gado na zauna kafin na mika mishi hotunan, ya kalleni sosai kafin yasa hannu ya karba, na kura mishi idanu sosai ina so in ga yadda zai karbi ganin hotunan..

Idanun shi suka fito waje sosai kamar wadanda zasu fado kasa, nuna su yake yi da hannunshi kamar wani tababbe, da kyar ya iya kakaro sautin “Naffee..sah.... Daga ina??..." cikin rawar murya yana nuna min hotunan, na kura mishi ido ina kokarin karanta kalar tsoro dana gani a cikin idanuwan shi, na tsoron asirin shi ya tonu ne ko kuma na wani abu daban?? Nace “ba kai bane ba koh Abbu??" na kura mishi idanu cikin tsananin tsoron jin amsar da zata fito daga cikin bakin shi. Kai ya girgiza min da sauri, “bani bane ba Nafeesah., I promise you bani bane ba!".

Wani irin sanyi ya xiyarci zuciyana da gangan jikina gabadaya, na silale daga kan gadon na fada cikin jikin shi na rungume shi kankam kamar zan tsaga shi, nadama ta shige ni sosai. Da ace tun a jiyar na mishi magana da hakika bamu yi kwanan rashin sukuni da bacin rai ba, da ace tun a jiya din na mishi magana da ban ji bugun zuciya da ya dinga yin kamar zai kashe ni ba, da ban kwana cikin dacin rai da fargaba ba..... Nasa kaina a cikin wuyan shi ina kuka a hankali wanda sautin

shi baya fita sai jikina da yake rawa saboda danne kukan da nake yi.

Abbu ya zaunar dani a kasan carpet din yasa hannu yana share min hawayen, sai da kukan yayi kasa kafin naji ya fara magana a nutse."waye ya baki hotunan nan? Yaushe kuma?" naja shessheka kafin nace "ban san ko wanene ba, kawai dai wani yayi mun sallama sai ya bani yace wai sako ne tun shekaranjiya, sai jiya ne na bude" ya kura min idanu kamar wanda yake mamakin abinda nace mishi.. Can yayi magana a hankali, "kuma shine kika boye min, why??"

Na girgiza kaina kawai, yace "look Nafeesah!" na daga kai na kalleshi, yace "na fahimci tsoron abinda zai biyo baya ne ya hana ki fada min. Naji dadin hakan kamar yadda naji haushin boye min din da kika yi. Daga yanzu kada ki sake yi mun irin haka don Allah kinji? Kome ya faru kada kiji tsoron fada min, ta haka ne kadai zamu gina rayuwar aure mai inganci irin wadda nake so kin gane??" na gyada mishi kaina a nutse.

Hotunan ya sake dagawa yana kara kallonsu daya bayan daya yana girgiza kai idanunshi jawur, “Wallahil-Azeem bani bane Nafeesah. Ban taba bin mata ba, ban taba kusanta kaina da zina ba, bane bani!” hannunshi na rike cikin nawa ina gyada kai, “wallahi na yarda da kai Abbu. Ban san me yasa na kasa fada maka ba tun farko, amma ba zan sake maimaita hakan ba” hancina ya dan ja a hankali yana dan murmushi, nima nayi. Hoto daya ya dago yana nuna min, “kalli nan ki gani” na kurawa hoton ido ina kallo, hoton Abbun ne a tsaye babu riga a jikin shi yayin da macen da aka nuno su tare har lokacin ba a ganin fuskarta a kwance akan gado, nace “me zan gani?” kirjin mutumin jikin hoton ya nuna min, “nan, kin ga babu alamun tabo dina” na kama baki cike da tsananin mamaki, ya aka yi ban kula da haka ba? Ba mamaki saboda idanuna sun rufe ne shi yasa. Wani tabo ne a kirjin Abbu kusa da kafadar shi, tabo ne babba wanda yace lokacin da yaji ciwon it took him almost 3 months kafin ciwon ya warke amma tabon yana nan, yanzu dana kalli mutumin jikin hoton sai naga babu

alamun tabon, kai karewa ma dana kare mishi kallo sam sai naga Abbuna yafi na jikin hoton kiba, to idan ba Abbu bane waye?.

Abbu ya kuta, “da alama wani ne yake so ya shiga tsakanin rayuwar auren mu Nafeesah, shine yasa aka yi photo editing din wani da fuskana aka kawo miki don ki tada balli, koma waye yayi haka ya gina ramin kuskure mai zurfi wallahi, I wouldn't spare him!”.

Wani tunani ya darsu a cikin raina, da sauri na kauda tunanin. Abbu ya kalleni “menene?” na girgiza kai, “m not sure don zargi bashi da dadi. Amma ranar da saurayin ya bani envelope din lokacin ina kokarin karya kwana, naga the same saurayin a tsaye shi da Dr Lubah... Ganin su kawai nayi, ban sani ba ko tana da hannu akan hakan?” Abbu ya dunkuke hoton hannunshi, “Dr Lubah!!! Zata aika, ta sha fada min zata yi duk abinda zata yi duk abinda zata yi wajen ganin cewa ta raba ni da farin cikina. Ban yi zaton da gaske take ba, I thought kawai tana fada ne don cika baki ashe da gaske

take? So she can stoop this low kawai don ta raba ni dake?” nace “ni fa kawai ganin su nayi tare, bani da tabbacin ko ita ce” yace “ki ma daina wani tantama, she's the one” nace “zato dai bashi da kyawu, kamata yayi ka bincika kafin ka yanke hukunci” yayi shiru kafin ya gyada kai, “haka ne kuma, zan bincika in shaa Allah.... Now.., food!” dan murmushi nayi tare da mikewa na nufi kicin shima ya biyo bayana.

Ranar tare dashi muka yi girkin, muka koma falo muka karya muna hirarrakin mu cike da nishadi, ranar ko nan da can Abbu bai fita ba, yana manne dani kamar chewing gum.Da haka rayuwar auren mu ta koma normal kamar, ko ma in ce fiye da da.

Bayan kamar sati biyu da yin haka, ina zaune a falo Abbu ya dawo daga office. Da murnata na tare shi, na taimaka mishi yayi wanka tare da cin abinci. A wajen cin abincin ne yake bani labarin yadda suka kare da Dr Lubah yace; “ai kin amsa laifinta tayi sai dana kai karar ta ga hukumar makaranta sannan, yanzu dai an mata warning

game da haka. Ance idan ta sake a bakin aikinta, shine fa bayan mun fito wai take bani hakuri wai sharrin shaidan ne, ni dai na gaya mata idan ta kara bari ma muka hada hanya da ita to ta tabbatar sai na kai karar ta" nayi dariya nace "ashe da gaske ita din ce dai?" ya girgiza kai, "ai ki daina wasa da lamarinta, matar bata da mutunci da kike ganinta. Sai da maganar ta kai ga sauran malamai nake jin ashe an taba kwantar da wata budurwa a asibiti data taba ganinta a tsaye ita da saurayinta, itace fa ta dauka ta maka mata a kai. Sai daga baya ma ake fada mata ashe er uwar saurayin ce, sanadin rabuwar su dashi dai kenan" na kama baki cike da mamaki, nace "to Allah ya shirye ta tare da masu hali irin nata" Abbu yace "ameen"...

A karshen watan muka koma ainihin gidan da zamu zauna. Wani dankareren babban gida a cikin Lamido Crescent, flat ne da dakuna bila adadin. Babban falo daya dauke saitin kujeru biyu, kicin, store, sai wani corridor wanda idan ka bishi zai sada ka da wani karamin falon inda anan Dinning yake sai dakunan much ni da

Anty Mubeenah. Dakin mu ciki ne da falo, sai dakin Abbu, na yara da kuma study room inda muke zuwa mu yi karatu abinmu. Komi na gidan sabo ne dal wanda Abbu ne ya dauki nauyin yin hakan, duk da dai akwai daki na musamman anan kusa da dakina wanda aka ajiye min jeren da Daddy yayi min.

Zaman gashi nan kadaran-kadahan. Muna zaune lafiya daga uwar har yayanta da maigidan, batun hali a wajen Anty Mubeenah har yanzu bata canza zani ba, tana nan kamar da da rashin kula da kanta, mijinta da rayuwar aurenta gabadaya. Abbu ya dauko en aiki wadanda suke zuwa suyi shara, goge-goge da sauran su, da kaina nake girki na in kuma gyara dakunan mu dana Abbu. Ina ji shi yasa hatta da yaran suke dokin zagayowar ranar girkina saboda dadadan abincin da nake dafa musu ba kamar abincin Harira da har lokacin tana manne damu ba.

Ranar va sai ga en uwan Anty Mubeenah a gidan ba?? Shakira da Umaimah kamar daga sama. Muna falo ina

koyawa Hafsy assignment lokacin, na daga kai da er fara'ata saboda nasan ba abin arziki ne ya kawo su ba, na gaida su. Suka amsa suna wani yatsine yatsine, wai “ina uwargida ran gida mai babban matsayi a gidan Ibrahim Galadanchi?” abin ma ya bani dariya, na girgiza kai kawai. Umaimah taja tsaki, “kamar fa wannan dangin masu kwacen mijin kallon uku-saura take mana, irin wuyanta ya isa yanka dinnan” Saddiqar tace “kyaleta, karyar banza take. Yo ni Allah
na tuba idan da ba don albarkacin Mubeenah ba wannan er tsakin ta isa in kalleta? Taci gaba da abinda take yi wallahi yanzu zan kwantar da mutum a kasa”.

Daidai lokacin Anty Mubeenah ta shigo falon, ganin en uwanta ta hau fara'ah, Umaimah tace “yauwa Yaya, wannan er iskar matar fa tana nema ta raina mana hankali, kinga wani kallo da take jefa mana ni da Anty Saddiqa??” Mubeenar ta kalle su kafin ta sake kallona, dan murmushi tayi ni na ma yi zaton ko zagi zata auna min, sai kawai naji tace musu “ko zo muje daki mana” da alamu suma abin ya basu mamaki ganin yanda suka

hangame baki, can Saddiqa ta gyada kai, ta jefa min harara ta shura takalmi tayi gaba Umaimah tabi bayanta, Anty Mubeenah ta kallemu tace “kiyi hakuri fa!” tayi gaba ba tare da taga yadda na hangame baki a dimauce na bita da kallo ba, abin ya matukar bani mamaki kwarai ba kadan ba. Nayi zaton zata goyi bayan en uwanta ne su hadu su zageni kila ma har da duka kamar yadda naji ana bada labari, sai naga akasin haka, har da bada hakuri ma. Na jinjina kaina tare da tsintar kaina ina mata addu'ar Allah ya dawo da ita kan hanya.

Da zasu tafi ma haka suka same mu a falon ni da Hafsy, ko er Allah ya kiyaye hanya din da na musu Allah bai basu ikon amsawa ba. Na tabe baki tare da daga kafadata, basu dameni ba ko Kaden, in dai muna zaman lafiya da abokiyar zama na to shikenan ni kam.

Ba a wani jima ba aka yi auren Harith shi da Ikram, na samu da kyar an bar ni naje wajen daurin aure. Wannan shine zuwana Kaduna na uku tun bayan da aka min Aure.

Ni'imah ta haifi santaleliyar yarinya mace taci sunan Halima mahaifiyar Basheer sai suke kiranta da Amal. A daren ranar ina kwance akan gadona a gajiye Abbu ya shigo dakin da yake ranar girki ta ce. Kan gadon ya hayo ya dauki kafafuna ya dora akan cinyoyin shi ya fara matsa min su, idanu na lumshe tare da kara lafewa akan gadon. Abbu yace "dube ta don Allah! Sai kije kiyi ta faman yin aiki da kai da kawo sai dare yayi kuma kizo ki dinga min raki" cikin muryar barci nace "to Abbu menene a ciki, yiwa wani yiwa kai balle su Ni'imah ne fa, idan na hidimta musu kamar kaina na hidimtawa" ya kuta, "just wait and see, idan kika haihu duk wadda bata miki wahalar da kike musu ba sai na bata musu rai" dan murmushi kawai nayi tare da maida idanuna na lumshe.

Ya juyo dani na koma rigingine, hannu ya kai yana dafa cikina, “wai ni tsaya, har yanzu ban yi ajiya anan wajen bane duk kokarin da nake yi?? Lokaci ya fara ja fa, muna bukatar jin kukan jarirai a gidan nan” nace “Allah bai kawo ba har yanzu Abbu” yace “ki ce in kara kaimi kawai” da sauri na girgiza kai, “a'ah, ba sai ka kara ba wallahi. Zan taya mu addu'ar Allah ya kawo su kawai Abbu” kai ya girgiza kamar wani karamin yaro, “naki wayon....” wuta ya kashe mana tare da janyo ni cikin jikinsa...

BAYAN SHEKARU BIYU DA RABI!

Na fito daga dakin Abdullahi hannuna dauke da tarin kayan wankin dana fiddo mishi. Duka yaran suna zaune akan kujera, Abdullahi da Qaseem suna game na Super Mario, Hafsy kuma tana wasa da wayata. Anty Mubeenah kuma tana gefen Hafsy tana duba jarida.

Abdullahi ya kalleni yayin dana harare shi nace “kalleshi dirty guy kawai, sai aukin fi'ili da gayu, idan ya dau wani

wankan sai kayi zaton abin har dakin shi ne sai ka shiga labari ya sha babban” Abdullahi yayi kasa da kai yayin da Qaseem yasa dariya, shima na harare shi.., “see who's laughing! Jiya dana shiga dakinta kasa numfashi nayi sai dana sa mask, wai anya kuna ma yin wanka??” Anty Mubeenah ta dan saki dariya, da sauri na juya na kalleta. Ganin ina kallonta yasa ta dauke kanta da sauri, nayi dan jim ina kallonta.

Kwanaki biyun nan ina ganin wasu canji a tare da ita, fuskarta tayi rama sosai, haka zan ga ta zauna tayi shiru cikin tunani gashi har zuwa lokacin bata bani fuskar da zamu yi sabon da zan tambayeta abinda yake damunta ba. Damuwar da take ciki na damu na, I really want to help. Na juya kaina daga kanta a hankali na tunkari kofa, Shuaibu mai mana wanki da guga na ba kayan na koma falo.

Na kallesu, “daga yau duk wanda ya cire kaya kar ya kuskura ya maida su cikin drawer, a sa a laundry bin sai a wanke, kuna ji na? Manya daku saboda Allah amma

wallahi Hafsy ta ma fiku tsafta” Abdullahi ya turo baki yana hararar Hafsy da take mishi gwalo, yace “ai saboda ita gyara mata daki ake yi, mu fa?” na Harare shi, “saboda ita yarinya ce, ku kuma kun girma, kayan da aka cire should always be put in a laundry bin ok??" suka gyada kai, nace “good!" na wuce dakina.

Ina shiga karan wayata ya min oyoyo, na dauki wayar tare da duba sunan mai kiran, ganin waye yasa na dauka da shakiyanci na “amarya, amarya!!" daga can cikin wayar Ramlah ta amsa, “ke dallah can! Aure fiye da wata biyar amma kina wani ce min amarya?" watanni biyar da suka wuce muka sha bikinta ita da Ayan wanda ana daurawa suka wuce states inda a can ne yake aiki, bayan bikin da wata daya muka gama karatun mu, yanzu dai fitar sakamako muke jira kawai.

Nace “habawata biyar ne fa kawai ba wasu watanni ba, Allah na tuba ni ko da ‘yayan ki ma amarya zan dinga ce miki" taja tsaki, “to Allah ya kyauta miki, ya zancen turarukan da na turo miki? Kin amso su kuwa?" nace “ai

da kanta ma ta kawo min har gida, Masha Allah sun yi kamshi sosai, kuma suna da kyau wallahi" tace “ai sai dana fada miki, yanzu ya za ayi wajen sauran abubuwan nan da nace a kawo min?" nace “idan na hada komi zan kira ita Nadiya din, sai ta taho miki dasu koh?" tace “to shikenan... Ina Abbu?" nayi murmushi, “Abbu yaje Beijing, suna da wani meeting ne a kamfani shine ya tafi" tace “ranar nan ai na kalli show din da aka bashi award din best prof na Universities din fadin Nigeria, naji ana maganar bashi VC a BUK koh?" na gyada kai, “yeah, he deserve it ai" tace “indeed, ana fadar ayyukan shi da sadaukarwar shi indai ta fannin karatu ne ai, Allah ya kara taimako" na amsa da “ameen" daga haka muka yi sallama da ita.

Toilet na fada na dauro alwala na fito nayi sallar La'asar, bayan na gama na hau en gyare-gyare a dakin babu kakkautawa da yake ba wani aikin yi ne dani ba duk da cewa ranar girki na ce dai. Wajen karfe biyar na tashi na shiga kicin din, Anty Mubeenah tana tsaye a gaban gas cooker da frying pan akai da alamu tana frying abu, na

kalleta cike da mamaki ita kuma ta kalleni da blank expression, tunda muke da matar nan sai ranar na taba ganinta a kicin wai da sunan girki, sai na dake kawai na shiga cikin store na fito da duk abubuwan da zan bukata. Da yake babban kicin ne, kuma yawanci komi na amfani a kicin din guda biyu ne sai na kunna wani gas din na fara girkina. Cikin kankanin lokaci kamshi ya bade ko'ina na gidan, ta gefen ido nake kallon Anty Mubeenah ina wasi-wasin dalilinta na yin girki yanzu. Har ta gama soya dankalin ta juye a cikin plate ta kashe gas din ta fita, na tabe baki naci gaba da aiki na. Ba a jima sai gata ta fado kicin din, ta tangwarar da plate din a cikin sink ta juya kamar cikin fushi.

Sai dana gama girkina idanu na ya sauka akan dankalin, na dauki kwara daya na kai bakina, frowning nayi. Dankalin tauri kamar danye ga dan banzan gishiri da yaci. Na gyada kai a hankali tare da zubar da dankalin na wanke kayan dana bata naje na jera girkin na shige daki. Wanka na fara yi kafin nayi sallah na jira aka kira Isha'i nayi kafin na fita falo muka fara dinner. Tun a

wajen jikina ya fara rawa, sanyi yake shigar ko wace kofa ta jikina sosai.

Hafsy ta kalleni tace “Anty Nafee, jikinki rawa yake yi baki da lafiya ne?" nace “zazzabi ne, yanzu zan shiga in sha magani ai" tayi shiru tana kallona, can tace “ko dai in kira Anty Raliya?" nayi saurin cewa “a'ah da wannan daren? Mura ce take shirin kama ni zan sha magani" tace “to Allah ya sauwake" bayan mun gama cin abincin muka dan yi kallo kowa ya wuce dakin shi. Shirin kwanciya barci nayi naja bargo na rufe jikina, rawar sanyi nake yi ina jin kamar an watsa ni cikin ruwan kankara hakorana har haduwa suke yi waje guda. Ina cikin wannan halin Hafsy tazo ta same ni, da sauri ta hayo kan gadon tana jijjiga ni amma na kasa daga kai in kalleta, fita tayi da sauri sai gata ta dawo ita da Anty Mubeenah. Da sauri ta dago ni tana tamvayar lafiya?? Ganin na kasa yin magana yasa ta hau daga drawers har ta lalubo paracetamol, Hafsy ta miko ruwa Anty ta bani maganin nasha na koma na kwanta. Ba a jima ba barci ya dauke ni, ban san sanda suka bar dakin ba.

Da asubahi koda na tashi babu zazzabin sai mura data min mugun kamu, nayi sallah ina ta atishawa da tari ba kakkautawa. Na shirya break fast na kai kan dinning na ajiye, ina cikin shiryawa din Anty Mubeenah ta fito daga dakinta, nan ta min ya jiki na amsa da sauki tare da mata godiyar dawainiyar ta a gare ni a daren jiya, ta wuce dakinta. Nima dakina na koma na kira Abbuna muka sha hirar mu har sai da Hafsy ta leko ta kirani sannan muka yi sallama na fita muka karya. Yaran makaranta suka wuce ni kuma na zauna anan falo ina kallo Anty Mubeenah kuma ta shige dakinta, na kula kwana biyun nan bata cika fita ba.

Wajen karfe goma na safe sai ga su Anty Ameenah da Anty Rahila sun zo wai ashe Hafsy ce ta kira su a waya tace musu bani da lafiya, na kama baki ina dariya nace “Lallai ma Hafsy! Zazzabi ne nayi jiya da dare fa, mura nake yi sai kuma nayi wankan yamma ina jin shine ya saukar mun da zazzabin, amma shine har da shela??" Anty Raliya tace “ai ba shela bace ba Nafeesah, gaskiya

ce. Idan wani abu fa ya faru??" nace “babu abinda zai faru ma in shaa Allah. Ai Hafsy din da Anty Mubeenah suka kula dani" na lura da kallon mamakin da suka jefe ni dashi kafin suka basar, Anty Ameenah tace “To Allah ya kara lafiya" nace “Ameen" sai ga Anty Mubeenah ta fito, nan ta samu waje ta zauna suka gaisa, basu jima ba suka mana sallama suka tafi suna jaddada min idan dai naji ciwon ya dawo in kira su fa, nace toh.

Mun fito daga cikin jifatu ni da Hafsy mun je shopping, ina kokarin bude mota mu shiga naji an kira sunana daga bayanmu cikin wata irin murya da naji kamar na san ta, “Nafeesah??" ga namaki na koda na juya Muneer na gani a tsaye, dauke a kafadar shi wata dan yaro ne zai kai kimanin shekaru hudu kila. Ya matso yace “Allahu Akbar! Ashe dai ke din ce, ya kike?" nayi murmushi, shekaru masu yawa sosai rabon da mun hadu kenan tun ma kafin in bar Kadpoly. Nace “lafiya na qalau Muneer, kai fa?" ya kalli Hafsy dake tsaye a gefena tana kallon

shi cikin alamun rashin sanayya, yace “diyar ki ce?" ni abin sai ma ya bani dariya, ya kalli zankadediyar budurwa kamar Hafsy yace wai diya ta?? Nace “ehh, baka ga muna kama ba?" sai yayi er dariya, ya nuna min yaron hannunshi yace “dana kenan, Suleiman... Ke fa?" na daga kafada, “Allah bai kawo ba har yanxu" yace “to Allah ya kawo masu Albarka" nace “Ameen" daga haka muka yi sallama kowa ya shiga motar shi yaja. A cikin mota nayi murmushi tare da gyada kai cikin kara sakankancewa da Girma na Subhanah! Lallai Hausawa sun yi gaskiya da suka ce wani baya auren matar wani kamar yadda wani baya haihuwar dan wani...

A daren ranar misalin karfe sha daya na dare na fito daga dakina da niyar zuwa kicin dauko ruwa, naci karo da Anty Mubeenah Zaune akan kujera cikin duhun falon wanda hasken dake waje ne daya dan shigo ta labulaye yasa na ganta, da farko tsoro ta bani kafin na dan matsa zuwa gabanta nace “Anty Mubeenah baki da lafiya ne?" ta dan dago a firgice ta kalleni kafin ta kauda kai, kai ta girgiza tace “lafiya ta qalau... Babu komi" kamar zan yi

magana sai na fasa, na tunkari kicin kafin in dakata dalilin kiran sunana da tayi “Nafeesah...!" na juya a hankali na kalleta “ma'am?" ta dan daburce, “umh... Koda yake ma ba komi, je ki kawai" na juya naje na bude fridge na dauko ruwa mara sanyi na sha anan cikin kicin din na maida goran ciki na fita.

Har lokacin Anty tana a yanayin tagumi kamar yadda na fara samunta daga farko, har zan wuce sai kuma na fasa. Na koma kusa da ita na zauna sosai ina fuskantar ta, hannunta na kamo cikin nawa na rike, a hankali nace “Anty Mubeenah..."...

Nace “Anty Mubeenah.... Ni ba karamar yarinya bace ba, kina cikin damuwa naga hakan rubuce akan fuskar ki. Kai ko makaho ya shafa ki yasan cewa kina cikin damuwa.. Nasan cewa ban kai matsayi ko girman da zan zama abokiyar shawarar ki ba, amma idan kina ganin babu damuwa kuma zaki iya, y can't u just tell me?? I'll be a good listener and a judger" tayi shiru tana kallona cikin nuna can I trust you? Na kai daya hannuna na shafa

bayan hannunta ina mata murmushi reassuringly, nace “trust me, wallahi u r safe with me... Ki yarda dani".

Numfashi ta ajiye a hankali, “na yarda dake Nafeesah, ke mutum ce ta gari mai hankali da natsuwa. Ina tunanin kila ki tsane ni akan abubuwan da na aikata...!!" tayi shiru tana kallona nima na kalleta ban yi magana ba sai data yi radin kanta kafin taci gaba da magana.

“Kamar yadda nasan cewa kin kula da yanayin zamana da Ibrahim Zama ne kawai muke yi wanda babu armashi ko na kankani. Auran hadi aka mana da Ibrahim ba tare da son mu ba, lokacin ina da wanda nake so. Haka aka kaini gidan Ibrahim ba don naso ba tunda duk yadda naso inyi akan kada ayi auren abin ya faskara. Ibrahim yana kyautata min a matsayin shi na wanda baya so na ma, amma ni na kasa yakar zuciyata akan ta so shi. Ina can ina karewa Mahmud wanda nake so mutuncina wanda kullum sai mun yi waya dashi ya jaddada min in rike mishi amana dai. Duk batanci na duniya babu kalar da ban yiwa Ibrahim akan ya sake ni ba amma yayi biris

dani hakan shi yake kara min jin kin shi a raina. It took us almost a year kafin mu kusanci juna, shima ni da kaina naji ina son yin hakan na kai kaina gare shi. Daga nan muka ci gaba da rayuwar ma'aurata amma fa idan naga dama don wani lokacin ko ya neme ni ma sai inyi refusing dinsa, idan kuma ya matsa to sai dai ya biya ni kudin sannan..." tayi shiru hawaye ya zubo mata, yayin da nake jijjiga kai cikin mamaki. Ban taba zaton cewa alakar Abbu da Anty Mubeenah tayi muni irin haka ba, Anty taci gaba...

“Cikin haka na samu cikin Abdullahi, yeah naji dadin samun cikin saboda a lokacin zugar en uwana tayi tasiri akaina da suka ce idan na fara haihuwa a gidan Ibrahim yayana zasu zama magada saboda duk da cewa a lokacin yana karatun masters, amma yana da kudi don bai dogara da kudin mahaifin shi ba, ya dogara da kanshi. Sai dai bayan haihuwar Abdullahi da wata takwas dana kara samun wani cikin mai dan banzan wahala sai naji ina dana sani akan amincewata akan haihuwa. Mun sha danbarwa da Ibrahim akan cikin nan,

nayi yunkurin zubar dashi sau ba adadi Allah ya nufa sai da yazo duniya. Wallahi Nafeesah sai da muka tsadance da Ibrahim ya biyani sannan na shayar da jaririn. Watan shi bakwai na yaye shi, babu ruwana da harkar yaran su duka shi yasa zaki ga shakuwar mu dasu bata yi zurfi sosai ba kamar yadda suka shaku da Ibrahim.

Bayan shekaru biyu na sake haihuwar Hafsy, daga nan ne naje asibiti aka saka min loop a mahaifa ta saboda bana son haihuwa da Ibrahim...."

Na zaro idanu waje sosai cikin tsananin mamaki, “loop Anty?" ta gyada kai, “abin ya ba Ibrahim haushi sosai, ya jima yana fushi dani kafin ya sauko ya hau lallashina akan in je a cire min ni kuma nayi biris dani har ya gaji ya daina yace zai karo aure, at first na firgita da jin haka daga karshe da naji shiru sai nayi zaton cewa tsakuwa ce yake taunawa don aya taji tsoro sai kwatsam naji zancen auren shi da ke. In fada miki na firgita ma bata baki ne, na shiga shock bana kadan ba sai dai na cije saboda a gani na bana son Ibrahim meye nawa na jin

haushi don zai kara aure? Sai daga baya na fahimci I was wrong! Ina son Ibrahim rashin kulawa irin nawa ne ya hana ni gane hakan, sai daga baya ne bayan ya daga min murya a karo na farko a tarihin rayuwar auren mu, sannan na fahimci halin da zuciyata take ciki game dashi amma ban san ko ta wace hanya zan sanar dashi ba Don haka naja bakina nayi shiru. Amma a en kwanakin nan gabadaya na rasa abinda yake min dadi, shi kuma kamar ya sani, yanzu ko kiran shi nayi a waya baya dauka ma. Zuciyata tana azabtuwa da hakan ba zan iya cigaba da jurewa ba, amma da wani ido zan kalli Ubangijina bayan abubuwan dana aikatawa mijina? Tell me, bayan duk my man and abubuwan nan dana aikata, da wani ido kike so in kalli Ibrahim??".

Na kalleta tun daga sama har kasa, tabbas ta banbanta da Mubeenar dana sani a da. Wannan Mubeenar ba wadda take cike da self esteem bace, sai wata Mubeenah wadda nadama take nukurkusarta. Tausayinta ya mamaye ni matuka.

Nace “kada ki ce haka Anty, shi Allah Gafurur-Raheem ne, yana yafe kuskuran damu muka aikata a gare shi matukar tuban muke nema da gaske. Abbu ma haka ne, ina tabbatar miki da cewa shi zai fi ma kowa jin dadin canzawar ki Anty" ta kalleni da sauri, “da gaske?" na gyada mata kai ina murmushi. Tace “to yanzu me kike so inyi?" nace “abu na farko daya kamata kiyi shine kije ki cire loop din jikinki, bayan hana haihuwa yana da side effects a jikinmu ba kadan ba, bana tantama kibar jikinki loop ne ya assasa miki ita" ta gyada kai cikin nuna yarda da abinda nace, “nima nayi tunanin haka. In Allah ya yarda gobe zan koma asibitin a cire min" nayi murmushin jin dadi, “we will do the other things later then... Bari inje in kwanta haka nan" na mata sai da safe na wuce.

Har na kusa kofata naji ta kira sunana, “Nafeesah!" na juya a hankali, “it was not bad opening up to you.." nayi murmushi sosai, “Anytime Anty" na shige dakin tare da rufo kofata na koma kan gado na kwanta. Tunanin yadda muka kare da Anty na dinga yi, na tsinci kaina da

addu'ar Allah yasa ta dore a haka, Allah kuma ya bamu zaman lafiyar da a kullum nake mana addu'ah. Da haka barci ya dauke ni cike da mafarkai iri-iri, mafi yawa daga cikin su shine na wani kyakkyawan yaro da yake bina da tuffa a hannu, na tashi da dan murmushi a fuskata. Addu'a nayi na shafa a fuskata na tashi na fada toilet na dauro alwala nazo nayi sallah.

Da yake ranar Anty ta karbi girki, ban fita falo ba sai da karfe tara tayi. Yara sun tafi makaranta, dana tambayi Harira Anty Mubeenah tace tace a fada min ta tafi asibiti, nayi murmushi kawai. Abinci na zauna naci, nayi gefe da plates din a zuciyata ina raya lokacin barin Harira gidan yayi.

Lokacin da Anty ta dawo har dakina ta leko ta same ni, tace “sun rubuta min magunguna in sha na sati daya sai in koma a cire min" nace “to Allah yasa mu dace" tace “ameen."

Daga ranar alakar mu da Anty Mubeenah ta canza, su kansu yaran sun yi mamaki kuma sun ji dadin hakan kada ma dai Abbu yaji labari wanda nake updating din shi da duk abinda ke faruwa. Ni'imah ta sake haihuwar diya Mace, a ranar muka je muka yi barka ni da Anty Mubeenah. A cikin mota muna dawowa nayi shiru ina tunanin anya a duniya zan ma haihu kuwa? Na tuna ina cikin shekarar aure ta uku kenan zuwa hudu amma har yau shiru babu bayani ko batan wata ban taba yi ba. Mommy tace wai itama hakan ce ta faru da ita, sai a cikin shekararta ta biyar ne sannan ta samu cikina, nayi ajiyar numfashi a hankali ina addu'ar idan da rabona Allah ya kawo masu albarka.

Anty Mubeenah taje an cire mata loop din, sai dai ance sabida jimawar abin a jikinta babu wata kulawa irin yadda ya kamata, ya taba mata mahaifa saboda haka da kyar mahaifar ta iya daukar ciki nan gaba. Hankalinta ya tashi kwarai da jin haka ni na dinga kwantar mata da hankali har ta nutsu. Ni na bata shawarar shiga From My Kitchen Institute da yake Allah ya budawa mai

makarantar Hadiza Dogon Daji ta bude reshe anan Kano bayan na Abuja, inda ta fara koyon salon girke girke ina kuma taimaka mata da wasu abubuwa. A gefe guda kuma na dora ta akan weight loss da slimming. Kullum muna gym muna aikin motsa jiki. Abbu ya dawo yayi sati daya ya tafi wata seminar inda daya dawo za a bashi VC.

Cikin wata daya kacal idan ba mugun sanin Anty Mubeenah kayi ba idan ka ganta a hanya ba zaka gane ta ba. Wannan kibar marar fasali da rashin gyara duk ya tafi babu shi, ta dawo tayi wani fresh da ita Masha Allah! Duk da dai har yanzu da sauran kibar amma ta ragu sosai. Musamman ta siya form din wata islamiyah anan bayan gidanmu inda take zuwa daukar karatu kowace rana da yamma, karfe hudu zuwa shida. Ko a yanzu kam Alhamdulillah! Zama na da kishiyata ya canza, idan ka ganmu zaka yi zaton cewa wasu shakikai ne ba kishiyoyi ba.

Result dinmu ya fita, sakamako yayi kyau sosai. Nayi clearance da komi, Abbu kadai nake jira ya dawo in nemi izinin shi in fara aiki da Lab din Aminu Kano Teaching Hospital.

Muna zaune akan dinning muna cin abinci, ranar Anty Mubeenah ce mai girki kuma ita ta dafa mana abincin da kanta don tuni muka sallami Harira bayan mun danka mata kudi masu tsoka da zata ja jari dasu, duk da cewa har yanzu dai sai a hankali amma she's improving sosai. Ta kalli plates dinmu, Jollop spaghetti da sauce din hanta, soyayyiyar agada, da coleslaw. Ita kuma nata taliyar ce kadai sai tulin vegetables akai, ta kai spoonful of cabbage bakinta ta taune ta hadiye da kyar, ruwa ta tsiyaya ta kai bakinta. “Nafeesah! This is a torture wallahi! Haba!! Wata na nawa bani da abincin daya wuce kabeji? Gaskiya na gaji haka nan wallahi, I want to eat chicken!!" ta fada da karfi tana watsa hannuwana sama kamar wata yarinya, aikuwa nan muka samu abin dariya, ni da yaran muka kwashe da dariya sosai, ta nuna mu da yatsa “dariya ma kuke yi koh? Just wait

nauyina ya dawo 65, idan na fara cin nama a gidan nan..." Qaseem yace “Mommy, Anty Nafeesah tace ko kin kai 65 din sau daya zaki dinga cin nama a sati fa!" ta harare shi, “inji wa? Kai dai ku jira in rage nauyin, babu wanda zai hana ni cin nama" ni dariya ma ta hana ni magana. A haka dai muka gama cin abincin cikin raha, na taya Anty Mubeenah muka kwashe kayan muka kai kicin muka wanke, daga nan na koma daki na kwanta wai in dan runtsa kafin La'asar tayi.

Ihun yara na jiyo a falo suna ga Abbu, haba! Na dira daga kan gadon da sauri na fita. A karamin falo muka ci karo dashi, tsaye a tsakiyar su Hafsy cikin suits bakake da farar shirt, na danne dokin in rungume shi da naji naje gefen shi kawai na zauna ina murmushi. Sai da yaran suka gama murnar su ya basu chocolates da tarkace ya tura su dakinsu sannan ya juyo gare ni.

Nade ni yayi cikin jikin shi cikin tattausar rungumar nan tashi. Nima na mayar mishi da wadda tafi tashi taushi, mun jima a haka muna jin dumin jikin juna kafin na zare

jikina daga nashi a hankali, na kalleshi ina dan murmushi, “ya hanya?" ya jingina kan shi da jikin kunya, “it was tiresome but Alhamdulillah tunda na iso lafiya" nayi murmushi “you must be kam... Yakamata ka watsa ruwa koh?" na mike da brief case dinshi a hannuna.

Ya mike shima yana sassauta neck tie din wuyan shi, daidai lokacin Anty Mubeenah ta fito daga dakinta. Sanye take da doguwar rigar Shadda wadda tabi jikinta sosai, now that I look at her very well, tana da diri da halittun jiki Masha Allah. Haka kawai naji wani abu ya makale min a wuya ganin yadda Abbu ya saki baki yana kallonta yayin da take kallon shi cike da so da kewa. Ganin kallon nasu ba mai karewa bane ba yasa na danyi gyaran murya sai lokacin suka dauke idanunshi a kan juna, na danne takaicin daya zo mun wuya nayi dan murmushi tare da cewa “dama wanka wai zai je yayi, amma tunda gaki bari in barku tare, inje in dan kwanta" na mikawa Anty brief case din, ban jira sun ce wani abu ba na shige dakina da sauri na maida kofar na rufe.

Numfashi na dinga ajiyewa da sauri kamar wadda tayi tsere, tabdijam! Idan har haka zan dinga ji idan naga Abbu tare da Anty Mubeenah to akwai matsala, lallai yakamata in san abin yi.

Da dare muka hadu a dinning wajen cin abinci, daga jin taste din abincin nasan cewa Anty really put her best effort don kuwa yayi dadi sosai, duk yadda taso taja Abbu da hira a wajen abun ya faskara har naji ta bani tausayi, sai dai wani sashe na zuciyata na raya min cewa kawai burga ce yake yi, amma a dokance yake da ita, hakan shi yake kara tunzura ni.

Bayan mun ci abincin muka hada kan komi muka kai kicin muka dawo falo, Abbu da yaran shi suna hirarrakin su, sai muka ja kujera ni da Anty Mubeenah muna tamu hirar har wajen karfe tara da rabi, na tashi na musu sai da safe na shige dakina.

Wanka nayi na dauro alwala, anan cikin bayin nayi shafa ina karfafawa kaina gwiwa daga munanan tunanika da

zuciyata ke kitsa min, babu abinda ya canza, Abbu yana nan a yadda yake kamar yadda Anty Mubeenah take, nayi dashe a zuciyar Abbu wanda babu wata 'ya macen data isa ta dakusar min dashi, sai dai ta nemi wani gurbin tayi nata dashen, da wannan naji karfin gwiwa ya shige ni. Don haka koda na fito nayi tozali da Abbu akan gado, murmushi nayi naje gefen shi na zauna. Lafiya lau muka yi sallama dashi, na raka shi har bakin kofa ya tafi bayan ya manna min pecks a kumatu da goshina. Na maida kofar na rufe, kan gado naje na kwanta na janyo wayata nayi en dube-dube da chatting har dare yayi kafin na kashe wayar nayi addu'ar kwanciya barci na shafa. Filo na janyo na rungume a kirjina na rufe idanuna, can kasar zuciyata Istigfar na dinga janyowa da hailala saboda korar shaidanin dake saka min abubuwa a cikin raina...

Alhamdulillah! Rayuwa mai cike da inganci da zama lafiya muke shimfidawa mu da mijinmu. Mun hade kawunan mu waje guda domin samun kwanciyar hankalin mijinmu. Yes, akwai kishi, sai dai kishin zamani

muke shimfidawa ba wai na dabbobi ba, kowa tana iyaka kokarinta wajen ganin ta faranta ran mijinta domin samun ragamar zuciyar shi don haka a takaice dai Abbu ya zama sha lelen mu.

Lokacin Hajji yazo, Abbu ya biya mana kujera mu duka banda Hafsy, muka je muka sauke farali. Bayan mun dawo naje Kaduna nayi kwana daya na dawo muka ci gaba da gudanar da rayuwar mu a nutse.

Kallon shi nake yi idanuna na shekin bacin rai da tashin hankali, "ban gane ba? Kamar ya ba zan yi aiki ba, akan me??" tunda muka dawo daga aikin hajji na dame shi da maganar son fara aikina amma yayi biris dani, sai ranar ne ya bani amsa da cewa ai ba zai barni wae inyi aiki ba, duk wahalar dana sha!.

A nutse ya kalleni cikin sanyin murya mai cike da lallashi yace "to menene abin tada jijiyar wuya kuma? Kin dai san cewa ba tun yau ba nasha fada miki cewa bani son mata na su yi aiki, nafi so su zauna a gida su kula min da gidana da iyalina. Beside Nafeesah baki nemi komi kin rasa ba a gidannan, aikin me kuma zaki je kiyi saboda Allah?"

Na cure baki waje guda ina yamutsa fuska, "to ni nace ne dama saboda kudi zan yi aiki ne? Kawai sabida ina so inyi aikin ne, m bored to death! Baka barina ina fita ina ganin mutane sai abu mai muhimmancin gaske ya taso, baka barina inje gidanmu in musu kwanaki sai dai wuni.... Ni wallahi idan ba so ake yi mutum kadaici ya kashe shi ba a bar shi yayi aiki!"

Kallona yake yi baki a dage cike da mamaki, tun da muka yi aure iyakata da Abbu Nafeesah yi kaza, ince toh., ko kuma Nafeesah ba zaki yi kaza ba ince toh. Amma yau yaga gabadaya na wani canza ne, abinda bai taka kara ya karya ba, maganar aiki ba tun yau ba yayi

making it very clear ba zai bar matar shi tayi aiki ba amma gashi ina tonon fada da maganar.

Na kawar da kaina daga kallon da yake min na mamaki, “a’ah! Yo mutum sai yaki fadin gaskiya haka kawai! Idab ma bazan yi aikin ba a dinga barina ina fita mana, amma kullum ni a garkame a gida kamar wata furzuna? Da yake ita er gaban goshi ce naga babu ranar banza da ba zata fita ba amma ko a jikin ka sai ni, me nayi maka ne saboda Allah??" kwalla ta ciko idanuna, da sauri na juya na shige dakina. Kan gado na kwanta ina ajiyar numfashi idanuna a lumshe. Kwana biyun nan zuciyata a wuyana take, kome aka yi da wanda ya kai da wanda bai kai bama jin haushin shi nake yi. Na dan ja siririn tsaki, meye ma na wani sako zancen Anty Mubeenah? Duk da cewa dai abin yana ci mun tuwo ne a kwarya, kun ganta nan kullum tana waje yawo, yawace-yawacen nan nata har lokacin bai ragu ba, karewa ma watarana sai ta fita sannan take fada mishi duk da cewa dai an samu saukin kin fada mishi da bata yi. To ni kuma Fisabilillah kullum ina garkame a gida, idan yara suka

tafi school Anty ma ta fita ni kadai ake bari inyi ta gantali a cikin gida, abin ya dame ni sosai.

Ina jin lokacin da aka taba kofa alamun an shigo cikin dakin, bayan juya baya da nayi sai na lumshe idanu na. Ya zauna a gefen gadon da nake kwance, yace “wai Nafeesah me ke faruwa ne? U never go against my words n you never raise ur voice on me, naga maganar aikin nan fa tun ba yau ba na fada miki cewa ba zan iya barin mata ta tayi aiki ba. Mubeenah tana da degree akan computer science ni na hana ta aiki but in return sai na bude mata saloon din can, ba gashi yanzu komi ya zama even ba? I'll do the same to u, Dan Allah kar ki maida maganar nan ta zama babba ranmu ya baci Nafeesah!"

Nayi shiru kawai ina sauraronshi. A en kwanakin nan kwata-kwata zuciyata a wuya na take, abu da wanda ya kai da wanda bai kai ba sai inji raina ya baci, akwai ranar da ina jan jagira hannuna ya kubceta bata mun fuska, wani irin bacin rai ya ziyarce ni a lokacin, duk abubuwan

da suke kan dresser din sai dana yi wurgi dasu suka fado kasa, abin zai baku mamaki da dariya idan kuka ga yanda na tsaya a kansu ina wani huci kamar tsohuwar macijiya, sai daga baya da fushin ya tafi kuma na dawo ina dariya da tu'ajjibi. Akwai kuma ranar da kadan ya hana in mazge Hafsy saboda nayi abinci tace gishiri yayi yawa, bayan a hakikanin gaskiya taste din bakina ya bace nayi ta zabga uban gishiri a cikin abincin ni da kaina dama sai dana yi tunanin haka amma data fada sai naji haushi.

Abbu ya dan tabo ni tare da juyo ni ina fuskantar shi, shiru nayi ina kallon kyakkyawar fuskar shi, ina so in gano laifi ko aibu a cikin abubuwan daya fada amma na kasa. Ban san abinda yasa nake fada dashi akan maganar aikin nan ba, lokacin da nake gida har addu'ah nake yi akan Allah ya kawo min miji wanda zai tsaya min akan komi kamar yadda Daddy yayi wa mommy, gashi yanzu na samu amma kuma na rasa abinda yasa na kasa yarda da hakan, m behaving really strange kwana biyun nan, wasu bakin halaye dana kasa gane su.

“Nafeesah??! Talk to me mana uhm?? Bana so muyi fada akan maganar nan please, kin dai san babu abinda zaki nema a duniyar nan da ba zan kasa miki shi ba, ba zan gazawa hidimomin ki ko kadan ba kin ji? Kuma In shaa Allah ba zan taba bari kiyi dana sanin kin yin wannan aikin ba, ok?" kai na gyada mishi a hankali, yayi murmushi a hankali, “uwww thanks my baby..." ya sadda kanshi saitin fuskana zai yi rewarding dina da kiss, naja wata doguwar shakuwa data sa ya dakata yana kallona, daga haka kuma ba sai kakarin amai ba? Na tashi da gudu na shige bandaki, sai dana amayar da duk abubuwan dana ci a take, Abbu yana tsaye a gefena yana dan bubbuga bayana har na gama aman, ya taimaka min na wanke bakina ya kaini kan gado ya kwantar ya koma toilet din.

Kafin ya fito na dukunkune cikin bargo ina rawar sanyi sosai, hankali tashe ya tarairayo ni jikin shi yana taba wuya na, waya ya dauko ya kira family doctor dinmu, Doctor Salmah. Bayan kamar mintuna arba'in ta iso,

lokacin zazzabin ya sauka sai jikina da yayi wani irin sanyi kamar an min duka, kasala duk ta lullube ni. Tayi duk wasu gwaje-gwaje da zata yi, daga karshe dai ta bani wata kwalba tace inje inyi fitsari a ciki, na dafa kafadar Anty Mubeenah muka shiga toilet, ta fita ta bar ni nayi fitsarin ina gamawa ta shigo muka koma dakin, Docta ta amsa kwalbar ni kuma na koma kan gado na kwanta, muka yi zuru-zuru muna kallonta tana saka strip a cikin kwalbar fitsarin.

Bayan kamar minti goma ta dago abin yadda duk zamu gani, bamu fahimci komi ba sai da muka ji tace “mashaa Allah!! Farfesa matar ka na da juna biyu!!" a rikice na kamo hannun Abbu na rirrike kamar zan tsinke mishi shi, ya kamo wuyana ya hada fuskata da tashi waje guda yana furta wasu addu'o'i da ake son mutum ya dinga furta su cikin halin tsananin farin ciki. Anty Mubeenah ta dafa kafadata ko ban fada ba nasan tana murna da abinda taji ne. Docta tayi er dariya ta fara tattara kayanta tana fadawa Abbu bata bincika ko watan nawa ba saboda haka ya kaini asibiti washegari a duba da

kuma lafiyata data jaririn yace toh. Nan ta mana sallama ta tafi bayan Abbu ya mata kyautar da bai san adadinta ba don hannu kawai ya saka a cikin aljihun shi ya damko kudi ya mika mata.

Ranar kam naga tattali da kulawa ba daga mijina ba ba daga 'ya'yan mijina da en uwanshi ba, ba daga kishiyata ba ba daga Iyayena ba kada ma dai Daddy yaji labari. A ranar ya kirani shi da Mommy ban ma san wanda ya sanar dasu zancen cikin ba suka taya ni murna da addu'o'i iri-iri Mommy kuma yadda zan kula da kaina take fada min tana nanatawa kamar karatu.

Cikin wata hudu ne lokacin da muka je aka duba, babu wata damuwa ko matsala a tare dani sai hawan jini wanda ba wani damuwa bani tunda dama it's a normal thing a wajen mata masu ciki, an dai bani abubuwa da zan dings ci da kuma abubuwan daya kamata inyi da wanda ba zan yi ba domin rainon cikina cikin sauki da kwanciyar hankali. A cikin mota a hanyar mu ta dawowa daga asibitin Abbu ya riko hannuna yana shafawa a

hankali yace “ya zancen aiki ya tafi koh?" na gyada mishi kai ina murmushi. Yayi er dariya tare da cewa “ai Doctor Salmah ta fada min cikin jikin ki ne yasa kika zama short tempered woman, haba! I was wondering dalilin da yasa mutum mai sanyin hali irin ki ya zama mai fada da zuciya cikin dan kankanin lokaci, amma tun da na gano kan abin, zamu dinga kiyayewa bacin ranki don tace hakan zai iya sawa jinin ki ya hau..... Allah ya sauke min ke lafiya baby" nayi murmushi nace “Ameeen Abbu nah..!".

Cikina sai daya shiga watanninshi na bakwai sannan ya fara girma saboda da babu wani girma kuma babu laulayi ba komi sai fresh da nayi da kuma cin abinci da shan tatacciyar madara. Kafin in shiga watan haihuwa ta kuwa na zama shirgegiya, zama da kyar tashi da dabara. Kullum na kan zagaye gidan sau hudu ko biyar don ance hakan yana da kyau sosai. Yanzu dai haihuwa kadai muke jira, komi is ready, hatta da cokalin da za a ba baby ruwa dashi ranar da aka haife shi an siyo an ajiye, komi unisex Abbu yake siyowa kuma guda biyu,

duk da dai naki yin scanning amma Abbu da Anty Mubeenah har ma da sauran mutane suna cewa wai girman cikina irin na en biyu ne, don Abbu ma cewa yayi wai yana mafarkin ya ganni ina wasa da yara biyu ina miko mishi su, ni dai fatana kawai Allah ya sauke ni lafiya.

Ranar wata Talata na tashi da matsananciyar nakuda, nan muka kwasa Zuwa asibiti. Nakuda nayi mai tsawo da wahala kusan yini daya ina abu daya, abin ya gigita ni. Ban taba sanin cewa zafin nakuda nake yi ba. Abbu da yayi jan ido ya shigo labour room din sai waje aka yi dashi saboda dana shiga mood din " duke kai ne ka janyo min wannan wahalar..." abin bai yi kyawu ba. Sai zuwa bayan Maghrib Baby ya fito, nan na fara ajiye numfashi, sai dai me? Wani ciwon ne ya sake turnike ni kafin kace me?! Wani yunkurin sai ga wani babyn. Na maida kaina kan gadon asibitin na kwantar ina ajiyar numfashi da karfi, nurse din data karbi haihuwar ta duba yaran tace "Masha Allah!! Maza ne Allah ya raya miki su!!". Tuni yaran suka hade dakin da kukan da aka san lafiyayyun

jarirai nayi. Nan dai aka shirya mu muka fito tsaf damu. Throughout lokacin babu abinda nake furtawa fili da ciki sai 'Rabbir-ham huma kamar Rabbiyaani Swigaara...!!' wa Mommy na da duk wasu matan duniya, haihuwa is really not a simple thing.

Ana fito damu Abbu da yara suka shigo, nan fa suka lullube yaran suna murnar samun kanne, Abbu dai ya samu ya lallabo yazo inda nake ya tallabo ni a cikin jikin shi ya rungume yana shafa bayana. Ya dago goshina ya bani peck a kumatuna, "well-done Baby, kinyi kokari really! Allah ya albarkace ku ke da 'ya'yanki" nace "ameen... Wani irin baby kuma? Ga babies dinka can" ya juya ya kallesu ya juyo ya kalleni yana murmushi, "me na fada miki? You were going to give me twins, next year ma haka, n the other year, n the other too...!" na zaro ido ina cewa "mutuwa kawai kake rokar min!" yayi dariya tare da saki na yaje ya dauki yaran, Anty Mubeenah kuma ta matso tana jera min sannu.

Sai washegari aka bamu sallama muka wuce gidanmu muka cigaba da karbar barka har zuwa ranar suna inda

yara suka ci sunan Abdul-Qadir da Mukhtar (Sunan Daddy na) muna kiran Abdul-Qadeer Ameer shi kuma Mukhtar Daddy. Aka yi taron suna aka watse aka bar mu da yara da Dattijuwa Hanne daga Malumfashi muna wankan jego.

Cikin dan tsakanin Abbu ya bude min babbar plaza wadda Daddy na ya cike min rabin shagunan plazar da kaya ana kula min dasu, rayuwa ta ko wani fanni tana gara mana cikin dadi da kwanciyar hankali babu abinda zamu ce da Ubangijin mu sai dai Godiya....

“Ameer!! Daddy!!!" na fito falo ina kwalawa yaran kira, Anty Mubeenah dake kicin tana dambun nama duk da ba girkinta ba ne, tana taya ni hada abubuwan motsa baki da muka saba yi saboda baki da kuma emergency food. Ta leko tace “ya aka yi ne ake neman dears haka?" naja tsaki, “yaran nan daure su zan fara yi a jikin gado

gaskiya, kullum jan magana da barna kamar wasu beraye? Kwalbar turare na mai kyau fa kawai suka dauka daga kan mirror suka hada ta da bango, shine da suka ga ta fashe suka tsere" Anty tayi Dariya tace “aikuwa yanzu suka bi su Qaseem garden wai suna tennis" nayi kwafa, “I'll just go and register them a makarantar su Qaseem ma kawai ko na samu sawaba da sanyin zuciya" Anty tayi dariya tana girgiza kai tace “ke da yaran nan naki koh?" ni kuma na juya zuwa dakina.

Abbu yana kwance akan sofa yana karatun jarida da yake ranar hutu ce, ya miko min hannu na karasa gefen shi na zauna ina turo baki, yayi dariya “yau naji ikon Allah! Ni da bani na bata miki rai ba sai kuma fushi ya dawo kaina, dama ana haka ne?" na turo baki “Allah ni wannan yaran naka ka saka su a makaranta kafin su saka min hawan jini, kullum sai sun shigo sun min barna ni da Antyn su. Hafsy yanzu da makullin dakinta take yawo saboda Ameer. Kayan dakin yaran nan babu abin dauka duk sun bata, jiya suka balle wardrobe din da

muka sayo musu last week a Prada saboda Allah meye haka??"

Abbu ya kwashe da dariya har da kwanciya akan kujera, nayi kuta, “na kula dama kai kake daure musu suna rainin wayau. Yara ba a isa a musu magana ba kawai sai ka hau cewa wai yara ne, har sai yaushe zasu girma??" ya juyo dani yana kallon idanuna, “sai wani kumburewa kike yi kina fada baby, Anya?? Kin san da cikin su Ameer ma fa haka kika dinga yi?" da sauri na dukunkune fuskata a kirjin shi. Ya shafa kaina yace “da gaske ne hasashe na kenan? Masha Allah La Quwwata Illaa Billah! You are going to bless me with another child again... Ohh Nafeesah the thing I have for you.... You Are Indeed a Blessing!!" na kara rungume shi a jikina sosai. Kamar yadda a shekaru masu dama da suka wuce, nake jin zill da duk farincikin duniya idan naji ni a kirjin mijina, yanzun ma hakan take. Har yau muna son junanmu, har yau muna girmama junanmu, har yau muna rungumar junanmu a halin farin ciki ko akasin sa. Babu abinda ya ragu daga son da muke wa junanmu.

Ya dago fuskata yace "that call on a celebration... Tunda yara suna nan zamu fita gobe, party and welcome our little princess... Mata zaki haifo mana yanzu baby.... Hafsy tace tana so ta koyi kitso, kinga idan muka samu mace shikenan sai ta koya a kanta koh?" na zaro ido ina dariya tare da kara shigewa cikin jikinshi, "Noo... Guda daya ta isa Abbu... En biyun nan ba sauki daga haihuwar har rainon, kana dai ganin yadda muke fama dasu a gidan nan" ya hade fuska ta da tashi har hancina yana gogar nashi... "haka kike tunani dai....". Kokarin zurfafa abin yake yi, har na saddakar na lumshe idanuna, yana gab... Saura kiris... Kawai sai barammmm!!! Karan turo kofa da sauri..... "Mammiiieeee!!!!" nayi sighing tare da bude idanuna, fararen kayan dana saka musu yanzun nan kafin su fasa min turare, sun yi dikin-dikin da datti da yake ba a jima da gama ruwa ba. Na zaro ido, "what??!" na fara kokarin tashi, Ameer ne ya fara xubawa a guje nan Daddy ya bi bayan shi, na juya na kalli Abbu, shrugging yayi tare da daukar jaridar shi yana murmushi, na girgiza kai tare da mikewa nabi

bayan yaran ina kwala musu kira kamar dai yadda na bude shafin......

Alhamdulillah! Masha Allah Laa Quwwata Illa Billah!! It has been really a very big hell of a ride, right?! But Mashaa Allah!! Mun kawo karshen shi.

Littafin NI DA ABOKIN BABA NA kirkirarren labari ne, baya da nasaba da rayuwar wani/wata, idan wani abu yazo daya da naki/naka, to wannan 100% arashi ne kawai.

Ina mika dimbin gaisuwa ta zuwa ga Dimbin masoya, mabiya Littafin Ni Da Abokin Baba Na! The Facebookians, Wattpadians, Whatsappians, and all, thanks ya very much da duk kaunar ku a gare ni yayin Posting din littafin, gyarerekin ku da karfin gwiwar ku, I Appreciate!!

Gaisuwa ta Musamman zuwa ga mutanen Fikrah! Kungiya ta hadin kai da ban mamaki, Ina gaishe ku da kuma godiya a gareku baki daya.

Abokiya, Yaya kuma Kanwa ta gari; Anty Zee, Alkhairin Allah ya kai miki a duk inda kike.

Masoya, mu tara a littafina na gaba mai zuwa cikin hukuncin Allah! Har kullum, it's Jedderh Lawals!!